NADIYA!

WRITTEN BY

JEEDDAH LAWALS

Sadaukarwar wannan littafi na duk wasu 'ya'ya ne da suka yi hakuri suka jure wa duk wani yanayi da hali da rayuwa da iyayensu ya jefasu ciki. Suka mikawa Allah lamuransu kuma suke cigaba da girmama iyayensu, suke kuma yi musu uziri da kokarin fahimtarsu. Allah Ya jikan Iyayenmu, Ya gafarta musu kura-kuransu, Ya kuma yi musu kyakkyawan tukuici da gidan Aljannar Firdaus. Ameen!

Tukuicin littafin NADIYA! Na ki ne, yar'uwata jinin jikina, Anty Zee. Allah Ya bar min ke, Ya kuma raya zuriya ameen.

'Bismillahir-Rahmaanir-Raheem!'

Kaduna, Unguwar Sarki.

Misalin karfe sha daya da rabine na dare, Nadiya na lafe a jikin bangon dan karamin dakinta, jikinta a dunkule a waje daya kamar kullin kaya, ta nade kafafunta yayinda ta sanya hannu ta zagaye gwiwoyinta dasu ta nutsa kanta a tsakankanin cinyoyinta. Kanta masifar buga mata yake yi kamar ana kada mata ganga. Ita kadai tasan yanayin da gabadayanta take a ciki, ciwon kan yaje mata da wani irin zazzafan zafi a cikin kirjinta daya sanya taji kamar ana mata suya ne a kirjin.

Idanunta da suka kwashe tsayin mintuna suna digar hawaye, babu abinda suke mata face zafi da zugi, kada ma kuma ayi maganar yadda dakin ya dauki wani matsanancin zafi saboda yanayin garin gashi kuma babu wuta.

Macece ita mai matukar dauriya, ba kananun abubuwa bane suke sanyata zubar da hawaye ba, amma a yawancin lokuta, lokaci dai kamar wannan, dauriyarta gazawa take yi.

Allah kadai yasan iya lokacin data dauka a haka kafin sautukan dake fita daga dakin dake kusa da nata babu kakkautawa kamar an jona da lasifika, su dan sarara, sannan ta saki wata irin ajiyar zuciya. Ta dago kanta da fuskarta da tayi dashe-dashe da hawaye da zufa da majina, ta jinginar da kanta a jikin bango. Tana jin yadda suke sauke ajiyar zuciya, haka itama take sauke nata daya bayan daya. Har zuwa lokacin da suka gama abinda suke yi har ya tayar da ita daga daddadan barcin daya kwasheta.

Waye yace wai jin sautin mu'amalar aure da mutane suke yi yana tasar da sha'awa? Ita kam zata so ganin ko wanene don ta fada mishi wannan kanzon kuregene. Don ita a bangarenta babu abinda hakan yake haifar mata sai

sanyata tsanar abin da aure da ma mazan baki daya. To ma menene abin jin dadi ga diyar da zata ji mahaifinta da matarshi, going at it kamar wasu sex addict?!.

Dan siririn tsaki ta saki tare da mikewa, tasan cewa ita da barci a daren ranar yau kuma shikenan sai na washegari idan Allah Ya kaimu. Ta dauki yar siririyar tocilan dinta ta haska, haske ya mamaye dakin. Dankwali ta dauka ta yafa a kanta, ta mike tsaye akan kafafunta da suka yi mata nauyi kwarai, ta daga labulen dakinta ta fita tsakar gida.

Gidan da unguwar, dama duniyar gabadaya, sun dauki shiru a dai-dai wannan lokaci, ba kamar hayaniya da cunkuson jama'a da suka saba dauka ba. Ta shiga bandaki tare da kimtsa kanta. Duk da cewa bata yin sallah, hakan bai hanata yin alwala ba ta fita ta koma dakinta.

Ta shimfida tafkeken abin sallah tare da daukar doguwar hijabi ta sanya a jikinta, zama tayi ta gyara murya, ta fara rero karatun al-qur'ani mai girma cikin tausassa kuma nutsattsiyar muryarta a cikin suratul-Aal_Imran. A hankali take rera karatun cikin karamar murya mai rauni, ta yadda ita kanta ba duka kalmomin ke shiga cikin kunnenta ba sai daidaiku, har ta gama ta shiga suratun-nisa'i itama ta gama, sannan ta ninke kafafunta ta daga hannuwanta sama, ta fara jerowa Allah kirari da kyawawan sunayenSa dari ba daya, kafin ta fara karanto mishi bukatunta na rayuwa daki-daki, daya bayan daya, cikin kaskantar da kai. Ta shafa wasu hawaye na cika mata idanu tayi kokarin mayar dasu, sai taji jikinta da zuciyarta sunyi sanyi a take, kuma taji kamar an dauke mata wasu gingima-gingiman kaya a kanta. Filo ta ja ta ajiye kawai ta dora kanta a kai ta dauki carbi ta fara ja. Ba ita ta samu barci ba sai gab da asubahi.

Bata tashi sanin inda kanta yake ba sai da wani irin azababben kukan yaro ya tasheta kamar wanda ake cakawa wani tsini a jiki, tayi firgigit ta tashi zaune tana sakin ajiyar zuciya tare da karanto addu'o'i a fili. Sai a lokacin idanunta suka sauka akan karamin agogon dake dakin taga karfe bakwai da rabi, ta zabura da sauri ta tashi tana laluben zaninta na wanka da kuma kayan wankanta ta fita tsakar gida. Kananun yaran gidan dake zuwa makaranta har sun shirya cikin shirinsu na tafiya, yayinda wadanda ba a kai

ga kaisu ba suna zaune a kofar dakin nata daga su sai dan feto da fuska dambare da kwantsa da busasshen koko da saleba.

Bata bi ta kan kowa ba ta fada bandakin tsakar gida, duk cikin gidan, da dakunan dake cikinshi, dakin da take cikine kadai bashi da mahadin bandaki, kaca-kaca ta sameshi, sai data bata wasu kyawawan mintuna biyar wajen gyarashi sannan ta fara wanka a gaggauce. A sukwane ta fita ta fada dakinta ta fara shiri.

Cikin yan mintuna kalilan ta fito cikin wata rigar buba ta jan material mai zanen furanni, ta dauki karamin yellow din gyale ta yana a kanta. Bakar jaka ta dauka ta watsa duk wasu abubuwan da zata bukata, ta zari bakin flat din takalmi ta zura a kafarta ta fita.

Ta jawo dakin ta rufe da key shima ta sanya a cikin jaka. Dakin Mama ta shiga, ita kadai ta samu akan doguwar kujera, ta duka ta gaidata a tsaitsaye ta sanar da ita fita zata yi, Mama ta kalleta a nutse, tace, "yau ma ba zaki karya ba zaki fita Nadiya, anya?"..

Dan murmushi tayi, "ai babu matsala Mama, zan samu abinci idan naje can".

Mama ta yada kai, "to shikenan sai kin dawo, Allah Ya kiyaye Ya kuma tsare, ki kula da titi!".

Ta girgiza kai tana dan murmushi ta juya ta fita da sauri.

Tuni Abba ya fita duk da cewa dakinshi a bude ta sameshi hakan ya tabbatar mata da cewa ba nisa yayi ba, amma hakan ma ya mata dadi tunda dai babu wanda zai tursasasu ganin fuskokin juna a yanzu.

Da yake gidansu ba a can cikin lungu yake ba, ba tayi tafiya mai nisa ba ta fita bakin titi. Kai tsaye napep ta tara ta shige.

Karfe takwas da wasu yan mintuna tana kofar shagonsu dake cikin Unguwar Rimi.

Babban shagone mai girma sosai, suna sana'ar cake da kayan makulashe irin su ice cream, doughnuts, special bread dinsu na banana da zuma da kuma yoghurt.

Lokacin da taje ma'aikatan da suke musu aiki har sun jima da zuwa sun yi goge-goge wajen ya fito tsaf yana ta sheki, wasu kuma suna can kicin dinsu masu hada dough na doughnuts nayi masu baking din cake da cupcakes suna yi, ta bisu daya bayan daya ta gaidasu ta kuma duba yanayin aikinsu da gyara musu wasu abubuwa da suka kauce kafin ta shiga dan karamin dakin da take canza kaya da kuma hutawa idan bukatar hakan ta taso.

Karfe tara suke bude wajen aikin, kasancewarta manager din wajen yasa bata cika shiga cikin tsarin ayyukan shagon ba, ta dai tsaya a supervising din abubuwan da suke yi da kuma masu yi. Sabon tsarin da suka bude cikin watan na herbal tea ne ma yasa take hadawa da bada odarshi da kanta saboda har lokacin basu kai ga samun kwararre a wannan fannin ba.

Apron kawai ta daura a saman kayanta mai dauke da tambarin wajen aikin nasu, 'Diamond-Ara cakes and snacks'. Ta rataye jakarta a jikin hanger kafin ta fita daga dakin ta rufe ta sanya key din a jikin aljihun apron din jikinta.

Shagon da yake babbane, zagaye yake da kujeru da tables masu kyau da quality, akwai wajaje da aka yi na musamman saboda VIP. Sai suka zagaye wajajen da gilasai, a waje daya idan ka shiga zaka samu leather seats green a zagaye da wajen, tv din kallo da aka hada games kala-kala saboda masu zuwa da yara wajen. Ta bi ko'ina tana dubawa da gyara wajen sai data tabbatar da cewa komi yayi yadda take so sannan ta tafi bayan kanta inda take yini.

Kanta din ta Gilashi ce saboda anan suke showcasing duk abubuwan da suke yi. Nan da nan ma'aikata suka fara fito da abubuwan da suka gama, aka jera a kanta din saboda masu saya su ci anan, yayinda wasu suke daga can store suna wrapping wasu a cikin takarda su sanya a cikin jaka saboda masu yin order.

Karfe tara suka bude shagon, kafin kace me kuwa wajen ya cika da mutane, yan aiki sai faman kaiwa da kawowa suke yi saboda kula da mutane. Su hudu ne a bayan kanta, masu kula da su cakes biyu, ita da wata Sakeenah suna zuba shayi a kananun kettle su mikawa Amaka ta dora akan karamin tray da kofunan tangaran ta dauka ta kaiwa tarin kwastomomi da suke zaune a jerin kujerun dake cikin falon zasu karya, ko kuma ta zuba a cikin dan

dogon thermo-plastic kofi a sanya a wata rectangular jaka mai dauke da tambarin wajen aikin nasu a hada da bread slice ko duka ko kuma cupcake ko doughnut ko kuma duka, a kaiwa masu tafiya kasuwa ko ofis dashi.

Kasancewar wajen da suke a gefen wata babbar ma'aikata yake wadda take da ma'aikata fiye da dubu biyu, ga manyan Makarantu na Firamare da Sakandare da kuma wata Institute ta koyon Kwamfuta, a bayansu kuma akwai babbar Coci da babban masallacin Juma'a, shi yasa a koda yaushe shagonsu baya rasa kwastomomi.

Basu samu kansu ba sai wajen karfe sha daya saura kafin mutanen suka daga. Masu gyaran wajen suka je suka sake gyarawa, masu aiki kuma suka koma kicin aka cigaba da wasu batch din na kaya.

Kafin su gama ta cire apron din ta makala a jikin hanger ta fita. Nan opposite dinsu wata babbar Rsstaurant ce ta Arabian Cuisine, sun riga sun saba da mai Rssaturant din sosai, Fatima, da kuma ma'aikatan wajen. Tana shiga suka fara gaisawa dasu, bata bata lokaci ba tayi odar abinda zata ci aka sanya mata a take away ta biya ta koma shagonsu.

Dakin hutunsu ta shige ta zauna, ta tsiyaya shayi ta zauna ta karya a nutse kafin ta sake fita wajen aiki.

Wannan karon decorating din cake da aka yi oda na Birthdays da Anniversaries ta fara yi wadanda aka riga aka yi baking. Lokacin da aka kira sallar azzuhur masu sallah sun je sun yi, suka fara amsar wasu Customaers din wanda yawanci meat pie da sansanyan kunun ayan da suke yi ya kaisu.

Haka ranar suka yini busy kuma cikin ayyuka kamar dai yadda suka saba a kowace rana. Karfe biyar na yamma kamar kowace rana suka rufe shagon. Babu wanda ya tafi a cikinsu sai da aka kimtsa ko'ina. Tana bayan kanta tana lissafin da suka yi a ranar da shigar da komi cikin littafin da suke yi, daya bayan daya ma'aikatan na mata sallama har suka tafi aka barta ita kadai.

Bayan ta gama lissafin ta bi komi nasu daki-daki tayi sorting komi saboda ayyukan washegari, ta duba abubuwan da suka fara yin kasa a shagon tare da daukar list don washegari ta bada a sayo, ko kuma ta shiga kasuwar da

kanta idan ta samu sarari tunda washegari zai kama public holiday, watakila cunkuson shagon nasu zai ragu.

Sai data tabbatar da komi ya kimtsu, ta kulle ko'ina ta kuma kashe duk wasu electronics kafin ta kulle shagon, sannan ta fita da leda mai dauke da kadan daga sauran kayan da basu samu sun sayar ba a ranar. A karamar farfajiyar wajen da take cin motocin da basu fi biyar ba, ta samu maigadin wajen yana sauraren radio. Nan ta mishi sai da safe ta shiga restaurant din su Fatima inda ta sameta cike da kwastomomi da yan aiki ana ta hada-hada kamar a lokacin garin ya waye.

Ita kanta Fatimar sai a tsaitsaye suka gaisa, ta bata cupcakes da doughnuts wadanda zata kaiwa yaranta, ita kuma tayi odar soyayyar shinkafa mai kwakwa da gasasshiyar kaza aka sanya mata a leda, ta musu sai da safe ta bar gidan cin abincin.

Mai napep ta tara ya kaita har kofar gida.

A matukar gajiye take kwarai, kanta sarawa yake yi har wani jiri take gani. A haka tana daga kafarta da kyar ta shiga cikin gidansu. Tun daga bakin kofa ta fara jiyo hayaniyar yara da sautin hirar matan gidan tana tashi kamar a cikin gidan biki. Babu wanda zai yi tunanin wai magriba tana gabatowa a hakan balle ayi maganar hakura da hirar hakanan a nemi mafakar yin ibada.

A soron gidan ta ci karo da su Fatima da sauran yaran gidan, kowa da kalar abinda yake yi, babu wanda ya daga kai ya kalleta ko ya nuna alamun yi mata sannu da zuwa, don haka itama bata bi ta kan kowa ba ta fada cikin gidan.

Lantana da Salame, matan mahaifinta, suna zaune daga bakin madafi, hayaki da kauri sun turnike gidan gabadaya amma kowa aikin gabanta take yi, suna hira da shewa kamar wasu kananan yara.

Tayi sallama a nutse ta wuce ta gabansu ba tare data kara kallon inda suke ba, kamar yadda suma babu wadda ta amsa daga cikinsu ko kuma ta kalleta.

Tana basu baya, Lantana ta juya ta kalli Salame tana tabe baki tare da shunata da baki, "yan bariki an dawo daga yawon ta zubar!".

Salame tayi wata yar dariya, "jibeta ko kunya bata ji bayan kowa yasan abinda taje tayi, sai a wani shigowa mutane gida ana hura hanci sai kace bamu san abinda ke wakana ba...!".

Juyawa tayi tana kallonsu da idanunta da suka fara canza launi, "me kuke cewa?!", ta jefa musu tambayar cikin rawar murya saboda tsananin fusata da bacin rai da suka dirar mata anan take.

Lantana tayi tsamo-tsamo tana raba idanu, sai ta hau kame-kame tana nade tabarmar kunya da bori, dama can yar kanzagin Salame ce. Bata samun kwarin gwiwar yin komi sai Salamen tana kusa da ita, kuma duk rashin kunyarta bata iya yi a gaban idon mutum.

Salame ta watsa mata wani irin kallo kamar taga kayan banza, "yo! Ai ba gulmar mutum aka yi ba, kuma gaskiyarmu muke fada balle ace, ehe!".

Ta gyara tsayuwarta, "shi yasa ai nake tambaya, me kuka ce?!".

Ta wani kyabe baki, "ke bari kiji in fada miki, ba fa tsoronki muke ji ba ko kuwa don kinga ana miki shiru ne? To na fadi na kara, nace daga yawon ta zubar kike! Sai a fita waje a gama lalata, a dawo mana tsakar gida ana wani hurawa mutane hanci, to mun san komi!!".

Dama ba tun yau ba tasan da kalar kazafin da suke jifanta dashi, taji a bakin mutane da dama. Maimakon ta nuna bacin ranta irin yadda Salame taso tayi, sai tayi kokari ta danne zuciyarta, ta kama kugu tana jefawa Salame din wani kazamtaccen kallo, tace, "da ke nake zuwa yawon tambadar hala?!".

Ta wani zabura kamar wadda aka jonawa bakin wuta a jiki, "ba dai ni ba sai dai uwarki don abu ta kazarki! (ta dankara wani irin zagi). Ke har kina da bakin cewa wani yana yawon karuwanci bayan karuwanci da dadiro a kugunku ya kare ke da matsiyaciyar uwaki??".

Kalmar ta matukar tabata, a zafafe ta daga baki zata mayar mata da amsa dai-dai da ita, ta jiyo muryar Mama a bayanta, "Nadia me yake faruwa ne?".

Ta juya da sauri tana kallon Mamar jikinta har rawa yake yi saboda masifar bacin rai, tace, "nima ban sani ba Mama. Wai kawai daga shigowata ban san hawa ba ban san sauka ba suka hau jifana da zagi da munanan kalamai."

Mama tace, "to kuma banda abinki Nadia don sun zageki sai me? Yau suka farane? Bai kamata kina biye musu ba don haka maza zo ki wuce daki, kinji ma har an fara kiran sallah."

Duk cikin gidan, ita kadai ce take fada mata magana ta bi a take ba tare da tantama ko neman karin bayani ba. Yanzun ma bata iya kara cewa komi ba sai wani kallo data watsa musu, ta juya ta wuce ciki abinta. Dakinta ta bude ta shiga, tasan maganar bata kare ba, Abbansu yana dawowa zata dawo sabuwa kal.

Tana jiyo Salame tana yiwa Mama ihun, "dama ai dole kice ta daina biye mana tunda ga mahaukata kamar ki!,' Mama dai bata tanka musu ba ta juya ta wuce dakinta.

Lokacin data fita bandaki don kimtsa jikinta tunda ta samu tsarki, har lokacin su Lantana abinda ya faru suke maimaitawa. Salame ta daga murya yadda zata jiyota sosai tana fadin wasu maganganu marasa dadi, bata ce musu komi ba sai kwafa da tayi ta shige bandakin kawai. Ranta ya kara baci data samu bandakin kaca-kaca kamar anyi shekara da shekaru ba a wanke shi ba.

Ta gama sallar isha'i, tana zaune akan abin sallar tana lazumi, ta ji alamun karar mashin din Abban nasu. Yaran gidan duk suka dauki shewar barka da zuwa suna mishi, kasancewar babu wuta yasa hayaniyar tasu ta karade gidan.

Gabanta ya fara bugawa sama-sama saboda tasan rigimar da Mama ta samu ta kashe da kyar ce zata dawo sabuwa dal.

Ila kuwa, tana jin karar lokacin daya bude dakinshi ya shiga. Tana nan zaune tana saurarenshi har ya shiga bandakinshi domin watsa ruwa, tasan hayaniyar yara ce ta hanata jin motsin wankan da yake yi, amma da ace

dare ya tsala ko kuma asubahi ce da sai ta ji. Tana dai jiyo hayaniyar su Salame da Lantana suna kara maida yadda aka yi.

Yana kuma fitowa daga wanka suka hau kora mishi bayani, babu ko duba da cewa bai gama hutawa ba balle a kai ga maganar cin abinci.

Yayi shiru yana saurarensu har suka dire aya, tana jiyo sautin muryarshi cike da fushi lokacin da ya ba Salame umarnin taje ta kirata.

Ko cikakken minti daya ba ayi ba kuwa sai gata ta banko kofar dakinta babu ko sallama, tayi mata kerere a daga bakin kofar tana watsa mata wani kallo na rainin hankali, "kije ana nemanki!"

Ta furta hakan cike da gatsali wanda ya kara sanyayar da gwiwar Nadiya din. Amma tayi ta maza ta matse don ma kada ta gama gano abinda ke cikin ranta. Sai dai fa ayi duk abinda za ayi a gidan don kuwa she wouldn't go down without a fight! Nadiya ce fa!!

Ta tashi tsaye tana watsawa Salamen kwatankwacin irin kallon da take mata, ta gefenta ta ratsa ta wuce ba tare da ta tankata ba.

Tana ji ta biyo bayanta tana fadin maganganu marasa dadin ji da daukar alwashi iri-iri. Tayi kunnen uwar shegu da ita, can a kasan ranta tana furta addu'a iri-iri, tana kara maimaitawa, wai Allah Yasa ta yiwa Abban nasu kwarjini ya ki yi mata ta'asar da tasan an shirya mata.

Tayi sallama a dakin a nutse, ta durkusa a gabanshi tana mishi sannu da zuwa, yayinda yake zaune akan kujera mai cin mutum biyu, Lantana a gefenshi tun kayan data sanya da safe data tashi barci sune a jikinta bata canza ba, itama Salamen kuwa duk zani ce ta tarda muje mu. Warin hayaki kawai suke yi duk sun cika dakin da hamami.

Da kyar ya amsa gaisuwar yana jefa mata wani irin wulakantaccen kallo, "me matana suka miki da zaki far musu da rashin kunya da maganganun banza dana wofi? Wai ke ba nayi miki shamaki da su bane?"

Ta daga kai tana kallon mutumin da ke amsa sunan mahaifi a wajenta. Amma mahaifi ko kuwa dai _sperm donor?!_

Don kuwa dai ba haka mahaifa suke ba. Ba haka iyaye suke treating 'ya'yan da suka haifa ba. Da ba don tana da tabbaci ba daga Mama wadda tace mata lallai shi din mahaifinta ne, kuma tasan Mama bata karya ko da wasa, to wallahi da cewa zata yi ba shi bane ya haifeta. Kila ma har wasu daga cikin iyalan gidan.

Tace, "Baba ina fa dawowa daga wajen aiki kawai suka tareni da maganganu da zagi, har suna kiran mahaifiyata da karuwa"

Budar bakinshi sai yace, "to dama mecece idan ba karuwar ba?!"

Sai tayi duf kamar an dauke ruwan sama. Yayinda shi kuma ya rufe idanu ya fara zabga mata ruwan fada, ta inda ya shiga ba ta nan yake fita ba. Zagi kuwa ta uwa ta uba, kai kace sa'arshi ce ita din ba wai diyar shi ba.

Duk yadda taso ta daurewa ranta ta danne kukan da yake cinta, gazawa tayi, dauriyarta ta kare, murya cike da rishin kuka take cewa, "ai dama ba so na kake yi ba, kafi girmama matanka akan 'ya'yanka. Shi yasa ba zaka taba iya tsayawa ka kwatanta adalci ba. Idan ka so adalci ai kamata yayi ka fara tambayata abinda ya faru ne, ba wai ka hau min fada ba haka kawai!"

Aikuwa nan ya kara harzuka, ya fara fadin wasu irin maganganu marassa jin dadi, har da cewa shi wallahi da haihuwar diya irinta gwara ma babu, "mutuniyar banza mutuniyar wofi! Ni zaki zauna ina fada kina fada saboda kin maidani sa'anki? Yar iska kawai, banza, bari ki gani...!"

Ya zabura ya taso da niyar bugunta, Salame tayi saurin rikoshi wai tana bashi hakuri, "haba Malam da girmanka ina kai ina biyewa yara marassa kunya kuna ja'in'ja? Don Allah kayi hakuri kada kayi fushi. Ni dai kawai na kawo maka maganar ne ba wai don bacin ranka ba sai don kawai kaja mata kunne, a matsayinmu na matanka, kuma iyayenta...!"

Tayi gaggawar katse maganganunta masu kama da digar dalma a cikin zuciyarta, "kinyi kadan wallahi, kinyi tsararo, baki ko kama kafar taka wannan matsayi a wajena ba! Mahaifiya daya na sani a gidan, kuma ba ke bace! Ba zaki taba zama ba kuma! Kije can dai ki nemo inda diyan naki suke amma ba ni ba!!"

Abbansu ya zabura yana kokarin tashi, "kun gani ko? Kun gani ko? Wannan yarinya... Wannan yarinya... Tashi ki bani waje kafin in sassaba miki kamanni a wajennan..."

Bata jira ya rufe baki ba ta tashi tayi gaba, ta wucesu tana watsa musu harara kasa-kasa. Tana ji ya bita da wasu kalamai da maganaganun zagi. Bata waiwaya ba har ta dangana da dakin Mama.

Maryam da Aminatu, sauran diyan Mama da suka rage a gabanta, suna falon sunyi tsuru-tsuru suna sauraron diramar da ke wakana a gidan. Ta wucesu ta shige can uwar dakan Maman inda ta sameta tana zaune akan abin sallah tana jan carbi.

Ta haye can karshen gadonta na karfe ta cusa kai a tsakankanin cinyoyinta ta saki wani irin kuka mai cin rai.

Tana jin Mama ta zauna a kusa da ita tare da dafa kafadarta ta shiga bata hakuri da tausassan lafazi.

Tace, "ba tun yau ba ina fada miki, kiyi hakuri da duk wani halin mahaifinku, ki daina ja-in-ja dashi musamman idan yana yi miki fada Nadiya. Iyaye har kullum hakuri muke yi dasu ba wani abu ba!"

Tace, "haba Mama! Haba don Allah!! Shi kenan kuma sai ya kasance kullu-yaumin ba za a taba tsayawa a saurari uzurin mutum ba sai dai duk zugar da za a kai a kanshi a hau kai a zauna babu wani bincike? Wannan ai ba adalci bane. This is not fair wallahi!"

Mama ta dan yi murmushi mai nuna takaici, tace, "kin san halin Abbanku sarai Nadiya, kin kuma fi kowa sanin haka halinshi yake. Don haka ban ga abin tada jiniyoyin wuya da bacin rai ba a nan. Kiyi hakuri ki jure koma menene, saboda watarana sai labari!"

Bata iya cewa komi ba sai jan shessheka data cigaba da yi tana sharar kwalla ranta a matukar cune.

Maryam da Aminatu suka shiga dakin suka zauna a gefenta suna kara tausarta, har dai taji ranta yayi mata dan sauki.

Ta umarci Aminatu da taje dakinta ta dauko musu take away din data je da ita. Maryam kuma ta dauko musu ruwa mai sanyi da kunun aya da Mama take yi na sayarwa. Nan suka zauna a falo suna cin abincin suna hirarsu har suka gama cin abincin.

Da yan wuta suka kawo suka kunna kallo a yar karamar tv dake manne a jikin bango a dakin. Ta zauna tana tayasu Assignment dinsu da bitar karatu. Ba ita tayi musu sallama ba sai da karfe sha daya ta gota.

Ta shiga bandaki ta watsa ruwa tare da dauro alwala, ta koma dakinta ta sanya kayan barcinta riga da wando marasa nauyi. Wandon ya tsaya mata a iya gwiwa, rigar kuma kamar vest take mai siririn hannu.

Tana dora kai akan katifa da niyar barci, abinda take gudu ya fara aukuwa.

Yau kam abin har yayi yawa, wani lokacin ma sai taga kamar da gayya suke yi mata abinda suke mata. Saboda ta kula sun fi kwaratsi da daga murya a ranakun da suka samu sabani da ita. Musamman Lantana din daya kasance ita ce da maigidan ranar, har wani ahi take da wani abu kamar wadda take shirin tayar da aljanu.

Ta dauko earpiece dinta ta makala a kunnen ta jona da wayarta. Karatun Qur'ani ta kunna ta kuma kure volume, ta koma ta kwanta. Amma duk da hakan barci ya kauracewa idanunta. Ta kasa tsayar da hawayen da suke mata zarya akan fuska suna kwarara, haka kuma ta kasa hana kanta daina

hasko mata munanan abubuwa da sake-saken da ranta yake mata. A haka wani irin wahalallen barci ya dauketa.

Ko da alarm dinta ya buga da asubah, ta kwashe fiye da minti goma a kwance kawai ta kasa tashi, jikinta kamar wadda trailer ta bi ta kanta haka take ji. Ji take kamar ma wadda bata yi barcin ba saboda yadda take jin kanta yana sarawa kamar zai rabe gida biyu.

Haka ta kokarta da kyar tayi alwala tazo tayi sallah.

Ta koma ta kwanta akan abin sallar, rabin jikinta kuma akan katifarta tana yin azkar dinta har dai gari yayi haske. Kafin ta tashi taje tayi duk abubuwan data saba.

Bakwai mai kyau ta gama shiryawa cikin riga da skirt na atamfa. A-shape ne wadanda suka bi jikinta kuma basu kamata ba. Bayan yar hoda da wet lips data sanya ta kuma zizarawa idanunta kwalli babu abinda ta kara. Ta dauki karamar hand bag ta leather ruwan kasa ta zuba abubuwan da zata bukata, ta fito ta kulle dakinta.

Ganin yan yaran duk a tsakar gida yasa ta shiga dakin Abbansu domin ta gaisheshi.

Sai data dan yi turus, ganin Lantana da Salame a kame a kan kujeru sun sanya shi a gaba kamar wani karamin yaro yana karyawa. Koda yake dama mai take tsammani? Ana gama Asubahi haka zasu shiga dakin su sanya shi a gaba. Da ace zai yini a gidan, to da ko nan da can ba zasu motsa ba. Duk kuma hakan gadin kada su kebance ne da Mama ko kuma ya dan yi tattaunawar sirri da iyalanshi. Magana ko wace iri ce sai dai ayi a gabansu. Shi yasa ai daga 'Ya'yan gidan zuwa abokai da danginshi, basu ganin kan kowa da gashi.

Ta riga ta san abinda zai biyo baya tun ma kafin ya furta lokacin data zube a gabanshi ta gaisheshi. Ya amsa a tsaitsaye, sai kuma ya tsayar da ita lokacin

data fara yunkurin tashi, "su kuma iyayen naki ba zaki gaishesu ba saboda rashin ta ido ko? Wai ke Nadiya me yasa ba kya jin magana ne?"

Bata iya cewa komi ba sai dan juyawa da tayi tana kallonsu kamar ta hadiye zuciya ta mutu, tace, "ina kwananku?"

Suka kuwa yi caraf suka amsa kamar dama jira suke yi.

Ta mike gwiwa a sage, rai yana suya zata fita. Sai kuma suka ci karo da Mama ita kuma ta danno kai zata shigo dakin hannunta rike da kwanon da zata dauki abincin da zata dafa tunda ita take girki ranar, kuma store din a cikin dakinshi yake.

Sai ta dan yi baya ta bata waje ta shiga, ta kuma koma ta tsuguna tana gaisheta. Ta amsa tana kallonta fuska dauke da fara'a, tace, "Nadiya har an fito kenan?"

Tace, "ehh wallahi Mama. Yanzu nake cewa bari inje in sanar dake zan tafi."

Tace, "to sai kin dawo, Allah Ya tsare. Yau ma ba zaki karya din ba zaki tafi?"

Tayi dan murmushi, "Mama kin manta yau alhamis? Azumi nake yi."

Tace, "hakane fa. To sai kin dawo."

Daga haka ta sa kai ta bar gidan.

Aikin ranar kamar na kowace rana ne, akwai kwastomomi da tarin ayyuka shi yasa ta koma gida a matukar gajiye likis. Tun ma kafin karfe tara tayi ranar ta kwanta.

Barci mai dadi da nauyi ya sureta. Kawai gabannin asuba sai taji ana maimaita yar gidan jiya kamar a cikin mafarki. Tayi lamo a kan katifa tana kokarin tunano me yake faruwa ne? Musamman data jiyo Salame ce tare da mahaifin nata yau. Girkin Mama ne, kuma ta tabbata ba a nemi izininta ko shawararta ba. Ta hau girgiza kai gabadaya kanta a juye da lamarin wadannan mutane. Su basu san suna take ka'idar Allah bane?

Akwai wani lokaci data taba tunkarar mahaifin nata da zance makamancin wannan. Farkon komawarta dakin ne lokacin tana makarantarta ta jami'a. Gani tayi shiru-shiru da kawaicin da kawar da kai da take yi duk basa yi. Ta fara samun matan nashi da maganar, ta ga dai basu da niyar su fahimceta ko kuma su gyara. Sai ma muzguna mata da suke yi musamman da suka fahimci cewa abin yana damunta kuma bata jin dadinshi sam. Wai sai ya zamana ma suna mata habaici da tutiya dashi. Sai abin ma ya koma yana bata dariya. Ta ga akan wani dalili to ita da ba kishiyarsu ba?

Don haka ta badawa idanunta toka ta tunkari Abban nasu da maganar. Ta nuna mishi rashin dacewar hakan da kuma illolin da hakan zai iya kawowa musamman ga yaran gidan da suke tasowa. Tunda watan watarana dai zata bar dakin ai, kuma 'ya'yansu sune zasu maye gurbinta. Bai dace su taso suna shaida wannan abin ba.

Babu abinda ya fi ci mata tuwo a kwarya ma irin daukar kwanan wata ya kaiwa wata, musamman kwanan Mama. Tunda dai ita tace ta hakura dashi shekara da shekaru, kuma zaman 'ya'yanta take yi.

Ya zauna yana saurarenta tana ta zuba bayanai kamar wani abin arziki. Sai data dasa aya sannan ne kuma ya rufe ido ya fara zuba mata rashin mutuncin da sai data yi dana sanin yi mishi maganar. Har da mata kashedin idan ta sake yi mishi katsalandan a al'amuranshi to lallai kuwa zai koreta ta bar mishi gidan, in yaso sai taje can wani waje na daban ta musu rashin kunyar.

Don haka ta daurewa kanta, ta kai na mujiya ta zuba musu kawai. Ta koma gefe tana addu'ar Allah Ya shiryesu, ita kuma ya bata mijin aure tayi ta bar musu gidan ta huta.

Shekaru ashirin da shida tana shirin haurawa da bakwai, amma har yanzu babu wani tsayayyen miji na a zo a gani.

Ranar haka ta yini cikin yanayi na bacin rai da damuwa da tunani. Rashin yin aure da son barin wannan gidan yana daya daga cikin manyan abubuwa da suka jagoranci damuwoyin da suka dabaibayeta.

Kasancewar Juma'a ce, sun fi samun kwastomomi da rana idan an fito daga masallaci, don haka zuwa lokacin da karfe hudu ta yi, abubuwa sun fara lafawa.

Tana bayan kanta tana lissafin cinikinsu na ranar da shigar da bayanai, Aramide ta shiga shagon hannu rike da makullin mota, gyale a kafada yana neman faduwa kasa.

Aramide abokiyata ce tun makarantarsu ta Jami'a, kuma ita ce jigon shagon nasu. Don haka tare suke kula dashi duk da cewa dai ita tafi zuwa a ranakun mako saboda tana aiki da kamfanin Indomie da bangarensu yake anan Kaduna.

Ta mata sannu da shigowa. Ganin yadda ta amsa a tsaitsaye, tasan watakila ta kwaso gajiya ko kuma bata jin dadi. Don ita din mutum ce mai kazar-kazar da barkwanci, shi yasa ma tasu tazo daya da Nadiyar sosai.

Ta dauki cup cakes da doughnuts da lemu mai sanyi ta kai mata. Ta amsa tana mata godiya, ita kuma ta koma ta cigaba da abinda take yi.

Tana aikin ne wani tunani ya darsu a ranta. Tunanin komawa gida ranar yasa take jin kamar ta dora hannu a ka tayi ta ihu kawai. Ta gaji kwarai da gaske, hutu take bukata daga wannan gidan da wannan rayuwar.

Tayi sauri ta gama abinda take, taje ta samu Aramide tace mata zata wuce gida da wuri. Bata tsaya jan dogon zance ba tace mata ta gaida gida.

Ta fita ta tari abin hawa, kai tsaye ya kaita tashar Kawo ta shiga motar Kano.

Tana zuwa motar saura mutum biyu ta cika da yake golf ce. Don haka ta zauna jiran cikon mutum daya.

Sai lokacin ta ciro wayarta a jaka ta kira Mama wadda ta daga nan take.

Tace mata, "Mama a mana addu'a, gani nan a hanyar Kano!"

Mama tace, "Kano kuma da wannan yammacin Nadiya? Anya? Ga dare yayi kuma ga yanayin hanya da wannan rashin tsaro da muke fama?"

Tayi dan murmushi, "babu abinda zai faru in shaa Allah Mama. Ni dai kawai kiyi mun addu'a!"

Mama tace, "to Allah Ya kiyaye hanya Nadiya, Allah Ya saukeku lafiya. Kin fadawa Abbanku dai ko?"

Nan da nan sai fara'ar fuskarta ta dauke. Tace, "in kira shi in ce mishi me? Na tabbata dai babu wani fatan alkhairi da zai mun, kila ma sai dai ya min fatan inyi hatsari a hanya in mutu tunda dama ba yau ya saba hakan ba!"

Mama tace, "duk da haka, mahaifinki ne ai. Kuma idan kinyi hakan hakkinshi kika fitar. Ki daure ki kirashi din!"

Tayi dan jim, kafin ta gyada kai kamar Maman tana gabanta, tace, "to shikenan, zan kira shi din in shaa Allah."

Mama tace, "yauwa Nadiya haka ake so. Ki gaishe da Jamilar idan kin je."

Tace, "zata ji in shaa Allah."

Nan suka yi sallama.

Lambar Anty Jamila ta kira, sai dai har tayi ringing sau biyu ta gama ba a daga ba. Sai ta kira lambar diyarta Rabi'ah.

Tana shiga ta daga kamar wadda take jira. Ta fara magana cike da azarbabi, "Mommy Nadiya ina yini?"

Tayi yar dariya, "kai Rabi'ah, Allah Ya shiryeki wallahi. Ina sallamar to?"

Sai itama tayi yar dariya cike da alamun jin kunya, tace, "Assalamu alaikum wa rahmatullah"

Ta amsa, "wa alaikumussalam wa rahmatullah. Ina Mommynki ne, ina ta kiran wayar tata amma bata dagawa?"

Tace, "aikuwa yanzu babu jimawa suka fita ita da Daddy. Ina tunanin ko wayar tana jaka ne ko kuma ta barta a gida."

Tace, "ok, to idan ta dawo da wuri ki fada mata ina kan hanya. Don kada ta tarar da missed call ta kira kuma yanayin network bata sameni ba."

Rabi'ah tayi tsallen murna ta dire, "da gaske? Allah kiyaye Mommy sai kin iso! Ki kawo min tsaraba fa!!"

Yadda taji tana murna da dokin zuwanta sai taji itama murnar ta kamata, tace, "to shikenan Rabi'ah, zan kawo miki in shaa Allahu!"

Suna gama wayar aka samu fasinja. Nan da nan aka rufe mota direba ya dauki hanyar fita daga Kaduna.

Sai da suka fita a tashar sannan ta lalubo lambar Abbansu ta tura mishi sakon ita dai ta tafi Kano gidan Anty Jamila. Sai dai har suka fita daga Kaduna suka dauki hanyar Zariya bata ga ya maida mata da amsar sakon ba. Don haka ta kada kanta gefe guda ta jinginar da gilashi tana kallon gari.

Karfe takwas da rabi suna cikin Kano, amma bata karasa gidan Anty Jamila dake can cikin Nasarawa GRA ba sai wajen karfe goma saboda yanayin abin hawa.

Mai napep ya tsaya a gaban tangamemen gate din gidan nasu. Bakin gate ne mai gida-gida sai wasu adon furanni da aka yi a jiki masu kalar zaiba. Kai daga gani ba sai ka tsaya tambaya ba kasan cewa ya ci kudi ba kadan ba.

Ta sallami mai abin hawar kafin ta karasa jikin gate ta kwankwasa, mai gadi ya leka yana tambayar waye? Daya ganta sai ya koma ya bude mata yana mai yi mata sannu da zuwa. Ta amsa mishi a matukar gajiye.

Motocin data gani a cikin gareji ya tabbatar mata da cewa su Antyn sun dawo. Ta raba ta gefen garejin ta bi ta gefen madaidaicin lambu da kuma wajen shan iska na gidan, ta shiga falon farko na gidan.

Babban falone sosai. An sanya kujeru manya-manya na leather sai babban center table, rabin bangon dakin wata katuwar plasma ce yayinda rabin kuma show glass ce mai girma da fadi da aka zuba abubuwan ado na tangaran da gilashi a ciki. Dim lights masu kyau suna ta sheki a ciki suna kara kawatata. Falon an fi amfani dashi saboda manyan bakin Daddy, amma su ma mutan gidan su kan fita su sha iska a wasu lokutan.

Tana bin wata kofa sai gata a tsakar gidan. Dakuna ne a jejjere daga kowacce kusurwa, Yayinda sauran tsakiyar gidan kuma aka shuka wata bishiya babba wadda ta bude daga sama ta saki rassai duk sai ta lullube gidan. All in all dai, gidan Anty Jamila gida ne wanda tsarinshi yayi matukar burge Nadiya. Domin gidane da daga gani kwalwa da dukiya suka jajirce wajen ganin an samar dashi. Kuma yanayin tsarin yana nuna rayuwa ta wayewa da kuma sanin darajar kai, ba irin ta gidansu ba.

Bangaren yaran gidan daban yake, duk da cewa dai a waje daya suke, amma kuma kowa bangarenshi daban yake.

Kana shiga daga bangarenka na dama, nan ne dakin yara mata yake. Idan kuma ka mike straight, nan zai kaika turakar mai gidan. Bangaren hagu kuma wanda ya dan shiga ciki nan ne bangaren maza.

Kai tsaye dakinsu Rabi'ah ta wuce. Tayi knocking kafin ta tura kofar dakin ta shiga. Dakin nasu yana da fadi matuka. Gadaje uku ne a dakin, guda biyu wadanda suka kasance bunk, a hade, suna daga jikin bangon kofar dakin, sai dayan kuma daya kasance single a daya bangon. Daya bangon kuma gabadayanshi wardrobe ce ta jikin bango, sai daya gefen da aka zuba desks na karatu, kowanne makale da laptop dinshi da sauran essentials, sai kuma karamar tv da aka manna. A tsakiyar dakin kuma an shimfida kafet mai taushi an zuba tuntu da wasu abin zama da hutawa masu kyau.

Rabi'ar tana zaune akan desk dinta tana rubuce-rubuce lokacin data shiga. Tana daga kai ta ganta, tayi tsalle ta wancakalar da abubuwan hannunta ta nufeta a sukwane tana ihun murna. Murmushi tayi itama ta rungumeta, nan suka hau juyi a tsakiyar dakin har dai suka dangane da gado suka zube a kai.

Sai data gama murnar tata sannan ta saketa, ta zauna a gefen gadon tana kallonta, "wai! Gaskiya sannunki da zuwa Anty, ya hanya?"

Tace, "hanya Alhamdulillahi, gamu mun iso ai!"

Rabi'ah tace, "sannu da hanya to. Mommy tace idan kin iso a miki sannu da zuwa zaku hadu da safe saboda tuni suka shige turaka ita da Daddy!"

Dan murmushi ta saki a tausashe, sanin halin Anty Jamilar sarai da yadda bata hada harkokin mijinta da komi yasa bata ji komi ba, sai kai data daga, tace, "to Allah Ya kaimu goben lafiya. A gajiye nake ai dama, ruwa kawai zan watsa in kwanta."

Tace, "to ki shiga kiyi, ga kayan barci da Mommy ta shigo miki dasu."

Tayi godiya tare da amsar kayan ta fita daga dakin ta fada toilet da yake fuskantar dakin. Shower stall ta shiga ta saki ruwa mai dumi a jikinta sosai, ta jima a ciki kafin ta fita tana jin yadda jikinta ya fara saki, gajiyar itama ta fara barinta.

Ta tsaya gaban karamar mirror dake makale a bandakin tana goge jikinta da tawul. Data gama ta dauki spray na CC mai sanyin kamshi ta fesa a jikinta kafin ta fasa ledar kayan ta sanya, dogayen riguna ne guda biyu na barci a ciki. Dayar bata da tsayi sosai da kadan ta sauka gwiwarta, kuma hannunta siriri ne haka kuma bata da nauyi. Dayar kuwa doguwa ce har kasa kuma tana da dan kauri haka hannunta dogo ne, tana da madauri a jiki kamar bath robe. Ganin su kadai ne a dakin kuma yanayine na zafi, sai bata dora ta saman ba, ta barta.

Tana komawa daki ta tarar har Rabi'ah ta baza mata kayan abinci duk da dai marassa nauyi ne. Dambun cous-cous ne da yaji hadin kayan lambu sai

kuma yankakkun kayan marmari da madarar hollandia yoghurt ta strawberry. Ta zauna tana ci suna taba hira da Rabi'ah, gajiyar tafiya yasa ta kasa cin abincin da kyau sai fruits din data sha sosai, ta kuma sha yoghurt din. Data gama sai ta rufe komi, Rabi'ah ta wuce ta kai kayan kicin ita kuma sai ta koma bayi ta wanke bakinta ta dawo daki ta kwanta. Rabi'ah tana sama ita kuma tana na kasa, ta kira Mama ta shaida mata sun sauka lafiya, ta hadata dasu Maryam suka mata sannu da hanya kafin su yi sallama.

Daga nan ta yada kai akan filo babu jimawa barci yayi awon gaba da ita. Ba ita ta farka ba sai da alarm ya tashesu sallar Asubahi. Bayan sun yi sallar, suka yi azkar, sake komawa suka yi suka kwanta abinsu.

Karfe tara da rabi ta farka. Jikinta ya saki sosai, babu kuma gajiya a tattare da ita sai rashin karfin jiki da kasala.

Ta sauka daga kan gadon ta fita tare da shiga toilet, baki ta wanke kawai. Ta bi dogon corridor din gidan ta shiga kicin. Ko'ina na gidan a gyare yake tas-tas, babu hayaniya wadda ta sanya mata natsuwa. Tana son rashin hayaniya da tsafta ita kam.

Yunwa take ji sosai, kuma ita ta tasheta. Ta fara bude-buden fridge da cupboards tana neman wani abu da zata fara dashi kafin ta yi abin kari, saboda tasan mutanen gidan zasu iya kaiwa sha daya ma basu tashi ba. Tasan kuma abu mai dan nauyi zasu bukata.

Freezer ta bude ta ciro kaza guda, ta fara wanketa ta dora akan wuta bayan ta yanka wadatacciyar albasa ta zuba kayan kamshi.

Sai ta dama quicker oats ta hada ta sha kafin kazar ta gama dahuwa.

Ta fara fito da abubuwan da zata bukata tana warewa. Kafin kace me, ta hargitsa gidan da tattausan kamshin girki mai dadi.

Dage-dagen kaza tayi da kayan lambu, sai ta soya kwai, ta yi toasting din biredi, sai shayi mai kamshi data hada. Ta riga ta gama sanin tsarin gidan, don haka tana gamawa ta samu flask da warmers ta zubawa Anty Jamila

nata da na mai gidan, ta debar musu ita da Rabi'ah, sauran kuma ta ajiyesu a wani mazubin na daban. Duk mai so daga cikin mazan gidan wadanda kannen maigidan ne dake karatu a BUK, sai yazo ya dauka duk da cewa bata ji motsin kowa ba yau.

Tana cikin wanke-wanke Anty Jamila ta shiga kicin din. Doguwar macece mai dan jiki, baka ce amma kuma kalar fatarta mai kyau ce da sheki saboda tana bata kulawar data dace. Saye take da doguwar rigar barci cotton, sai ta dora hijabi karama a sama wadda ta tsaya mata a kugu, kafarta saye da takalmin silifas mai taushi.

Nadiya ta juya tana kallonta lokacin data shiga kicin din, fuskarta dauke da murmushi. Durkusawa tayi tana gaidata, Anty Jamila ta jata jikinta tana dariya, "ai tunda naji gida ya karade da kamshi nace lallai Nadiya ta dira gidana!"

Dariya ta sake a tausashe, tace, "haba dai Anty! Ke ma fa bangaren girkinnan ba daga nan ba. Ni ai nawa sharar fage ne!"

Anty Jamila tace, "ba wani nan. Ke kanki ai kin san kafin a kamo kafarki a bangaren girki, za a jima gaskiya!"

Murmushi ta sake yi tana girgiza kai kawai.

Tray din data shirya musu kaya da maigidanta ta nuna mata, tace, "ga abin karinku na hada muku, Rabi'ah bata tashi ba shi yasa bata kai muku ba!"

Saboda ita bata shiga bangaren Maigidan. Bakin iyakarta dashi idan sun hadu a falo ta gaisheshi, ko kuma tayi dakonshi da safe idan tana kicin tana aikin girki.

Anty tace, "da kyau Nadiyata! Wallahi kamar kin san ina kewar girkinki dama. Bari idan Daddy ya fita, zamu shiga kasuwa anjima muyi siyayyar spices don gashin kazar nan da kike mana da kuma local mac-D dinki nake son ci."

Tayi murmushi tana gyada kai, "to shikenan Anty, Allah Ya kaimu!"

Anty ta dauki farantin ta fita, ita kuma ta cigaba da aikinta.

Data gama ta dauki nasu abincin ta kai daki. Sai lokacin Rabi'ah ta tashi, ta shiga bayi. Kafin ta fito har Nadiya ta gyara dakin, ta hada musu shayi. Suka zauna suna kari. Mama ta kira suka gaisa, ta hadata dasu Rabi'ah suka gaisa, kafin hira ta kacame musu ita da su Maryam. Nan ta barsu suna ta yi, ta kwashe kayan abincin nasu ta kai kicin.

Dakin ta koma ta fara tsifar kanta saboda ya fara datti, a gida kuma bata cika samun lokacin yin tsifar ba. Tana jin sanda Rabi'ah ta kashe wayar tazo tana tayata itama. Tana son irin gashin Nadiya wanda ya kasance baki, sassalaka kuma mai tsayi sosai. Ba kamar irin nata ba wanda yake mai tauri sosai duk da cewa itama ba laifi tana da tsayin gashin da kuma baki.

Bayan nan dakin Anty Jamila suka je suka gyara mata, daga nan suka shiga dakin mazan gidan don su gyara. 'Ya'yan Anty Jamila hudu, danta na farko Auwal da suke cewa Yaya, shekarunshi sha bakwai, yana Sudan wajen Yayan Babansu, sai Rabi'ah yar kimanin shekaru sha biyar, sai mai bi mata Abubakar Sadeeq shekarunshi goma, dai autanta Haroun, suna ce mishi Haneep, shekarunshi biyar.

Da yake tana da abokiyar zama, wani lokacin yaran su kan je gidanta suyi weekend ko hutu, ko kuma ita nata yaran guda uku su zo nan gidan nata. Da alama wannan satin suna can.

Da rana ta mulmula musu tuwon semovita da miyar yauki, suka ci suka yi nak kafin Anty ta daukesu a motarta suka fita. Shagon saloon dinta dake nan cikin Nasarawa gra din suka fara tsayawa, aka wankewa Nadiya kai aka kuma yi mata kalba saboda ta fi sonta akan kitso. Daga nan suka shiga kasuwa ta taya Antyn hado kayan kamshi na abinci saboda a cewar Antyn ta ma fi son hadin spices din Nadiya akan ta siya na kanti.

Sai yamma likis suka koma gida.

Da dare tayi musu gashin nama mai ruwa, ta hada musu da taliyar indomie noodles wadda tayi steaming dinta sai ta soyata a cikin kwai sama-sama bayan ta wadatata da kayan lambu da taruhu daya sa tayi dan yaji-yaji.

Bayan sun gama cin abincin sun jima suna hira a falon Anty. Sai wajen karfe goma saura kafin suka yi mata sai da safe. A dakin ma koda suka gama shirin barci, wata sabuwar hirar suka dasa. Bata ma san lokacin da barci ya kwasheta ba sai can wajen karfe hudu ta farka. Da taga alamun barcin ba daukarta zai yi ba, sai kawai tayi alwala ta fara nafila.

Da aka yi Asubahi ta tashi Rabi'ah itama tayi, sannan ta sake komawa barci.

Ranar ita da Rabi'ah suka hada abin kari. Lokaci yana ta karatowa, don a yadda ta saba, ana yin Azuhur take yin haramar tafiya gida yadda zata isa da wuri. Ji ta dinga yi dama kada ta koma. Idan ta tuno irin tsarabe-tsaraben dake jiranta sai taji inama... inama. Inama ba zata koma wannan gidan ba.

Da zata tafi Anty ta hadata da tsaraba mai yawa. Ta dauki dubu goma ta bata tayi kudin mota, dubu goma ta kaiwa Mama, dubu ashirin kuma ta kaiwa Abbansu. Ta mata godiya sosai da sosai.

Har tasha suka kaita ita da Rabi'ah. Sai da suka tabbatar ta samu mota kafin suka yi sallama da ita cike da shauki. Babu jimawa mota ta tashi suka dauki hanya.

Sun isa Makarfi, direban ya tsaya a wani babban gidan mai domin su sha mai. Da wannan damar fasinjoji suka sauka domin su gudanar da wasu bukatunsu.

Nadiya ta bi bayansu itama ta fitan. Shago ta shiga ta amshi gorar madarar Dudu mai sanyi ta samu gefe daya ta zauna a cikin shagon tana sha, idanunta akan motar tasu har zuwa lokacin da fasinjojin suka fara komawa. Ta tashi tsaye tare da jefar da robar lemun a cikin kwandon shara. Yunwa ce tayi guzurinta sosai, saboda tun karin safe babu abinda ta ci. Anty Jamila babu yadda bata yi da ita ba amma tace mata ba zata ci komi ba. Wani lokacin dama haka take, idan a halin tafiya take bata cika cin abinci mai nauyi ba saboda hakan ya kan zame mata matsala a yawancin lokuta.

Dai-dai lokacin da zata fita daga shagon, su kuma sun kawo kai. Karo suka gabza ba tare da saninsu ba. Abu biyu zuwa uku taji a lokacin, farko wani irin daddada kuma sansanyan kamshi mai kwantar da rai. Tana da son kamshi, tana kuma girmama mutumin da yasan kamshi da kuma darajarshi. Ita fa sau tari, tana gwada halayen mutane da irin kamshin da take ji a tattare da su ne.

Abu na biyu kuma shine yadda kanta ya bugi kirjin wanda suka yi karon. Hakan ya nuna mata cewa mutum ne mai tsayi, saboda itama babu laifi tana da tsayi gaskiya.

Na uku kuma, wani abu mai sanyi daya tsiyaya yana kwaranya a cikin jikinta, wanda ta fuskanci lemun Five Alive ne, Pulp, dake hannun mutumin ya tsiyaye a jikinta.

Kafin ma ta gama tantance wadannan abubuwan, taji an sanya hannu an yakiceta anyi baya da ita. Tayi ido hudu da abu, halittar data sanya taji wani abu game da wani da namiji, da bata taba ji ba a tarihin rayuwarta.

Fari ne, dogo kamar yadda tayi kintace, mai cikar jiki da cikar kamala. Akwai alamun hutu sosai a tattare dashi, bashi da rama duk da tsayin da yake dashi, hasalima yana da dan nama a jikinshi. Kalmar 'giant' ita kadai ta iya je mata kwalwa a wannan lokacin. Saboda duk inda za a nemi mutane giants, to mutumin ya kai sahu na farko.

Fuskarshi cike take da gargasa wadda ta kwanta mishi luf a fuska ta kuma kara kawata fuskar tashi.

Lebbanshi take kallo wadanda suka saki wani irin siririn tsaki, suna motsewa da tankwashewa zuwa alamun bata fuska, "baki kallon gabanki ne idan kina tafiya ko me?!"

Ya watsa mata tambayar cikin fusata da bacin rai. Nan da nan itama sai taji nata ran ya baci. Abinka da mai zuciya a makoshi, kiris take jira.

Tace, "ban gane ba Malam! Idan ban manta ba ina ga ai kaine ka kawo min karon! Tunda kai ne ya kamata ka kalli gabanka kai da zaka shawo kwana! Kuma kai ka zubar min da abu a jiki ko?!" Ta fada tana nuna mishi ta'adin daya mata.

Amma ko a kwalar rigarshi, ya sake jan wani tsakin ya zagayeta yana jefa mata harara, Hannunshi jaye da wani yaro, magana yake yi kasa-kasa wadda ta tsinci kalmar 'sai kace makauniya' da 'rashin tunani' a ciki. Ta bishi da kallo baki hangangan cikin tsananin mamaki. Wannan fa shi ake kira karfin hali barawo da sallama. A dakeka kuma a hanaka kuka? Ai ba ma zata sabu bane!

Tana shirin bin bayanshi ta danna mishi rashin kirkin da ba zai manta ba, direba ya fara danna mata horn. Wasu daga cikin fasinjoji ma masu gajen hakuri har sun fara lekowa ta taga suna mata magana da masifa. Ta kara juyawa tana hararshi, cikin sa'a lokacin shima ya juya. Ta kuwa kara kaifafa zafin hararar tata kafin ta wuce dakinta sassarfa, jikinta a jike, ta shige mota.

Hankicin hannunta ta jika da ruwa tana goge jikinta kafin lemun ya bushe mata a jiki. Tsinuwa kuwa da Allah Ya isa tafi cikin kwando wadda ta ja tun ma kafin su kai ga barin gidan man.

Ranta bai kara dagulewa ba sai da suka tarar da wani babban hold up a Rigachikum. Motar mai ce ta fadi a wajen, don ma Allah Yasa rayuka basu salwanta ba amma dai hanya ta samu matsala saboda ta dalilin hakan, gada ta lalace. Don haka hannu daya ake bi, ga shi ranar Lahadi ce.

Zafi da gajiya suka mata rubdugu, tun suna zaman jin dadi har suka fara na wahala. Sai suyi zaman fiye da minti ashirin a waje daya babu alamun zasu motsa, idan kuma suka dan matsa, bai bi su yi kamar taku hudu zuwa biyar ba sai a sake tsayar dasu.

Suna nan fiye da awa biyu cikin wannan yanayin, har ta fara tunanin ko itama zamewa zata yi kawai ta sauka daga motar, idan ta taka da kafarta ta fita daga cikin hold up din sai ta samu abinda zai karasa da ita gida kamar yadda taga sauran fasinjojin suna yi.

Motocin sojoji suka wuce ta gabansu, maimakon suyi gaba sai suka fara kokarin bude hanya, da alama wani ne zai wuce. Hakan kuma ya faru yafi sau a kirga a gabansu. Farko dan gidan Sarkin Zazzau ne ya wuce, na biyu kuma Kwamandan sojawan ne gabadaya, na uku da na hudu bama ta tsaya jin ko su waye ba saboda ita abin takaici ma yake bata. Yanzu kuma ko wanene? Ta tabe baki tana jan dan siririn tsaki.

Manyan motoci ne bakake guda biyu suke kokarin wucewa cike da securities, sai wata farar BMW a tsakaninsu.

Motar take kallo saboda ta burgeta sosai. Daga gani sabuwa ce, ko kuma ba a cika amfani da ita ba. Hankalinta ya nutsa wajen tunani da lissafin lokacin da itama watarana zata mallaki mota mallakin kanta. Bata kula da gilasan gidan baya da ake budewa ba sai da suka hada idanu biyu da wannan mutumin na dazu.

Ita yake kallo, ta kula. Da wani murmushin gefen baki yake kallonta, cike da arrogance daya matukar kara kona mata rai. Wato saboda yana ji da kudi da mulki shine har yake wulakanta mutane son ranshi? Bata ma san lokacin data saki wani dogon tsaki ba, tana jin yanda ranta yake kara baci. Ita fa bata kaunar mutum marar kirki, taga alamun wannan mutumin kuwa ya hardace rashin kirki babi-babi a kanshi. Da taga tsakin ma bai mata ba, sai ta kara da harara da murguda baki. Tayi gefe daya da kanta don ma kada ta tsayar da kanta anan tana kallonshi har ya kara bata mata rai. Bata san lokacin da suka wuce ba. Su kuma suka cigaba da zaman jiransu anan.

Ana kwala kiran sallar magariba a wasu masallatan, ta tura kai cikin gidansu ta shiga. Ace ma ta gaji fiye da kima, bata baki ne.

Gidan kwalam kamar babu mutane a ciki, in banda karar TV dake fita daga dakin Abbansu.

Taja tayi turus a bakin kofar dakinta, zuciyarta na harbawa da bugawa cikin wani yanayi marar dadi da taraddadi.

Kofar dakin take gani a bude, babu alamun kayanta a wajen ko a alama. Idan ma ba sani kayi ba, ba zaka taba cewa wani ya taba wanzuwa a wajen ba. An fara buge wani bangare na dakin, tare da kicin da Salame tasa aka ware mata lokacin da ake kan gyaran gidan. A maimakon kuma ta zuba kayan kicin din, sai ta kulleshi kawai tana zuba tarkacen kaya, da kayan sana'arta na kayan masarufi da take yi lokaci zuwa lokaci idan ta samu kudin yi.

Da alama mutanen gidan sun ji sallamar data kwala, saboda taga wasu sun fara lekowa ta bayan labule suna kallonta. Da alama akwai abinda suke tsammani.

Tsabar gajiyar dake cinta, bata iya amsa sannu da zuwa din da Maryam take mata ba, sai bin ta da kallo data yi, kafin ta kara kallon kofar dakin nata, ta sake maida kallonta ga Maryam din. Tace mata, "me ke faruwa ne a gidan haka naga an buge dakina?"

Mama ta fito daga daki da hijabi a jikinta, da alama sallah ta gama yi.

Tace, "Nadiya kece da wannan magribar?"

Sai ta kalleta kawai ta kasa mayar mata da amsa.

Mama ta cewa Maryam, "amso kayan hannunta mana ki kaisu dakina. Nadiya, shigo nan kinji?"

Sai dai duk yadda ta kai ga son ta motsa kafafunta ta kasa, yadda kasan wadda aka kafe a wajen.

Tace, "Mama ina zan je bayan kuma nan shine dakina? Menene yake faruwa wai? Ban gane ba!"

Kamar kuwa wadda take jira, Lantana tayi caraf tace, "me kuwa ke faruwa? Mai gidan yake bukatar wajenshi. Amaryarshi yake gyarawa wajen zama!"

Sai ta rasa me ma zata ji a lokacin. Kuka zata yi na wannan rashin adalci, ko kuma murnar karuwar da zasu samu zata yi? A gefe guda kuma tunanin matsayin da take dashi a wajen mahaifin nata take yi. Tana ganin ko rikonta

ake yi, ai tana da hakkin a sanar da ita, a bata notice, ba wai kawai tazo ta samu dakinta a balle ba.

Abbansu ya bude kofar dakinshi ya leko, "wai lafiya? Hayaniyar me nake ji ne haka da wannan magribar?"

Ta juya tana kallonshi tare da dan rusunawa, "babu komi Abba. Kawai dai na ga dakina a bude shine nake tambayar lafiya?"

Ya gyara tsayuwa yana kallonta fuska a cune cike da alamun ko ta kwana, "ehh! Dakin nake bukata saboda aure ya taso min na gaggawa, akwai matsala ne?"

Ta girgiza kai a hankali, kunar zuciyar ma ta kasa ji, bata jin komi. Tace, "ni kuma ina zan zauna?"

Yace, "ki samu dakin daya daga cikin iyayenki mana ki zauna? Dama ai ba zaman gidan kike yi ba, kwanciya kawai kike yi a ciki. Kinga ai gwanda a amfaneshi da kyau. Kuma dama can ai na fada miki cewa wajene na wucin gadi, saboda ke dai matafiya ce, don haka ban ga dalilin ware miki daki a gidana ba!"

Ta jinjina kai a hankali, idanunta kyas hawayen ma sun ki fita. Wannan ba komi bane cikin halayen Abbanta. Wannan ba komi bane cikin dubannin abubuwan daya aikata a gareta. Ta kalleshi a nutse, tace, "hakane. Allah Ya bada zaman lafiya to!"

Ta juya tana kallon Maryam da suka yi tsaye cirko-cirko, ta umarcesu dasu dauke kayan su kai dakin Mama kamar yadda tace.

Shi kanshi sai yaji alamun rashin dadi a ranshi, amma ya fuske. Fitowa yayi da niyar idan ta kama har korarta yayi don yasan Nadiya da kafiya da taurin kai, bai taba tsammanin zata bari su wanye lafiya ba.

Yace, "ki zauna anan ki dan yi maleji, idan an gama bikin, zan sa a tada miki wancan wajen na kusa da kicin kafin lokacin barinki gidan yayi!"

Tayi dan murmushi kawai, saboda tasan karshen maganar kenan. Bata da wannan matsayin da zai batar da kudin da zai gina mata daki, ita ta sani. "To shikenan, Allah Yasa!" ta furta a sanyaye.

Da wannan ya koma dakinshi ya maida kofar ya rufe, har da murda sakata.

Sauran matan nashi suka kwashi jikkuna a sanyaye suka koma daki, har da mai jan tsaki. Saboda duk ba haka suka so lamarin ya kasance ba. Itama kuma ta san hakan, shi yasa yau dai taki biyewa zuciyarta balle a kai ga yin batacciya.

Ta shiga dakin Mama ta tarar da kayanta a gefe guda, dama ba wasu tarkace ne da ita ba na a zo a gani. Don haka ita da su Amina suka sama musu waje suka ajiye.

Ta samu ruwan zafi a flask din Mama, tayi amfani dashi tayi wanka, tayi sallah, ta dan fara samun natsuwar da take bukata.

Mama tana kan kujera a zaune da carbi a hannunta tana ja, ta kalli Nadiya data gama waya da Rabi'ah.

Tace, "yau dai kinyi kyan kai da baki bari zancen dakin nan yayi tsawo ba."

Tace, "ai gani nayi idan ma na biye mishi ba ribar abun zan ci ba, zai iya ma cewa in bar mishi gidan. Shi kuwa mutum da gidanshi ai ba zaka mishi takama ba, sai ka barshi yayi duk abinda yake so dashi."

Mama ta girgiza kai, "ke dai kawai kin san halin mahaifinku sai shi. Amma in banda haka, yanda yake takamar yana da hakkin ya umarceki ki mishi biyayya, kema fa kina da hakkin idan abu irin haka ta taso ya sanar dake, idan ma ta kama ya lalubar miki mafitar inda zaki koma da sauransu."

Nadiya tayi dan murmushi, "Abba ne fa muke magana a kanshi. Ke kinsan ai wadannan abubuwa ba damunshi suka yi ba!"

Gidan tsit kamar babu mutane idan ka debe hayaniyar yaran su Salamen dake wasanninsu a tsakar gida. Da alama yau Abba ya tabo ran matan gidan, don kuwa da ana zaune lafiya ne da yanzu suna dakinshi suna ta hira da shewa abinsu. Dan murmushi tayi tana girgiza kai, tasan sarai maganar auren ce ta girgizasu, amma na dan lokaci ne. Ai yanzu ne sabuwar riritawa da kulawa zata fara.

In dai auren Abbansu ne, su kansu yaran gidan sun saba balle matan.

Ita a karan kanta, da wayonta dai, ba zata iya cewa ga iya adadin matan da Abban nasu ya auro ba. 'Ya'ya ma kuwa kusan hakan take. Idan aka zauna lissafi akan jima kafin a kai karshensu.

Bayan tayi sallar isha'i, ta zauna ta warware jakar tsarabarta. Mama taji dadin kudin da Anty Jamila ta bata, saboda dama suna cikin rububin yadda za a biyawa Maryam kudin jamb ne duk da Nadiya din tace ita zata biya mata.

Kudin Abbansu kuwa sai Mama ta damkawa a hannu ta kai mishi, shima kuma yayi godiyar sosai da sosai.

Amina ta kai mata abincin da aka yi da dare, shinkafa ce da miya. Miyar yadda kasan a lokacin aka markada kayan miyar saboda bata soyu ba ko kadan, shinkafar kuwa ita da tuwo bambancinsu kadan ne.

Da kyar ta iya cokali biyu, ta ajiye ta ture kwanon gefe guda. Dole sai lekawa tayi kofar gida ta samu wani matashin saurayi data saba aike, AbdulGaniyyu, yaje bakin titi ya samo mata shayi da biredi da wainar kwai, saboda bata so ta kwanta bata ci komi ba tunda da Azumi take da niyar tashi.

Tare suka ci abincin da su Amina. Fatima, yarinyar da take hannun Lantana, rikonta take yi saboda mahaifiyarta bata gidan, taje domin Amina ta tayata home work dinta na makaranta, ta zauna itama aka ci da ita.

Suna kallo da hira tayi shirin barcinta. Ta fito da katifarta da aka kai kuryar dakin Mama, ta shimfida a falon kusa da kofa. Mama taso taje su dinga

kwana akan gadonta tunda su Amina katifa suke shimfidawa a kasar gadonta, amma ta ki. Saboda ba zata iya hada wajen kwana da Maman ba.

Tayi kwanciyarta tana sauraren hirar da suke yi, har da karin ya'yan Salame da na Lantana da suka bi sahun Fatima.

Lokaci zuwa lokaci idan iyayen basu hana ba, yaran su kan leka dakin Mama ko suyi kallo ko kuma don su Amina su yi musu assignment.

Bata san lokacin da suka bar dakin ba saboda barci daya dauketa.

Ranar kwana tayi tana mafarkin daddadan turaren data shaka a jikin wannan mutumin da kuma yadda fuskarshi take cunewa lokacin da yake yi mata fadan ta dinga kallon inda zata.

******

Kwanaki biyu da yin haka, amma har an gama gyaran dakin da amarya zata tare fenti kadai ya rage. A cikin satin kuma aka daura musu aure. Saboda daurewa karya wani gu, Abbansu har Kamu ya hadawa amaryar tashi. Can aka tsinto bidiyo din yadda ya dinga barin kudin liki a wajen kamun a wajen yan ba-ni-na-iya din yan unguwarsu.

Don kuwa har gida suka yi sallama suka kaiwa matan. Mama data gani baki ta tabe tace 'Allah Ya kyauta.' Nadiya ma haka.

Don kuwa abin ya girmame mata. A ranar da safe ya gama tijara da ihun ba shi da kudin da zai biyawa yaran gidan na makarantar boko da islamiya. 'Amma da yake amarya ce, ita ai gata can yana mata barin kudi da na jiki a banza.'

Irin maganganun da taji su Lantana sun hade kawuna a kofar kicin suna ta furtawa kenan cike da bacin rai. Lokacin kuwa taje wucewa zata fita waje da safiyar Alhamis, tayi dan murmushi, tace, "a dai juri zuwa rafi, saboda watarana tulun zai fashe!"

Salame ta zaburo mata, "ke karamar yar iska! Allah dai Yasa ba dani kike ba don naji me kike cewa sarai!!"

Tayi banza ta kyaleta ta kara gaba abinta tana dariyar mugunta.

Yadda taga maganar bikin ta gigitasu gabadaya abin dariya yake bata. Ko kuwa dai don Abban ya jima bai yi auren bane shi yasa suka fara mantawa har suka saki jiki suna tunanin ko shikenan? Ta tare abin hawa ta tafi wajen aikinta abinta.

A shago ta tarar da Aramide. Tayi mamakin hakan saboda ranar aiki ce, koda zata je bata cika zuwa da safe ba sai can yamma idan ta tashi daga aikin. Kuma mafi yawanci ta kan je ne kawai don ta karbi wasu abubuwan ko kuma kudi idan bata da su a hannu.

Ta shiga dakin da take canji ta rataya Apron a saman doguwar rigar jikinta.

Yadda taga dakin a hargitse ya tabbatar mata da cewa lallai Aramide anan ta kwana. Tayi tsaye cikin mamaki tana kallon Aramide din da tayi zaune akan arm chair, sai lokacin ta kula da yadda tayi wani jugum-jugum kamar wadda aka yiwa mutuwa. Gefen fuskarta daya yana can gefe guda ta ki yarda su hada ido da Nadiya.

Ta taka ta matsa gabanta cikin nuna alamun damuwa, tace, "Ara, me yake damunki ne wai? Lafiya?"

Kai kawai ta iya girgiza mata bata ce komi ba. Ganin haka sai ta dafa kafadarta tare da juyota ta kalleta, ai bata san lokacin data ja da baya ba hannu dafe da kirji tana zare ido a kidime. Gefen fuskarta ya hau yayi wani irin kumburi, idonta a rufe yake ma ruf da kyar take iya daga shi.

Tace, "innalillahi wa Inna ilaihi raji'un! Aramide me ya sameki ne haka? Waye yayi miki haka?"

Dama mai neman kuka ne aka jefeshi da dunkulen kashin awaki, tana jin haka sai kawai ta dargwaje da kuka. Tayi-tayi har ya isheta, Nadiya ta kasa ce mata komi sai ban baki da kokarin tausarta da kalamai masu dadi. Zuwa

lokacin data gama kukan, fuskarta ta gama baci da hawaye da majina. Ta dauki tissue tana goge fuskarta tare da fyace majina.

Cikin murya data gama dusashewa da kuka take cewa Nadiya, "wallahi na gaji da wannan cin kashin da ake yi min Nadiya, na gaji! It's either in kai mutum kara ko kuma in kai kararshi wajen iyayenshi!"

Nadiya sai tayi sakato! tana kallonta cike da daurewar kai, tace, "wa ke nan? Ba dai maigidanki ba ko?"

Ta jefa mata harara cike da kulewa, "idan ba shi ba ta ya kike tunanin zan bari wani gardin yayi min wannan danyen aiki?"

Ta daga kafada tana dan tabe baki, "na sani?!"

Tayi kwafa tare da yin tsaki, "ban taba fadawa kowa halin da nake ciki ba har iyayena kuwa. Amma yanzu tura ta kai bango, na gama gajiya. Nadiya mutum ya mayar da ni kamar jakka, abu da wanda ya kai da wanda bai kai ba kawai sai kiga mutum wai ya hau ni da bugu babu gaira babu dalili? Ina dannewa ne ina cijewa saboda bana so a ga kamar na cika korafi ne, kuma bani da isasshiyar shaida saboda sau tari yana yin bugun nashi ne a inda mutane ba zasu gani ba balle a zargeshi da wani abu. Amma wallahi yau ya tsokanowa kanshi! Ke wallahi kotu kawai zan maka dan iska fakat babu wani jan dogon zance!"

Nadiya dai ta baza kunne tana sauraronta, ranta rabi cike da tausayi rabi kuwa dariya ce take tuketa tana dannewa.

Tace mata, "ba haka ya kamata ayi ba saboda komi na duniyar nan fa da kike gani dan hakuri ne. Idan kika kaishi kara yanzu saboda kina cikin fushi, kuma nan gaba kuka shirya to da wane ido zaki kalleshi da yan'uwanshi?"

Tace, "ai dama tsakanina dashi kotu zata shiga ba wani abu ba, don wallahi ba zan zauna ya nakastani a banza ba! Wai ma kinsan ko saboda me yayi min wannan mahangurbar?"

Nadiya ta girgiza kai.

Tace, "kawai saboda ya tambayeni ina links din hannun rigarshi nace ya duba cikin kayanshi. Kawai sai ji nayi ya kai min naushi a gefen ido! Ya kuma hau ni da jibga kamar wata jakar gidansu! Wai na raina mishi wayo saboda yana min magana ina maida mishi amsa gatsar babu ladabi! Nadiya mutum ga gori, ga shi da dan karen rashin mutunci. Duk wasu abokaina ya rabani da su saboda rashin mutuncin da yake musu idan sun zo inda nake. Yanzu abin ya tashi a kansu ya koma kan yan'uwana da dangina. Shikenan ranar nan har jaka yace min saboda na cinye malmalar amala hudu a gabanshi!..."

Nadiya kuwa me zata yi ba dariya ba. Ta dinga kyakyatawa har tana tuntsurawa.

Aramide ta tsaya tana kallonta cike da takaici. Sai da taga bata da alamun dakatawa sannan ta dada mata duka a cinya, tace, "baki da kirki wallahi Nadiya. Wato ma maimakon ki tausaya min shine zaki sanyani a gaba kina min dariya ko?"

Ta kai hannu tana goge hawayen da suka cika mata ido saboda dariya. Tace, "abin naku ne ai gwanin ban dariya. Kinga nan gaba sai ki dinga ba mutane shawara, a dinga hurawa kafin a ciza!"

Sai tayi turus tana kallonta. Ta yada kai gefe guda, tace, "ashe maganar nan ba zata taba wucewa a wajenki ba?"

Nadiya tayi saurin girgiza kai, "a'ah wallahi, ke kin fi kowa sanin cewa tuni data gama wucewa a wajena, kawai dai wata magana da kika taba fada min ne na tuna shine ta bani dariya..."

Sun hadu da Aramide a ABU Zaria, Division of Agriculture (DAG) inda duk suke karantar Home Economics. Itama Aramide haifaffiyar Kaduna ce amma iyayenta dukansu yarbawa ne, aiki ne ya kaisu Kaduna. Idan kaji Hausa a wajenta kuwa yadda kasan jakar Kano. Tasu tazo daya sosai da Nadiya, suka kulla kawance sosai.

A shekararsu ta karshe dai suka koma cikin ABU da zama sai suka hada suka kama gida off-campus.

A shekarar ne Allah Ya hada Nadiya da wani saurayi AbdulGaniyyu, shima Yoruba ne amma mahaifiyarshi bahaushiya ce. Yana da iliminshi babu laifi kuma yana aiki a Kaduna a hukumar NNPC. Babban mutum ne ba laifi, don ya ba shekaru talatin baya amma bai taba aure ba.

Yana da yawan hidima sosai, ga kyauta. Don kuwa kullum tafe yake da abubuwa iri-iri, kayan makulashe da tande-tande, kayan kawa da ado, har waya yaso ya canza mata a lokacin amma ta ki saboda ita har ga Allah bata da kudirin aurenshi saboda sam-sam bata jin auren nashi a cikin ranta ko kadan.

Bata san ya aka yi ba, ko cikakken watanni hudu basu yi da haduwa ba don har ya fara zancen idan suka je gida hutu wannan karon zai tura gidansu a tambayi aurenta. Kawai sai taga mutum ya janye mata rana daya. Sai ga Aramide ta fara fantamawa iyaka son ranta, tayi sabon saurayin dake mata hidima yana mata kashe-kashen kudi. Tun tana jin wai-wai a gari har dai ta gansu da idanunta, ya dai tabbata lallai Aramide ta mata snatching din saurayi. Tace umma ta gaida aysha don kuwa dama bata cikin yan kayan. Ta zuba mata ido tayi ta boye-boyenta, daga baya dai da kanta taje tana mata kame-kamen zance, wai wallahi kai tsaye gidansu ya aika yace yana sonta kuma iyayenta suka amsa da sun yarda shi yasa ita kuma bata zauna yin musu da su ba saboda ba zata iya bijire musu ba duk da tasan cewa hakan bai dace ba.

Nadiya dariya tayi sosai a lokacin, tace mata kada ta damu don kuwa ita har ga Allah abin bai dameta ba don dama bata sa a ka ba. Ta kuma yi musu fatan alkhairi, tace in dai namiji ne taje gashi ga ta nan.

Daga haka basu kara tada maganar ba. Suna gama makaranta kuma aka daura musu aure. Nadiya tayi musu kara sosai wajen halartar bikin da hidimtawa sosai a matsayinta na babbar kawa. Shima kuma AbdulGaniyyu din har aka yi aka gama bai taba nuna mata wani abu ba ko a fuska, don haka itama bata taba nuna mishi wani abun ba.

Biki aka yi gagarumi, irin nairar da aka barar abin sai ya baka mamaki. Amarya ta tare a gidanta dake Korau road, ita dai Nadiya tun washegari da suka koma suka kammala gyara mata gida, bata kara waiwayarsu ba.

Tare suka shiga camp da Aramide, da Allah Yasa itama tayi marriage certificate sai aka barta anan Kaduna.

Bayan sunyi service dinsu, Aramide din ta bata shawarar mai zai hana su kama hayar wajen da zasu bude shago na kayan ciye-ciye? Tunda ita Aramide din ta samu aiki a kamfanin Indomie, sai ya zamana Nadiya din tana kula musu da wajen? Aka yi haka kuwa, cikin dan kankanin lokaci an samu waje an gyara shi, aka bude wajen inda kwastomomi suka fara tururuwa. Jajircewar Nadiya da sadaukarwarta ya kai wajen matsayin da yake dashi a halin yanzu, don kuwa ita kanta Aramide din ta san da hakan.

Daga farko ita Aramide din cewa tayi mijinta ne yayi mata kyautar kudade masu yawa shi yasa ta yanke shawarar ta bude wajen. Sai da tafiya tayi tafiya daga baya dai Nadiya ta fahimci kwata-kwata zancen ba haka yake ba. Iyayen Aramide din su suka bata kudin wanda ya kasance na sadakinta ne da kuma wasu kudade da iyayen suka saba ba 'ya'yansu mata idan sun yi aure domin su ja jari.

Ita dai Nadiya hakan bai dameta ba, tunda ko babu komi tana jifar tsuntsu biyu ne da dutse daya.

Na farko tana gudanar da abinda tafi so a duniya, wato girke-girke, na biyu kuma ana biyanta da kudaden dake daukar nauyin dawainiyarta. Don haka bata da wata damuwa sam.

Ta muskuta ta gyara zama tana fuskantar Ara dake shan shayi da cupcakes a lokacin. Tace, "me zai hana ku zauna ke da shi kuyi magana ta fahimta? Idan yaso sai ku ajiye ground rules (dokoki) da watakila zasu iya taimaka muku wajen rage yawan dukan. Saboda gaskiya baya da dadi ko kadan."

Ta girgiza kai, "kina tunanin bamu yi hakan bane tun farko? Lokacin farko dana tunkareshi ma da wannan maganar ai wani dukan ma na janyowa

kaina. Wallahi wani mari daya falla min sai da naga taurari suna min yawo a idanuna!"

Nadiya ta jinjina kai cike da jimami, tace, "gaskiya dai yakamata ku canza taku, saboda hakan ba zai haifar muku da da mai ido ba. Nan gaba idan kuka fara tara iyali fa kuma mai zai faru? It's either ya dinga hadawa har diyan yana jibga, ko kuma su yaran suna ganin abinda ke faruwa su fara raina shi da tuhumarshi. Kinga hakan duk ba abu bane mai dadi gaskiya."

Tace, "nima hakan nayi tunani shi yasa kawai zan wuce wajen iyayenshi in fada musu abinda yake faruwa, watakila su zasu iya bullowa lamarin da mafita. Don kuwa kin san idan naje na fadawa iyayena abinda ke faruwa ba zasu taba tsayawa su kwatar min yancina ba kila ma sai dai su hada da min Allah kara. Don tun lokacin da yaje neman aurena sai da suka bani shawarar kada in aureshi don sun riga da sun yi min miji, amma na kafe akan sai shi. Yafi dai kawai inje in samu iyayen nashi."

Nan ma Nadiya dariya ta so ta saki jin yadda kalamanta suka saba da cewar data yi iyayenta suka matsa akan sai ta aureshi.

Iyayen AbdulGaniyyu mutanen Benue ne. Shi ya tashine a hannun kawunshi dake zaune a Kaduna wanda Allah Ya yiwa rasuwa jim kadan bayan AbdulGaniyyu din ya tafi jami'a. Shi kuma sai yaci gaba da zama anan har Allah Ya taimakeshi ya samu aiki.

Nadiya tace, "to Allah dai Ya. kyauta! Yaushe zaki tafi?"

Tace, "ai a yau ba sai gobe ba zan dauki hanya in Allah Ya yarda. Ni zan koma gidan wannan mutumin ya sabautani? So nake karshen satin nan a rufe shagon ma, ku tafi hutu ko da na sati biyu ne tunda dama bamu yi na shekara ba har yanzu. Nima hutun zan nema, saboda so nake idan naje in dan jima a can, wallahi garin ya fita a kaina gabadaya!"

Nadiya ta dan jinjina kai, "to shikenan, sai ayi hakan babu damuwa. Muma mun samu mu huta kafin ki dawo din. Dama na tara barci da gajiya sosai kwanakinnan."

Fita tayi suka cigaba da gudanar da ayyukansu kamar kullum. Bayan abubuwan sun lafa, suka fara shirye-shiryen rufe shagon da shawarwarin yadda hakan zai kasance. Sun saba yin hakan dama a duk karshen shekara, to kuma wannan shekarar data wuce ayyukan suka cunkushe musu basu yi hutun ba gashi har sun ci kwata. Nan da wata daya cikakke ma Azumi suke tunkara.

Saboda shirye-shiryen ranar bata koma gida da wuri ba sai wajen karfe tara na dare. Tayi sallama tana jan kafa saboda tsananin gajiya. Abbansu yana tsakar gida, matan sun zagayeshi zaune akan tabarma. Ko kwanukan abinci da aka kai mishi ba a kwashe ba. Ana ta hirar da bata da kai balle kafafu. Da alama ma su biyu kadai ke hirar, don shi hankalinshi yana kan wayarshi yana ta latsawa. A ranta tace 'har an gama fadan da fushin sake auren kenan?'

Ta durkusa a gefensu tana mishi sannu da gida, ya daga kai yana kallonta, "ke kuma fa daga ina da wannan daren? Wai ba na hanaku kai dare a waje ba?"

Tace, "wallahi ayyuka ne suka tsaremu a shagon saboda muna shirye-shiryen tafiya hutun shekara ne."

Yace, "to, to, na gane. Ai nayi zaton yawon banza kika tsaya. Ni dai kullum ina fada muku, a dinga kiyaye yin dare a waje. Saboda mutane basu cika ganin mutuncin mace mai yawace-yawace da kai dare a waje ba."

Ta gyada kai, "hakane Abba. In Allah Ya yarda zan kiyaye!"

Ta tashi ta tafi daki.

Ta tarar su Maryam har sun mata shimfida. Don haka tana gama shirin barci kwanciyarta tayi.

Ranar Litinin bata tashi da wuri ba, da tayi sallar Asubahi komawa tayi tayi kwanciyarta. Cikin ikon Allah kuma hayaniyar yara bata dameta ba don sai wajen karfe tara da rabi ta tashi. Maryam zata raka wajen registration din Jamb dalilin da yasa ta tashi da wuri kenan. Saboda daren jiya bata kwanta da wuri ba. Ta rasa dalilin da yasa yan kwanakin barci yake gagararta sosai musamman na dare.

Maryam ta shiga dakin dai-dai lokacin da take kokarin nade kayan shimfidar tata. Tace, "yauwa Adda, kin tashi? Dama ke kadai nake jira saboda tun dazu na gama shirina."

Ta gyada kai, "ok! Bani mintuna talatin, yanzunnan zan shirya. Abba yana gida ko ya fita?"

Tace, "yana nan. Naji yana cewa Lantana yau sai bayan Azzuhur ma zai fita saboda yana da meeting da ko wani Sanata ne ko me?!"

Nadiya ta tabe baki. Ta hade kan kayan ta mikasu daki kafin ta shiga wanka.

Cikin mintuna talatin din da tace kuwa ta gama shirinta tsaf. Riga da siket ta sanya na wani leshi ruwan madara, bata daura dankwali ba sai gashin kanta data kame a cikin band babba, ta dora bakar hijabi wadda ta tsaya mata a gwiwa. Kamar kullum ba wata kwalliya tayi ba ta a zo a gani, amma tayi wani irin kyau mai daukar hankali.

Suka fita tsakar gida inda ta samu Mama tana gyaran masara saboda ranar ita take da girki. Su Lantana kuwa da alama suna dakin Abba don bata ga giccinsu ba.

Suka mata sallama akan zasu tafi. Dubu biyu ta kunto a habar zaninta ta ba Nadiya wai su kara kudin mota, tace, "a'ah wallahi Mama, ki bar kudinki saboda da isassun kudi a hannuna. Ki ajiye kayanki kinyi wata hidimar dasu."

Mama tace, "to Allah Yayi albarka Nadiya, Allah Ya amfana!"

Tayi murmushi tace, "ameen ameen Mama! Mu ai addu'ar muke so!"

Sun samu Abba zaune akan kujera da takardar kilishi a gabanshi yana ta tauna, su kuma iyalan nashi suna gefe sun hade kawuna suna kus-kus. Salame sai kaiwa takardar naman hari take da idanu tana hadiyar yawu amma ya ki bata fuskar tagawa ma balle ta rokeshi.

Nadiya ta danne dariyar da take ciyota, da alama yau Abban cikin yan rowar yake.

Ta durkusa ta gaisheshi ya amsa mata sama-sama. Da yake itama ranar izgilanci take ji, sai ta juya gefen su Salame su ma ta gaishesu, sai dai daga jin gaisuwar bata kai ciki ba, suma haka suka amsa mata kadaran-kadahan babu yabo babu fallasa. Ko a kwalar rigarta ita kam.

Ta juya tana kallon Abban nasu, tace, "Abba zamu je ne wajen registration din jamb ta Maryam."

Jin haka sai yayi kicin-kicin da rai ya fara hura hanci kamar wanda aka aikawa da sakon mutuwa, "to! Sai kun dawo ko?"

Ta wani langwabar da kai gefe guda, "wai dama cewa nayi ka bamu kudin registration din ko? Dubu shida ne da dari uku, ga kuma kudin abin hawa..."

Kafin ma ta karasa ya katseta, "... ke dakata min don Allah da wannan lissafe-lissafen naki! Kudin kin bani ajiyarsu ne? Ko kuwa ni din asusunki ne da zaki dirar min da zancen kudi kai tsaye in dauka in bada! Ce miki aka yi sharo kudin nake yi a kasa ne ko kuwa shukasu nake yi?!"

Tace, "amma fa Abba tun wancan satin fa na fada maka haka kuma kai kace Allah Ya kaimu!"

Jin haka sai ta kara tunzurashi ma, ya fara sakar mata lissafin kudaden daya kashe a wannan satin wadanda rabinsu duk wajen amarya suka nufa, sai kuwa kudin fadar kishiya daya ba matan wanda dukansu dubu goma-goma ce ya basu.

Ita dai tayi kasa da kai tana bashi hakuri. Daga karshe dai ya tashi ya shiga daki, ya dawo ya jefa mata yan dubu-dubu guda uku suka zube akan

cinyarta, "gasu nan kuyi maneji da wannan. Idan kuma bai zasu isheku ba to ku bani kayana, tunda ba neman kai nake dasu ba!"

Ta tsincesu tas ta zuba a jaka tana mishi godiya. Ta yunkura zata tashi kuma sai ta koma ta zauna, ya daga kai yana kallonta warily don yasan maganar bata gama mutuwa ba.

Murmushi ta dan yi, tace, "Abba nace wai ka dan bani kilishin mana in kore mugun yawu!"

Tsabar rasa abinda zai ce mata da yayi a lokacin, takardar naman ya cukuikuye gabadaya ya mika mata, duk da cewa saura yajin kilishin kawai da dan guntun nama, haka ta amsa tana zabga mishi godiya, ta fita tana dariyar mugunta a ciki ita kadai.

Maryam ta girgiza kai tana kallonta, "wallahi wani lokacin ba ki da dama ko kadan Adda! Kin rabashi da nama kuma kin rabashi da yan canjinshi!"

Tayi dariya tace, "ke raba mugu da makami ibada fa! Idan ba ta haka ba ta yaya ma wai ake cin kudin Abba ne?!"

A haka kuma sai ta jinjina kai, "hakane kuma!"

Kai tsaye KASU suka wuce. Bayan an gama duk cike-ciken da za ayi, aka basu slip dinsu. Daga nan sai suka gangara unguwar Rimi gidan Yayansu Yaya Hannafi, mahaifiyarshi bata gidan kuma shima kusan sa'an su Anty Jamila ne.

Matarshi tana da kirki Anty Aisha, yana da rufin asirinshi dai-dai gwargwardo. Yana aikine da wani kamfanin kera robobi da reshensu yake nan Kadunar.

Anan suka yini a gidan. Da yake Nadiya ta iya jera lallen salatif, ta jerawa Anty Aisha shi kafa da hannu, Maryam kuma ta tayata tsifar kai. Da suka tashi tafiya ma da yamma ita ta hana tace dole su jira Magriba Nadiya ta sha ruwa tunda Azumi take yi, watakila kuma kafin nan Yayan nasu har ya dawo su samu su gaisa.

Don haka suka shiga kicin har ita suka hada abincin dare. Ta samu kunun tsamiya ta dama, don ya zame mata ka'ida, matukar tana Azumi dolene ta dama kunu ko ta hada shayi.

Suna cikin shan ruwan kuma sai ga Yaya Hannafi din ya dawo, yaransu uku, kuma dukansu sun tasa. Yanmata biyu suna boarding school sai karamin ne Ammar yake nan.

Ya tsaya suka gaisa suka mishi sannu da zuwa. Hira suka dan yi dashi sama-sama kafin ya tashi ya shige dakinshi. Dama can dai shi ba mai yawan jan yan'uwanshi a jiki bane, tunda zumuncinma da ba don jajircewar matarshi ba to da ba lallai ayi shi ba.

Da zasu tafi ya basu dubu biyu su yi kudin mota suka mishi godiya sosai kafin suka dauki hanya.

Suna gab da karasawa gida taji wayarta tana vibrating a jaka. Duk a tsammaninta Mama ce take nemansu shi yasa bata daga wayar ba.

Suna komawa gida kuma sallah suka yi, suka zauna cin abincin da Mama ta ajiye musu suna mata hirar Anty Aisha.

Sai da tayi shirin kwanciya can wajen karfe goma da rabi sannan ta tuna wayarta dake cikin jaka. Ta bude ta ciro wayar tana so ta hau whatsapp ta tabo Aramide taji ya ake ciki. Sai lokacin taga missed call din da aka bar mata.

Jikinta ne ya dauki wani irin sanyi ganin sunan mai kiran. Madam Zarah!

Mahaifiya ce, amma tafi jinta a matsayin wata dangi ta nesa, wadda babu sanayya da kusanci a tsakaninsu ko na azo a gani.

Kiran wayarta ba wai yana nufin tana so taji muryarta ko ta tanbayi ya take bane, tana da tabbacin ko dai wani abu ne ya taso a cikin dangi, ko kuma tana bukatar tayi mata wani abu ne. Tana da tabbacin hakan.

Canki-canka take yi, akan ta mayar mata da kiran ko kuwa. Laifine dai ta riga da tayi shi. Don kuwa idan akwai abin da Madam Zarah ta tsana, bai wuce ta kira wayar mutum ya ki dagawa ba.

A matsayinta na mace mai influence a cikin Kasarnan, gani take yi ba karamin nasara bane a gareka idan ta dauki wayarta ta kira ka ba, a ganinta ka ciri tuta sosai. Bata duba da cewa 'ya'ya da iyaye da yan'uwa bai kamata su shiga cikin wannan tsarin ba.

Ganin tunane-tunane ba inda zai kaita yasa ta mayar mata da kiran. Amma har ta katse ba a daga ba. Dama tayi tunanin haka.

Ta daga kafada ta gyara kwanciyarta abinta ta fara addu'ar barci.

Washegari kuma tunda safe sai ga kiran nata. Ta gyara zama akan abin sallar da take kai zaune ta daga baki dauke da sallama, kafin gaisuwa ta biyo baya, "Assalamu alaikum. Mommy barka da safiya, kun tashi lafiya?"

Daga can bangaren aka amsa mata a gaggauce, babu ya kike babu ya kwana biyu, kawai kai tsaye zuwa dalilin da yasa ta kirata.

Tace, "Nadiya kin tuna Hadiza yar wajen Kawu Kabir ko?"

Tace, "ehh, na tuna ta."

Duk kuwa da cewa ba tunata tayi din ba. Dangin Mamanta ba wani sani ta musu na azo a gani ba sai na kusa dasu sosai.

Tace, "satin wannan da zai kama za a fara bikinta a can Maiduguri. Don haka ki shirya kije sai mu hadu da ke a can. Zan turo miki Invitation card, at least kije a day before a fara events saboda a fara dake. Kin gane?"

Tace, "ehh... Amma Mommy....!"

"...Ba ki da kudin zuwa ne?" Ta katseta da wannan tambayar.

Tace, "a'ah, dama..."

Nan ma bata bari ta karasa maganar ba tace, "yauwa, to sai na turo miki da katin. Sofia tace a gaida ki!"

Ta katse wayar ba tare data bari Nadiya ta kara cewa wani abu ba. Tayi zaune da waya a hannunta tana kallo kamar wata sakara.

Shikenan duk wani tsari da tayi na hutun da zata yi an wargaza mata shi cikin dan kankanin lokaci.

Ita fa ba zuwa bikin bane yafi damunta, shiga cikin dangin Madam Zarah ne bata so. Ba a cikinsu ta tashi ba, shi yasa bata saba dasu ba. Akwai wadanda suke magana dasu suna gaisawa ta waya, amma suma yan'uwan Madam dinne na kurkusa wadanda yawanci daga 'ya'yan yayunta, sai ko na kannen mahaifanta dai. Amma sauran ba saninsu tayi ba, suma kuma basu santa ba.

Tana so ta sansu din, amma ta yaya? Da yawa wasu daga cikinsu kallon hadarin kaji suke mata idan taje wajensu, ta rasa dalili. Ko gani suke yi bara da roko zata je wajensu?

Dangin Mahaifiyarta mutanene da suka hada masu arziki da kuma masu rufin asiri. Suna zaunene a garin Maiduguri.

Mahaifiyarta rabi shuwa ce rabi bare-bari, iyayenta suna da rufin asirinsu dai-dai wa dai-da.

A cikin yan dakinsu akwai masu kudi sosai, su dai sune suka kasance masu rufin asiri. Watakila ko shine dalilin da yasa ma iyayenta suka yarda ta auri Babansu Nadiya din. Ko kuwa kaddara ce da tsananin rabo? Allah kadai Ya sani.

Tana da masaniyar a danginsu idan kaga wani ya auri bare wanda ba Kanuri ko Shuwa ba, to kudi yake dasu ba kanana ba. Saboda su sun fi yin auren gida ya-su ya-su kawai. Idan kuma sun fita to dukiya suka gani.

Shi yasa fa ita sam tsarin mutanen bai mata ba ko kadan. Shi yasa bata cika shige musu ba take baya-baya dasu.

Ta san dai cewa shi Alhaji Kabir mai aurar da diyar tashi, kawun mahaifiyarta ne. Dan wa da dan kani suke da kakarta, Dada Iyani, wadda itace Mahaifiyar Madam Zarah da sauran yayunta biyu, Hauwau da kuma Yasir. Wadanda dukansu suna zaunene a can Maiduguri din banda Madam Zarah, wadda take zaune a Jos.

Ajiyar numfashi ta ajiye mai nauyi, rufe wayar tayi tare da tashi ta nade abin sallar. Ta tashi taje ta gaishe da Abbansu, ta koma daki suka gaisa da Mama. Kafin ta fita tsakar gida ta fara shara.

Mama ta fito ita kuma ta shiga kicin ta fara kokarin hada abin kari.

Kosai suka yi shirin yi da koko. Da yake waken an gyara shi tun jiya, sai aka ba almajiri ya tafi markade.

Kafin ya dawo Nadiya ta gama hada kan tsakar gidan, Mama kuma har ta dama koko. Ta shiga kicin din ta zauna tana tayata suyar kosan suna hiransu kamar dai wasu manyan abokai.

Yaran gidan da suka fara fitowa don shirin tafiya makaranta, nan da nan suka kara wartsakewa. Murna kamar su yi me, don kuwa su ranar take sallah a wajensu.

Kowa idan ya zo zai amshi abin karinshi, sai Mama ta kulla mishi wani a cikin leda wanda zai tafi makaranta dashi. Abu ne da bai cika faruwa a gidan ba sai a dai-daikun ranaku wadanda suka zama na girkinta kawai. Don shi dai Abbansu baya bada kudin kashewa ko cin abinci a makaranta. Wanda Mahaifiyarshi taga zata iya sai ta bashi, amma ba dai shi ba. Su kuwa da mugunta ta cikawa ciki da shegen mako, babu mai iya wannan aikin. Shi yasa ma yaran duk basu cika mayar da hankali kan zuwa makarantar ba.

Lokaci zuwa lokaci dai Nadiya ta kan basu na kashewa a hanya, amma itama ba kullum ba.

Su Salame suka fito daga dakinsu suka je kofar dakin Abba suka coge suna ta harare-harare da yada maganganu. Nadiya dai kai kawai take girgizawa cikin tu'ajjibin wadannan mutane. Daga tashi tun da farar safiya kawai ku dinga neman mutane da fada? Ina dalili.

Da suka kai kwanukansu Mama ta zuba musu nasu, sai da suka kara kokarin tada rigima. Wai su ala dole ta zuba musu kadan, me zasu yi dashi?

Mama ta nuna musu nata itama wanda bai ma kai nasu ba, tace, "ni kunga ma wanda na tashi dashi. Idan kuma kuna ganin ba zaku amsa ba sai ku dawo dashi ai, dama nema muke yi."

Lantana taja wani dogon tsaki ta juya ta shige dakin Abba tana maganganu kasa-kasa, Salame ta bi bayanta itama.

Nadiya ta bisu da kallo kawai, kafin ta jinjina kai tana mai furta 'Allah kyauta!' a cikin ranta.

Bayan Aminatu ta tafi makaranta, ita da Maryam suka zauna suka yi wanke-wanke suka gyara madafin, sannan suka je suma suka karya.

***

Sai ana saura kwanaki biyu ta tafi sannan ta sanar da Abbansu game da tafiyar. Ya tabe baki yace mata, "Allah kiyaye hanya!" shikenan karshen zancen.

Dama bata sanyawa ranta zai bata kudin mota ba ko wani abu, tace, "ameen!" ta kakkabe zaninta ta tashi.

Cikin satin taji an ce amarya zata tare, ta san ba lallai ba tana gidan, sai dai ta dawo ta tarar da ita.

Akwati daya karami ta shirya kawai, saboda Madam tace an dinka mata ashoben biki don haka ba sai taje da komi ba. Abubuwan da zata bukata kawai ta dauka.

Ranar Assabar kuwa tayi asubanci ta dauki hanyar Maiduguri bayan tayi sallama da mutan gida.

Tafiya ce mai tsayi da yawa, don ba ita ta shiga garin Maiduguri ba sai da ana kiran sallar isha'i.

Ta tari abin hawa ya kaita har Unguwar Lamido inda nan ne Kakarta, Dada Iyani take zaune. Mijinta ya jima da rasuwa, 'ya'yanta su suka gina mata gidan da take zaune a yanzu bayan an sayar da wancan wanda suke zaune a ciki da.

Ta sauka daga kan abin hawan ta biyashi, kafin ta karasa jikin gate din gidan ta kwankwasa. Maigadi ya bude mata yana mai yi mata sannu da zuwa, ta amsa da kyar saboda gajiya, ta wuce zuwa cikin gidan.

A falo ta samesu su uku a zaune suna kallo, Dada Iyani din na zaune a kasan carpet suna kallo, sai Aisha diyar Anty Hauwau da Al-Ameen kaninta suna tayata hira.

Tayi sallama ta shiga, su duka suka daga kai suna kallonta. Dada Iyani ta fara tafa hannu tana mata oyoyo, sai taji murna ta lullubeta da kewar wadanda ta jima bata sanya a cikin idanunta ba.

Ta ajiye akwatin ta tafi da sauri ta fada jikinta cike da murna. Itama rungumeta tayi tana "oyoyo ga mutan Kaduna. Ku ne da wannan daren?!"

Sai da suka gama murnar sannan ta koma ta zauna sosai akan carpet. Aisha da Al-Ameen suka gaidata ta amsa tana tambayarsu Mamansu.

Aisha zata iya yin sa'ar Maryam dinsu, don ba zata wuce shekaru sha takwas zuwa sha tara ba, shi kuma Al-Ameen ba zai wuce shekaru bakwai ba. A tsakaninsu akwai Tameem Yayan Al-Ameen da kuma Muhajjatu kanwar Al-

Ameen, shekarunta biyu. Kasancewar Anty Hauwa din bata samu haihuwa da wuri ba.

Nadiya sun saba da Anty Hauwa sosai, don zata iya cewa sun ma fi sabawa da ita akan Madam Zarah. Lokaci zuwa lokaci su kan tuntubi juna su gaisa da tambayar juna ya suke, ba kamar Madam Zarah ba da idan ta kiraka to lallai akwai abinda take bukata a wajenka. Haka kuma da yake Anty Hauwa din tana aiki da WHO ne, su kan ziyarci garuruwa daban-daban, kuma tana yawan zuwa Kaduna. Duk lokacin da zata shiga Kaduna to sai ta lalubi Nadiya sun gaisa. Madam Zarah kuwa idan ba kai kaje inda take ba, to ba zata nemeka ba.

Dakin da zata sauka Aisha ta rakata, nan kusa da na Dada Iyani yake. Dakin yana da fadi, ga katifa babba da aka yada an shimfida mata sabon zanin gado. Ta ajiye akwatunta a gefen Katifar kafin ta fada bandaki ta watsa ruwa. Jikinta a matukar gajiye yake, ko'ina na sassan jikinta ciwo yake yi mata.

Bayan ta fito sallar da aka biyota tayi, kafin ta tashi ta nade abin sallar.

Zanine a jikinta wanda ta dora akan doguwar rigar barcin jikinta. Ta koma falo inda ta samu har Dada ta tafi ta kwanta sai Aisha da take kallo, Al-Ameen kuma yana barci.

Aisha ta daga kai tana kallonta, "yauwa, Adda, jiran fitowarki nake yi dama. Me za a kawo miki ki ci ne?"

Ta zauna yaraf a kan kujera tana mike kafafuwanta, tace, "gaskiya babu abinda zan iya ci yanzu saboda barci nake ji kwarai da gaske. Amma bari in shiga in hada shayi haka sai in sha kafin in kwanta."

Tace, "to bari in hada miki. Zauna huta naga alamun kin gaji sosai."

Cikin mintuna biyar kuwa ta hada mata shayin mai kauri, ta kai mata da burger wadda da alama daga oven ta fitar da ita saboda taji da dumi.

Ta ajiye kayan a gabanta tana dan murmushi, tace, "Madam ce ta kawo mana ita dazu. Kin san Dada ba cin irin wadannan abubuwan take yi ba shine aka ce bari a ajiye miki."

Ta dauka tana ci tana karewa hanyoyin da dakunan gidan suke kallo, tace, "ban ma ganta ba tunda nazo. Ko har ta kwanta ne?"

Aisha tace "wai Madam? Ai tunda yamma ta tafi gidan da take sauka."

Sai ta kame bakinta tayi shiru. Sam ta manta fa tunda dadewa take jin an ce Madam din gida ta gina na musamman wanda take sauka a cikinshi idan taje Maidugurin, saboda a cewarta wai can yafi tsaro.

Suna hira sama-sama har ta cinye burger din. Ta kai kayan kicin, ta dauki gorar ruwa ta yiwa Aisha din sai da safe wadda take ta kokarin tashin Al-Ameen ya wuce dakin da samarin gidan ke taruwa ya kwanta, ita kuma ta wuce wajen Dada tunda a can take kwana.

Tana shiga dakin baki kawai ta wanke ta yiwa kan katifa tsinke. Sama-sama suka gaisa da su Mama kafin ta kashe wayar gabadaya saboda mayen barcin dake janta kamar magnet.

Ranar sallar Asubahi ma sai da aka buga mata kofar daki. Ta tashi tana mika, har lokacin gajiyar bata barta ba. Sai lokacin taga alamun ta makara ashe don kuwa tuni gari ya fara haske.

Ta tashi da sauri ta dauro alwala ta yi sallah.

Bata koma barci ba, ta fita taje suka gaisa da Dada kafin suka shiga kicin ita da Aisha suna hada abin kari.

Suna aiki suna hira tana bata labarin bikin da za a fara a washegari. Wanda yarinyar zata aura dan gidan Sarkin Potiskum ne, shi yasa ake ta zuzuta bikin ba ji ba gani, ga kuma iyayen amaryar da suka kasance suma ba kananun masu kudi bane.

Iyalan Alhaji Idris Nalado, iyalai ne da suka yi kaurin suna a cikin garin Maiduguri. Ko ba daga bangaren arzikin da Allah Ya wadatasu dashi ba, kasancewarsu zuriya masu kyau kadai ya isa ya sanyasu a cikin jerin lissafi. Yawancinsu Kanuri ne gaba da baya, sai kuwa kalilan da suka kasance hadi da shuwa da kuma bafulatanai.

Shi Alhaji Nalado daya kasance shine Kakan Madam Zarah, mutum ne mai rufin asirinshi dai-dai gwargwado. Kaninshi kuma Alhaji Kachalla wanda suka hada uba daya dashi, shine mai arzikin. Sai dai sun taso kansu a hadene duk da kasancewarsu iyayensu mata daban. Kuma kasancewarsu manya a gidan, sun yi iyaka bakin kokarinsu wajen ganin cewa sun hada kawunan sauran kannansu da kuma 'ya'yansu waje guda.

Sai dai duk hakan ya zamana a kawai ne bayan da suka rasu. 'Ya'ya kowa ya kama harkar gabanshi. Hakan yasa suka tashi kai a ware, wani ma sai ya girma ya tashi da wani amma bai san dan uwanshi bane.

Mahaifin Madam Zarah Alhaji Lamin, shine babban da ga Alhaji Nalado, yana da kanne mata biyu da namiji daya. Mahaifiyarshi asalin shuwa ce, kuma da mafi akasari 'ya'yansu ita suka biyo, sai suke tashi tamkar wasu diyan larabawa saboda haske da kuma kyau. Duk cikin 'ya'yanta kuma babu wanda ya dauko kyawunta kamar Lamin din, wasu su kan ce idan ka ganinshi sai kayi zaton ko dan aljanine saboda tsabar kyau.

Bayan rasuwar Alhaji Nalado, rayuwar iyalanshi ta so shiga rikici saboda halin babu da rashi da suka shiga. Da ba don Alhaji Kachalla ba kam da basu san irin halin da zasu shiga ba.

Shi yayi ruwa yayi tsaki wajen kulawa da 'ya'yan marigayin, ya dauki Lamin ya mayar dashi cikin gidanshi da zama inda matarshi, Uwale, wadda ta kasance haifaffiyar garin Kaduna ta rike shi hannu bibiyu. Basu taba samun haihuwa da Alhaji Kachalla ba, kusan sau hudu tana samun cikin tana b'ari, ta haifi wani sau daya shima ko satin haihuwa bai cika ba ya koma.

Lamin ya cigaba da zama a hannun Alhaji Kachalla inda ya sanyashi a makaranta, a gefe guda kuma yana cigaba da daukar dawainiyar mahaifiyarshi da sauran kannenshi.

Cikin ikon Allah kwatsam sai Uwale ta samu ciki, tun suna taraddadin zubewarshi har dai suka saduda, da lokacin haihuwa yazo ta haifi diyarta mace sankaceciya aka sa mata suna Ummulkhairi. Lokacin kuwa Lamin ya haura shekaru sha biyar a duniya.

Tafi-tafiya rayuwa na ta juyawa, Lamin ya girma ya zama magidanci. Idan ba sani kayi ba, baka taba cewa ba Alhaji Kachalla bane ya haifeshi. Bayan Ummulkhairi Uwale ta sake haihuwar wata diyar taci sunan Sumayya.

Duk wasu harkokin Alhaji Kachalla suna hannun Lamin, shi yake kulawa dasu, kai sai da ta kai ta kawo ma gabadaya duk wasu shaguna nashi da kadarori Lamin dinne yake kulawa dasu, shi ya zamana kawai dai yana zuwa ya dan kewayasu ne ya dawo.

A haka cuta ta farat daya ta kamashi. Aka shiga zarya asibitoci da wajen Malaman gargajiya. Bayan doguwar jinya dai daya sha, daga karshe dai yace ga garinku nan.

Fadar irin tashin hankalin da iyalinshi suka shiga a wannan lokaci ma bata baki ne, sun yi kuka ba na wasa ba.

Aka yi zaman makoki aka gama, dangi da 'yan'uwa suka watse. Aka zauna aka zubawa Lamin idon ya tattara dukiyar mamaci ya ba magada amma shiru kake ji kamar an shuka dusa. Da aka ji shiru sai Uwale ta tunkareshi da kanta ita da yayanta da yaje daga Kaduna lokacin.

Ya rufe ido rikif ya hau fadan shi wata dukiya ke a hannunshi bayan wadda aka cinye a zaman jinyar Alhajin? Idan lissafi suke so ayi to su jira yayi lissafin, amma su kuka da kansu duk abinda zai biyo baya su suka ja saboda

yana da tabbacin idan har yayi wannan lissafin to ko gidan da suke zaune a ciki ba zasu tsira dashi ba.

Aka kada aka raya, amma mutumin nan yace shi fa babu ko asin kwabo a hannunshi. Mahaifiyarshi kuma ta mara mishi baya.

Wannan dalili dai shi ya kawo lalacewar zumuncin wannan ahali. Dama tsakanin Uwale da Salma ba wani zumuncine na azo a gani ba, suna yi ne don ganin idon mazajensu ba wani dalili ba.

Daga baya dai zance har sai daya kaisu ga shiga kotu. Sai a kotun ne da yaji matsi ya dauki takardun filaye biyu ya bada a cewarshi abinda ya rage kenan. Shaguna kuwa duk babu kaya a ciki kuma ya sayar dasu, wai ai lokacin da Alhajin yana jiyya da su aka dinga amfani.

Da haka dai zance ya kare saboda babu wasu takamaimun shaidu da zasu karyata zancenshi. Saboda ko da Alhaji Kachalla din yana raye shi dai bai cika fadin iyaka adadin dukiyarshi ba da abubuwan daya mallaka. Shi Lamin din shi ya san komi. Ya kuma zambacesu da hakan.

Babu jimawa da yin hakan ya kyankyatsa ginin gidanshi mai kyau kamar a gidan sarauta, ya je cikin dangin mahaifiyarshi ya samu budurwa lafiyayya aka daura musu aure ta tare.

Shekara kwana ga mai yawan rai, abubuwa da dama kuma sun faru cikin dan kankanin lokaci. Mahaifiyarshi ta rasu jim kadan bayan da Iyani ta haifi Yasir. Tsakaninshi da Hauwau shekaru biyu ne. Bayan wasu yan shekarun kuma ta sake haihuwar Fatima Zahra.

Arziki kullum yana ta tumbatsar mishi, dukiya da duniya sun zauna mishi sosai yan ta facaka yadda yake so. Sam ya manta da marayun Allah da ya ci amanarsu ya tauye musu hakkinsu. Bai ma san a wani hali suke ciki ba tunda ba bibiyarsu yake yi ba. Danginsu ma kuwa kowa ta kanshi kawai yake yi, daga yan karkashinshi yan abi yarima a sha kida wadanda dukiyarshi suke wa, sai masu jin tsoron su tankareshi da maganar saboda kada ya daina

hidimta musu, sai kuwa yan babu ruwana wadanda suma suna da nasu arzikin.

Rana guda kawai suka tashi da mutuwar Uwale, ashe rashin lafiya tayi da jinya sosai bai ma sani ba.

Yaji ana cewa dai taso ta koma can Kaduna da yaran, amma wasu daga cikin dattawan yan'uwansu suka hanata saboda sun san cewa idan ta tafi to bata da dalilin dawowa, zumunci da yaranta kuma zai yanke.

Amma su da suka hanata tafiyar kuma sun kasa tsaye mata. Dan sauran abinda ya rage na kadararta duk an siyar wajen jinyarta.

Ya kai kayan abinci ya zube musu, aka yi zaman makoki aka gama. Danginta da suka je suka hade kayanta waje guda tsaf, ba tare da sunyi shawara da kowa ba, ana yin addu'ar bakwai suka hade kan ya'yanta suka tafi. Sai zuwa aka yi aka samu gida kwalam. Daga baya ma ake jin cewa ashe an sayar da gidan shima.

Daga wannan tafiya da Ummulkhairi tayi da kanwarta bata kara bibiyar danginta ba.

Alhaji Lamin tuni shima ya shafe babinsu a rayuwarshi. Ya cigaba da fantamawa da facakarshi yadda yake so.

Daga baya ma sai ya yanke shawarar zai tsunduma harkar siyasa ne tsundum. Ya kuma fita din da karfinshi, nan da nan sai gashi yayi suna a ciki da wajen Maiduguri.

A kuma daidai wannan lokaci ne da yake ganin cewa tauraruwarshi ta gama yin hasken da babu abinda zai iya dusasar da ita, ta dauke wuta gabadaya.

Shagunanshi suka fara kamawa da wuta, kafin a samu a kashe wutar sai komi a cinye sai dai a tadda toka. Sai kwantainoni da suka dauko mishi kaya suka fara nutsewa a ruwa, masu kuma a kama.

Ya fara daga kadarori yana sayarwa, yana bin kan yan siyasa da manyan yan sanda da customs kan a sakar mishi kayan da aka kama, gefe guda kuma yana cigaba da kamfen dinshi.

Kafin shekara ta zagayo ya tashi a huhun-ma'ahu. Shi ba ga kudi da kadara ba, shi ba ga siyasa ba.

Tuni magoya bayanshi suka juya mishi baya da suka ga shima nema yake yi a wajensu, wadanda suka tsaya kalilan ne, suma don su karasa cinye yan canji daya rage mishi ne. Sune masu zuga shi da kara dorashi kan turbar bin malamai, suna kara gaya mishi lallai fa idan zabe ya zo to lallai zai cinye. Shi dai kawai ya saki kudi ya bada ana mishi sadaka da sauka, anan sauran yan kudaden nashi suka lume.

Kafin ya ankare zabe ya zo, kungiyar adawarsu ta ci. Ai hauka ne kawai bai yi ba a lokacin.

Sai gashi shine ya koma yana bin yan siyasa yana musu kanzagi da roko. Rayuwa dai ta juya mishi baya shi da iyalanshi, kamar ba a taba yi ba.

Su Fatima da suka taso cikin gata da jindadi da facaka, lokaci daya rayuwa tayi musu juyin bazata. Ta dilmiya su cikin garari da fadi-tashi.

Tana kan ganiyar yanmatancinta. Rayuwar dadi ta tashi a ciki, kuma ita ta sani, jinta cikin babu da rashi bakon abu ne a wajenta, wanda kuma ba zata iya dauka ba. Ta kasa hakurarwa kanta kamar yadda sauran 'yan'uwanta da iyayenta suka yi.

Ta daukarwa ranta alwashin, komai tsanani da wuya, sai ta sake taka matakin daula, sai ma gabanta ta fi bayanta kyau.

A gefe guda, a can Kaduna kuma. Mace daya ta sha alwashi kamar na Fatima, sai dai ita tayi ne domin ta rama wulakancin da aka yi mata. Ta ci alwashin tara kudi da mulki da duniya domin ta saka sharri da sharri. Ta ci alwashin jefa rayuwar Alhaji Lamin cikin garari irin wanda bai taba shiga ba,

shi da iyalanshi, har ma da tattaba-kunnenshi, babu wanda zata bari! Wannan kenan.

8

WACECE NADIYA?

Alhaji Auwal Iko wanda aka fi sani da 'Dan Iko', irin yan kanzagin yan siyasar nan ne da sarakuna wanda hakan ya samu asaline tun yana dan kankaninshi daya taba aikatau a gidan wani Sanata.

Iyayenshi talakawa ne tilis, haifaffun cikin garin Kaduna ne. Mahaifinshi ya rasu tun yana dan kankani, mahaifiyarshi ita ta raineshi har zuwa lokacin daya girma.

Bai yi karatun boko ba, na almajiranci ma da aka kaishi ki yayi ya gudo. Yarone mai matukar rashin ji da ra'ayin rikau, don dole mahaifiyarshi ta gaji da kaishi almajircin ta kai idanu ta zuba mishi. Da dan jarin da take ja na koko da kosai ta kaishi makarantar Arabi da boko, su dinma yaje yau ne gobe yaki zuwa.

Lokacin daya fara zama matashi ya samu aikin wanki da guga a gidan wani Sanata, yana kuma yi musu yan share-share da gyaran gida. Tafi-tafiya ya zamana ya fara yin suna a gidan saboda shi mutum ne mai shiga jama'a sosai kuma baya da shayin shiga ko'ina. A haka mai gidan ya fara sanyashi kananun ayyukan gida, a hankali sai gashi har ya zama direbanshi. Daga nan kuma ya zama na hannun damarshi wanda yake sanyawa yayi mishi yan ayyukansu na yan siyasa. Yau shine wajen wannan Malamin karbar taimako, gobe shine wajen wancan, jibi shine wajen wannan basaraken neman gindin zama da fadanci. Nan da nan sai yayi wani irin kaurin suna, kafin kuma kace me sai gashi ya fara tara yan canji.

A cikin wannan yanayi ya taso. Har zuwa lokacin da likkafa ta ci gaba lokacin da yayi sabon Ubangida wanda ya zama Gwamna.

Shi ya damka mishi filin gidan da yake ciki saboda yabawa da tsayawa da yayi ka'in da na'in ya goya mishi baya. Ya kuma bi shi da kudade masu kauri yace yayi gini dasu. Da yake kuma aure yake so, sai bai yi sanya ba ya tayar da gininshi.

Zance na gaskiya Auwalu akwai tsilla-tsilla, don kuwa babban dalilin da yasa yafi yin kaurin suna wajen abokan huldarshi shine yadda babu ruwanshi da bambance tsakanin aiki mai kyau ko marar kyau, in dai zai samu kudi, to shi fa babu abinda ba zai iya yi ba. Har mata yake dauka ya kaiwa mutanen nashi su biya shi. Harka irin wannan kuwa tafe take da rufewar ido da zuciya, kafin kace me kuwa, ya fada harkar bin mata ruwa tsundum. Mutum ne marar mafadi, babu wanda ya isa ya sanyashi abinda bai yi niyya ba sai dai mahaifiyarshi da a lokuta da dama ita ce take da wannan fadar. To itama ba kullum ba, harkar bin mata dai babu irin fada da nasiha da bata yi mishi ba, daga baya dai sai data dawo ta dinga binshi da addu'a kawai.

Cikin yawace-yawacen da suke yi ne Allah Ya kaisu wani kauyen Wuro-Yanka a can cikin Yola. Mazauna garin Fulanine usul, sai dai mafi yawancinsu fulanin yawo ne, watau wadanda basu da takamaiman gari ko wajen zama. Idan sun je waje ya musu, zasu zauna na iya adadin wasu kwanaki ko shekaru, daga nan kuma su kara gaba.

Anan Allah Ya hadashi da Juwairah. Bafulatana ce danya shataf, idan ka ganta kyawunta kamar wata diyar Aljanu. Allah Ya sanya musu kaunar juna kamar me, sai dai iyayenta suka ce ba zata auri bare ba. Babu ta inda bai bi musu ba amma suka ki, daga karshe dai ya zugeta suka je Dagacin garin ya daura musu aure da yaga iyayen kudin da Auwalu ya zube mishi. Iyayenta na jin haka suka ce aikuwa haihata-haihata ita dasu, sun yafeta har abada.

Nan fa idanunta suka raina fata, don kuwa cikin dadin bakin da yayi mata har da cewa in dai aka dauro musu auren to kuwa dole ma iyayenta su amince, sai kuma akasin hakan ya faru.

Ya kara kalallameta da wani dadin bakin, yace mata ai fushi suka yi da ita, amma zasu sauko. Don haka ta basu dan lokaci, daga baya zasu hakura.

Giyar kauna da dadin bakin Auwalu, da yake gwanine ta wannan bangaren, ta kwasheta, ta biye mishi ta bi bayanshi kamar yadda yace zuwa gidanshi daya gina a Kaduna.

Mahaifiyarshi Inna Deluwa sai ganinshi tayi da bafulatanar mata sama-ta-ka.

Da yake tana zaunene a nata gidan na daban, dan tsamurmurin wajene da marigayi maigidanta ya bar mata gado ita da Auwalun.

A gidan nata ya sauka da amaryarshi, wadda ta kasa ko motsin kirki saboda tsabar kunya data lullubeta.

Daya gama mata bayanin abinda ya faru, idanu kawai ta zuba mishi ta kasa cewa komi. Ji tayi kamar ta kama shi tayi ta hada kanshi da bango ko Allah Yasa ta huce takaicin maganar da Auwal yake daukar mata.

Ta kara kallon budurwar, yarinya ce danya shataf, bata tunanin zata haura shekaru sha biyar. To shima ba wani girma yayi ba, duka-dukanshi a lokacin ba zai haura ashirin da biyar ba, rigima ce kawai irin tashi.

Taga dai idan tace ma fada zata mishi bata baki ne, don kuwa abinda ya faru ya riga ya auku dai, sai dai fatan Allah tsare gaba. Watakila kuma hakan zai iya zame mishi sanadin shiryuwarshi da daina bibiyar matan da yake yi. Ga amaryar tashi da take a takure, tana tsoron tayi mishi fadan a gabanta taga kamar kila bata yi na'am da ita ba.

Don haka ta rufe zancen fada. Ta gyara mata mazauni tare da tashi nan-da-nan ta tayar da sanwa ta dafa musu abinci.

Zuwa bayan isha'i sun gama hutawa, sun ci sun koshi. Ya tashi tafiya bayan ya dawo sallah, ya nemi amaryarshi da taje su tafi gida. Inna Deluwa tayi kicin-kicin da rai tana kallonshi, tace, "wane gidan?"

Fir! Ta ki ya tafi da ita ko'ina tace har sai yayi mata garar kayan dakI sannan. Rai cune ba don yaso ba haka ya tafi.

Shi yasa har a yau da take ba a raye ba, Mama bata taba ganin suruka irin Inna Deluwa ba. Don kuwa ta mata halaccin da ba a taba yi mata ba. Ita ta tsaya tsayin daka sai da Auwalu ya mata jeren daki tsaf kafin ta tare, ita kuma tayi mata gara irin wadda uwa take yi. Duk kuma wanda ya tambayi dangin Juwairah zata ce diyar 'yan'uwanta ce dake Adamawa. Da haka sai ya zamana 'yan'uwanta sune suka dawo 'yan'uwan Juwairah din.

Ita dinma kuma da yake bata da hayaniya da kwaramniya, gata mace mai kawaici da hakuri, sai tasu ta kusan zuwa daya da mutane.

Ko lokacin data haihu ta haifi danta namiji AbdulHadi, haka Inna Deluwa ta sake daukarta ta maidata gidanta wanka. Ta kuma yi mata duk wata al'ada da uwa take yiwa yar ta idan ta haihu. Lokacin shekarunsu biyu da yan watanni da aure.

A kuma wannan zaman jegon ne komi ya sauya a zamanta da Auwal. Gabadaya sai ya bi ya canza mata, wulakanci iri-iri babu wanda baya yi mata ita da danta, ashe wata yar kyakkyawar budurwa ce ya kyalla ido ya hango.

Tana komawa gidanshi ko wata biyar cikakke bata yi ba, ya dankaro mata amarya ya kai.

Sai a wadannan lokutan ne Auwalu yake bambance mata tsakanin aya da tsakuwa, don kuwa yadda ya rufe ido ya dinga nuna kamar ita da babu duk daya a wajenshi abin babu kyan gani.

Inna Deluwa tayi fadan, tayi nasihar, tayi ban bakin, akan ya tuna yadda yaje ya rabota da danginta ya kawota cikin nashi dangin da bata sani ba, kuma duk ta dalilinshi. Daya daga baki sai yace ai ita tayi radin kanta ba tursasata yayi ba. Wannan maganar ta matukar bakantawa Juwairah rai, tayi mata zafi sosai.

Amaryar tashi ko wata shida bata yi ba suka rabu. Kuma kafin a rufa watanni biyu ya sake yin wani auren. Nan da nan sai ya zamana wani idon mata.

Mace duk inda ya kyalla idanu ya ganta to shi dai kawai ya aureta. Wanda abin takaicin daya samu abinda yake so a wajenta sai kuma wulakanci ya fara biyowa baya wanda kafin kace me sai a zo a rabu.

Ana cikin wannan yanayin sai ga amaryarshi ta biyu ta kai mishi dan jinjirin data haifa a gidansu wanda shima ba karamin rikici aka ci da Auwalun ba kafin ya kai ga sayen abin yanka. Abinda aka kayyade mishi kuma na maijegon da jinjirin ba kaiwa yake yi ba, don haka tana yayeshi ta kai mishi kayanshi.

Ana kaiwa kuma ya ba Juwairah shi yace ta hada da nata ta kula dashi, nan ne ita kuma tace ba zata yi ba. Ba zata kula da dan da bata haifa ba. Da wanda ta haifa ma ya ta kare?

Anan kuwa suka yi tashin hankalin da basu taba yi ba har ya kai ga mata gorin dangi, daga baya ma yace ta tafi wajensu duk da bai furta mata saki ba.

Bata yi shawara da kowa ba ta tattara yan kudadenta ta dauki danta, asubahin farko ta bar garin.

Sai dai abin ban tsoron shine da taje Adamawa bata samu yan'uwanta ba. A can ake ce mata ai sun fi shekara da barin garin kuma babu wanda yasan inda suka tafi kuma babu wanda ya bar mata sakon inda zata samesu koda taje nemansu daga baya.

Nan fa ake yinta. Idanunta suka raina fata data fahimci cewa bata da wata madafa ko mafita. Gidan Dagacin garin ta zauna na yan kwanaki tana tunanin mafita da tunanin abinda yakamata tayi a daidai wannan lokaci.

A kwanakinta na uku da zuwa garin ne Dagacin ya nemeta da zancen ya kamata fa tasan inda dare yayi mata, saboda shima dawainiyar dake kanshi da iyalinshi ta mishi yawa, gata kuma da danta yana kulawa dasu suma.

Ta kasa ce mishi komi sai idanu data dinga binshi dasu cikin tsananin mamaki da tu'ajjibin yadda dan'adam kan iya canza hali daga mumini zuwa dan iska. Kodayake, a wancan lokacin ai kudi ya gani, a wannan karon kuwa da ita ce take ci mishi kudin dole yayi mata wannan dibar albarka.

Ta iya daga baki da kyar ta ce mishi to ta gode da dawainiyar da yayi da ita. Ta kuma kara da cewa kuma Allah Yayi mata sakayyar abinda suka aikata mata. Idan har sun shiga hakkinta, to bata yafe ba.

Ta tashi daga gabanshi ta barshi yana mata ihun shi bai ga alkaba'in daya aikata mata ba tunda dai ai da kanta ta amince a daura mata auren da wanda iyayenta basu yarda ba, ba wani ya tursasata ba. Ta kwashi yan komatsanta tayi sallama da matanshi ta tunkari tashar mota.

Rasa inda zata nufa tayi, a iyaka tunani da tayi, ba zata iya cewa ga asalin iyayenta ba. Daga ina suke, ina suke nufa, ba zata iya fada ba.

Dai-daikun garuruwa kadai zata iya tunawa inda suka zauna, saboda duk inda suka je ba wani zama suke yi na azo a gani ba. Wuro yanka yana daya daga cikin garin da suka jima a cikinshi. Tasan ko tace zata shiga duniya neman danginta yana dai-dai da cewa tayi damarar neman jaki mai kaho, wanda yake abu mai kamar da wuya gurguwa da auren nesa. To amma ina zata nufa kenan?

Ta biya kudin motar Kano ta shiga. Aka yi ta tafiya kamar ba za a kare ba, sai can talatainin dare sannan suka isa.

Ta tsaya a cikin tashar tana kalle-kalle don kuwa ba tasan ina zata nufa ba daga nan.

Ga AbdulHadi yana ta tsala mata kuka, gajiya da yunwa su duka sun lullubesu.

Yan canjin daya rage mata ba wasu masu kauri bane. Ta matsa wajen wata mata dake sayar da abinci. Da alama ma ranar abincin kwantai ya mata don kuwa tashar ba wasu mutane bane da yawa. Ta bada aka sanya mata dafadukan shinkafa, ta kara da kunun gyada ta matsa gefe ta zauna tana ci

hannu baka hannu kwarya, don kuwa tun karin safe da tayi babu abinda ya kara shiga cikinta, tana yi tana mikawa AbdulHadi shima yana ci.

Da suka gama ta lallabashi yayi barci, ta samu waje tayi alwala sannan ta shiga biyan bashin sallolinta.

Data kula da wannan mata mai abinci dai rumfa take da ita a kusa da tashar, kuma anan take kwana, sai ta matsa ta sameta da hawayenta a ido ta roki data taimaka mata ta kwana a wajenta. Ta mata karyar ai ganin gida taje, kuma sai ta yanke shawarar ta koma gida kafin adadin data dauka ya cika, kuma abin bata taba zuwa ko'ina ita kadai ba tare da maigidanta ba, shine dare yayi mata kuma tana tsoron yin tafiyar dare ko kuma kwanan tasha ita kadai.

Matar ta tausaya mata kwarai, don haka ta mata. alfarmar ta kwana din.

Kafin safiyar ta gama yankewa kanta shawarar daukar hakuri ta koma gidan Auwal tunda bata da wani zabi wanda yafi wannan.

Gari yana wayewa kuwa ta yiwa matar nan sallama da godiya, ta shiga mota suka dumfari Kaduna.

Inna Deluwa sai ganinta tayi da tsakiyar rana kamar wadda aka jefo. Tayi salati ta sanar da Ubangiji. Ta kamata ta rungume cikin murna. Daga ita har Auwalun sun shiga cikin tashin hankali da damuwa kwarai da gaske. Don kuwa duk iskancin da yake yi, yana sonta kawai giyar mata da kudice take kwasarshi tana sa wa yana mata wulakanci.

Tafiyarta kuma ita ta kara tabbatar mishi da hakan. Shi yasa hankalinshi ya dagu yayi sama, gashi lokacin waya bata zagaya ko'ina ba, to ko da wayar ma wa suka sani da zasu tuntuba? Shi yasa suka mayar da hankali wajen addu'a kawai.

Kafin a sanar dashi dawowar tata yaje har sunyi wanka, Inna Deluwa ta hada miyar kuka da tuwon dawa da Juwairah din ta sameta tana tukawa ta kai mata ta ci tayi nak, sun kwanta ita da Abdul din sun hau barcin gajiya.

Sai gashi ragajab-ragajab kamar wani amale yana ta baza uwar babbar riga ko daga ina yake? Ganin suna barci sai yayi turus daga bakin kofa yana zabga fara'a yana tambayar Inna Deluwa da yaushe suka dawo? Ta amsa mishi ciki-ciki don kuwa har lokacin cikin fushi dashi take.

Zuwa dare ta sake hadasu ta musu sasanci da kara tausar Juwairah din. Ta amince da cewa zata riki da, amma fa ya daina mata gorin dangi. Ya amsa da saurinshi yace ya daina.

Da haka dai suka tattara suka koma gidansu, ta rike Hannafi da AbdulHadi ta rika kamar dukansu ita ta haifesu. Shima kuma Auwalun yayi mugun sanyi ya shiga taitayinshi, sai tattalinta yake yi.

Cikin lokaci kankani sai gata da wani cikin. Ya kuma nuna matukar farincikinshi da jin haka.

Ashe ba tare da sanin kowa ba, ya hadu da Barira, mahaifiyarsu Jamila. Lokacin itace ma Vice Principal a FGGC Munjibir, kuma haifaffiyar garin Kano ce a unguwar Galadanchi.

Ya je raka wani Ubangidanshi ganin diyarshi da take karatu a makarantar suka hadu da ita, jininsu ya hadu da ita. Kuma cikin dan kankanin lokaci zancen aure ya shiga tsakaninsu. Ya gundura mata karyar ai bashi da aure sun rabu da matarshi.

Aka yi aure ta tare abinta kasancewar kuma zawara ce, ta taba aure amma bata taba haihuwa ba sai abin yaje musu da rashin hayaniya.

Shikenan duk karshen sati yana tafe kan hanyar Kano, ya cewa Juwairah din ai wani aiki ne na musamman yake kaishi gidan Gwamnatin Kano, ita kuma ta hau kai ta zauna daram.

Kusan a tattare suka haihu su biyun, ita Juwairah ta haifi 'ya mace, Barira kuma ta haifi danta namiji.

9.

Diyar da Juwairah ta haifa bata dade ba ta koma sakamakon matsananciyar rashin lafiyar data yi. Suka yi jimami na dan lokaci suka hakura suka maidawa Allah lamarinshi.

Rayuwa ta cigaba da tafiya a haka. Auwalu kuma ya cigaba da aure-aurenshi. Juwairah tun tana jin haushi da tashin hankalinta har ta gaji ta hakurewa kanta. Tunda abin dadin matan basu cika zama ba. Abin takaicin shine da yawancinsu suke maida mishi 'ya'yanshi da zarar sun rabu. Don ma tun bayan Saminu bai kara kai mata da ba sai dai wajen Inna Deluwa yake kaiwa. Don kuwa a lokacin daya zaunar da ita yake bata labarin yana da wata matar a Kano har suna da 'ya'ya biyu da ita, akwai wasu yaran biyu a hannun Inna din. Itama kuma da wata diyar wadda ta sake haifa tana shayarwa.

Cikin ikon Allah kuma sai taji kwata-kwata hankalinta bai tashi ba sam. Ta tabe mishi baki tace to 'Allah raya!'

Ta tashi ta bar mishi wajen. Shi kanshi sai da yayi mamakin hakan.

A cikin wannan kwaramniya kwatsam sai Allah Ya hadashi da Fatima Zahra. Sun je can Maidugurin lokacin ana ruguntsumin siyasa kuwa.

Tun bayan da karayar arziki ta samu Lamin, gabadaya komi ya cukurkude ya rikice, abubuwa duk sun tsaya musu cak.

Lokacin Hauwau tayi aurenta, Allah Ya hadata da wani mutum magidanci ya nuna yana da sha'awar aurenta kuma yayi alkawarin tsaye mata tayi karatu har ta gama. Babu bata lokaci kuwa aka daura aure ta tare a gidanta. Anan Maidugurin suke da zama saboda mijin nata Lakcara ne yana koyarwa a Jami'ar Maiduguri.

Yasir shi kuma cikin ikon Allah ya samu scholarship a Bangladesh ya tafi.

Ita kuma Zarah ta samu ta gama karatun sakandaren da kyar babu zancen cigaba da wani don kuwa a lokacin ta abincin ci ma ake yi karewa.

Fatima Zahra wata irin yarinyace mai tsananin son abun duniya. Tana da son hutu da watayawa, kuma zata yi duk abinda zai kai mata yan kudade komi kankantarsu kuwa. Tana kuma da kutse-kutse da tura kanta wajen masu hannu da shuni. Duk da dai yawanci su masu mu'amala da ita kyawunta ne yake dibarsu suke so suyi kawance da ita.

Kawancen ne ma ya hadata da wata diyar wani hamshakin mai kudi, wanda yake na hannun damar Gwamnan da ya ci takara a wancan lokacin. Kuma so take yi ta samu dama, ta rokeshi akan ya taimaka ya hadata da wani Kaninshi dake zaune a Kano kuma babban darakta domin harkar fim take so ta fara.

Daga farko so tayi Lamin ya hadata da mutanen da shi ya sani tunda har lokacin suna dan yin hulda da wasu manyan mutanen. Shi kuwa yayi tsalle ya dire yace ba a gidanshi ba, ya kuma fada ya kara nanata mata, matukar ta shiga harkar film to haihata-haihata shi da ita, sun rabu kenan.

Ita kuwa wata kawarsu ce ta tsole mata idanu. Tana tsakiyar karatun sakandare ta ajiye ta tafi harkar film. Kuma cikin ikon Allah da yake taje da kafar dama, sai gashi cikin abinda bai gaza shekara guda ba har tayi suna tayi arziki. Don taji ance ma har motar tukawa ke gareta. Yadda kuma abokanta suke zugata da kara nuna mata baiwar kyan da Allah Ya mata, suna fada mata Fadilar da ko rabin kyanta bata yi ba ta samu wannan daukaka ina ga ita? Sai kanta yake kara huruwa suna kara mata karfin gwiwa. Wannan dalili yasa ta nemi yin kawance da Karimah ta kuma samu damar shiga jikinta da iyayenta.

A cewarta, ko basu yi mata hanyar shiga film ba, zasu mata hanyar haduwa da wani babban wanda shi zai iya yi mata hanyar.

Nan da nan kuwa dai gashi ta riga ta zama kamar yar gida, ya zamana duk wasu shirye-shiryen abubuwa da ake yi na walimar da mahaifin Karimah ya hadawa sabon Gwamna da ita ake yi. Don hatta ranar da Gwamna da iyalanshi suka tare a gidan Gwamnati da ita aka je. Anan kuma suka hadu da Auwalu wanda shi kuma Gwamnan abokin Ubangidanshi ne na kut-da-kut.

Duk wani namiji dake cikin gidan wannan a lokacin Zahra ta tafi da imaninshi. Kuma kowa a shirye yake da tace zata aureshi a daura musu aure.

Cikin ikon Allah sai hankalinta yafi karkata ga Auwalu. Don kuwa akwai shi da iya tsara zance, ga kuma naci da rashin zuciya in dai akan macen da yake so ne. Ga shi ya rufe ido ya dinga mata barin kudi ba ji ba gani.

Duk wulakancin data dinga mishi ko a jikinshi bai dinga nunawa ba, sai ma salo da dabaru na sace zuciya daya dinga je mata dasu iri-iri.

Har dai ya tashi komawa Kaduna bata bashi wata gamsasshiyar amsa ba amma bai karaya ba. Don kuwa ko wata guda cikakke bai yi ba ya sake koma mata tafiya ta musamman

Anan suka daidaita da ita. Ya galla mata karyar matarshi daya da danshi daya amma sun rabu da matar shi kuma dan yana wajen mahaifiyarshi.

Ya kuma nuna mata yana da irin makudan kudaden nan, don yana ma gab da shiga siyasa. Jin haka sai tayi caraf tace ta amince.

Nan da nan sai ga magana tayi karfi, abin mamakin har aka yi aka gama abokan ango ne ke ta kaiwa da kawowa babu danginshi ko daya. Amma barin kudin da suke musu yasa babu wanda yayi gigin cewa ba haka ba.

Allah kadai yasan iyaka adadin kudin da Auwalu ya kashewa Zarah. Zai iya cewa tunda yake bai taba kashewa mace rabin abinda ya kashe mata ba, har Juwairah din kuwa. To amma da yake so ya rufe mishi ido, ko a jikinshi.

Ta bangaren iyayenta ma kuma da dangi sun yi iyaka bakin kokarinsu sun mata duk abinda ya dace.

Ranar daurin aure kwatsam sai ga dirar Ummulkhairi diyar marigayi Alhaji Kachalla gidan.

Wasu jibga-jibgan motoci kosassu kamar ana ciyar dasu suka yi mata rakiya, sai ga bodyguards na take mata baya.

Kai tsaye kuma gidan bikin ta yiwa dirar mikiya babu wanda ta nema a cikin dangi.

Nan da nan sai murna ta hadu gida biyu, aka taru ana ta murna ana mata sannu da zuwa da nan-nan da ita kamar a dauketa a goya a baya.

Ta yini guda cur cikin dangi ana ta hira da ita da raha gwanin dadi. Zuwa yamma ta tashi tafiya don tace ba zata kwana a nan ba, an riga anyi mata masauki a masarautar Borno, kuma idan gari ya waye ba zata biyo ba daga can zata wuce.

Ta yiwa yan uwa kyauta ta kudade masu yawa, suna ta mamaki da godiya baki ya kasa rufuwa, amma aka rasa wanda zai tambayeta inda ta samu wadannan kudade. Tana da aure ko bata? Wani hali take ciki? Duk babu wanda ya mata wannan tambayar.

Sai da zata tafi dinne ta bukaci ganin Lamin. Duk a zaton mutane kyautar bajinta shima zata mishi kamar yadda ta musu. Suka shiga uwar daka suka rufe.

Shiru-shiru suka jima a ciki, me suka ce, me suka tattauna? Allah kadai ya sani. Zuwa can bayan lokaci mai tsayi ta fito, tayi waje kai tsaye ta shige mota aka ja suka tafi.

Sai ga Lamin ya fito daga daki yana ta zabga zufa kamar wanda aka watsawa ruwa, idanu sun rine sunyi jawur sai kace wanda yayi kuka. Mutane suka dinga binshi da tambayar lafiya? Amma babu amsa.

A haka dai aka lallaba washegari aka tafi kai amarya dakinta. Kalilan daga cikin danginta sune masu yin rakiyar. In ka debe Hauwau sai wata Yayar Babarta, Iya Lantu sai kuwa kanwar Lamin din Harira, sai maza guda biyu.

Suka je suka dawo da daddadan labarin diyarsu tayi goshi. Don kuwa irin gidan da aka kaita da kayan alatun da aka zuba mata, ko diyar wani hamshakin mai kudin sai haka.

Ana ta wannan murna da yiwa juna san barka, watarana Lamin ya fita kawai sai ganinshi aka yi ya fadi, barin jiki ya shanye. Aka kwasa hankali tashe aka yi asibiti dashi. Bayan dogon bincike dai likita ya tabbatar da cewa damuwa ce tayi mishi yawa, jininshi ya hau da yawa. Kuma babu abinda zasu iya yi akai sai dai kawai a rubuta magungunan da za a dinga bashi, sai kuma yayi kokari ya rage yawan damuwa.

Haka aka kwasheshi aka koma gida aka hau jinya.

Amarya mutanen Kaduna, tana can tana ta shan amarcinta bama ta san kalar wainar da suke toyawa ba. Soyayya ake zubawa kamar ba gobe, yadda kasan su hadiye juna ita da Auwalu tsabar so. Yace mata yana aiki a Kano, don haka kwana biyu yake yi anan ya tafi wajen aikinshi yayi kwana biyu. Bata kuma taba tambayar wani aiki bane yake yi wanda har ranar karshen sati sai yaje. Ita dai tunda ya ajiye mata duk abinda take bukata shikenan. Ga talbijin dinta da bidiyo, ya sayo mata kaset-kaset sai wanda ta zaba, kwana take yi ta yini kallo babu abinda ya dameta.

Abinda dai yake ci mata tuwo a kwarya shine yadda har ta tasar ma cinye wata daya a gidan babu wani dangi nashi data ga ya taka kafa yaje inda suke.

Shi kuwa dama tunda auren ya gabato, ya sanarwa da Inna Deluwa da Juwairah zai yi aure. Juwairah ta yada kai gefe guda tace 'Allah bada zaman lafiya!' don kuwa ita abin ya riga ya zame mata jiki yanzu.

Inna Deluwa ce ta dinga kallonshi kamar wani wanda ya samu matsalar kwalwa, musamman da ya karkace kai ya hau bata labarin ai ba a gida daya zai hadasu da Juwairah ba. Saboda ita din yarinya ce, wadda ta tashi a gidan hutu bai kamata ya dauketa ya kaita gaban kishiya ba da hayaniyar yara.

Inna Deluwa tace, "wallahi kai dai anyi mutumin banza Auwalu! Har kana da bakin dagawa kacewa Juwairah wai ba zaka hadata da kishiya ba saboda yarinya ce kuma gidan hutu ta tashi? To ahir dinka wallahi! Aure ba zan hanaka ba, kaje kayi tayi matsalarka ce, 'ya'yane kayi ta tarawa kowa da uwarshi, daga baya kai abin zai dawo yana ciwa tuwo a kwarya. Amma wai raba kan mata wannan shine ban yarda dashi ba sam! Ka kawota nan kamar yadda ka kawo wadanda suka fita. Wannan ita ce magana!"

Ta tashi ta barshi anan.

Amma duk da haka bai ji maganarta ba, sai yayi kunnen uwar shegu da ita ya cigaba da bidirinshi. Wannan dalili yasa koda aka kawo amarya da yace su je su ga daki basu je ba.

Dama Inna din a shake take dashi. Bata taba sanin yana da wata matar ba a Kano sai a wannan dan takin kafin aurenshi da Zahra din. Rana daya sai mata ta musu sallama a gida da yaranta biyu mace da namiji, don namijin ma da alama ya haura shekara goma macen kuma zata yi takwas.

Ta amshesu da hannu bibiyu, ta basu wajen zama ta kai musu ruwa suka sha. Bayan sun gama hutawa sai take tambayarsu ko daga ina?

Budar bakin mata sai ce mata tayi ai matar Auwalu ce.

Tace 'wace mata kuma yar nan?'

Ta sake ce mata, 'matar Auwalu dai dake zaune a Kano?!'

Inna tayi salati da salallami, taji kamar ta dora hannu aka ta dinga kwala ihu. Sai suka hau kallon-kallo ita da mata da yara, Inna ta rasa abin cewa. Don kuwa iyaka rikicewa tayi.

Tana cikin wannan yanayi sai ga Juwairah ta shiga gidan hannu rike da kwanukan abinci data dafa zata kaiwa Inna din.

Inna tace, "yauwa diyar nan, zo kiji min wani lamari! Wai matar Auwalu ce tazo daga Kano!"

Ga mamakinta sai taga Juwairah din ko dar bata yi ba. Ta zauna a gefenta tace, "to! Kwarai kuwa ya taba fada min cewa yayi aure a Kano matar har ta haihu. Lallai shekara kwana ga mai yawan rai! Kinga yara sun girma tubarkallah!!"

Inna tace, "yanzu kin san da hakan shine baki taba fada min ba?"

Ita kuma mata kallonsu take yi cike da mamaki, ta kasa boyewa dai ta daga baki ta tambayesu, "wai ko kanwar Auwalu ce wannan?"

Juwairah sai tayi dan murmushi kawai, bata yi mamaki ba da Auwalun bai sanar da ita yana da mata ba sam. A halayen Auwalu ai kalilan ne bata sani ba.

Inna ta kada baki tace, "kanwar ina? Matarshi dai. Ai ita ce matarshi ta lalle!"

Ta dinga kallonta da mamaki zane akan fuskarta. Don kuwa ko ba a fada ba to ta girmi Juwairah din nesa ba kusa ba.

Tana nan sai ga Auwalun ya shigo bararam-bararam, karin hula a gefen kunne. Kafafunshi furtutu kamar wanda aka tono daga rami. Yana ganin wadda ke zaune a tsakar gidan sai yayi turus, ya hau share zufa.

Ita kuwa wani murmushin takaici tayi, ta kalli Inna tace, "dama Inna ba wani abu bane ya kawoni face in zo in nuna miki yan jikokinki ki gansu. Tunda shi Uban nasu yaki sadasu da ku balle ku san juna!"

Inna ta hau gyada kai, "kwarai kuwa yar nan, kinyi kyan kai! Kin kyauta sosai wallahi, Allah Ya shi albarka!"

Ta kama hannun yaran tana kokarin jan su da hira. A gefe guda kuma aka dinga kallon-kallo tsakanin Auwalu da Juwairah da Barira dake ta watsa mishi wani kaskantaccen kallo.

Zuwa can kuma ganin ya coge a bakin kofa yana ta muzurai ya kasa cewa komi yasa ta tashi tsaye ta kama hannun yara, ta cewa Inna, "to Inna zamu koma. Dama zuwa muka yi mu ga gida, ku ganmu mu ganku muma. Amma in Allah Ya yarda zamu dinga zagayowa ana gaisawa."

Inna ta rasa abin dauka ta basu, sai yan abubuwan tabawa da ba a rasa tsofi dasu ta basu. Suka yi sallama ta kama hannun yaranta suka wuce.

Da suka je gaban Auwalu, ta watsa mishi wani mummunan kallo taja tsaki ta zagayeshi ta wuce.

Kamar wanda aka dankare a tsaye, har suka fita ya kasa yin wani motsin kirki. Inna ta kalleshi tana girgiza kai, tace, "ban san me kake so ka zama ba Auwalu, amma wannan dai ba hali bane na kwarai wallahi. Allah Ya shiryeka Ya dawo da kai kan hanya." Ta tashi ta shige uwar daka.

Juwairah ma kuwa bata ce mishi komi ba ta tashi ta hau yan ayyuka a tsakar gidan don ma kada ya nemeta da wata magana. Ya gaji da tsayuwarshi ya lallaba ya fita.

Washegari asubahin fari ya yiwa Kano tsinke. Sai dai duk yadda yaso ya shawo kan Barira ta riga tayi fushi sosai. Ta ma ki bashi fuskar yin magana. A takaice dai ba a yi sati ba sai daya rubuta mata takardar saki. 'Ya'ya kuma tace ba zata bashi ba ya kai mata su gidanshi. Daya so nuna mata jan ido sai ta mishi duniyanci itama, ta nuna mishi akan wannan maganar zasu iya zuwa har kotun koli don kuwa ba zata yarda ba. Idan kuma ya matsa to wallahi zata iya sanyawa a batar mata dashi.

A haka dai suka yi sasanci, da cewar zai dinga aika musu duk abinda zai iya duk karshen wata. Ya koma ya sanar dasu Inna wannan labari. Duk da basu ji dadin hakan ba, sai suka yi addu'ar Allah Yasa hakan shi yafi alkhairi.

To kuma sai gashi ko wata ba a rufa da yin wannan zance ba ya kara babbako wani zancen auren a Maiduguri. Kuma yake zancen ba zai hadasu gida daya da Juwairah ba. Abin daya konawa Inna rai kenan.

10.

Sai ta wayar Auwalu suka samu daga can Maidugurin aka kira Zahra aka sanar da ita halin da ake ciki, hankalinta yayi kololuwar tashi, babu bata lokaci ta tafi Maiduguri. Lokacin watansu daya da yan satika da yin auren.

Halin data sameshi ya matukar tayar mata da hankali kwarai. Yana nan a kwance sai dai a kwantar a tayar, baya 'Uhm' baya 'uhm uhm!' sai dai ya bi mutane da kallo. Gabadayan Iyalinshi babu mai nutsuwa a tattare da shi.

A sati biyun da tayi anan babu wani canji da aka samu na azo a gani. Takurawar da Auwalu yayi akan ta koma gida da kuma yadda Dada Iyani itama take mata korafin ta koma dakinta hakanan, yasa ta hakura ta tafi din ba don ranta ya so ba.

Ta koma suka cigaba da gudanar da soyayyarsu ita da Auwalu, lokaci zuwa lokaci kuma tana kiran gida su gaisa ta kuma ji yadda jikin Lamin yake.

Ana nan sai ta fara laulaye-laulayen ciki. Hankalin Auwalu kacokam sai ya koma kanta kamar a kanta aka fara mishi haihuwa. Kulawa da dadi na duniya babu wanda bai jiyar da ita ba. Kai gabadaya ma sai daya kwashe fiye da wata daya bai je wajen aikin nashi a Kano ba. Tsakaninshi da Juwairah da 'ya'yan dake gabanta sai dai ya leka a tsaitsaye ya bata abinda ya sawwaka na cefane ita da Inna Deluwa, ya kara gaba. Ita kam tuni ta dawo daga rakiyarshi, tun tana fadan abinda yake kai musu na cefane din baya isarsu, har dai tayi hakuri ta sallama. Allah Ya taimaketa tana sana'o'inta iri-iri, ba a zaune take ba. Don haka ko da wani abu da ake bukata ita take yiwa kanta. Don kuwa ko su Saminu da AbdulHadi da kaninsu Tanimu dan wata Bafulatana daya aura ta kai mishi dan bayan sun rabu, ya daukesu ya kai almajirci can Jama'are bai kuma kara bi ta kansu ba sai in sun je gidan ya gansu, ita take dawainiya dasu. Duk sanda za a kira a nemi wani abu, mawuyaci ne ya dauka ya bada sai ita ce mai badawa. Daga karshe ma

ta roki Malamin nasu daya sanyasu a makarantar boko, kuma ita take musu bukatun makarantar tunda ta gwamnati ce. Bata ma tunanin yasan da zancen suna makarantar, idan kuwa ya sani to bai taba fada mata ba.

Ita fa gabadaya komi nashi ya fita a kanta sam. Kawai dai tana zaune dashi ne don bata da wani zabi wanda yafi haka.

A kwana a tashi, Zahra ta fara warwarewa daga laulayin da take yi. Jikinta yayi kyau yayi luwai hankalinta a kwance yake, bata da wata matsala sai ta rashin lafiyar mahaifinta da kullum jikinshi ke kara hautsinewa.

Da take ta samu Auwalun ya bata jacen wayar salular hannunshi. Wani lokaci da suka je taron nadin sarautar wani hakimi da aka yi a Zaria, aka ba manya-manyan na hannun damar Gwamna kyautar salulolin a kwalinsu, ciki har da Auwalun. Ta samu da wayo da kissa ya bata tsohuwar tashi ya hada mata sabon layi, don haka kusan kullum akan waya take tana gaisawa da yan'uwa.

Cikin ikon Allah cikinta ya shiga watanshi na shida, aka aika musu da mummunan sakon rasuwar Alhaji Lamin a wata safiyar ranar Talata. Tashin hankali wanda ba a sa mishi rana! Suka kwasa gabadaya har Auwalun suka tafi Maiduguri.

Rasuwar tashi ta girgiza iyalinshi da ma al'umma da dama, duk da cewa ya dade yana jinya amma dai babu wanda yake bashi rasuwa. To dama rayuwa da mutuwa duk suna hannun Allah ai, idan kuma Yaso kaje gareShi, ko da ciwo ko babu sai kaje.

Aka yi zaman makoki aka watse, aka bar Iyani da zaman takaba. Itama Zahra satinta uku ta koma. Duk da cewa taso ta yi zamanta anan har ta haihu don ta dinga debewa Iyani kewa, amma Auwalu ya nuna sam bai yarda da wannan zancen ba. Don haka ta tattara ba don rai yaso ba ta tafi.

Zancen rabon gado kuwa babu shi, don kuwa babu wani abu daya bari sai ma bashi da kudaden mutane dake kanshi. Don haka ne ma aka yanke shawarar a sayar da gidan da suke ciki tunda yana da girma sosai, sai a samu madaidaici a saya, in yaso sauran kudaden sai ayi biyan bashin dasu.

Zahra ta koma Kaduna da niyar su sake sabunta kauna da soyayyar da aka jima ana cin bashinta. Sai dai abin sai yaje mata ba a yadda tayi tsammani ba. Don kuwa a bakin mutanen unguwa ta dinga jin wai Auwalunta aure zai kara, kuma ma bayan hakan, wai yana da wata matar, da tarin 'ya'ya wadanda ba ma matar dake zaune a gidan nashi bace ta haifa, wadanda sauran matanshi ne na baya suke haifa mishi.

Kai tsaye tace karya suke yi. Don kuwa kwata-kwata hankalinta ya kasa daukar hakan. Ta kasa yarda da hakan. Gani take yi idan ta yarda zata iya hadiyar zuciya ta mutu.

Allah Yayi ta da wani irin kishi wanda ita kanta ba zata iya kwatanta shi balle wani mutum ya iya fahimta. Ita ko a gidansu tsakaninta da 'yan'uwanta kishinsu take yi idan taga iyayen sun basu kulawa fiye da wadda suke bata. To ina ga kishiyar da take hada miji da ita?

Yarjejeniya suka yi da Auwalu tun farko, ya mata alkawarin ba zai taba yin aure ba. Matukar tana raye kuma a gidanshi, babu shi babu wata matar har abada. Ire-iren alkawurran da yake yi mata kenan har a bayan aurensu. Ita kuma ta yarda dashi dari bisa dari, don kuwa bai taba bata wata kofa da zata yi zarginshi ba.

Da taga dai maganganun sun yi yawa, sai ta mishi maganar. Kai tsaye kuma ya karyata, ya fitittike ya dinga fadan karya da gaskiya, wai shi ashe duk kokarin da yake yi a kanta bata gani, zarginshi ma take yi, har tana iya yarda da zancen mutane yan zauna gari banza da dama su abinda suka iya kenan su dinga shiga tsakanin ma'aurata don su rusa musu farincikinsu? Da wannan maganganu dai ya dan kwantar mata da hankali maganar ta wuce na dan lokaci.

Ranar nan dai tace su kaita gidan amaryar da suke cewa zata auri Auwalu, ta gani da idonta, idan kuma karya suke yi, ko kuma sabani ne aka samu, wani Auwalun daban ake magana ba nata ba, sai taji.

Suka shirya da yamma tace mishi dubiya zata je, tinkis-tinkis suka samu abin hawa suka yiwa unguwar Rigasa tsinke.

Suna zuwa layin da yarinyar take ma tayi kyakkyawan gani, don kuwa mashin din Auwalun ne a fake a kofar gidansu yarinyar, shi kuwa yana a tsaye ya jingina da mashin din, yarinyar a gabanshi suna hira. Da alama ma wata hirar yake mata ta nishadi data bata kunya, don kuwa tasa hannune a fuskarta ta rufe tana dariya shima yana yi.

Yadda kasan wadda wuta ta daukewa haka ta ji, ta kasa tsayuwa waje guda sai data jingina da bango sannan.

Wannnan duk bai isheta ba. Bayan ta dawo cikin hayyacinta ta gama daidaituwa, kuma sai ta bukaci da su rakata gidan nashi. Su kuwa dama da yake abinda suke so kenan, sai suka kara mikar hanya. Lokacin har ya ma kara fente gidan don kuwa a yadda ake cewa bikin bai fi wata daya ba saura.

Ga yara nan kanana su biyu yan mata suna wasanninsu, kai daga gani babu tambaya tsatson Auwalu ne don kuwa kamar tasu har ta baci.

Kasa karasawa cikin gidan ma tayi, don kuwa tasan idan ta shiga to lallai aika-aikar da za ayi ba karama bace.

Suka juya suka koma gida. Suna ta zugata da mata hudubar kada ta bari ya raina mata wayau wannan karon tunda dai taga komi da idanunta, amma ita gabadaya hankalinta ma ba a kansu yake ba, sam bata fahimtar ma abinda suke cewa.

Tayi dauriyar da zata yi, da kyar ta iya jira aka yi sallah. Ta dauki waya ta kirashi kamar gaske tace yaje tana son ganinshi. Sai ga gogan cikin dan kankanin lokaci ya fado gidan yana ta fara'a, har da guzirin tsirenshi a leda.

Yana shiga ta maida kofar daki ta rufe gam. Ya juya don ya tambayeta lafiya? Sai yayi karo da ita da galam din kalanzir da ashana a hannunta.

Hauka ta mishi irin wanda bai taba gani a cikin duk matayen daya taba sani ba ko aure, kai ko a labari bai taba jin kwatankwacin wannan abu ba.

Ta rantse ta maya, sai dai ta kashesu su duka akan dai ta zauna da kishiyoyi har biyu ba ma daya ba. Ita tafi karfin a yaudarata a ci mata mutunci, tafi karfin ta hada miji da wata.

Ya bata baki, yayi lallashin, har ya rasa da irin kalmar da zai bata hakuri ma akan ta tsaya ta saurareshi.

Kai da taga fadan ma baya mata kawai sai ta hau kwararawa kanta kalanzir din wannan, shima ta fara watsa mishi. Nan yayi wuf ya cafko hannunta ya kwace ashanar ta karfi tare da amsar galam din ya rufe. Ya bita da kyawawan maruka har guda biyu, amma ta ki saduda, bakinta kuma ya ki rufuwa. Ta tashi daga faduwar da tayi dalilin marin daya mata, ta sake ciwo kwalarshi tana kokarin shakeshi.

Kici-kaca suka hau dambe dashi, shi abin har mamaki yake bashi wannan karfin hali. Da kyar ya samu ya yakiceta ya jefar, ya bude dakin ya fita tare da rufeta ta baya.

Yana ji tana ihun ya dawo ya gani, daga nan kuma ta hau fashe-fashen kayan daki tana auna mishi zagi da tsinuwa ta kowace fuska, yayi biris da ita. Ba shi ya koma dakin ba sai da dare ya tsala lokacin barcin wahala yayi awon gaba da ita.

Kwanakin da suka biyo baya kuwa cikin matsanancin fada da tashin hankali suka yi shi. Kwata-kwata ta ki bari su huta daga ita har shi. Ita tace matukar ba zai fasa zancen auren nan nashi ba sai dai ya sallameta ta tafi, shi kuwa yace bata isa ba. Ai shi yake aurenta ba ita ba. Kuma bata isa ta haramta abinda Allah bai haramta ba.

Sati biyu da yin haka ta sake tada wani bala'in jin ya kai kayan lefe, wannan karon wuka ta so caka mishi, wanda ba don Allah Ya matukar sanyawa da sauran shan ruwanshi a gaba ba, to da sai dai wani bashi ba.

Babu shiri ya samo mota ya sanyata ya dorata kan hanyar Maiduguri, ita kuwa tace tafi nono fari, tana jiran takardarta. Shi kuwa yace wannan shine ba zai yiwu ba.

Kuma ta tafin yayi aurenshi matar ta tare a gidan da Zahra din ta zauna.

Shikenan tunda ya auri Salamatu yadda kasan ya auri diyar gwal. Gabadaya hankalinshi ya juye ya koma kanta. Baya iya zuwa ko nan da can sai da izininta. Kai a takaice ma dai mantawa yayi da babin Zahra gabadaya. Ko nemanta baya yi, itama kuma da yake ta shaka bata nemeshi din ba.

Lokacin data haihu ma sai Iyani ce ta kirashi ta sanar dashi haihuwar. Bakin gwargwado kuma yayi abinda ya dace, ya aika musu duk kudaden abubuwan da suke bukata, sanar suna ta zagayo yarinya ta ci suna Nadiya.

Zahra tayi wankanta mai kyau. Kwatsam tana gama wanka sai ga shi ya dira, wai shi yaje daukarsu su koma gida.

Ta tambayeshi ya zancen aurenshi? Shi kuwa yace mata matar tana nan, karewa ma tare zai hadasu da ita taje su zauna. Tace to salin-alin kawai ya dauki takardarta ya bata, kada ma su ja maganar da tsayi. Don kuwa ita dai ta gama aure dashi har abada.

Wannan zance kuwa sai daya kaisu har gaban manyanta. Su kuma suka nuna goyon bayan hakan. Tunda a cewarsu ai yaudararsu yayi. Su 'ya'yansu basa zama da kishiya. Maimakon ma ya godewa Allah daya samu suka bashi auren 'yarsu, kuma sai ya kara musu da sakayyar kishiya? Ba zai yiwu ba.

In dai har ya dage lallai sai yayi zaman aure da ita, to kuwa babu shi babu hadata da kishiya. Shi kuwa yace ko yar gwal ce bata isa ta hanashi sunnah ba. Kai tsaye suka nemi ya saketa, shi kuwa sai yayi ban tsoro, ya tauna tsakuwa don aya taji tsoro. Ya rubuta mata saki daya. A tunaninshi zata tsorata tace ta hakura, sai yaga ko a jikinta ma. Sai ma cewa da tayi kafin a tafi a zauna dashi ya kayyade abinda zai dinga bata na shayarwarta, kuma idan ta yaye diya zata maida mishi kayanshi tunda ba da ita taje ba. Ta dauki jaririyarta ta bar wajen.

Shima kuwa sai ya shaka. Bai sake bi ta kanta ba ya kada kanshi ya tafi. A ganinshi ai zata nemeshi tunda yasan tana sonshi, ba zata iya rayuwa babu shi ba.

Kwananshi biyu da komawa suka je daukar kaya har da Zahra din aka je. Suka samu amarya suka zazzaga mata rashin da'a, suka kuma kwashe kayan gidan tas ko allura basu bari ba. Har TV da firjin da sauran kayan amfani daya dauka ya ba Salamatu wanda shi ya siyawa Zahran sai da suka bi suka dauka, suka kara gaba.

Kwanci tashi asarar mai rai, Zahra har ta fita idda abinta. Auwalu daya zauna yana jiran ta nemeshi dasu mayar da aurensu yaji shiru, kafin ya ankare har an kwashi shekara da rabuwarsu. Gashi yana sonta don so, amma kuma yasan ta riga ta mishi nisa yanzu.

Zahra kuwa tana yaye Nadiya ta hade mata kayanta ta aunata Kaduna. Duk yadda Iyani da su Hauwau suka so ta bar diyar a hannunsu ki tayi, a ganinta hakan da zata yi shi zai kara konawa Auwalu rai.

Ta kai mishi diyar da kanta ta dungurar mishi da ita. Babu ko gaisuwa balle tambayar bayan rabuwa, sai bakar magana data yaba mishi ta kara gaba. Yarinya na kuka ta rarrafa ta kamata tana ihu, amma haka ta wancakar da ita ta bar gidan babu ko dar. Zuciya ta rufe mata ido.

Daga nan kai tsaye Kano ta nufa inda Karimah ta hadata da wani darakta, cikin kankanin lokaci kuwa ta fada harkar film.

Auwalu ya rasa yadda zai yi da diya. Ya ba Salame ita don ta rike, tayi tsalle tace ta rantse da Allah ba a isa ba. Ita da ko nata dan bata gani ba sai a hadata da rikon dan kishiya? Ba zata karba ba. Ala dole sai daukarta yayi ya kaiwa Juwairah don Inna Deluwa ba dadin jikinta take ji ba balle ya kai mata.

Ita kuwa Juwairah da lokaci daya Allah Ya sanya mata kaunar yarinyar, ta karbeta da hannu biyu ta rika tamkar ita ta haifeta.

Ba a jima ba ya gyarawa Salame daki a gidan ta baro waccan ta dawo nan. Rigima babu irin wadda bata tayar ba, duka yayi biris da ita ya kyaleta. Suka zauna ita da Juwairah wani zama na doya da manja, don kuwa babu zaman lafiya a cikinshi ko kadan.

Zahra kuwa ta shiga industry da kafar dama. Nan da nan sai gashi tayi wani irin suna na ban mamaki. Duk wani mai kallo kai har ma wanda baya yi yasan da sunan Zahra Madam. Wanda sunan ya dauko asali ne daga film dinta na farko inda ta fita a wata Madam mai sayar da abinci a tasha. Da yake kuma film din ya karbu sosai, sai sunan ya bi ta.

11.

Nadiya ta tashi a hannun Juwairah wadda daukacin gidan suke kira da Mama. Tasan cewa Mamar ba ita ta haifeta ba, amma kuma ita a wajenta Mama din Uwa ce. Domin kuwa bata taba bambantata da 'ya'yanta na cikinta ba. Duk abinda zata yiwa 'ya'yanta, to kuwa Nadiya tana ciki. Lokacin data tasa ta fara yin wayo, Mama ita ta daukesu ita da Haulatu diyarta da kuma Nazifi kaninta wanda kusan sa'an Nadiya dinne, watanni shida ta bashi, ta kaisu makarantar boko da Islamiya ta dinka musu uniform. Lokacin kuwa Saminu da AbdulHadi sun mallaki hankulan kansu, suna ta sana'o'in hannu iri-iri suna tallafawa Mama don kuwa Abbansu ta kanshi yake yi. Sannu a hankali yan siyasa sun fara watsi dashi. Idan ba lokacin da siyasa ta kankama ba, ba a cika nemanshi ba. Don haka wannan abu ba shi kadai ya shafa ba, ya shafi har mutanen gidan baki daya.

Zahra bata taba waiwayar Nadiya ba tun bayan tafiyarta sai da ta kusa yin shekara goma. Lokacin Allah Ya karbi ran Inna Deluwa bayan doguwar jinyar cutar hawan jini da ciwon sugar data sha, a lokacin Nadiya shekara biyar bata cika ba, don haka ba wani saninta tayi ba.

A wadannan yan lokutan ne kuma ya auro Lantana. Data shiga gidan kuma sai suka hade kai da Salame, ita har lokacin bata taba haihuwa ba. Wannan hade kai da suka yi sai suka mayar da gidan kamar wani gida na yan dirama da wasan kwaikwayo. Kullum cikin tsokanar Mama suke da jan ta da fada, Nadiya tana mamakin dalilin da yasa ta tsokale musu idanu, tunda shi wanda suke yi dan shi din Mamar dai ba a gabanshi take ba.

Tun bayan auro Lantana da yayi da kamar shekara daya da Mama ta haifi Maryam, bata kara taka kafa taje dakin Auwalu da sunan kwana ba. Shima kuma bai taba nemanta ba. A lokacin ya zama dai kamar kawai tana zaman 'ya'yanta ne a gidan.

Babu irin zagi da gori da Nadiya bata gani ba a wajensu Lantana. Tun tasowarta sun sha kiranta 'shegiya, diyar karuwa' ko su ce, 'shegiya wadda uwarta take yawon ta zubar!' da kalamai dai munana irin haka. Tun abun yana damunta yana sanyata kuka har ta hakura ta gaji ta zuba musu ido. To ita uwar ma bata santa ba, bata taba sakata ko wani danginta a ido ba, balle tasan wace kalar waina take toyawa ba. Tana ganinta a cikin fina-finai dai. To suma fina-finan ta daina yi, ta samu wani hamshakin mai kudi ta aura.

Lokacin data cika shekara goma kuwa kwatsam sai ga Zahra da yan'uwanta sun je ganin Nadiya. Zo kaga murna a wajen Nadiya kuwa ranar, yadda kasan tayi me.

Aka musu masauki a dakin Mama wadda ta karbesu hannu bibiyu. Suka je musu da tsaraba cike da bayan booth din wata rantsetsiyar mota da suka je a cikinta. Nan da nan kuma sai jikinsu Salame yayi sanyi. Domin kuwa a kallo daya idan ka yiwa Zahra, kaga macen da babu zancen raini ko wulakanci a tattare da ita. Ta fito a ainihin Madam dinta sak, kai daga gani hutu da naira sun zauna mata.

Irin shigar da tayi ma kadai ta isa ta isar maka da sakon bata daga cikin ajin su Salame da kurar data kawosu.

Da diyarta guda daya taje a hannunta yar kimanin shekara uku. Tayi aikin film na kusan shekara biyar, tauraruwarta ta haska kwarai da gaske, a sanadin haka Allah Ya hadata da Alhaji Shehu Balogun, dan garin Jos ne haifaffe, kuma suka yi aurensu ya tafi can da ita.

Shahararren dan kasuwa ne kuma attajiri, ya rike matakai daban-daban a gwamnati tun daga kan sanata ya dawo dan majalissa mai wakiltar jaha, daga karshe dai ya kama kasuwanci ya rike. Yana da mata har biyu a lokacin daya auri Madam Zarah, amma daga aurenta cikin dan kankanin lokaci sai

da suka rabu dasu duka. Ya zamana ita kadai ce a gidan. Ya sakar mata kudi iya son ranta, ta fara fantamawa yadda take so.

To da yake itama bata son zaman banza, sai ta fara kasuwanci abinta. Ta kuma samu hanya ta Gwamnati da masu mulki a hannunta. A hankali-a hankali sai ta zama kamar wata broker a tsakanin manyan masu kudi. Tana da kudi tana da hanya tana da connections a sassa da fadin Najeriya har ma da kewaye. Idan wani babban yana son ganin wani babban, ita ake nema. Idan hanyar shigo da kaya kake nema daga kasashen ketare, ita ake nema. A halin yanzu Madam Zarah ta zama wata aba a cikin kasar Najeriya. Yan siyasa nemanta suke da idanunsu, domin kuwa magana daya tak idan tayi a kanka, zata iya canza maka kaddararka, maganarta zata iya sanyawa kaci zabe ko kuma ka fadi. Haka duk wani dan siyasa ko basarake ko wani dan kasuwa da zata goyi bayanshi, to shikenan fa shi kakarshi ta yanke saka.

A halin yanzu ta mallaki shaguna manya-manya da ake mata kasuwanci, kayan gado, kayan kicin, kayan ado da kawa na mata da maza. Hakazalika tana da gidauniya fiye da uku wadda kawai ta taimakon talakawa ce da marasa karfi. Duk inda taji wani labari na neman taimako, zata yi aike ko kuma ta taka da kafarta taje ta kai taimako. Da wannan sai ta saye mutane maza da mata, babu babba babu yaro kai babu talaka babu mai kudi. Mutane da dama fadi suke yi da zata daga baki tace tana neman takarar shugaban kasa ko ta Gwamna, to da a guje zata haye. To amma ita siyasar ba a ranta take ba, tafi son dai ta marawa masu yi baya, ta haka sai ta samu damar juyasu yadda take so.

Yini guda suka yi a gidan, har kusan yamma Auwalu yaje suka gaisa. Bakinshi yaki rufuwa da irin abubuwan arzikin da suka kai mishi, ga kuma aljihu da Zahra din ta cika mishi da kudi.

Da suka roki alfarmar ya basu Nadiya su tafi da ita taga danginta tunda anyi arashi lokacin an basu hutun makaranta, babu musu ya amince musu.

Suka tafi masauki suka kwana, washegari asubar fari suka yiwa Maiduguri tsinke.

Nadiya taje taga danginta suma suka ganta, dadi ranta har sai da tayi kukan murna.

Satinsu daya anan tana ganin gari, kafin kuma suka wuce Jos gidan Madam din.

Nadiya bude baki kawai tayi ganin irin gidan da Madam din take rayuwa. Fadar ya hadu ma bata baki ne, babu kuma zancen a kwatanta haduwa da tsaruwar gidan, don kuwa baki ba zai iya bayyanawa ba.

Gida ne gari guda, dauke yake da parts parts, wasu ma har ta gama satinta guda a gidan bata taba takawa taje bangaren ba.

Yaran maigidan su uku da yake duka mazajene, a gidan suke zaune amma har ta juya Kaduna bata taba sanyasu a cikin idanunta ba. Bangarensu ma bata sani ba, saboda basu cika shiga inda Madam din take ba, gashi inda suke din da yar tazara don haka ko fita zasu yi ba a sanin lokacin da suke fita da dawowa.

Komawarta Kaduna hankalinta ya kara nutsuwa, taji dadin bayyanar Mamanta sosai. Zagin da su Salame suke mata da gori ya ragu sosai, ko sun zaga dinma hakan sai ya daina damunta.

Karatunta take yi bilhakki, duk lokacin da suka samu hutu kuma Madam takan aika mota har gida a dauketa a kaita Maiduguri ko can Jos din. Ga dawainiya da take yi musu da iyalin Mama. Da yake Saminu da AbdulHadi sun jima da tafiya Lagos, Allah Ya taimaka musu duk suka samu abin yi a can don shi AbdulRazak ma har yayi mata a can, sana'a ta zauna mishi, to yana yiwa Mama aike duk lokacin daya samu to basu cikin matsala da matsi. Ba kamar da ba da idan Abbansu bai kai abinci gidan ba suke zama cikin garari, ko kuma idan matan gidan sun girka suka basu kadan suyi kwanan yunwa. Yanzu kuwa ko a jikinsu, abincin ma idan sun dafa suka basu suka ga bai musu ba, tuni Mama zata kunna sabon risho da Yaya Saminu ya sai mata, ta dafa musu wani abu su ci.

Shi Saminu Allah Ya taimakeshi ya samu aiki a wani kamfanin kera kayan robobi anan cikin Kaduna, da yake daga shi har AbdulHadi karatunsu a NCE ya tsaya wanda shima da fadi tashi suka gama, daga nan kuma suka tafi Lagos neman kudi. Dace ne aka yi yazo Kaduna yaga ana neman ma'aikata

yayi applying, cikin ikon Allah kuma Ya samu. Don haka ya dawo nan yana aikinshi. Kuma iyaka bakin kokarinshi yana taimakawa su Mama din da duk abinda ya samu.

A haka da duk hutun da suka samu na makaranta take zuwa ta yi shi a Maiduguri ko Jos, sai suka fara fara sabawa da mutane. Hatta da samarin gidan Madam. Cikinsu sun fi sabawa da dan gidan Alhaji Shehun na biyu, Irfaan, shekarunshi a lokacin kusan ashirin kenan.

Idan taje ya kan taimaka mata da bitar karatuttukanta, musamman bangaren turanci, ya iya shi kamar wani bakin bature, don haka idan taje wajenshi take makalewa yana taimaka mata da spelling da pronunciations.

Matsala ta farko dake fuskantar gidan Madam, shine babu kwabar yara a cikin al'amuranta. Ita duk abinda yaro yayi kawai dai-dai ne matukar hakan zai mishi dadi. Wannan yasa bata taba sanyawa Nadiya da su Irfan ido ko wani shamaki game da kusancin da suka yi ba, kuma bata taba gargadinsu ba.

Sannan shigar mutunci da addini sam ba a gabanta suke ba. Ita a karan kanta ta sha fita da wandon leggings da yar bubu da hula kawai. Akwai lokuta da dama da idan zata fita din sai Nadiya ta mata magiyar ta samu gyale ta yafa. Balle a kai ga maganar sallah. Don kuwa a rana idan kaga tayi sallah akan lokacinta dubi gani.

Akwai lokacin da yini guda tana ta aikin tarbar mijinta da ya kwashe wata biyu a kasashen turai, haka aka kwashe yini guda bata yi sallah ba, Nadiya bata kawo komi ba kawai sai tayi tunanin ko bata yin sallar ne.

Sai can an gama komi bayan isha'i ta sameta a dakinta tana ta jera sallah a gaggauce, kai idan ka gani hankalinka ma baya iya dauka. Ta sanyata a gaba zata fara mata nasiha, aikuwa ta wanketa tas da zagi har da la'adar mari, babu shiri ta bar mata dakin.

Ba a jima da yin hakan ba kuma ta sake komawa gidan hutu. Wannan zuwan da tayi ta fara fahimtar sauyi a tattare da Irfaan. Shekarunta sun shiga na goma sha biyar, don haka halittunta sun fara bayyana sosai da sosai. Ga

yanayin kayanta dake gidan Madam din duk kananu ne, sau tari haka take yini da hijabi a jikinta saboda kayan suna fitar mata da surarta sosai.

Ranar da dare suna tare da Irfan a falon Madam ne, littafine a hannunta yana fada mata kalmomin turanci da fassararsu tana rubutawa. Bata san ya aka yi ya karasa kusa da ita ba tunda akwai tazara a tsakaninsu, sai da taji shi ya kama gefen hijabinta yana kokarin cirewa.

Ta ja baya da sauri tana watsa mishi wani irin kallo, fuska a hade take tambayarshi, "meye haka kake yi?!"

Wani sakaren murmushi ya saki, "ni? Me nake yi? Taimaka miki zanyi ki dan ji sanyin jikinki haka nan, naga alamun hijabin tana takura miki!"

Ta hade fuska, "to bana so! Kada kuma ka sake yi mun hakan gaskiya, bana so!!"

Ta fara hada kayanta jiki na rawa zata bar mishi wajen. Dama zancen gaskiya ta fara takura da irin kallon kurillar da yake mata, da wasu maganganun banza da yake mata wadanda take nuna kamar bata ji ba. Kawai fita zata yi daga harkarshi tunda abin haka ne.

Tana ta wannan sakar zucin bata san ya aka yi ba sai jinta tayi a jikin mutum. Ya kama fuskarta yana kokarin hade bakinsu. Kici-kici suka fara kokowa dashi, ala dole sai ya cire mata hijabi.

Ta kuwa kware baki ta kwala ihu. Sai ga mutanen gidan sun fito a sukwane, Madam Zahra da wata bakuwa da tayi abokiyarta, sai Nanny din Safiya da Safiyar biye da ita hannu rike da kayan wasa.

Suka samesu sunyi cirgai-cirgai a tsaye, Madam ta tafa hannu, tace, "ke lafiyarki kike yiwa mutane wannan ihu?"

Tana haki da shessheka ta zayyane mata abinda ya faru. Tana rufe baki Irfan yayi caraf ya fara korawa Madam nashi bayanin, "A'ah Mommy! Ni fa wasa ne nake mata, nace ta cire hijabinta ta sha iska, shikenan kawai sai ta hau kwala ihu. Ni ko tabata ma fa ban yi ba!"

Nadiya baki ta saki cike da mamaki tana kallonshi. Madam kuwa tsaki ta saki tana hararar Nadiya, "dalilin da yasa kike kwalawa mutane wannan ihun kenan? Wallahi nayi zaton ma macijine kika gani ko wani abu! Ni kaina so nawa ina fada miki ki daina yawo da hijabi a gida sai kace wata matar Limami amma kin ki? Shi ba Yayane a wajenki ba? Ashe bai isa ya yanke hukunci a kanki ki bi ba? To daga yau na hanaki sanya hijabin a cikin gida. Allah kuma yasa ki kara sanyawa kiga abinda zai biyo baya! Stupid yarinya kawai ta tsoratani a banza!"

Kawar tata ta kalleta da mamaki, tace, "haba ke kuwa Madam. Irin haka tsayawa kake yi ai ka bincika komi a sannu musamman tunda ta fito ta fadi ga abinda ya faru, ba wai ki bita da fada ba. Musamman ma ni ban ga laifinta ba. Tunda kema kin san gidanki gidane na jama'a, bai dace ma wadanda ba muharramanki ba su dinga kara-kaina a sashenki ba!"

Aikuwa sai Madam din ta juya kanta, ta rufe ido ta zuba mata rashin mutunci. Daga karshe ma tace ta fita ta bar mata gida tunda ita munafuka ce.

Jiki a sanyaye Nadiya ta ja kafafu ta koma dakinta.

Kwana tayi tana canki-cankar ko dai ta tafi gida ne. To tasan da tayi maganar Madam zata ce saboda abinda ya faru jiya ne.

Ta ja jiki ta shiga wanka a bandakin dake hade da dakinta. Tana tsakiyar shafa mai bayan ta fito daga wankan kawai sai ji tayi an turo kofa, ta juya haka sai suka hada ido da Irfan. Yayi tsaye yana mata wani kallo na yan iska

da murmushi akan fuskarshi, yace, "Baby Nadiya, Mommy tace ki fito mu karya!"

Ya kuma yi tsaye yana kallonta ido cikin ido kamar dai ba zuwa yayi ya sameta ba daga ita sai tawul daure a jikinta ba.

Kasa mishi magana tayi har ya gama kare mata kallo ya juya ya tafi. Ta hadiye wani tukukin bacin rai a cikin ranta, zuciya na mata suya cike da takaici da bacin rai. Ji take kamar ta yi me. Haka dai ta shirya ta fita wajen karin.

Suna gama karyawa Madam ta suri jaka, dama a shiryenta take cikin wani pencil skirt dinkin atamfa da rigar bubu wadda ta tsaya mata a gwiwa, dankwali kawai ta kashewa dauri ta fita haka nan sangam-sangam wai taje ta gano shagunanta. Ta bar Safiya a wajen mai rainonta saboda sun samu hutun Prenursery da ake kaita, Madam kuwa dama bata cika daukarta ba.

Su uku kadai suka yi karin, daga ita sai Madam da Safiya. Bata ga Irfan ba tun bayan shiga dakinta din da yayi. Don haka sai ta dan saki jikinta, suka zauna ita da Habiba da Safiya suna wasa har Safiyar tayi barci, Habiba ta dauketa don taje ta kwantar da ita.

Ta shiga kicin ta bude firjin ta dauki ruwa zata sha. Kashedin Madam da taji na sanya hijabi yasa ta saka gown mai dan matsakaicin gyale, amma da yake gown din ba mai fadi bace, sai ta bi shape din jikinta ta zauna sosai. Kawai ji tayi an kama mata mazaunanta da hannu biyu ana murzawa, ta zabura tayi tsalle bakinta dauke da bismillah, ruwan da take sha duk ya bi ya zube a tsakiyar kicin din, robar ruwan ma tayi nata wajen.

Irfan ya bi bayanta yana kokarin rungumota, sai ga su suna kokawa da juna.

Ya kamo kirjinta yana damka, yana sakar mata wasu maganganu da tsabar rikicewar data yi ta kasa fahimtar ko me yake cewa ma. Da Allah Ya bata sa'a ta daga kafa ta harbeshi a tsakanin cimyoyinshi, sai ta kwasa tayi dakinta a guje ta barshi anan a kasar kicin a kwance yana malelekuwa dafe da mararshi.

12.

Bata tsaya dogon tunani ba , ta hade kan kayanta ta kimtsa. Babu wanda ya sani, ta fita ta nufi tashar mota sai Kaduna. Kudaden da suke a hannunta ba masu yawa bane, da kyar da magiya direban ya iya yarda ya kaita Kaduna da cewar in sun je za ta cika mishi. Suna isa kuwa da bayan la'asar ta samu mai mashin shima ta mishi magiya ya ara mata kudi ta biya direban, shi kuma yana kaita gida ta shiga ta amsa wajen Mama ta kai mishi.

Mama ta kama baki ganin Nadiyar duk a firgice, daga ganinta kasan tafiyar ba ta dadi bace. Saboda ba haka ta saba dawowa ba. Yawanci idan zata dawo direba ake hadota dashi, ya kaita ya juya. Sannan zata je musu da tsaraba iri-iri da aike cike da bayan booth din mota. Amma ranar sai gata zikal dinta. Sai bata ce mata komi ba.

Sai data bari ta nutsu, ta tada kwanan abinci guda, yadda take cin abincin ma hannu baka hannu kwarya, sai kayi tunanin ko ta kwana ne bata ci abinci ba.

Mama ta zauna cike da sigar jan zance, take tambayarta yau ko direban dake kaita baya nan ne? Sai lokacin ta dargwaje mata da kuka. Tayi zaune tana kallonta cike da mamaki har tayi ya isheta, kafin ta fede mata zani har bindi.

Abin kam bai yiwa Mama dadi ba sam, ta kuma so ta kira Madam din ta mata zancen ba haka ya dace ba, kuma ba haka ake yi ba, sai Nadiyar ta dakatar da ita. Don kuwa tasan ko tayi mata maganar ma ba lallai hakan ya haifar da d'a mai ido ba.

Dare yana yi ta lallaba dakinsu inda suke zaune ita da Haulatu da Zainab, dukansu kusan sa'anninta ne, sai Basira kanwar Zainab, mahaifiyarsu daya, da Abban ya aurota a can Mallawa, sai da Basirar ta girma ma ta tasa kafin a ka maidasu gidan.

Gidan ba wani mai fadi bane, ga su kansu dakunan ba wasu masu yawa bane. A da ma gabadaya yaran gidan daga mazan har matan a daki daya suke kwana. Sai da Yaya Saminu yaje gidan watarana yaga hakan, sannan ya yiwa Abban maganar rashin dacewar hakan. Sannan ne fa shi Yaya Saminu din yayi kokari aka fitar da dakin soro inda mazan suka koma can da zama. Su kuma matan aka bar musu wannan.

Washagari kuwa tunda safe sai ga wayar Madam. Fada ta dinga yi tun karfinta, ita fa ala dole Nadiya ta mata rashin kirki ta gudo daga gidanta akan abinda bai taka kara ya karya ba. Tace tunda kuma abin haka ne, to kada ta kara je mata gida, ta mata iyaka. Ita kuwa ta doki cinya tace ta fi nono fari.

Ta cigaba da zuwa makaranta abinta. Lokaci zuwa lokaci Mama ta kan bata kudin mota taje Maiduguri idan aka yi hutu, ta musu yan kwanaki kafin ta koma. A haka sai aka wayi gari ta kwashi shekaru da dama basu hadu da Madam ba.

Ita da kanta ta nemeta lokacin data shiga sakandare, suka cigaba da gaisawa. Amma bata kara zuwa Jos ba. Sai dai idan sun hadu a Maiduguri, ko kuma idan wani abu ya kaita nan Kaduna ta je inda take su gaisa.

Tun tana yar kankanuwarta babu abinda yake burgeta irin girke-girke da kuma baking. Wannan dalilin yasa koda taje cike jamb ta cike Home Economics kawai.

Duk gidansu ita kadai ce mace wadda tayi karatu wanda ya wuce na sakandare. To ba ma kowa yake zuwa makarantar ba sai yan kananun yara. Ita kanta da ba don jajircewarta ba da naci, da babu inda karatun nata zai je. Suna ss2 ita da su Haulatu aka musu aure ita da Zainab, ita Haulat mijin a Bauchi yake, Zainab kuma a garin mahaifiyarsu ta samu mijin auren. Da Abban ma cewa yayi itama Nadiyar ta fitar da mijin, a lokacin ita ko tsayuwa da samarin ma bata yi ba. To wane miji zata fitar?

A kuma lokacin ne Anty Jamila da Yayanta suka nemesu da kansu, suka je gidan suka ga juna.

Ganin matakin da karatun boko ya kai Anty Jamila da Yayanta, ya kara karfafa mata gwiwar kara tsayawa tayi karatu. Ita Anty Jamilar tana koyarwa a BUK ne, mijinta kuma yana aiki da In Land Revenue anan Kano. Yayinda Yayanta Abdur-Razak yake aiki da kamfanin Riyadh Airline, a can kuma yake da zama shi da iyalanshi.

Zuwan Anty Jamila gidansu shi ya kara gyara musu rayuwar gidansu nesa ba kusa ba. Kusan hidimar auren su Haulatu duk su suka yi ta, da Yaya Saminu da Yaya AbdulHadi. Shi kanshi Abbansu sai da suka saya mishi motar hawa saboda mashin dinshi ya samu matsala a lokacin. Kuma Anty Jamilar ce ta hana Abbansu hada auren Nadiya da wani dan gidan abokinshi da yaso a sanya ranar auren ranar da aka daura auren su Haulatu. Ita kuma Basira da yake ta fitar da nata mijin, sai aka sanya nata auren.

A kuma cikin yan shekarun ne ta fara fahimtar wai sautukan da take jiyowa a dakin Babansu cikin dare na menene? Ta sha jin su Haulatu suna tambayar Mama wai cikin dare suna jin wasu abubuwa na fita daga dakin Babansu na menene? Sai Mamar tace musu tari ne, ko kila bashi da lafiya ne, ko wani abu mai kamar da haka. Suna yarda a da din, amma kasancewarsu yara masu yawan shige-shigen abokai da kuma yawan karance-karance, yasa kafin a kai ko'ina ma suka fahimci zancen ba haka yake ba.

Ta taba jin Zainab tana fadawa Haulatu ai wannan sautin fa idan Ma'aurata suna tarawa ne suke yinsu. Tafi-tafiya kuma da shekarunsu suka kara tasawa, watarana sai taji Haulatu tana cewa ita fa wannan sauti yana daga cikin dalilan da yasa take so tayi aure, wai itama taje taji me ake ji.

Tayi tsaki a lokacin tana jinjina kai, don kuwa ita bata ga abin burgewa da sha'awa anan ba.

Mahaifinta ne fa. Ace kuma duk lokacin da zai kebance da matanshi sai kowa na gidan ya sani? Ina dalili. Musamman da a dan takin ta samu labarin wai a can bayan unguwarsu wata yarinya tayi cikin shege, da aka matsa mata da

tambaya tace wai ai iyayenta ta gani suna yi, shine suke gwadawa da wani yaro dan unguwarsu sai wannan tsautsayi kuma ya auku.

Ga shi tun suna ma kokarin bari sai cikin dare idan sawu ya daga, har abin ya kai sun ma daina damuwa. Musamman bayan auren su Haulatu da suka hade a daki daya da su Maryam ga su Fatima, zaka ga gari ya waye tangaran amma suna yi kowa na jiyosu. Kuma mace ta fito tsakar gida tana juya mazaunai kai a sama ta shiga dakinta babu kunya, gabadaya rayuwar gidan sai ta gama fita a ranta.

Shi yasa tana samu da Allah Ya bata sa'a Anty Jamila da kanta ta bada aka cika mata jamb. WAEC dinta da NECO duka sunyi kyau, sai ga shi DAG sun bata admission.

Ta samu Abbanta da murnarta ta fada mishi, sai ya karkace baki yace sai taje wadda ta daure mata wani gu din ta biya mata kudin makarantar, don kuwa shi dai ba da yawunshi ba. Sai jikinta yayi sanyi. Idan da abinda ta tsana a rayuwarta to bai wuce roko ba. Kwata-kwata bata son shi, abubuwa da dama idan ba karfinta suka fi ba, bata cika daga baki ta roki ayi mata abu ba. Mace ce ita mai kokarin tsayawa a kan kafafunta, tun tana yar yarinyarta kuwa. Don kuwa koda tana gida a lokacin, tana yin kananun sana'o'i na hannu, kuma da su take toshe kofofin matsaloli idan sun taso mata.

Ta samu waya ta kira Madam ta sanar mata da yadda suka yi. Tace ta kwantar da hankalinta, in dai karatu ne ta mata alkawarin har sai ta gaji da yi. Sai hankalinta ya nutsa.

Kuma kamar yadda tayi alkawarin, haka aka yi. Ita ta biya mata kudin registration, ta bada aka mata komi daya kamata har gidan da suka zauna da Aramide ita ta kama musu, ta mata provision da duk wani abu daya kamata. Da lokacin tafiyarta kuma yayi, ta sa aka bude mata account wanda take sanya mata kudin da zata dinga bukata a duk karshen wata.

To cikin ikon Allah ma da yake ko a makarantar bata yi kasa a gwiwa ba, aiki ta dinga yi a kananun restaurants da kuma amsar kwangilar birthday cakes da sauransu, sai ya zamana bata zauna haka nan ba hannu babu komi.

Madam ita ta tsaye mata akan abinda ya shafi registration da accommodation, sannan lokaci zuwa lokaci ta kan aika mata na provision da kuma na batarwa. Anty Jamila ma da Yaya Saminu suna yin wannan kokarin. Don haka abin sai yaje mata da sauki sosai fiye da yadda tayi tsammani.

Tana makarantar Mama take bata labarin Anty Jamila da Yaya AbdulHadi sun sayi wani gida anan bayansu za a hade da gidan da suke ciki don a kara fadada shi. Abu na farko da tayi shine ta tuntubi Yaya Saminu da zancen ya taimaka a samu a cire mata dakinta daban. Saboda dama hada daki da su Fatima da sauran yaran gidan ya fara damunta. Dauke-dauke ake mata, sai daya zamana ma kayanta gabadaya a dakin Mama suke don bata isa tace an taba mata kaya ba sai su Salame su yi ruwa da tsaki su ce sharri take yiwa yaransu.

To kuma sai ware mata dakin ma ya zama dama ba ayi hakan ba. Aka ware dakin kusa dana Abbansu, gashi dan karami wanda ya kasa kwashe tarkacen kayanta.

Bugu da kari kuma da Salame ta fahimci alakarsu tana takurata, sai ta kara kaimin bada himma. Sau tari Nadiya tasan da gayya take wasu abubuwan, ko in suna hira da Abban a dakinshi kaji tana ta kara sauti da bude murya duk dai don Nadiya ta ji ta din. Abin ya bata takaici watarana ya bata dariya. Ta ga ita dai ba kishiyarta ba, balle tace idan tayi hakan zata ji haushinta ko kishinta.

Bata sani ba ko wannan dalilin ne yasa gabadaya taji maza basa kanta? Ta kasa tsayawa ta saurari wani namiji da kunne mai kyau balle har ta iya bashi damar aikawa gidansu. Saboda gabadaya ji take yi an cire mata son auren a cikin ranta. Bata tashi taga mu'amalar aure mai kyau a inda take ba a tsakanin ma'aurata. Bata ga ana mutunta mace a inda ta tashi ba. Bata ga ana bada hakkin aure yadda yakamata ba. Sai ta hada duka mazan tayi musu daurin goro. A wajenta su dukansu halinsu daya. A gareta kam, su

duka mazan basu da bambanci. Ita kam da za a barta ma, tana da tabbacin zata iya dawwama a haka ba tare da tayi auren ba.

Wannan kenan!!

☆☆☆☆☆

Sun gama hada abin da za ayi kari dashi, ta koma dakinta tayi wanka ta shirya cikin wata Arabian gown purple color mai adon duwatsu. Ta nannade gashinta a cikin ribbon, a ranta tana raya yakamata ta samu ta wanke kanta ko kuma ayi mata kitso.

Tana fita falo ta samu Dada da Aysha a zaune suna hira. Sai karin bakuwar fuska data gani. Daga ganinta kasan yar gida ce saboda tana yanayi da su Aysha amma bata tunanin ta san fuskar.

Ta zauna a gefen Dada ta gaisheta, kafin ta mayar da hankalinta kan bakuwar itama ta gaidata. Ta amsa mata fuskarta dauke da murmushi.

Lokaci guda ta fahimci irin mutanen nan ne da murmushi baya barin fuskarsu. Doguwa ce sambal, don zata iya fin Nadiyar a tsayi. Sai dai hasken fatarta bai kai na Nadiya din yawa ba duk da dai itama tana da nata hasken. Daga ganinta kuma kasan zata dara Nadiya a shekaru a kalla da biyu ko uku.

Dada tace mata, "wannan Halimatu ce diyar kawunku Yasir, ba lallai ki santa ba saboda ba anan ta tashi ba. Gabadaya karatun sakandare dinta da na Jami'a a Amurka tayi, bata jima da dawowa nan ba."

Nadiya ta jinjina kai, kwarai tana jin labarin kam. Lokacin da shi Kawu Yasir din yaje can Washington DC yayi aiki da gidan Rediyon DW na tsahon

shekaru bakwai. Taji ance dama akwai diyarshi da suka baro a can tana karatu.

Suka sake gaisawa kafin Dada ta dora da cewa, "Fatima ta turota kije ta miki awon kayan da za a dinka miki na biki, ita ce madinkiyar taku."

Tace, "to babu matsala, bari in karya da sauri sai mu tafi!"

Cikin yan mintuna kalilan kuwa ta gama. Ta tashi taje ta dauko takalmi da jaka, suka yiwa Dada sallama suka fita.

A motar Halima din suka tafi wadda taji su Aysha suna ce mata Anty Lima. Don haka itama ta bi bayansu.

Kafin su karasa shagon nata hira sosai ta barke a tsakaninsu. Nan da nan sai suka zama kamar wasu wadanda suka dade da sanin juna. Ta fahimci Anty Lima din bata cika son hayaniya ba da shisshigi, kuma Allah bai dora mata girman kai irin na sauran yan'uwansu da kannenta ba, don haka tasan tasu zata zo daya.

Bata tunanin duk cikin iyalin Kawu Yasir akwai wanda suke magana dashi. A duka iyalan nashi babu na zaba. Kowa kallon wani wanda ba su ba yake yi kamar wani mabaraci ko miskini, idan kaje inda suke sai su dinga maka wani kallo na raini da kaskanci, ita kuwa taga a wane dalili zata zauna ana rainata bayan ba nema ba take yi a wajensu? Don haka ta ja jikinta gefe. Ko Maidugurin taje idan ba wani abu na dole ba, baka ganinta a wajensu. Amma dai taga Anty Lima din kamar ba irinsu bace.

Shagon nata yana nan a Kuntau Road. Ta karanta fashion and Textile design ne a can Washington din, kuma yanzu haka tana aiki da wani kamfanin dake kera lesuka ne a Turkey, shi shagon kawai ta bude shi ne saboda tana son dinki. Amma ba ita take yin dinkin da kanta ba. Tana da madinka dake mata aikin, yawanci ita sai dai ta duba musu aikin ne ko kuma ta zana musu irin design din da take so su kuma su yi.

Wajen ya matukar burge Nadiya. Kai daga gani kasan cewa kaga wajen harkar manya ba ta yara ba.

Suka shige can inda Anty Lima din take gudanar da ayyukanta tana nuna mata kayayyakin Nadiyar da Madam ta bada a dinka musu ita da Safiya.

Wasu ma an riga an dinka, gown din da zasu sanya ranar dinner ce da kuma atamfar kamu tace mata tafi son ta dauki measurements dinta kafin a dinka.

Ta dauki measurements din nata ta ba wanda zai yi dinkin, ita kuma ta tsaya ta hade kan kayan Safiya da yake an gama dinka nata, idan sun je gidan Madam sai ta bada. Akwati guda haka ta cika shi ta shake kamar kayan amaryar ne ba na yan biki ba.

Suka fita suka shiga mota. Har sun dauki hanyar gidan Madam din sai Anty Lima ta kalleta, tace, "wajen kunshi zan je, ko zaki je kema sai a miki kunshin?"

Ta kalli hannunta da yayi fari tas, rabon da tayi kunshi har ta manta. Tace, "muje to. Bani da abin yi yau din dama. Gashi dama rabona da inyi kunshi har na manta."

Don haka ta juya akalar motar zuwa wani wajen.

13.

Ba su suka isa gidan Madam ba sai can bayan la'asar. Bayan kunshin da aka yi musu, har kitso sai da aka yiwa Nadiya din. Irin ainihin kitson bare-bari aka mata, wani ya yi gaba, wani kuma yayi baya. Da yake bata son fitar da gashi waje, sai ta hadeshi a tsakiyar kanta ta daure kawai.

Gidan Madam din madaidaicin gida ne, flat. Securities biyu ne a zaune suna gadi a lokacin. Sai da Anty Lima ta fada musu ko su waye su, suka kirata ta

bada izinin a barsu su shiga sannan aka bude musu gate. Nadiya kai kawai ta dinga jinjinawa cike da mamakin wannan lamari na Madam.

Anty Lima ta ajiye motarta kusa da wata hadaddiyar jeep Rav4 baka tana ta sheki.

Suka fita daga motar, hannunta rike da akwatin kayan Safiya suka shiga falon Madam din.

Ita kadai suka samu a hadadden falon nata da ya sha saitin wasu Italian Royal kujeru.

Tana zaune akan daya daga cikin kujerun ta hakimce, hannu daya rike da wayar Samsung Galaxy tana dannawa, a ajiye akan karamin teburi kuma data dora kafafunta akai, sabuwar fitowar wayar iPhone ce.

Ta ajiye wayar da sauri ta tashi tsaye tana yiwa Nadiya din oyoyo, "oyoyo my baby! kitawu nasaraye (nayi kewarki sosai)" da yaren bare-bari.

Itama ta rungumeta fuska dauke da murmushi, ta manta rabon data sanya mahaifiyar tata a idanu, kullum sai dai ta waya. Sai dai tafi fahimtar su zauna a hakan, saboda zamanta ita da Madam a waje daya ba zai taba haifar musu da da mai ido ba. Ita dai Madam bata son a shiga harkarta, tana da son mulki ta yadda duk abinda tace kayi kawai ita a sonta kace mata to ne babu tambaya balle shakku. Ita kuma Nadiya bata iya gani ta kyale, sannan ba zata taba amincewa abinda ya taka shari'a ba ko kuma take ganin ya kaucewa tunaninta. Ta hakane sai ita da Madam din basu cika samun daidaito ba a lokuta da dama.

Ta saki Nadiyar tare da rungumo Anty Halima itama tana mata oyoyo kafin suka nemi waje suka zauna.

Hira ta barke sosai a tsakanin su ukun wadda tafi karkata tsakanin Madam da Anty Lima. Nadiya dai binsu take yi da ido, idan anyi abin dariya ta dara ko kuma ta bisu da murmushin yake. Tun kafin aje ko'ina zaman har ya fara isarta. Saboda hirar tasu duka ta ta'allaka ne a wajen yadda Anty Lima tayi

sa'ar rayuwa take. Ta kammala makaranta cikin nasara, ga aiki tana yi, ga shago tana da shi, ga kuma hadadden saurayi dan masu kudi da take dashi a hannu, me yafi wannan dadi da alfahari? Nadiya tasan idan tace zata zakalkale to lallai sai Madam ta fada mata maganar da zata bakanta mata. Kila tace 'ba kamar Nadiya ba!' Ko kuma tace, 'dama ace Nadiya ce!'

Ire-iren wadannan maganganu ba karamin bakanta ranta suke yi ba idan tayi su. Sai taga kamar Madam din ta raina abinda take yi kuma take samu.

Anty Lima take tambayar Madam din, "ni ina Sophie ne ban ganta ba?"

Madam tayi dan murmushi, tace, "Sophie tana gida, sai gobe zata taho. Kin san fa tana ta shirye-shiryen tafiya Egypt. Medicine take son karanta. Yanzu haka ana zancen bude mata asibiti ne idan ta dawo!"

Anty Lima da Nadiya duk suka nuna jindadinsu game da hakan.

Madam ta kalli Nadiya kasa-kasa, "ke kam ai kin barar da garinki ya zube a kasa! Da ace kema kin nufi wani bangare na kiwon lafiya da ba shikenan ba kakarki ta yanke saka? Kinga da babu ruwanki da neman aiki tunda ga asibiti nan a gida!"

Tayi dan murmushin yake kawai, ta dauki kofi da aka tsiyaya musu lemu a ciki ta kai bakinta tana kurba. Tana so ta tambayeta, 'sai kuma tayi ta zama kenan tana jiran har a budewa Safiya asibiti kuma taje ta mata aiki? Ko kuma tace, saboda shi shagon da take managing bashi da muhimmanci a wajenta kenan ko kuma don Madam din ta raina sana'ar?'

Amma duk sai ta kame bakinta bata ce komi ba. Don tasan tana bude baki to hirar arzikin da suke yi zata watse ne.

Sai Anty Lima ce tayi yar dariya, tace, "Mommy ai kuwa suma caterers suna samun yan canji fa babu laifi. A yanda take fada min yadda shagonsu yake daukar manyan mutane nasan fa ba karamin kudade take damka ba!"

Maimakon Madam din ta bata amsa sai ta tabe baki ta dauki wayarta daya ta hau latsawa. Itama sai bata damu da hakan ba, don bata so hirar tasu tayi tsayi. Suka cigaba da hirarsu da Anty Lima.

Sunyi sallar magriba ta fara neman yanda za ayi ta koma gida tunda Anty Lima din anan wajen Madam zata zauna har zuwa bayan biki. Basu cika zaman lafiya da sauran yan gidan nasu ba. Ita ce diyar fari, mahaifiyarta kuma ita kadai ta haifa ta rasu. Sauran matan da Babanta ya aura ba wai son tsakani da Allah suke mata ba. Ta sha wahala kwarai da gaske a hannunsu. Shi yasa da zasu dawo Nigeria daga Washington ta makale a can ta ki dawowa. To da Allah Ya taimaketa mahaifinta yana sonta sai abubuwan suke mata sauki.

Amma a yadda take fadawa Nadiya, rayuwar gidansu kusan kwatankwacin ta gidansu ce, bambancinsu kadan ne. Ga yaran gidan duk sun rainata saboda iyayensu basu muhimmantata ba a wajensu. Ga matsalar rashin aure da ta sha fama da ita, shekarunta talatin da biyu a yanzu amma bata taba aure ba. Ta sha gori da suka da wulakanci har da na Allah tsine. Amma da yanzu kuma ta samu miji na nunawa sa'a, dan gidan wani tsohon Janar ne, kuma matukin jirgin sama, duk kuma sai suka koma suna neman wajen zama a wajenta. Ita kuwa tace ai ba haka ake yi ba.

Nadiya ma kam tace kwarai tayi gaskiya, don kuwa ba taren Allah da Annabi bace ba kenan, ta son abin duniya ce.

Madam ce ta hanata tafiya lokacin data leka dakinta da niyar yi mata sallama, "ki zauna wajen Halima kawai, saboda goben da safe ina so a hada abin kari mai kyau, za a kai gidan Hajja Umma!"

Ita bata ma ji labarin Hajja Umma din zata je wajen bikin ba. Duk da bata santa ba, amma tasan labarinta a bakin mutane sosai.

Tace, "to shikenan. Me kike tunanin za a dafa mata ne?"

Ta yi jim tana tunani kafin ta daga kafada, "just cook something fancy! (Kawai ki dafa wani abu mai dadi da kuma tsada), a hada da wuri dai kafin karfe tara. Mu kuma ki dafa mana wani abin mara nauyi saboda ban taho da cook dina ba, already har na fara gajiya da abincin restaurants din garin nan! Sam basu iya abinci to my liking ba!"

Nadiya dai tayi dan murmushi ta amsa mata da 'to' ta juya ta koma dakin Anty Lima.

Ita kadai ta shiga kicin din, ta bar Anty Lima a daki tana waya da wanda zata aura bayan sun gama sallar isha'i kenan. Kasancewar dare ne kuma sun yi yan ciye-ciye, sai ta musu jollop din macaroni, ta kuma hada musu shayin chamomile.

Suna gama ci Madam ta musu sai da safe ta wuce daki, itama Nadiyar kayan da suka yi amfani dasu ta wanke kawai ta koma daki tayi shirin barci. Anty Lima ta bata aron kayan barci ta sanya. Ta zauna akan stool din madubi da earpiece jone a kunnenta suna waya da Aramide.

Labari take bata irin fadan da iyayen Mijin nata suka mishi akan irin abinda yake mata, sun kuma yi yarjejeniya dashi akan cewa duk ranar daya kara daga hannu ya tabata da sunan duka to a bakacin aurensu, kuma babu su babu shi, yace ya amince.

Nadiya ta tayata murna da kuma addu'ar Allah Yasa karshen abin kenan. Daga nan suka jima suna kara tattaunawa game da yadda zasu kara fadada wajen kasuwancinsu da kuma abubuwan da suke ganin zasu kara jawo musu kwastomomi. Lokacin da suka gama wayar tuni Anty Lima ta jima da yin barci. Ta kwanta a gefen katifar tare da yin addu'ar kwanciya barci ta kwanta. Babu jimawa barci ya kwasheta.

***

Tun sallar Asubahi da tayi bata koma barci ba. Ta dora karamar hijabi a saman kayan barcin jikinta ta fada kicin. Duk wani abu da za a bukata akwai a ciki, komi a shirye tsaf kamar dama can da mutane a cikinshi ba wai zuwa suke yi su tafi ba.

Babu bata lokaci ta hau aiki. Alkubus tayi niyar yi, don haka ta yi kwabin ta ajiye.

Kafin ya tashi ta ciro tantakwashi da naman kasa a cikin firiza ta hau tafasawa. A gefe guda kuma ta hau kwabin special Banana bread dinta. Kwararren kwas tayi akan shi ta online a kasar Indiya wanda ya dauketa kusan watanni biyu, bata taba yi ba amma yana daya daga cikin menu din da suka tattauna jiya da Aramide akan zasu kara shi a shagonsu.

Zuwa karfe takwas na safe ta gama cin karfin aikin sai abinda ba a rasa ba. Da yake abincin da dan yawa tayi, sai ta samu warmers masu kyau ta zubawa Hajja Umma nata, sauran kuma ta shirya musu akan dinning table.

Madam Zarah ta fito daga dakinta misalin karfe takwas da mintuna arba'in. Bathrobe ce kawai a jikinta sai tawul data nada a kanta, daga ganinta daga wanka ta fita.

Ta samu Nadiya a kicin tana kokarin dura kunun gyada a cikin flask. Taga tuni har ta kammala komi sai wanke-wanke dake jiranta.

Tace, "thank God Nadiya, barci ya daukeni na manta in tasheki ashe har kin kammala komi."

Nadiya tayi murmushi, ta juya tana fuskantarta, "Nda watu ya (Barka da safiya Mama)"

Tayi murmushi, "Kin tashi lafiya Nadiya, ya aiki?"

Tace, "Klewa slai (lafiya lau).

Sau tari ko waya suke yi da Madam din basu cika hausa ba sai Kanuri ko Turanci. Shi yasa itama idan ta je can din take kokarin juya harshenta.

Ta nuna mata inda ta ware abincin Hajja Umma din a cikin wani kwandon zuba abinci mai kyau, tace, "ga shi an hada komi. Wannan kunun kawai zan zuba shikenan!"

Ta matsa tana daga kwanukan tana gyada kai cike da gamsuwa, "good, good! Yayi sosai. Bari in kimtsa yanzu-yanzu sai in kai mata!"

Nadiya ta bita da kallo cike da mamaki lokacin data fita daga kicin din.

Iyaka saninta ita dai Hajja Umma da Madam din basa ga maciji a tsakaninsu. Amma yanzu shine Madam din da kanta ce zata je kai mata abinci da kanta ba aike ba? Ta jinjina kai a ranta tana fadin 'lallai in da ranka ka sha kallo!'

Cikin yan mintuna Madam din har ta fito cikin wata doguwar rigar Bubu ta shadda data sha dinkin surfani na yan Senegal. Bata daura dankwali ba sai gyale data dora a saman kanta daya fitar da sassalkan bakin gashinta da yayi kwance luf. Idan ka ganta a lokacin sai ka rantse Yayar Nadiya ce ba mahaifiyarta ba, saboda iya daukar gayu da kuma yanda yarintarta take fita kullum.

Nadiya ta tayata daukar kayan zuwa wajen motarta. Ta shiga gidan gaba ta tashi motar tana fadawa Nadiya kada su jirata saboda ba anan zata yi karin ba. Amma ta zubawa security dinta abincin, kuma su zauna a gidan har ta dawo saboda masu planning da decorations zasu je, tunda anan gidanta za ayi kamu da misalin karfe biyar na yamma. Nadiya ta amsa da 'to'

Ta koma tayi duk yadda tace, kafin ta wuce daki. Anty Lima tana bandaki da alama wanka take yi. Ta dauki waya ta kira Aysha ta fada mata idan da yadda za ayi ta kai mata akwatinta ko kuma kayan da zata sanya saboda kayan Anty Lima sun yi mata yawa. Aysha tace tunda ga direban gidansu

nan yaje kai wasu bakin Mamansu gidan Dada din, bari ta bishi sai ta kai mata kayan, ta mata godiya ta katse wayar.

Suna waya ita da su Maryam Anty Lima ta fito daga wanka. Ta zauna tana ta shafe-shafen mayuka da turaruka sai kace wadda zata canza fata, Nadiya dai tana ta binta da kallon mamaki. Ita sam wadannan shafe-shafen bata ganin amfaninsu.

Anty Lima ta kalleta lokacin data ajiye wayar akan katifa, tace, "Kanna (sister) sannunki da aiki, na jiyoki a kicin kina ta aiki wallahi barci da gajiya ne suka hanani tashi in tayaki."

Nadiya ta girgiza kai, "kai haba, babu komi wallahi. Wannan aikin a wajena kam ai ba komi bane, kada ki damu!"

Tayi dariya, tace, "kaji fa professionals. Bari inyi sauri dai inje in ci delicacy dinnan da zafinshi kafin ya huce, kin san yafi dadi!"

Tayi yar dariya kawai ta shige bandaki don ta watsa ruwa.

Allah Ya taimaketa kafin ta fito daga wankan har Aysha ta kai mata kayanta. Ta bude akwatin ta ciro riga da siket na wani material mai taushi. Da yake bashi da dankwali sai ta dora hular turban akanta.

Ta fita falo ta samu Anty Lima da Aysha suna hira. Ta zuba abincin da zata iya ci a plate, ta zuba kunun gyadar da yawa a cikin kofi ta kara madara da zuma a ciki, ta koma wajen su Aysha suka cigaba da hirar da ita.

Anan ne take jin cewa a ranar Safiya zata zo, don sunyi waya ma da Aysha tace mata suna hanya don a Kaduna ma suka kwana.

Anan kuma take jin ashe Madam hanyar bude wani babban Arena ne take yi a Kaduna mai dauke da manyan shaguna, kuma Hajja Umma tana da manyan Realtors a hannu da zasu iya taimaka mata. Ga kuma bugu da kari

kanin mijinta Marigayi shine Controller Janar na Najeriya. Da yake tana samun matsala wani lokaci wajen shigo da kayanta daga kasashen ketare, shima tana bukatarshi a gefenta yayinda kuma yaki bata hadin kai. Shine take so ta biyo ta bangaren Hajja Umma din.

Ta tabe baki a ranta tana jin babu dadi, dama a ranta sai da tace wannan mutuncin da Madam take yiwa Hajja Umma ba na Allah da Annabi bane, wani abu take bukata.

Ita kam sai take ganin bata san inda Madam zata kai son kudi da duniya ba, daidai gwargwado tana da kudinta da rufin asiri, haka ma mijinta, amma ita sam bata gani, kullum cikin neman kari take.

Maimakon tayi kokari ta gyara zumuncinsu da Hajja Umma daya tabarbare, su koma tsintsiya madaurinki daya kamar dai yadda yakamata su kasance, amma ita ta kudi da duniya take.

Ta san hakan dama ce sosai da zata iya kusantasu da Hajja Umma din, tunda ba cika shiga cikin al'amuransu tayi ba. Ta dauki shekaru da dama bata ji ance taje Maiduguri ba, haka ma bata ji ance wani yaje inda take ba.

Maimakon Madam tayi amfani da hakan ta kusantota jikinsu, a'ah, sai dai ta kusanta kanta da ita saboda wani dalili nata na daban.

Ta girgiza kai a ranta tana addu'ar Allah Ya kawo karshen wannan takaddama tasu.

Sun yanke shawarar kawai su yada zango anan gidan Madam din har Aysha da kuma Safiya da zata zo, saboda gidan Dada ma baki za a kai sosai. Amma tunda Madam ba baki zata ajiye anan ba, nan din zai fi musu dadin zama.

14.

Karfe biyu na rana suna zaune a farfajiyar gidan akan kujeru da lemuka a gabansu da fruits suna ci suna hirarsu, suna kuma kallon masu gyara da suke ta kaiwa da kawowa suna hada wajen. Aka bude gate wata galleliyar lafiyayyar Benz munch ta gangaro ta shiga gidan.

Suka tsaya da hirar da suke yi duka suka juya suna kallon motar da kuma wadda take kokarin fitowa daga bayan motar.

Ta zuro kafarta daya waje dake saye cikin wani hadadden sneakers na kamfanin Ryka, da bakin wandon jeans.

Safiya ta fito daga cikin motar bayan wasu yan mintuna, hannu daya rataye da yar madaidaiciyar jakar hannu, dayan kuma rike da wayarta dake makale da earpiece a kunnenta tana waya.

Wandon jeans din jikinta irin crazy dinnan ne, an tsattsagashi daga tsakiya. Sai dai maimakon ya nuna fatar jikinta, sai aka done kofofin ta yadda dai akwai tsagar amma kuma bata nuna fata. Da yake skinny ne sai ya bi ya lafe mata a jiki gabadaya. Rigar bubu din data sanya data tsaya mata a tsakiyar cinya ma ba wani abu na azo a gani ta boye a jikin nata ba. Ta sha kitsonta kalba kuwa ta attach, ta zubo mata har baya. Sai ta dora siririn gyale a saman kanta.

A shekaru na goma sha tara kacal a duniya, tauraruwar Safiya tana matukar haskawa. Irin yan gatan yaran nan ne na masu kudi da suka tashi cikin gata da dadin rayuwa, iyayenta sun tsaye mata, bata san Fadi-tashin rayuwa ba kamar yadda sauran wasu mutanen suke fama. Wannan yasa ta tashi a matukar sangarce.

Kasancewar ta fi Nadiya garin jiki da kiba, ko a yanzu zata iya kamo Nadiyar a tsayi da fadin jiki. Don ba kowa bane zai yarda da cewa Nadiya ta bata shekarun data bata ba.

Ta taka cikin kasaita da nuna isa, cikin gidan take niyar shigewa ba tare data kalli inda su Nadiya suke ba, direban daya tukata kuma yana binta da akwatunanta a baya.

Nadiya kasa daga baki ma tayi ta mata magana tayi, ta manta rabon data sanyata a cikin idanunta.

Sai Anty Lima ce ta daga baki ta kwala mata kira, sannan ta waiga ta kalli inda suke.

Ta tafi da sassarfa cike da murnarta suka rungume juna ita da Anty Limar cikin murna. Nadiya tana zaune tana kallonsu fuska dauke da dan murmushi. A ranta tana jin babu dadi da kuma tunanin ta yadda aka yi suka rasa shakuwar yan'uwantaka a tsakaninta da Safiya din.

Ta tashi tsaye tana kokarin rungumar Safiya din lokacin da suka gama murnar ganin juna ita da Anty Lima. Jinta take yi banbarakwai, kamar wata sabuwar halitta.

Ita kuwa Sophie ko a jikinta, ta rungumeta tana tsallen murna, "Kanna! Kitawu nasaraye (Yaya! Na yi kewarki!)"

Tayi murmushi cike da jindadi tana maimaita mata itama hakan.

Bayan sun gama murnar ganin juna, suka tayata shiga da kayanta ciki. Dakinta daban wanda dama a ciki ta saba sauka, kusa da na Madam. Tayi wanka ta ci abinci, suka sake fita wajen masu shirye-shiryen suna kallonsu.

Sai wajen karfe takwas na dare ma sannan aka fara gudanar da taron bikin. Zuwa lokacin duk sun shirya cikin ankon bikin da za ayi a ranar, jar lafaya ce suka sha mai taushi. Sophie duk ita tayi musu kwalliya da yake ta iya sosai. Nadiya kam bata bari an fente mata fuska ba, ta dai ce a mata kwalliyar sama-sama. Su dukansu sun fito sharr abinsu kamar ka daukesu ka gudu.

Wajen event din ya tsaru iya tsaruwa. Su Madam ana can a teburin iyaye, sai feleke ake da iyayi. Idan kaga irin kwalliyar da taci da adon data dauka sai kayi zaton ko ita ce uwar amaryar ko ma amaryar gabadaya. Amarya kuma ita da angonta suna kan teburi a zaune, angon yayi shigar wata galleliyar shadda ruwan madara da babbar rigar ta sha surfani tun daga sama har

kasa, da hularshi baka ta Dara. Amarya kuma tayi shigar lafaya itama ruwan madara, kitson da aka yi mata ya sauko a gefen fuskarta, hannu da kafa ta sha lallenta mai kyau. Kallo daya zaka mata kasan cewa ka ga yar asalin bare-bari. Sunyi kyau ita da angon nata kamar ka daukesu ka gudu.

Suna can a teburin da suka kebance kansu ita da Anty Lima da Safiya da kuma Aisha.

Nadiya bata yi wata kwalliya ba ta azo a gani. Ta nannade kitson da aka yi mata a cikin tafkeken ribbon ta kulle, duk da rashin fitar da gashin da tayi idan ka kalli gargasa da gashin daya kwanta a goshinta zaka san cewa tana da gashi.

Zaune tayi tana kallon Safiya data dame cikin kalar tata kwalliyar, kitson data yi duk ya barbazu, wani ya watsu a gefen fuskarta, wani kuma ya sauka a bayan wuyanta ya gangaro zuwa saman kirjinta. Selfie kawai take watsawa kanta a wayarta. Nadiya ta girgiza kai ta mayar da kanta ga su Anty Lima da suke hira.

Ko awa daya cikakkiya ba ayi ba da fara sha'anin taji har ta fara kosawa da zaman wajen. Dama can ita ba ma'abociyar halartar irin wadannan al'amuran bane.

Zuwa lokacin ita kadai ta rage a teburin nasu, tunda aka kira yan'uwan amarya filin rawa don su taka duk suka tashi suka barta da sauran daidaikun mutane da basu shiga filin rawar ba.

Ta dauke idanunta daga kan Madam da Safiya da suka dage tun karfinsu suna zabga rawa kai kace wasu shakikai ne. Don Safiya ma har kama kafadar Madam din take yi tana wani girgiza da kanainayewa kamar wata macijiya, ita kuwa Madam baki ya ki rufuwa, sai like take mata da kudi.

Tayi kwafa a sanyaye bayan da suka hada ido da Madam ta daga mata hannu kafin ta juya ta cigaba da kwasar rawarta, ta dauki kofin da suka tsiyaya lemu a ciki ta kai baki ta kurba. To me zata ce? Fadan da yafi karfinka ai dole ka maidashi wasa.

Zuwa can taji wayarta tana vibrating a cikin karamar pouch data rike a hannunta. Ta zaro wayar ta duba, ganin Rabi'ah ce mai kiran yasa ta tashi ta bar wajen, musamman data ga ta ajiye mata missed calls har uku tasan kiran gaggawa ne.

Can waje ta fita saboda har a farfajiyar gidan ana jiyo sautin kidan da yake tashi. Layin babu kowa sai motoci da suka yi jere suka kewaye wajen iri-iri.

Ta matsa gefen wata farar Sedan ta dannawa Rabi'ah kira. Tana fara shiga ta daga. Tun ma kafin su gaisa ta fara watsa mata tambayar idan za ayi velvet cake da kuma whipped cream icing ya za ayi? Kuma me da me ya kamata a sanya?

Tayi yar dariya tana tarar numfashinta, "haba Hajiya dan dakata mu gaisa mana tukuna! Saurin me kike yi?"

Tace, "wayyo Anty Nadiya Sorry, wallahi mantawa nayi. Kin ga second batch ne fa nake yi na cake din saboda na farkon bai yi ba yadda ake so, kuma nayi pre heating din oven dina already."

Nadiya tace, "to yanzu dai mu fara gaisawa tukun. Kin dai san bana son irin wannan wayar ko?"

Cike da saduda tace, "na sani Anty. To Assalamu alaikum, ina yini?"

Tayi dariya tare da amsawa. Tambayarta tayi abubuwan data sanya a cikin cake din, kafin ta mata karin bayani da gyara a inda ta kuskure. Hirar tasu bata yi tsayi ba suka yi sallama saboda Anty Lima data dinga danna mata kira.

Ta katse kiran Rabi'ah tare da amsa na Anty Lima dake kan kira a lokacin. Tambayarta tayi ko tana ina? Tace mata waje ta tafi amsa kiran waya amma ga ta nan dawowa.

Ta juya cikin takun sassarfa zata koma wajen bikin. Hankalinta yana kan kokarin mayar da wayarta cikin jaka lokacin data taka kafarta cikin gate din gidan.

Daidai lokacin shi kuma ya kawo kai zai fita, suka yi karo.

Kasancewar shi ya dan duka kansa kasa saboda kofar jikin gate din ba tsayi ne da ita ba, suka hada goshi ji kake garamm! Gabadaya sai da taji duniyar tana juya mata saboda buguwar da kanta yayi. Bata san lokacin da wayar hannunta ta fadi ba, ita kuma tayi taga-taga tana shirin faduwa saboda wanda suka yi karon dashi da karfinshi ya fito. Da ba don shi ba kuma da sai ta kai kasa din.

Yayi azamar sanya hannu ya rikota, bakinshi da nata na furta 'Hasbunallahu wa ni'imal wakil' a lokaci guda.

Ta samu ta tsaya akan kafafunta, hannu dafe da goshi, ta daga idanu tana kallon mutumin da niyar watsa mishi tambayar baya kallon gabanshi ne? Shi kuma bakinshi yana furta, 'sorry!' a lokaci guda.

Duk sai suka tsaya suna kallon juna cike da mamaki. Maganar da tayi niyar yi ta makale mata a makoshi.

Shi kuwa gira ya daga, cike da wannan izza da rainon wayau da bata manta ba. Yace, "such a small word huh? Ke idan kina tafiya baki duba gabanki ne ko me? Ko kina da matsalar idanu ne?"

Ta bata rai tana hadiyar wani yawu na takaici, wayarta ta duka ta dauka ba tare data dubata ba. Ta daga kai tana kallonshi fuska a cune, "ina ga dai naka idanun ne suke bukatar a tambayi ko suna aiki ko basa yi. Saboda in case baka gani, kai ka kawo min karo ba tare da ka duba inda kake zuwa ba. Kamar yadda kayi mun a wancan lokacin!"

Ta ratsa shi ta shige gidan rai a bace, bata cika son yin tsiwa ba saboda tasan bata da kyau idan ta fara. Taimakon da Allah Yayi mishi daya a wajen

biki suke, inda bata son ja wa kanta attention. Amma da ba don haka ba da sai ta wankeshi tass ko ta huce takaicin daya kara kunsa mata a karo na biyu. Babu ma kamar data duba wayar hannunta taga tayi raga-raga, gashi bata sanya mata screen guard ba. Ji tayi kamar tayi me! Ta dai cije ta karasa wajen su Anty Lima inda suke zazzaune suna ta dambe da naman kaji da lemuka da aka shirya bayan fitarta.

Ta zauna tana harare-harare ita kadai. Saboda bacin rai ko kallon naman bata yi ba duk da yadda kamshin naman yake kai mata.

An cigaba da gudanar da shagalin biki har zuwa wajen karfe goma sha biyu na dare. Duk da haka basu samu sukunin tafiya makwanci ba sai wajen karfe daya na dare. Saboda sai da suka taimaka aka rage tarkacen dake wajen duk da wadanda suka shirya event din su suka yi aikin, amma Madam tace su sa musu hannu don a samu a gama da wuri. Don haka a matukar gajiye suka kwanta. Da kyar ta iya tashi tayi sallar asubahi.

Ta koma ta kwanta kenan, a ranta tana raya yadda zata kai har karfe goma ko sha daya ma bata tashi ba, sai ga Madam ta kwankwasa musu kofar dakin.

Ta tashi zaune tana kallon Madam din wadda har lokacin kayan barcine a jikinta, daga alamun fuskarta kuma ko sallar asubahin ma bata kai ga sallata ba. Ta amsa gaisuwar da suke mata a tsaitsaye, da alama sauri take yi.

Nadiya take kallo, "Nadiya ya za ayi ne? Jiya mantawa nayi fa in fada miki yau ma za a kaiwa Hajja Umma abin kari. Ina ga ai za a samu a hada ko?"

Jikinta a matukar gajiye yake, bata kuma tunanin zata iya aikin da Madam din ta bukata. Sai dai sanin halin Madam din, tasan ba tambayarta take yi ba, umarni ne kawai take bata, yasa ta daga baki tace, "to me za a dafa ne?"

Tace, "kawai ki dafa duk abinda ya dace da abinda dattijuwa zata ji dadinshi. Amma ki sake yin kunun gyada saboda taji dadin na jiya sosai."

Nadiya ta amsa da 'to!'

Ita kuma ta juya ta tafi.

Ta tashi da kyar ta nufi kicin din, Anty Lima ta bi bayanta zata tayata aikin. Duk da yadda taso ta koma ta kwanta, ki tayi. Don haka suka shiga tare.

Tuwon shinkafa ta malmala da miyar agushi ta yi kunun gyadar. Ta hada komi ta zuba a mazubai masu kyau ta ajiye. Sai ta kara yi musu couscous da sauce din kifi don tasan ba lallai Madam da Safiya su ci tuwo da safe ba.

Bata ma iya tsayawa karyawa ba saboda tsabar barci da take ji, ayaba kawai ta iya ci da tuffa, suka koma suka kwanta. Bata san lokacin da Madam ta bar gidan ba. Sai can wajen Azzuhur da suka tashi, suke jin tana can gidan Hajiya Umma, yau har da Safiya suka tafi.

Kasancewar shagalin ranar na yamma ne, da suka yi sallah suka ci abinci, sai ta dauki sauran tuwon da suka yi suka tafi gidan Dada. Acan suka shirya tare da su Aysha, suka tafi can wani wajen tarar baki na musamman inda a can ne za ayi Mothers Eve.

Suka fita daga motar Anty Lima ita da Aysha da Anty Lima din da wata cousin dinsu diyar kanwar mahaifiyar Anty Lima din, Zainab.

Wata tsanwar atamfa suka shiga, Nadiya an mata dinkin gown wadda ta bi jikinta sosai ta lafe. Duk da cewa ba wani matseta tayi na azo a gani ba, amma yanayin yadda ta fitar mata da surarta yasa data tashi sanya gyale, sai ta samu mai yalwar fadi kuma mai duhu ta yafa. Su Anty Lima ma sun fito gwanin kyau cikin nasu ankon. Ita skirt tayi straight, an tsaga mata shi daga baya. Nadiya har maganar yadda sharabarta take a waje ta mata, amma tace mata hakan ba wani abu bane, ai ta ma yi shigar mutunci. Ta sanya rigarta half gown wadda shape dinta ya fita da kyau, ta kuma yi mata matukar kyau. Ita da kanta ta kashewa Nadiya daurin kallabi mai kyau. Suka jera suka shiga wajen cikin taku na daukar hankali.

Gab da zasu shiga wajen da ake event din suka ci karo dashi cikin zugar matasan samarin danginsu, diyan yan uwansu Madam.

Ta duba iya dubawa, ita dai ta kasa gano ta ina suka hada iri da wannan dan wulakancin mutumi. Ta kasa daurewa dai sai data daga baki ta tambayi Anty Lima.

Ta saci kallon samarin da duk suka bisu da kallo sai kace sun ga wani danyen nama.

Anty Lima tace, "wai wancan? Nima gaskiya ban wayeshi ba. Amma cikin su AbdulHalim nake ganinshi. Watakila ko abokinsu ne tunda ba cikin zugar angwaye yake ba."

Zainab dake sauraronsu tunda suka fara maganar tayi caraf ta amshe zancen. Tace, "wai wancan haddaden gayen? Ance fa babban dan Hajiya Umma ne. Bata taba zuwa nan dashi ba sai wannan karon shi yasa duk ba a san shi ba!"

Suka kalleta da mamaki, Anty Lima tace, "kai jama'a! Dama Hajiya Umma tana da babban da kamar wannan? Ashe matar ba ta yau bace!"

Nadiya tayi dan murmushi. Zainab kuwa tace, "hummn! Aikuwa dai danta ne. Naji an ce ya kama naira har ya gaji. Yanmatanmu fa duk sun rikice wallahi, ance har da masu zarya gidan Hajiya Umma ko da wadda zata dace ya kyasa!"

Abin ma sai yaso ya bawa Nadiya dariya. Tayi murmushi tana girgiza kai, a ranta tana fadin lallai kuwa da aiki ya gansu. Don kuwa dai ita bata ga abin so a wajen wannan dan rainin wayau din ba da jiji da kai. Ai ko a kafa aka daura mata shi wallahi a sukwane zata cireshi ta yar!

15.

Kwanaki fiye da biyar ana ta shagalin biki kala-kala abin kamar ba zai kare ba. Har dai zuwa ranar litinin da aka daura aure. Washegari kuma aka tafi kai amarya gidan angonta. Su Anty Lima da Safiya su ne tan rakiya, ita dai ta lafe a gida tace sai sun dawo. Sun kuwa koma cike da zazzaudin gidan da aka kai amarya da santinshi. Ita dai tace Allah Ya bada zaman lafiya.

Har kuma zuwa wannan ranar kullum ita take dafawa Hajiya Umma abin kari.

Wani lokacin ma har da dare Madam ta kan sa tayi gashin kaza ko nama akai mata, ta kuma hada mata lemu na lemun zaki da kankana da take yi ko kuma na zobo akai.

Ranar Alhamis ta tashi da azumi a bakinta. Tunda asubahi da suka gaisa da Madam ta fada mata ranar Assabar take son komawa gida.

Tace to Allah kaimu. Ita kam sai ta kai litinin, saboda Alhamis ta sama Safiya zata wuce America.

Karfe goma na safe suka fito ita da Anty Lima, itama ranar zata koma can gidansu, zata sauke Nadiya a gidan Anty Hauwa wadda ta dawo jiya laraba.

Tun daga daki suke jin sautin kida yana tashi kasa-kasa. Sai da suka fito falo sannan suka ga ashe abin ba na wasa bane.

Safiya ce a tsakiyar falon saye da wani wando baggy, da karamar rigar top mai karamin hannu, kitson kanta ta barbaza shi ya zuba a bayanta da gefen fuskarta. Ta kure volume jikin speakers din falon, ga ring light nan ta tsayar tana ta tikar rawar 'Mi Gente' sai wani girgije-girgije take da juye-juye.

Abin ban takaicin shine yadda Madam tana can kan dinning a zaune da abincin karin da Nadiya ta hada musu tana ci hankalinta kwance, sai ma thumbs up da take jefawa Safiya din idan tayi wani juyin daya burgeta.

Suka ratsa ta gefenta suka wuce ko alamun ta gansu bata nuna ba. Nadiya tana so tayi magana, tsoron abinda zai kai ya kawo ya hanata. Dole ta kame bakinta ta bame.

Suka je suka yi sallama da Madam din. Ita kanta Nadiyar bata tunanin zata dawo gidan idan ta tafi, watakila gidan Anty Hauwa zata yi zamanta har zuwa jibin, ko ta koma gidan Dada kawai. Kayanta ta dawo ta dauka ko ta tura Aysha ta dauko mata.

Rayuwar Madam da iyalanta ba abinda idanunta zasu rufe bane ta nuna kamar bata gani ba. Don kuwa rayuwace da zubinta da tsarinta yafi kama dana mutanen Turai ba wadanda karatun Allah da Annabi ya ratsa ba.

Haka za ka tsinci uwa da diya ana hira ana shan hannu kamar abokai, wannan duk sharar fage ne akan ka duba ainihin menene ya sanyasu dariyar. Wadda yawancinta akan tik-tok da Safiya din take yi ne inda take da mabiya masu tsananin yawa. Kuma yawanci raye-raye ne take yi da bin wakoki, sai kuma bangaren fashion da take tabawa. Tana nuna trending abubuwa dake tafiya da zamani da sauransu. A cikin rawar, da kuma fashion din, Nadiya bata ga na zaba ba, tunda dukkaninsu babu wanda zaka gani da shiga ta mutunci ko wadda musulunci ya bada umarnin ayi.

Kuma babu wanda Madam din ta taba daga baki tace ba daidai bane, sai ma kara mata karfin gwiwa da take yi da kuma yaba mata.

Ga rashin iya magana da girmama na gaba a wajen Safiya din. Ita kanta Madam bata tsira ba a wajenta balle su Nadiya yan karere. Ana hira sai kaga ta kalli uwar wai tace mata, "Mom you are silly!" ko kuma Idan wata maganar tayi kaji tace, "this is so stupid!"

Kuma da rana daya hakan bai taba bata ran Madam ba. Ko a fuska bata taba nuna mata ba. Shi yasa Nadiya ta kame kanta waje daya, don bata bukatar raini ko kadan. Musamman tun watarana data taba yiwa Safiyar magana akan gashin attachment data sanya a kanta da kuma wani wando mai kama da 3 quarter data sanya wanda bai saukar mata idon sawu ba wai zata tafi unguwa a haka. Ta kalli Nadiya din kerere tace, "gaskiya ki daina shiga

harkata kin gane? Iyayena ma da suka haifeni basu takura ni, duk abinda naga dama shi nake yi, don haka kada ki kara sanya min baki a cikin al'amurana! Ina ruwanki da ni ne? Kiyi rayuwarki inyi tawa!"

Taja tsaki ta kara gaba tana wasu maganganu cikin turanci. Tun daga ranar Nadiya ta kai na mujiya ta zuba mata.

Madam ta kalli Nadiya lokacin da suke kokarin wucewa bayan sun mata sallama.

Tace, "kinga na manta shaf! Ki shirya anjima da dare zamu je mu gaida Hajiya Umma."

Kafin ta maida mata da martanin wani abu, Anty Lima tayi tsalle cike da murna ta dafeta, cewa take yi, "Mommy don Allah nima zan je kinji?"

Madam tace, "to shikenan, amma fa ki shirya da wuri kinji?"

Ta gyada kai cike da murna, yayin da Madam ta juya ga Nadiya tana kallonta, tace, "ke kuma ki kimtsa cikin shiga mai kyau. Na sanki da rashin son daukar ado, amma yau dai gaskiya kiyi shiri da kyau, kina ji na?"

Bata iya ce mata komi ba sai kai data daga mata.

Suka wuce ita da Anty Lima.

A mota take bayyanawa Anty Limar mamakin wannan hali na Madam da yadda take shigewa Hajiya Umma.

Anty Lima ta dan kalleta rabin hankalinta a kan tuki. Tace, "ke na fa ji ana kishin-kishin din da gaske Hajiya Umma mata take nemawa danta. Ita kuma Madam shagone babba suke son budewa a nan Kaduna, to kuma dai basu da takamaiman mai shige musu gaba a wannan harkar. Ita kuma Hajiya Umma tana da mutane sosai a ofishin haraji da harkar filaye. Naji ma an ce kamar dan nata yayi aiki da Ministry of Tax."

Nadiya ta jinjina kai tana dan tabe baki. Anty Lima ta cigaba da cewa, "naji an ce ma kokarin neman kujerar Gwamna fa yake yi. To a yadda dai naji, ita

Madam tana son yin amfani da connections din Hajiya Umma ne, ita ma Hajiya Ummar tana nemawa danta diyar da take da connection ne da kuma mutanen da zasu goyawa danta baya a harkar siyasarshi, kin gane?"

Nadiya ta gyada kai, ba wai don ta fahimta din ba.

Anty Lima ta kalleta dai-dai tana danna hancin motarta gidan Anty Hauwa, tayi parking. Nadiya na kokarin fita ta dakatar da ita ta hanyar tambayarta, "kin san dalilin abincin da kike dafawa ana kaiwa Hajiya Umma kullum kuwa?"

Nadiya ta kalleta cike da alamun tambaya, "ba na tara bane da bakunta?"

Anty Lima tayi wata irin dariya tana girgiza kai, tace, "gaskiya you are so naive! To bari in fada miki, wannan abincin na kamun kafa ne. Don kuwa a yadda nake jin labari a gari, shine Madam ta sanya 'ya'yanta cikin jerin matan da Hajiya Umma take nema. Ki kuma tsaya da kyau kiyi tunani, duk cikin danginmu wa yake da exact abun da Hajja Umma take dashi bayan Madam? Tana da manyan mutane a hannu, tana da talakawa masu yawa da idan tace su zabi wane zasu zabeshi a guje. Musamman a yankunan Kaduna da nan wajajen Jos saboda tana yawan tallafawa mutane."

Nadiya ta ja numfashi tana kallonta alamun tambaya zane baro-baro akan fuskarta, tace, "yanzu duka meye amfanin wadannan abubuwan da kike fada min? Don bana tunanin ni dai na fahimceki!"

Anty Lima ta dafa kafadarta, tace, "saboda bayan Safiya akwai ki! Kin kuma fi ni sanin cewa idan ta kama, a tsakanin ku biyun nan fa za a iya zabar daya. I'm just telling you ne saboda kada abin yazo miki as a shock idan muka je can, don naga Madam din bata da niyar sanar dake komai!"

Nadiya tayi zaune a wajen ta kasa ko daga kafarta saboda tsananin mamaki da tu'ajjibi. Jikinta yayi sanyi kamar wadda aka watsawa ruwan kankara.

Kafin daga baya ta motsa da kyar cikin rashin kwarin jiki ta bi bayan Anty Lima da tuni tayi nisa.

Ta auna duk awon da zata yi taga kwata-kwata zancen ma ya girmami kwakwalwarta. Sai kawai ta watsar da komi ta barsu a inda Anty Lima ta furtasu.

Shigarsu gidan Anty Hauwa da irin tarar data musu yasa ma gabadaya sai ta karasa mancewa da komi.

Yinin nan guda haka suka yi shi a gidan. Anty Lima taje gida ta dawo can wajen Magriba.

Bayan ta sha ruwa, sun cika cikinsu sunyi nak, suka yi sallama da Anty Hauwa din suka juya.

Suka samu tuni har Madam ta kammala shirinta don haka suma a gurguje suka fada daki suka shirya.

Anty Lima ta saka wata doguwar riga ta atamfa gown mai kyau, ta yafa mayafi madaidaici ba tare data daura dankwali ba. Nadiya kam Abaya ta sanya maroon kirar kasar Turkiyya. Tayi nadin gyalen abayar a kanta. Sai ta fito das gwanin kyau duk da cewa ba wata kwalliya ta azo a gani ba ta yi. Musamman da yake rigar ta bi jikinta das. Yanayin jikinta mai kiba dai-dai wa dai-da yasa mawuyaci ne ta sanya kaya basu amsheta ba. Tunda tana da kira da zubi da tsarin jiki mai kyau.

Suna gama sallar isha'i suka fita.

Safiya yau riga da siket aka sanya na leshi. Ta ci kwalliya kamar zata gidan biki. Ta nada daurin dankwalinta aka ya zauna daras kamar inji ya daura mata. Suka fita su duka suna ta zuba kamshi wane kamfanin turare.

Anty Lima da Nadiya suna gaba Anty Limar na tuki a cikin motarta, Madam da Safiya na baya sun hade kai suna ta kus-kus baka jin me suke cewa. Suka dauki hanya suka tafi.

Gidan da aka yiwa Hajja Umma masauki a can main house din family dinsu yake. Unguwa ce guda da suka ware ya zamana kusan duk su suka mamayeta sai daidaikun mutane da ba a rasa ba.

Madaidaicin gidane, flat mai dauke da dakuna uku sai kicin da kuma sitting room saboda shan iska.

Aka yi musu iso zuwa cikin falon inda suka samu Hajiya Umma din a zaune akan kujera mai daukar mutum biyu.

Duk yadda Nadiya take tunanin ganin matar sai ta ga ashe ganinta ya fi jinta. Yadda taji ana 'Hajiya! Hajiya!!' Sai tayi tunanin wata babbar mace zata gani, sai ta ga ashe girman nata ba wani can bane. Sai taga magidanciyar mace mai cike da izza da takama da mulki da dukiya. Kwarjininta ya cika falon. Duk rawar kan Safiya dana Madam sai gasu sun shige taitayinsu. Suka zube a kasa kan gwiwoyinsu suna gaisheta.

Ta amsa musu fuska kadaran-kadahan, babu alamun wasa balle a ga fuskar raini a tattare da ita ko kadan.

Sai da tayi musu umarnin su zauna sannan ne suka nemi kujeru suka zauna.

Nadiya dai ta zauna a darare kamar ace mata 'arrr!' ta ruga. Falon take karewa kallo, a sace kuma tana karewa Hajiya Umma kallo wadda suke hira da Madam. Kodayake Madam din ce take kokarin janta da hira ita kuma tana amsawa da kyar kamar wadda ake tursasawa.

Wannan mulki da iko sai ya daurewa Nadiya kai. Mace sai kace wata jinin sarauta? Ta girgiza kai kawai cike da Al'ajabi. Lallai fa gaskiyar bahaushe da yake cewa wai gaba da gabanta aljani ya taka wuta. Ita dai kam yau taga hakan da idanunta. Har Madam ce take zama tana yar murya a gaban wani? Lallai in da ranka zaka sha kallo.

Aka shigo musu da kayan motsa baki da ruwa da lemuka. Ta tsiyaya ruwan a cikin kofi kadan tana kurba saboda har zuwa lokacin cikinta a cike yake. Tun kafin su dade a wajen amma tuni har ta kosa a tashi.

Tun kafin ya karaso cikin falon, kamshin nan nashi ya sanar da zuwanshi. Yayi sallama da tausassar muryarshi, duk suka amsa.

Sai lokacin taga alamun murmushi akan fuskar Hajiya Umma. Ta daga kai tana kallonshi, tace, "yauwa Babangida! Yanzu nake kokarin aikawa a kiraka. Karaso ka zauna!"

Ya zagaya ta bayan kujerar da Nadiya take zaune, kamshin nan nashi more prominent, duk kinta, sai data lumshe idanunta tana kara shakar kamshin.

Ya zauna a kujerar kusa da Hajiya Umma hankalinshi kacokam a kanta. Yace, "gani Ummah!"

Ta mishi nuni da su Madam, "Ga Zahra'u da 'ya'yanta da nake fada maka, ku gaisa!"

Sai a lokacin ya daga kai ya kallesu daya bayan daya. Kallon nashi yaso yayi tsayi akan fuskar Nadiya, kafin ya janye ya mayar kan Madam. Ya dan zame daga kan kujera ya gaisheta ta amsa fuskar nan cike da fara'a.

Dan dakatawa yayi yana kallonsu, hakan yasa suka bude baki suna gaisheshi. Nadiya dai baki kawai ta dinga motsawa har aka gama gaisuwar. Daga nan ta bame bakinta ta daure, yar hirar da yaso yaja su da ita bata yi tsayi ba ta mace saboda babu abin cewa.

Falon ya dan yi shiru na yan mintuna. Sai Hajiya Umma ta sauke kallonta akan Safiya dake danne-dannen waya. Tace, "'yata Safiya! Yau ko a gidan nawa za a hada min kunun da ake kawo min? Kinga mai son kunun nan a zaune, tun jiya yake mita da tambayar kunun gyada!"

Falo sai yayi tsit! Aka hau kallon-kallo tsakanin Madam da su Nadiya. Safiya ta fara raba kallo tsakanin Hajiya Umma da Madam cikin alamun tambaya. Madam kam sai ta hau kame-kame, in ba don dare ba, Nadiya sai ta rantse da Allah ko zufa ce ta gani tana yanko mata.

Hajiya Umma ganin shiru babu mai shirin motsi yasa ta kalli Madam cikin alamun tambaya. Tace, "Zahra'u diyar taki ko kunyata ne take ji?"

Madam ta dan zaburo, "ah! eh... Dama!! Nadiya ko ke zaki shiga ki dama mata kunun?"

Ta juya tana kallon Hajiya Umma cikin dariyar yake, "dama... dama gani nayi Nadiya ta fi ta iya kunun shi yasa...! Nadiya tashi mana!!" Ta yi maganar cikin daga murya ganin Nadiya din bata da alamun motsawa balle ta tashi.

Da sauri ta tashi itama tana inda-inda, "ina ne... kicin din...?"

Hajiya Umma tana shirin daga baki tayi magana, Babangidan nata ya tashi da sauri, "bari in nuna mata. Dama ruwa na shigo zan dauka saboda na dakina ya kare!"

Ya wuce yana kallon Nadiya a kaikaice, "yauwa nan ne!"

Jiki a sanyaye ta bi bayanshi tana satar kallon Madam dake ta raba idanu. Gabadaya ta kasa gane me yake faruwa ne balle ta iya rarrabe tsakanin fari da baki.

Kicin din nasu kusa da kofar shiga yake. Ya tura kofar ya shiga tana bin shi a baya. Kai tsaye wajen firjin ya nufa ya daga ya dauki ruwa, ya fasa ya juya ya jingina da firjin din yana sha. Ya daga gira ganin har lokacin tana a tsaye, ya mata nuni da dirowa, yace, "ki daga nan, zaki samu duk abinda kike so anan. Amma ki dan dama kunun da yawa saboda wanda ake bani baya isa ta."

Ta kalleshi, a ranta tana mitar 'rashin ta idon wannan mutumin!' amma a fili sai kawai ta wuceshi ta kara gaba ta hau dage-dagen drawers din tana fito da kaya.

Tana jinshi ya gama shan ruwan ya jefa gorar cikin dustbin, amma maimakon ya fita sai ya tsaya. Ita kuwa tayi kamar bata jin shi ta cigaba da gudanar da ayyukanta.

16.

Tana jin shi yana ta yan kaiwa da kawowa a cikin kicin din ba tare da yace mata uffan ba, itama bata furta mishi din ba. Ya gaji da bin-binintun shi dai ya bar kicin din.

Ta kammala komi cikin kankanin lokaci tunda suna da komi a ajiye. Ta dauko flask mai kyau ta fara zubawa a ciki. Sai gashi tsulum! kamar wanda aka jefo daga sama. Yana ganin ta kammala shima ya sungumo wani flask din wanda ma ya fi wanda ta dauka girma, yace, "yauwa, dan zuba min anan. Ai dama ke nake ta jira tun dazu don kada ki juye duka!"

Bata ce mishi komi ba ta warci flask din ta fara zuba mishi. Data zuba kamar rabi zata maida ta rufe, yayi sauri yace, "a'ah, cikawa zaki yi. Wannan ai har da safe ma zan sha kayana."

Ta watsa mishi harara a kaikaice, ta cika mishi ta ajiye flask din a gefe. Ya dauki kayanshi shi kuwa yayi gaba babu ko na gode. Ta ja dan siririn tsaki kafin ta cigaba da abinda take yi.

Bata bar kicin din ba sai data wanke duk abinda tayi amfani dashi, ta gyara wajen kamar ba ayi komi ba. Ta dauki flask din da kofuna ta koma falo. Ta

samesu duk sunyi jugum-jugum kamar a gidan makoki, banda karan TV dake aiki baka jin komi.

Ta karasa ta ajiye kayan a gaban Hajiya Ummah, ta tsiyaya kunun a kofi ta mika mata, ta koma ta zauna.

Sai data shanye kofi daya ta kara zuba wani ta sha rabi, sannan ta kalli Madam, ta kirata da murya mai nuna rashin wasa, "Zahra'u!"

Madam ta amsa cikin sagewar gwiwa.

Tace mata, "'ya'ya, 'ya'ya ne, sannan kowa da irin baiwar da Allah Yayi masa. Don haka babu zancen wai ace wance ce tayi kaza alhali kuma ba ita bace. Wannan tauye hakki ne da rashin gaskiya, kada ki sake yin haka kina jina?"

Madam ta gyada kai kanta a kada. Nadiya tasan kunya ce da takaici suka mata rubdugu. Ita kuwa Hajiya Umma ko a jikinta, sai kai data gyada.

Tace, "zaku iya tafiya. Duk abinda ake ciki zaki ji daga gareni."

Ta daga murya ta kira daya cikin yan aikinta, sai gata ta taho dauke da jaka ta mikawa Hajiya Umma. Ta amsa ta sanya hannu a ciki ta fito da envelope-envelope ta mikawa su Nadiya kowa dai-daya, suka amsa suka mata godiya. Daga nan suka mata bankwana suka tafi.

A mota ma haka suka tafi babu mai cewa uffan har suka karasa gida. Suna zuwa kuwa kowa makwancinshi ya nufa.

Sai da suka shiga daki suka daga abinda Hajiya Umma ta basu. Kudi ne yan dari biyar-biyar sabbi gal, kowa dubu hamsin. Nadiya ta nade su ta sanya a jaka, ta fara shirin kwanciya barci.

Har ta kwanta, suna cikin yin waya da su Maryam, Anty Lima data fita daukar ruwa kicin ta shigo dakin da saurinta tana tsallen murna.

Nadiya ta kashe wayar tana kallonta fuska dauke da dan murmushi, "ke kuma lafiyarki lau kuwa yau?"

Ta zauna a gefen katifa har lokacin bakinta dauke da murmushi, tace, "ke Madam naji tana waya da Hajiya Umma yanzu!"

Ai sai Nadiya ta gyara zama tana kallonta, "ya aka yi, me ya faru?"

Tace, "abin fa ya fado kanku ku biyu. Naji tana ce mata cikin ku biyun dai za a dauki daya!"

Sai ta dan yamutsa fuska, "wane abu? Kuma kamar ya cikin mu biyu za a dauki daya? Ban gane ba!"

Anty Lima ta dan ja tsaki, "ke fa matsalata dake kenan wallahi, baki cika tsayawa ki fahimci al'amura da kyau! Ina nufin a jerin matan da ake shirin zabarwa Habib, dan wajen Hajiya Umma, to ke da Safiya aka zaba. Yanzu a tsakanin ku biyun ne za a zabar mishi daya!"

Ta dafe kirji tana kara gyara zama, "Innalillahi wa Inna ilaihi Raji'un! Me kika ce?!"

Anty Lima sai ta tsaya tana kallonta kamar wata wadda wani sabon kai ya tsiro daga jikinta, ta danna mata harara, tace, "to menene a ciki? Sai in ga hakan ai ba wata matsala bace. Ina ganin Habib ai mijin aurene na nunawa sa'a. Yana da hankalinshi, yana da sana'arshi, ga iliminshi, don naji ance har phD yayi. To kuma me za a nema a wajen miji da yafi wannan? Ko kuwa matar da yake da ita ne zata tsorataki?"

Ta ja dan siririn tsaki, "ba zaki gane bane wallahi Anty Lima. Gayen ne kwata-kwata bai min ba, kuma fa ni har ga Allah ni fa har yanzu ban shirya yin wani aure ba. Idan ma auren ne a barni inyi shi da wanda nake so. Amma ni don wata matarshi meye hadina da ita? Tayi rayuwarta inyi tawa. Kawai auren da shi dinne bana tunanin zai haifarwa wani da mai ido."

Anty Lima ta tabe baki, "aikuwa sai kiyi ta fatan kada ta fada kanki!" Tayi kwanciyarta ta bar Nadiya tana canki-canka.

Itama kwanciyar tayi, amma gabadaya sai barci ya kauracewa idanunta sam. Tsoro kai tsaye ya bi ya mamaye mata zuciya. Tunaninta daya idan fa aka ce ta auri wannan mutumin me zata yi? Bata tunanin gaskiya zata iya zaman aure da mutumin da bata so kuma bata sani ba, kai ina! Ba zai yiwu ba. Amma kuma idan ta duba ta wani bangaren taga alamun ita kanta Madam din ta fi bukatar ayi da Safiya, sai taji dan sanyi a cikin ranta.

Tunda idan ba da Safiya take so ayi ba, me yasa zata yi karyar Safiyar ce take girkin da ake kaiwa Hajiya Umma?

Da dai taga barcin ba zuwa zai yi ba, sai ta tashi kawai ta dauro alwala ta fuskanci alkibla.

Ranar rayuka uku kwana suka yi basu runtsa ba. Ita tana fata da buri da addu'ar Allah Ya tsallakar da ita wannan ibtila'i da yake kokarin tunkarota. Wata tana addu'ar Allah Ya mallaka mata Habibullahi Makama. Shi kuma yana addu'ar Allah Ya mallaka mishi daya daga cikinsu.

☆☆☆☆☆☆

Washegari ta shiga dangi don yin sallama dasu. Tunda safe data tashi ta hade yan komatsanta waje daya, Anty Lima ta bata jaka mai fadi ta sanya sauran kayanta da basu shige cikin akwatu ba a ciki.

Itama Anty Limar kayanta ta hade saboda a ranar zata koma gida.

Suka yi sallama da Madam tun da safe din saboda tasan ba lallai su kara haduwa ba. Madam din bata mata maganar komi ba game da abinda ke faruwa, don haka itama bata ce mata komi din ba. Har kudin mota ta tura mata ta account, Nadiya tayi godiya.

Da zasu rabu da Safiya ta dan mata wa'azi da hannunka mai sanda game da rayuwar duniya. Musamman yanzu da take shirin shiga cikin turawa ta zauna a cikinsu. Nadiya tasan abin na Safiya sai abinda ya karu don kuwa ba raguwa zai yi ba.

Sai can yamma ta dire a gidan Dada, tunda data gama zagayen wadanda zata zagayawa zuwa fitowar masallaci, sai ta dire a gidan Anty Hauwa. Itama da zata taho haka ta hadata da atamfofi har kala biyu manya da takalma, Nadiya ta mata godiya sosai.

Kafin karfe tara na dare tuni ta gama shirin kwanciya. Tana cikin yin shafa'i da wutiri taji wayarta tana kara. Da tayi sallama sai ta dauki wayar da niyar bin bayan mai kira, sai taga Madam ce. Data kira bata dauka ba sai ta kyaleta har ta katse, tana katsewa din kuma sai gashi ta dawo da kiran. Don haka ta daga.

Suka gaisa kamar yadda suka saba, har tana tambayarta ko har ta kwanta ne? Tace mata a'ah, shafa'i ne tayi da wutiri. Madam tace, "Habib, dan gidan Hajiya Umma gobe zai koma can Kadunan, ita kuma sai ta kara kwana biyu kafin ta koma. To shine nace mata ke ma ai gobe zaki koma, sai tace to ki shirya idan zasu tafi sai su wuce dake."

Tayi saurin girgiza kai kamar tana ganinta, tace, "Mommy, na fa riga na gama shirin komi da komi, kuma ni fitar wuri zan yi gaskiya saboda da wuri nake so in isa gida!"

Madam tace, "to ke in banda abinki tafiya a motor gida bai linka na haya ba sau dubun dubata? Kuma ai zaki ma fi isa gida da wuri."

Tasan sarai Madam din ta fita gaskiya, amma kuma tafiyar ce bata son yi dasu kwata-kwata. Ta sake daga baki da niyar nunawa Madam tsarinta fa bai yi ba, tace, "to ai kinga ba saninshi nayi ba, kuma shima hakan take. Kinga kuwa tafiyar tamu ba lallai tayi dai-dai ba. Sai inga kawai gwanda kowa yayi tafiyarshi ko?"

Madam tace, "sai ku san juna ta dalilin haka ai. Ki shirya da wuri, wajen karfe takwas zasu zo su daukeki."

Ta katse wayar ba tare data bari Nadiya ta sake cewa wani abu ba.

Ta ajiye wayar yaraf! akan cinyarta jiki a matukar sanyaye. Gabadaya wadannan abubuwa dake faruwa ta kasa fahimtarsu. Ta rasa ta yaya zata fahimcesu. Ya za ayi ita dake kokarin nesanta kanta da abu kuma a dinga kokarin kusantata dashi? Yanzu da zancen aure yake lilo a tsakaninsu, gani take kamar idan ta rabu dashi hakan zai iya zama gaskiya.

Don haka kafin ta kwanta, ta riga ta gama yankewa kanta shawarar abinda zai faru kawai.

Asubahin farko, ta gangara akwatunta ta fito. Ta bugawa Dada kofa, ta bude ta fito da tasbaha a hannunta alamun lazumi take yi.

Ta kalleta da mamaki, tace, "Nadiya, sammako kika bugo kuma? Nayi tunanin zaki bari garin ya gama wayewa?"

Tace, "ai Dada saboda yanayin hanya shi yasa, gwara in fita da wuri din zai fi."

Dada ta yi mata fatan alkhairi sosai. Maigadin gidan ya fita ya samo mata abin hawa ta loda kayanta a kai ta hau, sai tasha.

Sai dai zuwan nasu tashar sai suka tarar da jira. Dole ta shiga mota ta zauna bayan ta biya kudi, aka hau jiran fasinjoji.

Suna nan zaune har bakwai ta kusa rufawa, gabadaya ta fara kagara da zaman jira.

Sai taji wayarta tana kara. Data duba ta ga lamba ce babu suna sai ta mayar ta cikin jaka ta ajiye. Bata cika kin daga sabuwar lamba ba, amma dai wannan lambar ji tayi hankalinta bai kwanta da ita ba, don haka ta ki dagawa.

Aka yi ta kira tana kin dagawa har sai da aka ajiye mata missed calls kusan guda hudu, daga karshe dai ta daga cikin nuna alamun gajiyawa.

Ta kara wayar a kunne, tace, "wai waye ne?"

Shi kuma mai kiran ya tareta da tambayar, "Nadiya kina ina ne?!"

Sai da taji zuciyarta na canza bugawa, amma ta danne zuciyartata. Duk da ta fahimci mai tambayar kuma sai ta mayar mishi da wata tambayar, "waye ne wai?"

Daga can ya fara bata amsar tambayar tata, "kina ina...?"

Kafin ya karasa kuma sai taji yace, "got you!"

Kafin kuma ta ankare kawai taga mutum a tsakiyar kanta.

Ya tsaya ta gefen da take yana kallonta ta cikin bakin gilashi daya rufe fuskarshi da shi, wai ya hau yi mata alamun ta fita daga motar.

Ta kuwa danna mishi harara ta juya kanta gefe guda. Wannan bakar masifa har ina! Ta gudu din ma bata tsira ba sai an dauki hanya an biyota har tasha sai kace wadda tayi sata? Tafiya ko? To ba zata hau motar ba sai taga yadda za ayi da ita.

Ganin ba fitar zata yi ba sai ya koma ga direba, bata san me suke cewa ba, bayan yan mintuna sai taga ana fitar mata da akwatu daga mota. Ta juya tana kallonsu cike da mamakin wannan karfin hali. Da taga dai da gaske fitar da kaya suke yi, sai ta tashi ta fita daga motar, tana tambayar direba lafiya kuma?

Direba ya kalleta, yace, "yata, kiyi hakuri kin ji? Komi na rayuwa fa hakuri ake yi da shi kinji? Ki daure ki taushi zuciyarki ki bi mijinki. Don bai shirya da wuri ba sai kawai ki ce zaki tafi ki bi motar haya? Dama ana haka ne? Yanzu

dai tunda gashi ya shirya din, kuma kinga motar ma har yanzu ko rabin cika bata yi ba, ki daure ki bishi din. Allah Ya kiyaye muku hanya!"

Wallahi tsabar mamaki sai ta ma kasa daga baki tayi magana, sai cira idanu data dinga yi a tsakaninsu.

Ta kalleshi, rannan nata idan yayi dubu a bace, tace, "wai wacece matarka?"

Yayi wani murmushin tura haushi, "ga ki nan a tsaye kina kallona!"

Ta jinjina kai kamar wata tsohuwar kadangaruwa tana kwafa, ta juya ta kalli yaron mota dake kokarin daukar kayanta, tace mishi, "Malam ajiye min kayana!"

Babu musu ya ajiyesu ya tsaya yana raba kallo tsakanin ita da Habibu din.

Ta kama akwatinta taja, ta kalli Habib, tace, "kaje ka nemi inda matarka take amma ba Nadiya ba. Tafiya kuma ba zan yi da kai din ba, ka kama hanyarka ka tafi salin alin!"

Ya daga kafada, "ke dai zaki zo mu tafi salin alin saboda kinga lokaci yana kara ja. Don haka tun kafin dare yayi mana, ki zo mu tafi kafin in ciccibeki daga ke har kayan naki wallahi!"

Wata irin dariya ta kwace mata mai cike da takaici da bacin rai. Bata ma iya ce mishi komi ba kawai ta juya zata tafi. Motar ma ta fasa hawa. Gwanda ta tafi wani wajen, kai ta gwammace ta tafi a kafa akan ta bi bayan mutumin nan su tafi tare.

Kamar wani wanda yake jira, ya tattare hannun rigarshi tsakaninshi da Allah har da dan dukawa wai zai dauketa. Taga dai tsakaninshi da Allah daukar nata zai yi a tsakiyar tasha, ga mutane sun zubo musu ido suna kallo.

Sai tayi saurin dakatar dashi, tace, "tsaya, tsaya! Zan tafi da kafafuna!"

Yayi murmushin samun nasara, ya kama akwatinta har da karamar jakar hannunta don ma kada tayi yunkurin tserewa ta barshi da kayan sanyawa. A yadda ya fara karantarta yasan zata aikata fiye da haka ma.

Ya nuna mata hanya, "yauwa, muje!"

Haka ya sanyata a gaba kamar wata diyarshi, suka tafi. Direba yana tambayar kudin motarta fa data biya? Ya juya ya kalli wata tsohuwa dake cikin motar yace a biya mata kudin mota dasu.

Haka suka bar tashar nan tsohuwa na ta kwarara musu addu'ar Allah kiyaye, Allah Ya tsare. Shi kuwa direba ya dage yana karawa Nadiya nasihar a kara hakuri, zaman aure dan hakuri ne. Ji take kamar daga Habibu din har direban ta kamasu tayi ta hade musu kawuna.

Suna fita daga tashar suka samu lafiyayyar bakar Jaguar tana jiransu. Da kanshi ya bude booth ya sanya kayanta a ciki.

Ya dawo har lokacin jakarta tana hannunshi, ya bude mata gidan baya. Taja tsaki, ta harareshi, ta murguda bakin, taga shi dai ko a jikinshi wai an tsikari kakkausa. Sai ta kara jan wani tsakin ta shiga. Ya maida kofar ya rufe, ya zagaya daya gefen shima ya shiga ya zauna.

Sai da yaga direba ya tashi mota sun dauki hanya, ya kuma tabbatar ya dantse kofofi, sannan ne ya mika mata jakarta da wayarta take ta faman ruri.

Ta warci jakar kamar fada, shi kuwa yayi wata irin siririyar dariya data kara bata mata rai.

Ta ciro wayar ta ga Anty Lima ce take kiran nata. Tayi-tayi ta daga kiran wayar taki motsawa. Abin tun faduwar da tayi take bata matsala, wani lokaci sai screen din yaki dannuwa. Tunanin idan ta koma gida ta hade yan canjin hannunta ta canza waya take yi.

Ganin wayar ba daguwa zata yi ba, da takaici ya cikata sai kawai ta kasheta ta jefa cikin jaka.

17.

Tunda suka dauki hanya bata iya ce mishi komi ba, kanta a gefe daya don ma kada yayi gigin tunanin janta da hira.

Hakan bai dameshi ba ko kadan, haka yayi ta yunkurin janta da hirar kuwa ta hanyar watsa mata tambayoyi daban-daban, amma duka tayi biris dashi. Don kanshi ya hakura ya hau kiraye-kiraye da dage-dagen waya.

Basu sarara da tafiya ba sai da suka shiga Damaturu, ya yiwa direba magana akan su tsaya a gidan abinci.

Suka tsaya a wata restaurant mai kyau, ya bude kofar ya fita kafin ya kalleta yace, "ki fito muje mu nemi abin karyawa ko?"

Ta kalleshi a kaikaice tace, "nagode!"

Shi kuwa bai kara ce mata komi ba suka fita shi da direban suka shiga gidan abincin.

Ta kwantar da kanta a jikin kujera tana binsu da kallo har suka shige. Yunwar take ji sosai, cikinta sai kugi yake, amma saboda tsabar taurin rai ta kasa tashi ta bi bayansu. Sai ma rufe idanu da tayi wani wahalallen barci yayi awon gaba da ita.

Bata san lokacin da suka dauka a ciki ba, sai da taji an bude motar an shigo sannan ta dan farka. Data duba lokaci sai taga sun dauki kusan mintuna talatin.

Ta gyara zama a hankali tana kara gyara zamanta.

Yana zama direba ya tashi mota suka kara daukar hanya. Ya mika mata leda madaidaiciya, ganin bata amsa ba yasa ya dora mata ita akan cinyarta.

Tayi biris da ita na dan lokaci. Kamshin dake fita daga ledar yana shiga hancinta yasa yunwar dake nanikarta ta kara tasowa, don dama daren jiya ba wani abin kirki ta ci ba.

Ta daga ledar tana zaro kayan ciki a hankali kamar wata mai tsoron dagawar, ta fara zaro samosa, meatpie, danginsu spring rolls da lemuka guda biyu na exotic, har da karin tarkacen cakuletin dairy milk da alewar bounty. Ta tabe baki kamar ba wani abin arziki ya mata ba.

Ta fara cin kayan a hankali tana korawa da lemu, kafin kace me ta kusa cinye komi. Sauran da suka rage ta dukunkune su a cikin leda, ta kara kwantar da kanta a jikin kujera ta koma wani barcin.

Wannan kam yayi nisa sosai. Jifa-jifa dai ta kan farka ta duba inda suke da kuma lokaci kafin ta koma, bata tashi daga barcin sosai ba sai da suka shiga Kano. Nan ma sai da suka tsaya ne a wani masallaci na matafiya sannan.

Su duka suka fita, su suka wuce bangaren maza, ita kuma ta wuce na mata.

Daga nan suka sake daukar hanya. Tafiya lumi-lumi gwanin dadi, sai gashi ana kiraye-kirayen la'asar suka shiga cikin Kaduna.

Babu wata kwakkwarar magana data hadasu har a lokacin.

Ya juya ya kalleta yana ce mata, "a ina zamu ajiyeki?"

Tace mishi, "idan mun je Kawo kawai ku ajiyeni, zan karasa da kaina!"

Ya sake kallonta fuska a dan gintse, "tambayarki nake inda zamu ajiyeki."

Ta turo baki kamar zata ce wani abu, sai kuma ta canza shawara. Ta fada mishi unguwar da zasu sauketa.

Da taimakon kwatancen da take yiwa direban sai gasu har a kofar gidansu.

Yana yin parking, ta bude murfin motar ta fita kamar wadda ake mintsina a cikin motar.

Direba ya fita ya bude booth ya fitar mata da kayanta. Sai ga yaran gidan sun fito aka hau murnar ganinta da kuma fadan wanda zai daukar mata kaya.

Bai fita daga motar ba, sai gilashin motar na bangarenshi daya bude, ya dan zura kanshi waje yana mata magana, "baki ji ba!"

Yi tayi kamar ba zata juya din ba, sai kuma ta juya tana kallonshi, fuskar nan idan ka ganta kamar wadda tayi tuntube da kashi.

Wata jaka yake mika mata irin gift bag dinnan ruwan hoda, tayi tsaye kawai tana kallonshi babu alamun zata matsa ma balle ta amsa. Sai ya yafici Fatima, ita kuwa ta ruga da gudunta taje har da dukawa tana gaida shi. Ya mika mata jakar yace mata, "rikewa Antynki wannan ko?!"

Ta kuwa sanya hannu biyu ta amsa, kafin ma Nadiya tace mata wani abu har ta falla cikin gidan da gudu.

Shi kuwa ya kalleta, ya sakar mata murmushi, ya rufe gilashin mota direba ya ja suka yi gaba.

Tayi tsaye a kofar gidan tana bin motar da kallo har ta wuce. Mamakin wannan al'amari take yi, karfin halin mutumin ai har ya wuce misali.

Ita abin gabadaya ya fara daure mata kai. Wannan shisshigi da ake mata ya fara shigar mata hanci da kudundune fa. Tayi kwafa ta wuce cikin gidan itama, a ranta tana fadin zata taka mishi birki matukar ya kara hada hanya da ita.

Tana shiga gidan ta kula da canjin da aka samu. Ita gabadaya ta ma manta da zancen amaryar Abbansu zata tare, sai da ta ci karo da bakuwar fuska a zaune akan dan dandamalin dakin Mama da farantim shinkafa a gabanta tana aikin tsinta.

Su Salame da Lantana kuma suna kofar dakin Salame din wanda yake fuskantar na Mama, sun baza tabarma akai suna ta zubda ruwan habaici.

Data musu sallama sai taga sun watsa mata kallon banza, suka kara da harara da tsaki. Don haka ta dauke kanta daga garesu, ta karasa kofar dakin Mama da take a tsaye, kai tsaye ta rungumeta cike da kewa da jindadin ganinta.

Bayan sun gama gaishe-gaishensu, amarya ta juya tana mata sannu da hanya.

Ta kare mata kallo cike da mamaki. Da ake cewa amaryar ta Babansu yarinya ce, bata yarda ba sai data ganta da idanunta sannan.

Yarinya ce danya shataf, da kyar idan ta haura sha takwas. Amma wai a hakan ma aurenta ne na biyu.

Ta amsa mata a nutse, kafin ta karasa cikin dakin.

Ta shige can cikin dakin Mama ta watsa ruwa don bata tunanin zata iya shiga na tsakar gida. Data fito ta sanya doguwar riga ta jan material marar nauyi, tayi sallah.

Kafin ta gama har Maryam ta kai mata danwake, da alama shi suka yi a gidan da rana. An yanka mishi albasa da tumatiri da latas, ta zauna ta ci sosai da sosai ta kora da ruwan sanyi.

Ta jona wayarta a caji, kafin ta fita wajensu Mama da suka koma kofar kicin yanzu ita da amarya. Amarya na jajjagen kayan miya a turmi, Mama kuma tana kokarin dora tukunya akan wuta.

Nan ta zauna suna hirarrakinsu tana tayasu da wani aikin har aka yi Magriba.

Ta fahimci amaryar ta Abban nasu babu laifi tana da hankalinta, kuma bata da rawar kai. Gashi tana girmama Mama sosai, don hatta da ita kanta Nadiya din bata kiran sunanta kai tsaye, sai dai tace Antyn yara. A ranta take tunanin wata kila ita za ayi zaman mutumci da ita.

Har ta gama shirin kwanciyarta, sunyi waya da su Dada da Anty Lima har da Anty Hauwa. Data kira Madam bata dauka ba sai ta tura mata sakon cewa ta isa gida lafiya, itama Safiya sai data kirata suka gaisa.

Idanunta suka sauka akan jakar da aka bata dazu, wadda ta dorata akan TV stand, bata kuma kara bi ta kanta ba sai a lokacin.

Ta so ta kyaleta tayi ta zama anan, amma curiosity ya hanata. Ta tashi ta dauki jakar, ta koma ta zauna tare da fara zaro abubuwan dake ciki.

Ta zaro idanu cikin tsananin kaduwa da mamaki, zuciyarta na duka ganin gyallelen kwalin wayar Samsung a ciki. Ta hau kwale kwalin wayar har ta ci karo da ita, taga da gaske dai wayar ce ba wasa ko tsokana ba. A bayan kwalin an lika karamar post it card an rubuta, 'fansar wayar da na lalata miki. Fatan za ki karba' a turance.

Ta kama baki cike da mamaki, kafin kuma ta janyo sauran abinda ke ciki. Kwalayen turaruka ne masu kyau kusan kala hudu, da Borneo Oud, Oud Violet, Nishane, Amouage, Thomas de Monaco Raw Gold. Su kuma a jiki an rubuta 'to a fellow perfume lover'

Ta tabe baki kamar yana gabanta. Ta rasa ta yadda aka yi cikin dan kankanin lokaci har ya fahimci tana da son kamshi. Da alama dai yana da kula, 'da kuma sa ido ba!' Wani sashe na zuciyarta ya ayyana mata hakan.

Ta zauna na tsayin lokaci anan tana tunanin abinda ya kamata da sake-sake. Daga karshe dai ta janyo wayarta ta dannawa Anty Lima da yake karfe goma bata kai ga yi ba.

Tace mata ita dai gaskiya zata mayar mishi da kayanshi don bata ga dalilin da zai sa yayi mata wannan kyautar ba.

Anty Lima tace, "to wai sai me don ya baki kyautar waya da turare? Kin rokeshi ne kika ce ya baki?"

Tace, "wa? Allah Ya tsareni!"

Tace, "to kin gani? Shi yayi radin kanshi ya baki, don haka ki amsa da hannu bibiyu. Ina ruwanki da shi da kayan daya baki? Idan kin tashi ki ware min turare guda don nasan zasu hadu sosai, na ji turarukan da yake amfani dasu masu kyau ne kuma suna da kamshi."

Tayi yard dariya, "Allah Yaa kyauta miki wallahi! Sai ki bari sai nayi tunani na tabbatar zan rike din sannan. Sai da safe, barci nake ji!"

Suka yi sallama ta kashe wayar.

Kwanciyarta tayi ta ajiye kayan a gefe.

Da asuba tayi mamaki da taji Abbansu ya fito ya bi daki-daki wai yana tashinsu sallar Asubahi.

Abin ya bata mamaki matuka, ta kame baki cike da tsananin mamaki. Mama da ta sallame sallah ta kalleta ganin yadda tayi hangangam da baki tana bin wannan lamari da kallo, tace, "Nadiya ki tashi kiyi sallarki kada lokaci ya kure kinji!"

Haka ta lallabata ta tashi tayi alwala tayi sallah.

Gari yana yin haske ta je ta gaishe da Abbansu.

Ta fito daga dakin nashi ta tsinci Salame tayi kerere a kofar dakin amarya, ita kuma amaryar ta ci kwalliyarta da wani mini skirt dinta da yar yaloluwar riga zata shiga dakin Abban nasu.

Tana ganin Nadiya sai ta hau fara'a, "a'ah! Antynsu kin tashi kenan? Ina kwana, ya gajiyar tafiya?"

Gaisuwar tata sai ta bata kunya, tace mata, "Gajiya fa Alhamdulillah. Ina kwana?"

Salame ta ja wani dogon tsaki, dai dai lokacin Lantana ta fito daga nata dakin da riga da zane daban-daban, fuskar nan tata dagaje-dagaje da alama dai ita ko sallar da aka tashesu bata kai ga yi ba.

Laminde tace, "oh ni Yaya! Jiya kinji tashin hankalin da naji kuwa?!"

Nadiya ta kalli Laminde din cike da mamakin abinda tace, a tunaninta ko rashin lafiya ta kwana da ita.

Salame ta dannawa Amarya harara, "jiya ke kika ga tashin hankali ko ni! Wallahi ban taba ganin rashin mutunci ba irin na jiya. Kawai aka hanani barci don tsabar jaraba da kwarzaba da rashin tunani! Kai baka ganin gidanka gidane na yara, kuma dakina da inda kake bango-da-bango amma ba zaka yi tunanin hakan ba? Wannan ai shiga hakkine da rashin sanin darajar dan Adam!"

Sai lokacin ta fahimci abinda ke faruwa a wajen, dariya ce ke kokarin kufce mata, ta sanya hannu tana rufe baki don kar ta fito.

Ita kuwa amarya bata nuna ta fahimci abinda suke nufi ba, sai ta bisu daya bayan daya ta gaishesu, ta juya ta fada dakin Mai gida ta barsu anan ba tare da ta jira sun amsa ba.

Suka bita da harara kamar idanunsu zasu fadi. Lantana tayi kwafa tace, "yar iska kawai! Da alama dai wannan karon tsohuwar karuwa aka kawo mana!"

Salame tace, "bar ni da ita, in takamarta iskanci, ni ai na fita iyawa! Wallahi sai na gasa mata gyada a tafin hannunta!"

Nadiya da har lokacin take wajen tana kallonsu da murmushi akan fuskarta, ta kyalkyale da dariya har da tafa hannuwa, suka hau binta da kallo kamar wadda ta samu tabuwa.

Tace musu "ai shi yasa masu iya karin magana suke cewa wai a dinga sara ana duba bakin gatari. Kuma dai sannu bata hani na zuwa sai dai fa a dade ba a je din ba!"

Suka zaburo mata a lokaci guda, "me kike nufi?!"

Ta haskesu da wani murmushin tura haushi, "abinda nake nufi kenan!"

Ta shige ta barsu anan suna ta sakin maganganu sai kace wadanda ke shirin tada bori.

Da ta nunawa Mama wayar da Habibu ya bata da kuma abubuwan da suka wanzu a Maiduguri. Itama dai shawarar da Anty Lima ta bata ta maimaita mata, tace ta amsa tayi amfani da su tunda dai shi ya bata kyauta ba roka tayi ba. Kuma dai babu mai mayar da hannun kyauta baya sai shaidan. Don haka ta amsa kawai.

Maryam da take jinsu kuwa tayi tsalle ta dafe tsohuwar wayar Nadiya din, tace, "dama ina ta jiran ranar da zaki yi sabuwar waya ki bani wannan, sai in ba Amina ta wa."

Da yake ta hannun nata karama ce.

Nadiya tayi murmushi, tace "to shikenan. Bari idan na dauke kayan cikinta sai a bada a canza screen din, sai a canza."

Suna karyawa suka fito da kayan wanki jibgi guda, ranar haka suka yini suna aikin wanki ba kama hannun yaro. Da suka gama suka shiga dakin Mama shima suka gyara har da canza zaman kayan dakin.

Zuwa yamma ta dauke duk abubuwan da take bukata daga tsohuwar wayarta zuwa sabuwar, ta bada a kai tsohuwar wajen gyara.

Ta kira Aramide tana tambayarta game da wajen aiki, ta bata tabbacin an je an share komi an gyara, don haka idan sun je gobe aiki za a hau yi kawai babu bata lokaci. Tace itama satin sama zata dawo saboda wajen aiki. Suka yi sallama akan hakan.

18.

Kwana da kwanaki suna ta wucewa a hankali. Nadiya ta koma ta cigaba da gudanar da ayyukanta kamar da. Tuni ta manta da abin wani Habib da kurar data kwasoshi. Musamman da tun barinta da shi na karshe bata kara gani ko jin labarinshi ba.

Wata ya shige a haka, sai gashi har an fara zancen shigowar azumi nan da wata daya.

Zaman gidan nasu sai ya rikide ya koma wani yanayi na daban. Yadda su Salame suka so shine idan amarya ta zo, su yi kokari su janyeta ta koma cikinsu, su dinga muzgunawa Mama. Sai abin ya juye ya koma kansu.

Don kuwa ita dai amarya ba ta tasu take yi ba, ta kama Mama da 'ya'yanta ta rike kam da hannu biyu. Babu abinda ya dameta, yadda kowa yake kiranta Mama itama abinda take kiranta da shi kenan. Haka zata zage ranar girkin Mama ta tayata kamar ita ke girkin, ita kuma Mama ranar girkin amaryar sai su Maryam da Amina su tayata. Itama Nadiya idan tana nan ta kan tayata din.

Nan da nan kuma sai suka saba sosai, ya zamana dakin Mama nan ne wajen zamanta. Hakan kuma sai ya zama abin gulma da maida magana a wajen su Lantana. Su ce Mama ta asirceta, su ce ta mallaketa, su ce ta maidata baiwa. Zance dai kashi-kashi. Ita kuwa Mama da yake dama can ba kulasu take yi ba, sai tayi kunnen uwar shegu da su. Itama amaryar da Allah Yayi ta marar son rigima, sai take kyalesu bata shiga harkarsu.

Har yaran gida suka sa wai su dinga yiwa amarya rashin kunya, ko kuma Idan ta aikesu su ki zuwa. Shi din ma da ba don Nadiya ta taka musu burki ba da sai abin ya fi haka.

Ranar juma'a ta taso daga shago da dare dai-dai lokacin data saba dawowa. Tayi sallama ta shiga gidan, da yake girkin amarya ne ranar bata tsaya ta sayi abinci ba. Tunda tana da tabbacin kwanon abincinta yana nan.

Su Salame dama ba a zancensu, tuni ta fita ta harkarsu akan abinci dai. Saboda su dai farko ba kasafai suka cika tsayawa su dafa abinci mai dadi ba. Na biyu kuma abincinsu suna saukeshi a tukunya, da shi da babu duk daya ne. Idan kana kusa da su kayi wuf ka mika kwano su zuba maka, idan ka zauna jira kuwa sai su ce maka ai ya kare yara sun cinye. Ta sha biye musu akan hakan su yi ta fada, su mata gori su zageta tas, shima Abbansu idan ya dawo ya sameta yayi ta zagin har ya dinga hadawa da zagin 'katuwar banza da ita ta zaune mishi a gida yana ciyar da ita a banza! Idan ta ji haushi ta bar mishi gidan mana ko ta dinga ci da kanta!'

Da taga abin ya kai ga haka sai ta yiwa kanta fada. Tunda dai Allah Yasa tana da rufin asirinta dai-dai gwargwado. Shagon da take zuwa shi ya taimaka mata take sauke nauyin al'amuranta da dama. Sai ta kara da lissafin abinci a ciki. Idan ba girkin Mama ba dama ba abincin su ke ci ya ishesu ba. Don haka ta kyale musu kayansu.

A dakin Mama ta ci karo da Basira ta je gidan, da 'ya'yanta uku. Ta zauna suka gaisa da ita tana tambayarta ya kwana biyu, saboda sun jima basu gaisa ba. Gwara Zainab suna yawan yin waya da ita tunda da waya a hannunta, ita kuwa Basira da yake bata da wayar a hannunta sai idan ta

samu aro sannan ne take kiransu. Shima kiran sau tari bai wuce ta ce Nadiyar ta tura mata kudi ba ko kaya.

Ta kunce ledar sauran doughnuts da suka yi da cupcakes, ta bada biyu aka ba amarya, su Fatima ma ta basu biyun su raba, ta ba yaran Basira dai-daya sauran kuma ta barwa su Maryam.

Tayi sallah, ta zauna aka zubo mata abinci zata ci. Daga Basira har yaran suka zuba mata idanu yuu! Suna kallo kai kace sauran yunwa ne. Sai kawai ta mika musu kwanon, suka karba suka hau ci hannu-baka-hannu-kwarya. Kafin kace me! sun tada faranti guda. Suka tsaya suna lasar hannu da kwano.

Ta kallesu da tausayi zane akan fuskarta. Tace, "ko baku ci abinci bane? Maryam je ki tambayi Anty amarya ko da sauran abinci a basu."

Maryam tace, "wallahi sauran abincin kenan dama na ki ne ya rage, sai na Abba. An zuba musu tun dazu sun cinye!"

Taga yanayinsu dai su duka taga babu alamun sun koshi, ita kanta Nadiyar yunwar take ji saboda ko da rana bata tsaya ta ci abincin ba sosai.

Don haka ta bada aka sayo musu shayi da biredi suka kara da shi.

Tayi tunanin idan Abba ya dawo su Basira din sun gaisa, tafiya zata yi kamar yadda ta saba. Sai taga da yazo ma Basirar bata je ta gaisheshi ba. Yaran ma bata bari sun fita wajenshi ba. Sai tasan ba lafiya ba.

Wannan shine karo na kusan barkatai da Basira din tayi yaji ta je gidansu, a wannan tsakankanin kuma mijinta ya saketa har sau biyu.

Ta tambayeta, 'yau kuma lafiya?'

Ta bude baki tace, "yaji na yi!"

Nadiya ta kama baki, tace, "yanzu yaji kuma saboda Allah da Annabi? Me ya faru ne?"

Tace, "menene ma bai faru ba? Aure idan mata tana ciyar da kanta da 'ya'yanta ai babu shi, don ban ga abin yi ba a gidan da miji ba zai fita ya nema ya kawo min ba. Sai dai idan ni na samu in ciyar damu. Sakina ma zai yi wallahi, Mali zan tafi neman kudi!"

Nadiya ta dafe baki cikin mamaki, Mama kuwa ta hau sallalami da salati. Tace, "ke yar nan! Yaran kuma kiyi yaya da su?"

Tace, "yo in barsu wajen ubansu mana tunda ba dasu naje gidan ba! Yau ma don nasan idan yaga yaran ba lallai ya biyoni ba, ai da wallahi a can zan baro su. Amma yanzu daya bani takardata, kayan dakina zan sayar inyi tafiyata sai in kai mishi yaranshi!"

Mama ta sanya musu baki, tace, "a'ah fa Basira! Ita rayuwa da kike gani fa yar a bi ta a hankali ce. Shi kuwa zaman aure dama ai ya gaji haka. Musamman ga mutum marar tsayayyen aikin yi. Dole fa sai matarshi tana hakuri, itama kuma idan da hali ta dinga taimaka mishi. Sai kiga watarana hakurin yayi mata rana!"

Ta tabe baki, tace, "ai wallahi in dai da cuta a ciki fa ba zan yi wannan hakurin ba! Zaluncin ai yayi yawa!"

Nadiya kallonsu kawai take yi, Mama tana ta kokarin tausar Basira ita kuwa tayi biris da ita.

Tasan halin Basira sarai, bata da hakuri, kuma akwai kafiyar kai idan ta yankewa kanta abu.

Ta numfasa tace, "ke ma fa Basira kina da naki kason laifin a ciki! Waye yace miki mijine kadai yake hakuri da mace ita ba zata yi da shi ba? Kin san halin mijinki sarai, ai yana da kokarin yi. Kuma lokacin da yayi miki hidima ai yayi, me yasa baki taba korafi ba sai yanzu? Ashe ke ba zaki iya zama ki rufawa

mijinki asiri ba a lokacin da ba shi? Shikenan ke kullum kina tafe akan hanya yau kinyi yaji gobe kin kaso aure? Yanzu kuma kice wai kasar ma zaki bari kwata-kwata ki tafi neman kudi? Saboda rashin wadatar zuciya da rashin godiyar Allah irin naki? Sau nawa ana baki jari iye? Ina ce ko wancan watan da ya wuce Yaya AbdulHadi dubu saba'in ya tura miki ki ja jari, me kika yi da ita ne cikin abinda bai gaza wata biyu ba?!"

Budar bakinta sai cewa tayi, "yo wai kema kina ta wani tada jijiyar wuya kina fada. Me kika sani ne a cikin rayuwar auren da abinda ke cikinta? Gaskiya ki daina yi min irin wannan katsalandan din! Ki bari idan kinyi auren kin hadu da miji irin nawa kin fahimci ko me kenan. Yauwa!"

Ta saki tsaki.

Nadiya tayi wani dan murmushi dake nuna bacin ran da kalamanta suka haddasa mata.

Tace, "kwarai kuwa, ban yi aure ba Basira, ban kuma san me ke cikin rayuwar auren ba don haka Allah Ya baki hakuri da katsalandan din da na miki. Sai dai ita duniya ai ta fi bagaruwa jima, kuma ni nasan wallahi da ni ce a yanayin da kike ciki, ba zan tattara in kashe aurena ba wai in tafi duniya neman kudi. Su yaran nawa su yi yaya kenan? Tunda haka ne kuma, ki tanadi wajen zaman yin idda kin dai san Abba ba zai barki ki zauna mishi a gida ba!"

Yana daya daga cikin dokokin Abban nasu, mace in dai ya aurar da ita, to daga ranar ta bar gidanshi har abada. Shi da ita sai dai zuwa gaisuwa da yini, amma kwana ma shi bai amince ba saboda yace hidima ce suke kai mishi.

Don haka da ya fuskanci ma wai yaji kika yi ko auren ya mutu, yake rufe ido ya zabga miki rashin kirki, komi dare kuwa sai kin bar mishi gida, babu sassauci.

Sai idanun Basira kuma suka raina fata, tayi narai-narai da ido.

Tace, "yanzu ya zanyi to? Gashi Innata itama tana gida fa, yanzu idan na kwasa na tafi can abubuwan sai suyi musu yawa!"

Nadiya ta tabe baki tace, "shi yasa ai masu iya magana dama su kan ce wai a dinga sara ana duban bakin gatari!"

Ta juya tayi kwanciyarta ta kyale Basirar anan tana maida yadda aka yi.

Washegari tunda farar safiya sai ga Abbansu ya dira a kofar dakin Maman.

Dama Nadiya tasan dole sai ya san da zuwanta, tunda ko ita ta buya bata je inda yake ba ko 'yay'anta, dolene matan gidan zasu bashi labari.

Ya kankance idanu yana kallon Basira din data tsuguna tana gaida shi. Ko amsa gaisuwar bai yi ba ya hau watsa mata tambayar, 'me take yi a gidan?'

Ta karkace kai zata hau kora mishi bayani, yayi gaggawar dakatar da ita, yace, "kinga, ba dogon bayani nake nema ba, ga mijinki can ya doko min sammako ya zo nemanki da 'ya'yanshi, don haka ki kwashesu ku tafi salin alin. In ya so idan kun koma gidan sai kuyi duk wadda zaku yi dai, amma ba anan gidan ba. Kin sanni sarai, kin san bana daukar wannan rashin hankalin da hauka! Idan ma auren kika kashe daga karshe, kada ki kuskura in ga ko mai kama dake ne a kofar gidana. Don wallahi sai na sanya katako na sassake miki su, kin dai ji na fada miki!"

Ya juya fuu! ya wuce yana mai kara maimaita mata lallai nan da yan mintuna ta bar gidan.

Basira ta dora hannu aka zata kurma ihu, Nadiya tayi gaggawar dafe mata baki data hango su Salame suna lekensu ta kofar dakinta ita da Lantana.

Samu suka yi ita da Mama suka tausheta akan tayi hakuri ta bi mijinta tun kafin Abba ya tata mata rashin kirkin da yake ikirari.

Nadiya tace mata, "idan ma rashin sana'a ne matsalarki, kinga wajen aikinmu muna neman masu wanke-wanke da goge-goge, idan kina so sai a baki, tunda albashin babu laifi yana da dan kauri!"

Nan da nan kuwa sai ta hau zubda fara'a, tace, "Yo Anty Nadiya da tun wuri kika yi min wannan bayanin ai da bamu kai ga haka ba. Aiki ni ko wane irine in dai za a biyani ai wallahi ina so!"

Nadiya tace, "tun farko idan baki manta ba ai na miki zancen aikin lokacin kina cikin ganiyar jin dadin arzikin mijinki, kika ce min ke mijinki ya tsaye miki don haka baki bukata ko?"

Sai ta hau nade tabarmar kunya da bori, ta hau dariyar jin kunya, tace, "dadina da ke Anty Nadiya ba dai riko ba! Ni dai don Allah ki min kokarin aikinnan kinji? Kuma don Allah kiyi hakuri akan maganganun dana fada miki jiya, raina ne ya baci da yawa."

Nadiya tace, "ni kuwa me yasa zan yi fushi don kin fada min gaskiya? Ai gaskiya ce, ni da ba sanin rayuwar aure nayi ba meye nawa na baki shawarar yadda zaki zauna da mijinki?!"

Da haka dai ta musu sallama ta bi Mijin nata bayan Mama ta bata kayan masarufi dangin su sabulai na wanki da wanka da su omo da kayan su maggi da su daddawa, har da dora mata da dubu biyu. Haka tayi ta musu godiya ta tafi.

*****

Kamar yadda tayi alkawari kuwa, a satin daya biyo baya Basirar ta fara zuwa shagonsu. Aka bata aikin goge-goge da wanke-wanke, biya kuma mai kauri ake mata wanda Nadiya take da tabbacin zai iya rufa musu asiri a rayuwar takatsantsan.

Sati biyu da yin haka suka je Kano gidan Anty Jamilah ita da Maryam. Mijin Anty Jamilah din aka yiwa aikin koda a asibitin Murtala dake nan Kano din suka je dubashi.

Da suka je din kuma sai suka tarar ana yiwa kanwar abokiyar zaman Anty Jamilah din biki, don haka suka shiga ciki aka yi ta fafatawa da su.

Daga zuwa wajen dinner da dare, Yayan amarya ya tafi ya saukesu ita da su Rabi'ah da abokan amaryar guda biyu da aka yi musu masauki anan gidan Anty Jamilah din, sai bawan Allah Ya mannewa Nadiya.

Tun a wajen dinner din ta kula da yadda yake ta bibiyarta da kallo da magana, duk kuma yadda tayi kokarin yakiceshi wannan bawan Allah ya ki amincewa.

Sai daya samo lambar wayarta a wajen Rabi'ah, haka ko shigarsu cikin gidan ya dameta da nacin kira da tura sako, shi fa tsakaninshi da Allah sonta yake yi. Duk kuma yadda taso ta fahimtar dashi akan cewa ita dai ba wannan ne a gabanta ba, ya ki saurarenta.

Haka washegari da safe yaje gidan ya kasa ya tsare, shi fa ala dole sai taje sunyi magana. Bata yi niyyar zuwan ba kuwa sai da Anty Jamilah taje ta furtomata sannan.

Ta dauki hijabi ta dora akan doguwar rigar material dake jikinta, ta tafi ta sameshi a falon farko.

Yana ganinta ya jimke hannu alamun gaisuwa, yace, "ranki ya dade! Barka da fitowa... Takawarki lafiya Hajiya Nadiya. Ina godiya da wannan karamci da aka min na bani damar ganin wannan kyakkyawar fuska taki a wannan hantsi mai albarka!"

Duk kinta sai da tayi dan murmushi. Ta fahimci mutum ne shi mai barkwanci da ban dariya. Ko a maganganunshi zaka fahimci hakan.

Ta zauna a kujerar dake fuskantarshi tace, "wannan kirari duk ni kadai dai?"

Yace, "ai kin cancanci fiye da hakan ne ma. Idan kina so in nuna miki kuma to mu fara."

Tayi gaggawar girgiza kai, "a'ah, hakan ma nagode... Ina kwana?"

Yace, "lafiya lau. Da fatan dai kin tashi lafiya? Allah dai Yasa su Rabiah sun bar kin ke kinyi barci da kyau. Don idan ba haka ba lallai fa zan shiga har gida in zanata!"

Yar dariya kawai tayi da jin haka.

Ya gyara zama yana kallonta a nutse, duk da haka fuskarshi a sake take babu daurewa.

Yace, "Malama Nadiya, kamar dai yadda kika sani, Sunana Abdullahi Aminu. Sannan ni likita ne, ina aiki a Aminu Kano Teaching Hospital. Shekaruna talatin da hudu yanzu a duniya, ba kuma zan boye miki ba, nayi aure amma mun rabu da matar. A zance na gaskiya kuma, da na ajiye auren ne a gefe, babu ranar sake wani, amma a yanzu dai har ga Allah na ganki ne, ina sonki, kuma in shaa Allah ina son hakan ya kaimu ga aure!"

Ta jinjina kai tana kare mishi kallo a hankali. Yanayin jikinshi dogo ne, bashi da kiba, yana da tsayinshi dai dai misali. Ba zaka kirashi baki ba, haka ma ba zaka kirashi fari ba. Sannan duba da shekarunshi daya fada mata, idan ba sani kayi ba sai kace shekarun nashi basu haura talatin ba.

Tayi tsai da ranta tana kara tunani. Zata iya cewa wannan shine karo na farko a shekaru fiye da biyu da wani namiji ya nuna sha'awar aurenta kai tsaye. Ta sha samun samari da magidanta da ke zuwa wajenta, wadanda tun kafin lokaci ya ja ma take fahimtar ba aure ya kaisu ba. Soyayya da holewa kawai suka je yi, ita kuwa ta zubar dasu a take ba tare da bata lokaci ba.

Taga shi auren kamar yadda suke fadi dace ne. Kuma zaman gida da take yi, ba zabar hakan tayi ba, ba kuma don tana jin dadinshi bane. Menene ma amfanin cigaba da zaman gidan da a kowace dakika nuna maka ake yi ba fa

wajen zamanka bane na dindindin? Kuma ba a gajiya da goranta maka rashin aure kamar kai ka janyowa kanka?

Watakila idan ta nutsu, zata iya samun abinda take so a wajen Abdullahi din.

Tana daya daga cikin mutanen da suka yarda ba wai lallai dole sai anyi soyayya ba ake yin aure. Ta fi yarda da cewa kawai dai fahimtar juna ta fi taka rawa a wannan bangaren.

Don haka ta nisa ta kalleshi, tace mishi, "to Malam Abdullahi, naji duka kalamanka kuma na gamsu. Amma kayi hakuri ka bani wasu yan lokuta domin in tattauna da manyana, saboda kada in yanke hukunci ni kadai."

Ya gyada kai, "ehh, kwarai hakane, da gaskiyarki kam! To yanzu zuwa yaushe zan baki kenan? Yau ko gobe?"

Ta saki yar dariya a tausashe, tace, "a'ah Malam, me kake ci na baka na zuba ne haka? Ka dai bani yan kwanaki dai!"

Ya langwabar da kai gefe daya, "to ni dai ina rokon alfarmar a daure a tunana lamarin nan nawa da wuri. Saboda so nake as soon as possible inyi caraf dake, kafin inji ana min guda a tsakar kaina wani yayi awon gaba dake!"

Ta yi murmushi kawai tana girgiza kai.

Sun jima sosai suna hira da shi anan har sai da aka kira Azzuhur kafin suka rabu da shi.

Ko a yinin haka suka yini suna waya, motsi kadan ya kirata, a zauna ayi ta hira abin har ya fara gimsarta.

Da dare ta samu Anty Jamilah da zancen, ta tambayeta ko me take gani ya kamata tayi a shawarce?

Tace mata, "Abdul fa yana da hali na gari, gaskiya mawuyaci ne ki samu wani ya fada miki akasin haka. Sannan ko a yanayin mu'amala da mutane, mutum ne mai tausayi da tausasawa. Idan kina ganin hankalinki ya kwanta da shi, to ki bashi dama ki ga inda hakan zai kaiku. Amma dai kam babu wani mutum da nake ganin zai dace da ke kamar shi din!"

Hankalin nata bai kwanta dashi duka ba, amma a hankali a hankali watakila hankalin nata zai kwanta dashi dari bisa dari.

Don haka data koma daki ta kirashi ta sanar dashi abinda ta yanke. Irin murnar da yayi ba kadan bace, har hakan ya bata mamaki.

Tace, "sai dai wani hanzari ba gudu ba!"

Yace, "me fa?"

Tace, "to ina sa ran cigaba da karatuna saboda yanzu haka admission nake tsammani daga ABU Zaria daga nan zuwa ko wani lokaci. Ina fata hakan ba zai zama matsala ba?"

Yayi saurin cewa, "ko kadan! In shaa Allah hakan ba zai zama matsala ba!"

Tace, "to nagode!"

Haka suka kusan raba dare suna hira. Sai data gaji tace mishi kanta yana ciwo sannan ya mata sai da safe.

Washegari suka koma Kaduna. Kwanakin da suka biyo baya kuwa soyayya ake sha ita da Abdullahi din ba ta kadan ba. Ko kuwa ita a bangarenta hira zata ce? Gata nan dai. Ita dai duk wani dokin masoyi da kewa da shauki da ake ji na masoya, bata jin ko kadan a tattare da Abdullahin.

Sai dai har zuwa lokacin tana ba kanta uzirin zata so shi a hankali. Tunda dai shi ta tsayar a matsayin wanda zata aura.

19.

Ranar Alhamis basu bude shago da wuri ba saboda sun zauna meeting akan yadda yakamata su gudanar da tsarin azumi da ake sa ranshi kwanaki uku masu zuwa ko biyu.

Su duka sun fi ta'allaka akan a cigaba da tsare-tsaren da aka saba yi kamar dai sauran azumummuka da suka wuce. Wanda zasu dinga bude shagon da yamma, ana yin kayan ciye-ciye saboda masu son motsa baki bayan shan ruwa.

Sai kuma aka kara shawarar a dinga gashin kaza da kuma yin tatattun lemuka na kayan marmari don a dinga hadawa dashi. Da wannan shawarar duk suka yi amanna, aka ware mutane biyu da zasu dinga kula da wajen da dare din saboda daga Nadiyar har Aramide kowa kafin a sha ruwa yake tafiya gida, meeting din ya tashi.

Kasancewar ranar Aramide bata je wajen aikinta ba, sai duk suka hadu har ita aka cigaba da sallamar kwastomomi da gudanar da ayyuka kamar yadda aka saba.

Wajajen karfe hudu da rabi ne, Nadiya tana cikin decorating din wani 4 steps cake taji daya daga cikin ma'aikatan wajen tana nemanta.

Ta juya tana kallonta cike da alamun tambaya, sai tace mata, "wani yaro ne yazo yana nemanki!"

Tace, "ni kuma?" cike da mamaki.

Tace, "ehh! Kwatancen da yayi dai kamar na ki ne, kuma ya ambaci sunanki!"

Tace, "to shikenan!"

Dama saura kadan ta kammala abinda take yi, don haka tace mata taje tace mishi ya dan jirata.

Ta kammala touching din da take yi, tayi packaging din shi nan da nan, ta bada a kira masu kaiwa su kai, ita kuma ta fita wajen da ake jiranta.

A bangaren VIP aka ajiyeshi, can kuma aka nuna mata data tambayi wanda yake nemanta. Ta wuce can cike da mamakin wane yarone wanda zai je yana nemanta a dai dai wannan lokacin.

Zaune yake akan daya daga cikin kujerun dake wajen, da remote control na game dake wajen yana bugawa.

Yaron ne kuwa kamar yadda aka ce, bata tunanin shekarunshi zasu haura bakwai. Yana saye da wasu kyawawan cotton din sweat pants na yara na Nike ruwan toka, da farar vest. Ta kalleshi kamar ta sanshi, amma kuma ta kasa tunano a inda ta san shi din.

Ta matsa ta zauna a kusa dashi, shi kuma daya ganta sai ya ajiye abin wasan nashi ya juya yana kallonta da murmushi, "Anty Ina kwana?"

Ta murmusa itama sosai, Allah Yayi ta da son yara ita dai, tace, "lafiya lau boy. An ce kai ne kake nemana?"

Ya gyada mata kai, "Daddy ne ya kawoni nan yace in zauna a wajenki zai je ya dawo!"

Ta dan juya kanta cike da mamaki, tace, "Daddynka kuma? wanene shi?"

Yace, "Habib Abdullahi Makama?!" cikin sigar tambaya.

Jin sunanshi kadai ma sai daya sanya taji bugun zuciyarta ya canza. A duka kwanakin da suka wuce tun bayan daya ajiyeta a kofar gidansu ya wuce, karya take yi tace babu wata rana da zata fito ta koma ga mahaliccinta bata tunano wannan mutumin ba. Abin har ya kusa zame mata jiki, yin tunaninshi a lokacin da taje yin kwanciya barci. Da kuma yawan tunanoshi a cikin yini, randomly zata ji kawai ya fado mata a rai. Ko kuma ta tsinci kanta da tunanin ko me yake yi a daidai wannan lokacin? Wasu dararen kuwa har da

mafarkinshi da tunanin wannan daddadan kamshin nashi, wanda ta samu ta lalubo turaren da yake amfani dashi cikin wadanda ya bata, itama ta mayar dashi nata turaren.

Yaudarar kanta take yi, da take cewa wai tuni ta manta da sha'aninshi da kurar data kwasoshi. Ita tasan karya take yiwa kanta.

Duk kuma yadda taso abinda ke tukarta a zuciya kada ya bayyana, sai daya bayyana din. Ta rasa fara'ar kirkirowa tayi ko da ta yake ce kuwa, haka bugun zuciyarta ya ki saisaituwa duk yadda taso ta saisaita shi din kuwa.

Ta daure dai da kyar tace, "ok, kwarai na ganeshi. Yana ina yanzu?"

Ya dan daga kafada, "ban sani ba nima. Kawai dai yace in zauna a wajenki zai dawo ya daukeni. Kuma bai ce ga lokaci ba."

Ita abin ma sai ya girmame mata, mamaki ya hanata motsi. To ita kuma a su wa? Da zai dauko danshi ya kai mata? Sai lokacin ta tunashi a matsayin yaron data gani tare dashi lokacin da suka ci karo a Makarfi. Ashe har d'a ma gareshi amma yake tata rashin kirki haka sai kace na wanda bashi da responsibility na lyali. Koda yake ai dama Anty Lima tace yana da Mata, mutum kuwa mai mata ai ba zai rasa d'a ba ko ma 'ya'ya idan ba wani ikon Allah ba.

Tayi dan murmushi don kada yaron yaga kamar ba ta so zamanshi anan ba, tace, "to shikenan. Zaka iya zama anan kai kadai har zuwa lokacin da zan kammala abinda nake yi?"

Ya gyada mata kai.

Don haka ta barshi anan ya cigaba da wasanshi, amma sai data dauki kayan tabe-tabe ta kai mishi ya ci da lemu. Haka duk bayan yan lokuta zata leka ta inda yake ta ganoshi da abinda yake yi.

Data sake komawa a wani lokaci sai ta sameshi yana gyangyadi, don haka ta kama shi taje ta kwantar dashi a dakin hutunsu, ta koma ta cigaba da ayyukanta.

Da rana ta mishi take away din jollop din shinkafa aka kai mishi ya ci.

Yinin nan guda na ranar anan yayi shi. Yaron yana da wayo, kuma yana da saurin shiga rai. A hirarrakin da suka yi da shi taji cewa shi kadai ne a wajen mahaifin nashi. Kuma bata tunanin ma Mahaifiyarshi tana gidan saboda koda wasa baya ambatarta, sai dai Babanshi din, da Granny da tasan bata wuce Hajiya Umma, da Anty. Wannan kuma bata san ko wacece ba. Sai wajajen karfe hudu na yamma sannan security din wajen yaje yace Ammar yaje inji Babanshi.

Ta samu leda babba ta zuba mishi cima iri-iri na makulashe ta damka mishi a hannunshi.

Tayi tunanin ta barshi ya tafi shi kadai kamar yadda yazo, sai kuma tayi tsoron yanayi da ake ciki da kuma abinda kan iya zuwa ya zo idan aka samu matsala ta dalilin haka. Don haka ta kama hannunshi suka fita farfajiyar wajen inda security ya nuna musu wata farar Elantra, a gefenta kuma bakar Highlander ce.

Kafin ta karasa wajen motar, ya fito daga bayan Elantra din.

So tayi ta buga mishi warning din kada ya sake kai mata dan shi wajen aikinta, kai ko inda take ma kada ya sake tunkara. Don bata ga alakar da zata hadasu dashi ba. Sai kuma yayi mata wani irin kwarjini a ranar.

Farar shadda ce ya sha ta sha surfani baki, ya dora bakar hular Dara a kanshi, kafarshi ta sha takalmi sai ciki shima baki.

Kasancewarshi mutum mai dan gwabin jiki, da kuma kalar jikinshi da ta kasance mai dan duhu, sai shigar ta matukar haskashi, ta kuma fitar mishi da kamala da cikar haibarshi.

Ta kasa ko hada ido dashi balle ta samu bakin iya gaida shi. Shi kuwa hankalinshi yana ga dan shi, ya kama hannunshi yana tambayarshi 'ya yake?' da kuma 'ya ji dadin zamanshi anan?'

Shi kuwa yana ta amsa mishi da 'ehh!'

Ya juya yana kallonta a nutse, cikin tausassar murya yake ce mata, "nagode da kulawa da kika yi da shi Nadiya. It means a lot!"

Ta kasa cewa komi sai, "uhm!!"

Tana so ma ta daga baki ko yaya ne tace mishi wannan ya zama karo na karshe da zai mata haka, amma ta kasa. Shi kuwa yayi tsaye yana kallonta, ba tare da yace mata uffan ba.

Sai kuma ta juya da sassarfa ta koma cikin shagon babu ko waiwaye.

Tana lekensu ta cikin taga, tana kallo har suka fita daga wajen, bakar motar nan tana take musu baya. Ta saki ajiyar zuciya a hankali tare da sauke numfashi, tuhumar kanta take yi, anya ba nema take ta wuce makadi da rawa ba kuwa?

Zuciya cike da sake-sake ta gama ayyukan ranar ta wuce gida.

Washegari Juma'ah ta tashi da farinciki akan sakon samun gurbin karatun Masters data yi a jami'ar Ahmadu Bello Zaria. Wanda suka tura mata shi ta email dinta a ranar da safe.

Ranta fari tas, tuni ita har ta gama tsara yadda karatun nata zai tafi da kuma aikinta da take yi. Tunda saboda shagon ne ma yasa ta yanke shawarar tsayawa a kusa da gida, amma da ba don haka ba so tayi ta cilla can Kudancin Nigeria ma abinta.

Ta so su hadu da Abba ta sanar dashi da wuri tunda ana gama sallah zasu fara darasi, don cikin azumi ma zata je tayi registration. Sai bata samu haduwa dashi ba saboda ya fita.

Don haka ta bari sai da dare sai taje ita da Mama, ita ta mishi maganar karatun. Sai ta bar Mama ta mishi zancen Abdullahi da shima yake so a bada rana da lokaci magabatanshi su je. Saboda shima so yake yi da zarar anyi sallah a tado zancen biki gadan-gadan.

Sam ranar bata yi mata tsayi ba. Sai taga nan da nan kafin tace me har lokacin rufewa yayi, ta dauki hanyar komawa gida.

Haka kawai taji gabanta yana faduwa, wani irin abu ya danne mata kirji, gabadaya ta nemi sukuni da jindadi ta rasa. Yadda kasan wadda aka fadawa sakon mutuwa.

Cikin tsananin mutuwar jiki ta shiga dakin. Ga mamakinta sai ta tarar da gidan ra-rai, yadda kasan babu wani rai da ke ciki.

Duk da cewa girkin Mama ne ranar, tasan idan lafiya to da ka samu su Lantana suna abinda suka saba. Ko Mama din da Amarya suna aikinsu idan yayi musu dare. Amma babu kowa. A ranta tace ko lafiya?

Ta wuce daki abinta, sai ta hangi Lantana da Salame suna lekenta ta tagar dakin Lantana suna kus-kus. Tace, "to! Ashe dai suna gidan!"

Tayi wucewarta dakin Mama ta samu Amarya ma tana can, ta musu sannu da gida kafin ta rage kayan jikinta, ta watsa ruwa kafin ta nemi wajen yin sallah.

Bayan isha'i su dukansu suna falon Mama suna kallo, Mama din kuma tana dakin Abbansu. Duk da bata fadawa Nadiya ba, sai tayi tsammanin ko zancen Abdullahi din zata yi mishi. Tunda ita Mama din da kanta tace zata fadawa Abban nasu a maimakon Yaya AbdulHadi da ita Nadiya din tace a fadawa ya fada mishi.

Zuwa can sai ga Mamar da kanta ta leka tace Nadiya din taje.

Zuciya na dukan uku-uku, haka ta dauki hijabinta ta bi bayan Mama. A ranta tana saka da warwarar ko me yake faruwa? Tunda a tunaninta a sukwane Abban zai karbi zancen zuwan su Abdullahi tunda dai neman kai yake yi da ita. Tana da tabbacin da za a bi tashi ma, kila yace kawai a daura auren kafin azumin ta tare. Ita tasan zai iya aikata fiye da haka ma. To menene zai sa yace yana nemanta? A ranta tace kila nasabarshi yake son sani. Ta gyada

kai cikin aminta da haka, sai ta kara samun kwarin gwiwar daga kafa ma ta bi bayan Mama din.

Sai dai shigarsu dakin Abban nasu sai ta ja tayi turus, ta kasa gaba ta kasa baya kamar wadda aka kafe a wajen.

20.

Kusan rabin dakin na shi shake yake da kaya data rasa gane ko na menene. Katan-katan na lemuka, kwalaye na alewa da cingam da biskit har basa kirguwa, ga huhu na goro. A sama kuma ga bandir din kudi yan dubu-dubu sabi gal a ajiye.

Ta lalubi kasan kujerar da Abbansu yake zaune ta durkusa ta gaisheshi.

Ya amsa mata da fara'a sosai, wadda tunda take rabon data ga irinta a fuskarshi har ta manta.

Mama yake kallo, don fara'a bakin nan nashi har kunne. Cewa yayi, "Zuwairah, kinga da gaske da ake cewa da haihuwar yuyuyu gwara daya kwakkwara! Yau dai na yarda da hakan. Gashi yau ina zaune diyata zata yi silar zuwana Makkah!"

Ta hau kallonsu shi da Mama din cikin alamun daurewar kai. Kafin ta kai ga tambayar ainihin abinda yake faruwa, Abbansu ya yi mata nuni da kayan dake shake a dakin.

Yace, "ki kalli wannan tarin kaya na arziki da girmamawa haka, kayan na gani ina so din ki ne. Mun sanya ranar aurenki bayan sallah da kwanaki goma!"

Tsabar kidima gabadaya sai ta tafi tayi wani irin zama a gaban Abban nasu daga durkushen da tayi. Tace, "me?!" Cikin tsananin fargaba da tashin hankali.

Ya kalleta yana hade fuska, "ihun meye wannan kike mana a wannan wajen ana maganar arziki? Ki kiyayeni fa Nadiya, ki fita nesa da ni wallahi! Ni ai dama nasan shegen bakin ciki irin naki ba lallai ya barki ki barni in dangwali arziki yadda yakamata ba. Zance dai ya riga ya gama mutuwa, an zo neman aure, ni kuma na bada. Babu kuma zancen fasawa. Don haka ki zama cikin shiri, da an gama sallah zan sallameki kema ki kara gaba."

Ya maida hankalinshi ga Mama, "ki fada mata sai ta gayawa shi wancan da take bada sakon zai turo, iyayenta sun mata miji. Ki kuma sanya mata ido da kyau, idan ta kuskura ta sake waya da wani kato wanda ba mijinta ba, wallahi sai na sassaba mata!"

Nadiya ta rasa duk wata kalma daya kamata tayi magana da ita a wannan lokacin.

Maganar ma da Abbansu yake yi sama-sama take jinta.

Tana jin shi yake ba Mama umarnin kudin saman dubu dari, ta daukesu ta mika mishi. Su kuma su alewar da biskit, ta zauna ta daukarwa matan, a warewa Madam nata da na yan uwanta, itama Nadiya a daukar mata wanda zata ba abokanta. Sauran kuma ta ajiye mishi su.

Sai ta ji ta fashe da wani irin kuka mai cike da gunji, ta hade hannuwa biyu tana rokonshi, tace, "ka yiwa Allah da ManzonSa Abba, kada ka yi min haka. Don Allah don Annabi ka barni in auri zabina!"

Ya kuwa zaburo mata, yace, "wani zabi kike nufi? Duk zabi da damarmakin da na baki a baya sau dubun-dubata baki taba kawo min zabin naki ba sai yanzu da kika ga arziki ya tako ya zo inda nake da kafafunshi sannan?

Nadiya idan baki kiyayeni ba fa wallahi zan mugun sabar miki! Aure kuma kamar anyi an gama ne, tashi ki fita ki bani waje, mutuniyar banza kawai!"

Ta tashi ta fita da sauri, fuska ta gama jikewa da hawaye.

Ta shige can kuryar dakin Mama ta haye kan gado ta lafe, ta saki wani irin kuka mai cin rai. Tayi-tayi, har sai data ji kanta yana sarawa. Tana jin wayarta tana ta kara amma ta kasa samun kuzarin daga kiran. Haka Mama ta shigo ta sameta, ta zauna tana lallashinta da ban baki da kalamai masu sanyaya rai, amma ran nan na Nadiya ya gama dugunzuma. Ta kasa daina kukan.

Mama sai ido ta kai ta zuba mata, ta kyaleta tayi kukan ma'ishi, ta zauna tana shessheka da jan hanci.

Mama ta kalleta cike da tausayi, tace, "yanzu su wannan koke-koken da kike yi na menene Nadiya, Iye? Ashe ke ba zaki yarda da kaddara ba? Ba zaki iya rufe ido ki bi maganar iyayenki ba? Anya Nadiya rayuwa zata yiwu a haka?"

Sai ta kara dargwajewa da wani kukan, tana kukan take cewa, "haba Mama! Abun ai sam babu adalci a ciki ko kadan! Ta ya za ayi ace a fitar min da miji ba tare da sanina ko amincewata ba har a karbi kudin aure da aka kawo? Kuma a ce min dole sai na aureshi ba tare da ni an duba abinda nake so ba? Waye zai zauna da shi idan ba ni ba? Ko babu komi ai sai a sanar dani ko? Kuma a tambayeni ba a bani umarni ba!"

Mama ta dan hade fuska, tace, "ki fa dinga tauna maganganun dake fita daga cikin bakinki Nadiya! Ke in banda zamani ma da yazo mana da wani sakaran canji, ina har 'ya mace take da zabi akan wanda zata aura? Mutane nawa aka daurawa auren ba ma su san junansu ba, amma gasu har yanzu suna zaune da mazajensu lami-lafiya? Me kike tunanin ya kawo hakan idan ba bin maganar iyaye da yi musu biyayya ba? Idan kika hakura, kika mikawa Allah lamarinki kuma kika yiwa iyayenki biyayya, sai kiga sakayyar hakan ta zame miki abinda zaki duba a gaba kiyi farinciki da alfahari da shi!"

Ta daga baki zata kara mayar mata da wata amsar mai cike da gardama, sai taji wayarta tana kara yin kara. Ganin Anty Lima ce mai jera mata kiran yasa ta daga ta karata a kunne.

Ita kuwa tana jin ta daga tace mata, "amarya manya!"

Tayi dum, "kamar ya amarya?"

Tace, "amarya mana! Naji ance yau an kai kudin aure har an sanya ranar auren ma!"

Tace, "ashe ku har labarin ya riskeku? Ni sai yanzu nake jin labarin ma!"

Sai Anty Lima tayi dum, tace, "wai kin ma san waye zaki aura?"

Tayi dan tsaki, "ina fa! Ai bani ma da wannan mutuncin da za a fada min. Sai gargadin dolene in aureshi ko ba na so!"

Anty Lima kuwa ta kyalkyale da dariya, tace, "to fa! Wannan wane irin aurene haka?"

Ta tabe baki, "oho! Ni dai nasan rabon da ayi irin wannan auren tun zamanin su Inna Deluwa!"

Ita kanta Mama dake jinta a lokacin sai data saki dan murmushi, ta mata dakuwa da hannu tana cewa, "ki fa kiyayeni Nadiya!"

Anty Lima kuma tace, "ai ki ma kwantar da hankalinki. Don kuwa kin san ko ma wanene, kuma nasan ma In shaa Allah ba zaki ki shi ba don kuwa ba shi da makusa. Dan gidan Hajiya Ummah ne, Habibullahi!"

Kawai sai ta kashe wayar. Ta dora hannu aka ta dargwaje da kuka. Mama sai ta tsaya kawai tana kallonta cike da mamakin wannan abu na Nadiya.

Cikin kuka tace, "tabdijam! Wallahi Allah in dai wanda za a aura min ke nan na rantse da Allah sai dai a kai mishi..."

Mama tayi maza ta tareta, tace, "kul! Nadiya, kul! Ki kiyayeni da wannan zancen naki na banza da wofi!"

Sai ta kara sautin kukan nata, tace, "haba Mama! Wannan rashin adalcin da me yayi kama? Shi Abban yasan halin mutumin ne? Ko kuwa yasan da irin niyyar da suka zo neman auren nawa? Kawai don dukiya ta rufe mishi ido sai ya kama ya aurar da ni haka kawai?"

Mama tace, "ban fahimci abinda kike cewa ba? Wace niyya kike magana a kai?"

Ita kuwa ta zauna ta fada mata duk abinda Anty Lima ta fada mata, da dalilin auren da manufarshi.

Mama tayi shiru tana saurarenta har ta gama, tayi ajiyar zuciya. Tace, "hakika wannan ba dalili bane na neman aure. Amma kuma hakan ba zai zama sanadin wargajewar aure ba. Don haka shawarar da zan baki ita ce, ki dage da addu'a kawai. Idan alkhairinki ne, Allah Ya tabbatar da auren. Idan kuma ba alkhairinki bane, Allah Ya musanya miki da wanda ya fi shi. Don kuwa Nadiya, idan kinga an fasa wannan auren to ikon Allah ne kawai. Ya fi miki ki sanyawa ranki salama!"

Ta tashi ta bata waje tana kara fashewa da wani kukan.

Nan Amarya ta sameta itama da nata kalar ban hakurin da shawara, amma Nadiya bata yi alamun ta saduda ba. Sai gajiya tayi ta tashi, Mama da take jinsu ta girgiza kai kawai a ranta tana addu'ar Allah Ya sanyaya ran Nadiya din. Don kuwa rigima ce kawai za a sha da bacin rai a banza, don ta bangaren Abbansu fa aure babu fashi.

Ranar barci sai barawo. Nan ya saceta akan gadon Mama tana ta bakin rai, ko kayan jikinta bata iya cirewa ba.

Tunda asubahin fari kuma sai ga kiran Madam. Wai kiranta tayi ta tayata murnar auren da zata yi, sannan kuma tana so su fara tattauna shirye-shiryen da zasu yi. Duk da cewa dai ta bangaren ango sun ce aure kawai za a daura, babu events babu komi, sannan kuma basu bukatar a yiwa amarya komi, haka nan suke so a kaita zikal dinta. Amma ita Madam din saboda jama'arta dake nan Kaduna din da wadanda zasu biyota, dolene zata shirya liyafa.

Nadiya tace mata, "Mommy ki daina wannan shirye-shiryen don kuwa aure dai ba da ni za a daura shi ba. Nace bana so, kuma ba shi nake so ba. Don haka tun wuri ma a fada musu cewa su je su nemo matarsu a inda take!"

Madam kuwa tace, "an ki a fada musu din Nadiya! Amma ke za ki iya zuwa ki tari Abbanki ki fada mishi tunda shi ya amshi kudin ya kuma furta musu ya basu, ki ga idan bai karya miki kafafu ba! Wai ke me yasa baki da tunanine ko kadan? Arziki yana kiranki amma kina guduwa?"

Ta cune baki kamar tana gabanta, "to ni ai ban ce yazo inda nake ba ko? Kuma ma auren ai ba don manufar Allah da Annabi bane za a yi shi. Dukanku son ranku kuke bi shi yasa ni kuke shirin sanyani a tsakiya!"

Madam tace, "lallai Nadiya wuyanki ya isa yanka! Ni kike fadawa wannan maganganun?"

Tayi shiru tana ta harare-harare ita kadai.

Ita kuwa ta cigaba da cewa, "wallahi ki gode Allah ba a kusa dake nake ba da sai na zubda miki hakora wallahi, sai dai a kaiki gidan mijin da wawulon baki! Aure kuma ko? To sai dai kiyi duk abinda zaki yi, amma kamar an daura ne an gama! Ban da ma shashanci irin naki da rashin sa'a da rabo, kamar irin Hajiya Umma su nemi hada zuriya dake amma ki ce baki so? Kin kuwa san irin matan da ke kara-kaina a kanshi kuwa?Suna so ya daga ido koda sau daya ne ya kallesu amma ke kin samu hakan a banza ki ce baki so? Kina

ganin kin kai ajin Habibullahi kuwa? Ko baki san ya wuce da ajinki bane? Shashashar yarinya kawai wadda bata san Annabi ya faku ba!"

Ta kashe wayar.

Nadiya tayi zaune da waya a hannunta tana kallo, hawaye suna gangarowa akan fuskarta.

Can kuma sai ta share hawayen, ta shiga cikin jerin contacts dinta ta lalubo sunan Anty Jamila ta danna mata kira. Tana dagawa, kafin ta kai ga yi mata sallama ma, sai ta fasa mata kuka.

Nan da nan ta rikice ta fara tambayarta lafiya? Tana kuka da shessheka take fada mata ai Abbane zai mata auren dole. Bayan ita bata ma san mutumin ba kuma bata san halinshi ba.

Anty Jamila ta kama baki da mamaki, tace, "shi Abban?"

Ta amsa mata da saurinta, "eh! Wai har ya sanya rana bayan azumi da kwana goma...!"

Ta karashe tana kara sakin wani kukan.

Anty Jamila tace, "kada ki damu Nadiya, daina kuka kinji? Bari in kira shi muyi magana da shi ta fahimta. An mishi zancen Abdullahi ne?"

Tace, "ehh mana! Amma yace wai ya riga ya bada ni!"

Tace, "to daina kukan! Bari in kirashi yanzu!"

Tace, "nagode Anty. Don Allah ki fada mishi ni ba shi nake so ba, kuma mun riga munyi alkawarin aure da wani!"

Anty Jamila dai ta samu ta lallabata ta kashe wayar.

Ta koma ta kwanta tayi wani lamo sai kace abin tausayi. Bata yi niyar zuwa shago ba ranar sai da taga mutan gidansu suna neman wuce makadi da rawa sannan.

Shiga goma idan Amarya zata yi dakin Mama to sai ta rangadawa Nadiya guda ta bita da kirarin amare.

A gefe guda kuma ga su Salame can a tsakar gida suna ta sakin maganganu marassa kan gado suna shewa. Salame cewa take 'auren banza! Karyar tsiya ce kawai suke ba wani abu ba! Amma in banda haka, me zai hadin biri da gada? Farin ne fa kawai na fata ba wata tsiya ba!'

Maganganun nasu suka isheta, shima zaman ya isheta. Saboda bayan tunane-tunane da saka-da-warwara babu abinda take yi. Ta kuma kasa samun mafitar da take so.

Wajen karfe goma da rabi dai ta lallaba ta fito, rataye da yar karamar jaka a kafadarta. Har zuwa lokacin bata ko karya ba, har tayi wani zuru-zuru ta yi yar fuska.

Suka ci karo da Lantana a tsakar gida ita da wata yarinyar makotansu wadda yar dakin Salame ce. Hadiza ta kalli Nadiya tana ce mata, "kaji amare manyan mata! Sai muka sha kayan sanya rana yau. To Allah Ya sanya alkhairi!"

Nadiya ta kakaro murmushin yake tace, "uhm!" kawai tayi gaba.

Lantana kuwa ta tabe baki, ta harari Hadiza, "kin ji matsalarki ai ke kam! Kin iya zubar da aji a wajen da bai dace ba. Shi taya murnar auren na menene? Ni ai gwanda ma dai mutum yayi auren, ya shiga daga ciki dai yaji me ake ji, da irin masifar da ke cikinshi. An gama rabar da abinda ake auren dominshi a waje dai nasan mutum ai wallahi bai isa yayi daraja da mutunci a wajen namiji ba! Irinsu ne da sun shiga zaki ga an yo waje dasu! Yo ba a ganinsu da kima!"

Nadiyar tana jiyota, Amma ba ta tata take yi ba. Sai lokacin take fahimtar masu iya magana da suke cewa wai, 'ana ta kai wa ke ta kaya?!'

Hadiza kuwa sai ta kalli Lantana ta kyalkyale mata da dariya kawai ta shige dakin Salame.

Yadda kasan wadda kwai ya fashewa a jiki haka ta dinga takawa tana tafiya har ta fita bakin titi.

Kanta a kulle yake gam, ta rasa ta ina yakamata ta dafowa wannan al'amari daya kullo mata.

Tasan tunda Madam ta gama yin na'am da zancen, shima Abba ya amsar musu kudi, to zance ya kare. Don kuwa idan da akwai abinda Abbansu baya yi shine ya karbi kudin aure kuma daga baya yace zai maida haka kawai siddan, bai taba yi ba. Tasan kuma a kanta ba zai fara ba.

To amma kuma me yasa zai fara auren dole a kanta? Ya sha yin ikirarin cewa shi dai ba zai taba tursasa d'anshi ya auri wanda bai so ba tunda ba shi zai mishi zaman auren ba. To amma me yasa ita zai yi mata auren dolen? Saboda rashin galihu? Ko kuwa kudin daya gani ne suka rufe mishi idanu?

Ranar babu aikin data iya tsinanawa, yini tayi tana kiran Yayunta da abokan Abban da sauran Dattawan cikin danginsu da take ganin zasu iya sanyashi ya canza ra'ayi, amma bata samu taji zancen daya kwantar mata da hankali a wajen ko mutum daya ba.

21.

Ruwan da aka yini ana yi duk shi ya kara sanyaya mata jiki. Ranar ko da suka rufe shago bata tafi ba, ta zauna ita kadai anan tana ta lissafe-lissafen iska. Don kuwa duk zaren data kama sai taga karshenshi a cukurkude yake. Kawai sai ta tashi ta hau kaude-kauden kayan wajen. Washegari dai za a tashi da azumi da yardar Allah. Don haka sai can bayan Azzuhur zasu shiga shagon. Hatta da abubuwan da zasu bukata a washegari duk sai data fitar da komi, wai duk don ta cinye lokacinta anan don kuwa bata ma son komawa gidan da wuri.

Tana gudanar da yan goge-gogenta, yayinda take sauraren suratul Ma'idah daga speaker dake jone a shagon tana bi a hankali, ta ji alamun kamar ana kallonta.

Ta juya da shirin fadawa wanda ya shiga din cewa sun rufe shago, sai ta tsaya tayi kim tana kallon Habibullahi Babangidan Hajiya Ummah da shima yayi tsaye a bakin kofa yana kallonta.

Ya jima a wajen yana sauraren yadda take bin kira'ar karatun cikin taushin murya da kwarewa yadda kasan ita ce ma Alaramma Gwani Abdullahi Zariya gabadaya.

Ya dade yana kallon yadda take gudanar da ayyukanta cikin natsuwa da taka-tsantsan da kulawa. Yadda jikinta yake juyawa cikin wani salo mai daukar hankali da ita kanta bata san ta mallakeshi ba. Ya dan lumshe ido a hankali bakinshi dauke da murmushi marar sauti ganin yadda tayi wani kicin-kicin da rai, dan leben nan mai tudu da cika yana tabewa da melewa cikin alamu na tsiwa. A ranshi yake cewa, 'manta da matan da babu abinda suka iya sai kwalliya kawai da iya yi. Who like boring things? Ta kowace siga kuma, Nadiya is not boring. Macece mai cike da kalubale a tattare da ita iri-iri. Wannan challenge din, he wants to taste it!'

Ya taka a nutse zuwa kan kujeru da kwastomomi ke zama ya zauna yana kallonta, murya kasa-kasa mai cike da tura haushi yace mata, "two chocolate cupcakes please."

Aikuwa ta shaka din kamar yadda ya so, ta fara danna mishi harara kafin tace, "mun rufe shago na yau, za ka iya karawa gaba please."

Maimakon kuma ya tashi din, sai ya sake sakin murmushi, ya gyara zamanshi yana fuskantarta sosai. Yace, "Nadiya ko babu komi in ci darajar Angonki na gobe da zan zama. Bakonka Annabinka, ko kun rufe shago a matsayina na bakonki na cancanci ko da ruwa ne ai da lemu ko?"

Ta wani yatsine baki, "wani ango? Kuma wani aure? Ka je ka tambayi wanda ya baka auren kaji idan na yi na'am da hakan. Bako ko? To ba na maraba da kai, don haka zaka iya karawa gaba zuwa inda ake so ka je."

Ya dan yi ajiyar numfashi, "Nadiya, ki fa dinga duba irin maganganun dake fita a bakinki, ki bar ganin kina yaba min duk zancen daya zo bakinki fa ina yin shiru. I have my limits."

Ta kara tabe bakin dai, "sai ka daina zuwa inda nake kuma ka daina ja na da zance kaga idan hakan zata faru. Aure kuma ina kara fada maka, kaje ka kwashi kayan da kuka kai kasan ma inda zaka kaisu tun kafin lokaci ya kure maka. Ba zan aureka ba, ba kuma zan yi zaman aure da kai ba!"

Ya koma ya jingina da kujera tare da linke hannuwanshi a kirji yana jefa mata wani irin kallo, kallo mai cike da gargadin ta kama bakinta kamar yadda yace. Jikinta ya so yayi sanyin, amma ta ki ta saduda balle ta sadda kai. Gani take kamar idan ta mishi rashin kirki, zai iya janye maganar auren.

Sai kuma ya sake sakin wani murmushin, ya mata nuni da kujera tare da cewa, "ki zo ki zauna magana nake so mu yi dake ta fahimta."

Ta harareshi, ta harari kujerar daya nuna mata, ta kara gyara tsayuwarta alamun dai babu inda zata matsa.

Tunanin ta tafi ta barshi anan ma kawai take yi, ya ci kanshi shi kadai idan zai iya.

Shi kuma da yaga haka sai ya daga kafada, ya tashi shi ya bita har inda take. Ya tsaya a gabanta yana kallonta, hannu saye cikin aljihun wandon nikakken yadin Nules mai taushi ruwan zuma. An yiwa rigar dinkin senator daya tsaya mishi a gwiwa, hannun rigar kuma gajere ne.

Kusancin nasu yaso yayi yawa, amma tsabar taurin rai ta ki ta matsa ta ja da baya. Ta kama kugu tana kallonshi ido cikin ido fuska a cune tana hararshi.

Da ta san yadda hakan yake kara kayatata a cikin ranshi, kila da bata yi hakan ba.

Ya daga baki yana mata magana, kamshin mouthwash mai citrus yana bugunta a fuska. Yace, "zuwa nayi kiyi min list abubuwan da kike bukata. Zan je Umarah cikin wannan satin, so daga can nake so in sayo duk abinda ya dace. Ina son sanin size din takalminki, maybe har tsayinki saboda dogayen riguna ko? Da kuma irin kalolin da zaki fi so... Sai kuma me ma...?" ya dakata da lissafin da yake yi cikin alamun tunani. Ita kuwa ta saki baki da hanci tana kallonshi, bakinta ya ma kasa motsawa balle ta katseshi.

Yace, "yauwa, an ce har da size din undies da kuma....!"

Ta daga hannu cikin karaji, "dakata Malam! Dakata nace!!"

Ya kuwa yi shiru yana kallonta, idanunta har wani ruwa suka samu kawowa na tsabar bakin ciki da takaici.

Tace, "wai baka ji me nake cewa bane? Aure na ce bana yi, ba zan yi ba. Don haka a matsa gaba. Kada ka sake yi mun wannan zancen, tam!"

Yace, "idan kuma na ki fa?!"

Tace, "sai ka san wadda zaka yi zaman auren da ita, Amma ba da ni ba. Ban da ma tsabar rashin zuciya an ce maka ba a sonka Amma sai ka nacewa mutane? Ina dalili!"

Yayi maza ya hade fuskarshi, dan murmushin dake kai ya bace bat! Yace, "ki daina ganin fa ina zaune kina dankara min magana son ranki Nadiya, idan nace zan baki amsa ba dadinta zaki ji ba. Aure kuma da kike cewa na dole ne, ai ba ni ne na tilasta miki ba ko? Kuma ba ni ne na karbi kudin auren naki ba. Yadda kike ihu da ikirarin auren dole nima ai auren dolen ne, ba cewa

nayi na gani ina so ba, amma duk da haka ai baki ganni ina ihun ba zan aureki ba ko?"

Bata san ya aka yi maganar tashi ta bata mata rai sosai da sosai ba. Sai kawai ta saki wani irin tsaki, tace, "kada ka raina min wayau mana! To waye yace yana so ka so shi dama? Sonka din banza! Auren kuma da ba da zuciya daya za a yi shi ba menene amfaninshi?"

Yace, "hala ke ce zaki yi shi ba da zuciya daya ba ko? Ni dai nasan da tsarkakkiyar zuciya zan yi shi"

Tayi mici-mici da idanu, "Allah sa ma da daudaddiyar zuciya zaka yi shi, ni meye nawa a ciki? Ni dai na fada aure ne ba zan yi ba!"

Hannu ya sa ya murde mata baki, duk dauriyarta sai da taji kamar ta saki fitsari a wajen saboda azaba. Ya jefa mata wani wulakantaccen kallo, yace, "believe me Nadiya, idan da ba don umarnin mahaifiya ba, ko a kafa aka daura min ke zan kunceki ne in ruga nima. Aure kuma, sai anyi shi ko kin ki Allah. Don Allah idan an daura mana auren kiyi abinda zaki kinji? Magana kuma da kike yi duk yadda ta zo bakinki ki cigaba, but consider yourself warned Nadiya. Nan gaba zan miki abinda ya fi murde baki ma!"

Ya zagayeta ya fita daga shagon ba tare daya kara kallonta ba.

Ya bar ta nan tana ta aikin tsiyayar da hawaye, rannan bakikkirin. Ji take kamar ta dinga kwala ihu saboda takaici. Waye shi? Me yake takama da shi? Shi har ya isa ya zo inda take ya dinga zabga mata maganganu marassa dadin ji ma kamar haka? Amma ta kasa daga kafa ta bi bayanshi kamar yadda zuciyarta take umartarta da tayi hakan.

Nan ta kara jimawa tana shakar kuka, da kyar ta iya hada nata-i-nata ta wuce gida.

Ranar sai wajen karfe tara ta koma.

Tana dira kuma Abba ya tareta da nashi fadan, Aiken data dinga mishi na mutane akan maganar ya janye aure. Ya zageta tas, yace aure kuma babu

fashi tunda ya karbi kudi. Don kaniyarta ta kashe kanta in taga dama ma karewa.

Ta koma daki nan ma Mama da Amarya suka sanyata a gaba da nasu kalar wa'azin da nasiha, ita dai kam ji take yi duniyar ma gabadaya tana wani juya mata. Ji take kamar duka mutanen duniyar sun hade bakine sun juya mata baya.

Da abin ya isheta Sai ta dargwaje musu da kuka, amarya ta fara aikin lallashinta Mama kuwa sai ta saki tsaki, tace, "don Allah kyaleta taje tayi duk abinda taga dama kuma tunda dai ta ki jin lallashin. Yarinya a dinga dama da ke amma kiyi biris da mutane saboda kunnen kashi ne da ke? Sai kiyi duk abinda kike ganin daidai ne a wajenki tunda mu ba zaki ji maganarmu ba."

Ta karkade zaninta ta barsu anan amarya na kara bata baki.

Aka kai mata abincin dare, ta samu ta tsakura haka nan ta barshi anan. Wayarta ta kashe gabadaya saboda taga Anty Lima na ta danna mata kira, ga Abdullahi da shima har ya gaji da kiran ya koma aika sakonni. ita kuma bata son takura ko kadan.

Saboda ciwon da kanta yake mata sai data sha magani sannan ta kwanta. Ko a cikin barcin ma, tufka kawai take yi da warwara, yadda zata samu ta bulle daga wannan aure. Shi yasa barcin bai haifar mata da komi ba sai tarin ciwon kai da ciwon jiki daya bar mata.

Da kyar ta iya tashi can wajen karfe biyun dare, ta dauro alwala mai kyau ta je ta fuskanci alkibla ta fara sallah. Koda ta daga hannunta sama, bakinta dauke yake da addu'ar Allah Ya hana yiwuwar wannan aure ta huta.

Bata samu ta kwanta ba sai da suka yi sahur sannan. Wannan karon kam barcin mai nauyi tayi sosai, don bata tashi ba sai can wajen karfe goma sannan.

Shima vibrating din wayarta ne ya tasheta. Ta zauna da kyar har wani jiri-jiri take gani ta daga wayar. Tayi tunanin Anty Lima ce ko Abdullahi, amma ga mamakinta sai taga Safiya ce.

Tayi dan murmushi, a ranta tana cewa yau watarana? Watakila itama ta kira ne ta mata tsiya kamar yadda jiya su Aysha suka dameta da Rabi'ah.

Ta daga murya a shake mai cike da barci, "Hello, Sophie manyan kasa. Ya kike?"

Shiru ta ji tayi kamar babu kowa ma akan wayar. Ta fara "Hello... Hello?! Kina ji na?!"

Zuwa can kuma sai taji kamar ana shesshekar kuka. Sai jikinta yayi sanyi, tace, "Safiya? Lafiya, me yake faruwa?"

Cikin rishin kuka tace, "har kina da bakin tambayata lafiya bayan abinda kika yi mun?"

Kanta ya daure da mamakin wannan abu, tace, "ban gane ba, me kike nufi Safiya? Me nayi miki kuma?"

Tace, "in case baki sani ba, Habib was meant to be mine, ba naki ba! Anyi mun alkawarin aurenshi tun ba yau ba, na gama tsara yadda rayuwata zata tafi a matsayin matarshi tun kafin ki san da zamanshi. Me yasa zaki zo ki wargaza min shirina? Me yasa zaki shiga cikin rayuwata? Me na miki?!"

Ta dargwaje da wani irin kuka mai tsuma zuciya.

Nadiya ta kasa cewa komi. Ta rasa abinda zata ce. Sai da kyar ta iya daga baki tace, "ban san me kike cewa ba Safiya, Amma ina mai tabbatar miki da cewa ko ma menene, ban san komi akai ba. Yadda kika ji maganar auren nan sama-ta-ka, nima haka na ji ta. Ni wallahi neman ma yadda za ayi in rabu da wannan karangiyar auren nake yi amma na rasa ta yaya zan yi hakan!"

Safiya ta ja hanci, tace, "kada kiyi gaggawar bari kanki ya fasu don kinga an zabeki a kaina. You don't know half of what's awaiting you a cikin wannan auren. Ki kula!"

Da wannan gargadi mai girgiza rai ta kashe wayar.

Nadiya ta bi wayar da kallo ranta a jagule, har ga Allah ranta bai yi mata dadi ba. Yadda taji Safiya tana kuka ya sanyayar mata da jiki, daga jin yadda take yin kukan kai da kanka kasan cewa da gasken yi take yi, da gaske son Habibun take yi. To ita kuwa me zata iya yi akan haka? Wannan abu ne wanda ya fi karfin tunaninta.

Ta kira Anty Lima, saboda ita kadai ce wadda ta fi kusa da duka Madam da Safiya. Tana da tabbacin zata iya sanin ko ma menene yake wanzuwa.

Anty Lima ta ja numfashi ta aje bayan da Nadiya ta gama kora mata bayanin abinda ya wanzu. Tace mata, "tabbas, wannan zance haka yake. Tun farko, Madam ita zabinta shine Safiya ta auri Habib. Naji ita kanta ta gama tsara komi, har yadda karatun Safiya din zai kasance bayan auren nasu. To kuma abinda duk basu yi tsammani ba shine da aka zabe ki a madadin Safiya din. Babu wata amsa da suka bayar wadda ta wuce cewa kin girmi Safiya, kuma kin fi ta sanin rayuwa. Don haka ne sai itama Madam din ta ajiye zancen auren su Safiyar a gefe. Ita kuma tun bayan da Madam ta bata tabbacin cewa Habib nata ne, saboda tana da tabbacin cewa za a zabeta, sai kawai ta ba ranta cewa ya zama mijin nata. Kawai ta fara son shi abinta da tsara abinda zai faru idan ta aureshi. Nima ta kirani dazu tana kuka ta ce min Madam bata kyauta mata ba."

Nadiya ta dafe gefen kanta da yake matukar sarawa, tace, "me zan yi Anty Lima? Yaya zanyi? Bana son abinda zai sa in shiga hakkin wani ko kadan Anty Lima. Bana so in zalunci rayuwar Safiya!"

Anty Lima tayi kasa da murya cike da lallashi, tace, "Nadiya, babu zancen cin zali a cikin wannan magana. Ba ke kika ga Habibu kika ce kina son shi ba, ba

kuma ke ce kika ce kina son shi ba. Me yasa ba zaki zauna kiyi tunanin watakila alkhairin a tattare da ke yake ba da Safiya ba shi yasa aka zabeki a madadinta? Kada kiyi butulci da ni'imar Allah Nadiya. Ke da bakinki kike fada min addu'ar da kike yi akan Allah Ya kawo miki miji kiyi aure, me yasa kuma yanzu kin samu damar hakan kike neman butulcewa Allah? Sai me don manufar Hajja Umma da Madam ta daban ce game da auren? Ke ki yi shi don Allah mana, ki yi shi don saboda raya sunnar Ma'aiki Sallalahu Alaihi Wa Sallam!"

Nadiya tayi shiru hawaye suna tsiyaya daga idanunta, maganganun Anty Lima din suna ratsata.

Tace, "to Safiya fa? Kinji fa cewa tayi...!"

Anty Lima tace, "ki manta da zancen Safiya Nadiya. Ki duba gabanki ke dai. Safiya a yanzu take kan ganiyar yammatancinta. Ina kuma kara tabbatar miki da cewa, ba son Habibullahi take yi ba, son irin rayuwar da zata yi a matsayin matar Habibullahi dinne take yi. Saboda tun farko da irin wannan tunanin Madam tayi galaba a kanta ta shuka mata irin wadannan tunane-tunanen. Don haka ki kwantar da hankalinki, Safiya is an adult, ki barta tayi dealing da matsalar da ita ta janyowa kanta ba ke ba!"

Ta gyada kai a sanyaye, "nagode Anty Lima!"

Tayi dan murmushi, "anytime Nadiya, anytime!"

Ta kashe wayar itama tana dan murmushi. Sai taji ranta ya dan yi mata dadi. Magana da ita ya sanya taji wata natsuwa tana shigarta a hankali.

Mama da take sauraren hirar tasu, tayi dan murmushi itama a hankali. Ta cigaba da jan carbinta tana hailala da salati.

22.

Karfe bakwai saura, ya shiga gidan nasu. Daga Masallaci yake, hannunshi rike da hannun Ammar da ke ta bashi labarin irin abubuwan da suka faru a makarantarsu yau.

Kai tsaye bangaren Hajiya Ummah ya wuce kamar yadda al'adar gidan nasu take. Duk azumin duniya a can suke shan ruwa. Haka karin safe da abincin dare kullum a can suke haduwa da duka iyalan gidan su ci.

Ya samu Shukurah zaune a tsakiyar hadadden falon na Hajiya Ummah. Tsarinshi da komi na falon idan ka gani sai kayi tunanin ko wani gidan sarauta ne ka shiga.

Ta dan kalleshi a kaikaice lokacin daya shiga, ta mayar da kanta kan tarkacen kayan shan ruwa da ke gabanta, har ta rasa wane abu ma zata ci daga ciki.

Hajiya Ummah kuma tana kan dinning a zaune, da alama itama sai lokacin take buda baki. Ya wuce wajenta kai tsaye shima ba tare daya kara kallon inda Shukurah din take ba.

Ammar ya karasa wajen Hajiya Ummah da sauri, ya zauna akan kujerar dake kusa da tata. Babu bata lokaci ya sanya hannu cikin fruits da aka yanyanka ya dauki tuffa ya kai baki. Daga Habibun har ita, murmushi kawai suka yi a tausashe.

Ya karasa haye matakalar da zata sadashi da teburin, shima ya ja kujera dake fuskantarsu ya zauna. Ya bude baki yana gaishe da Ummah din tare da yi mata barka da buda baki.

Ya dauki faranti yana kokarin zubawa kanshi abinda zai ci, yayinda ita kuma Hajiya Ummah ke bude baki tana kiran mai mata girki, Lailah. Nan da nan sai gata ta fito daga kicin kamar dama jiran kiran take yi.

Tace mata, "zubawa Babangida abinci."

Ko kafin ma ta kai ga daga kafa ta karasa kusa dashi, ya dakatar da ita. Yace, "bar shi kawai, zan zuba da kaina."

Don haka ta juya ta koma inda ta fito. Shi kuma ya zuba kayan marmari da kunun tsamiya a cikin kofi ya koma ya zauna. Yawancin lokuta bai cika cin abinci ba idan yayi azumi har sai bayan yayi sallar isha'i.

Ummah ke jan shi da hira game da tafiyarshi Umarah tunda shi zai rigasu tafiya ita da Shukurah, da abubuwan daya kamata ya duba game da kayan lefe da za a hada.

Shukurah da take jin maganganun da suke tattaunawa, ta ture kwanon Sultan chips dake gabanta, ta tashi tana kokarin fita daga falon.

Ummah ta daga murya tana kwala mata kira, "Shukurah ina zaki je ne haka bayan ko sallah baki yi ba?!"

Bata amsa ba, ta bude kofa tayi fitarta tare da maida kofar ta rufe da karfi kamar zata babbagota daga jikin ginin.

Ya kawar da kanshi kamar bai san abinda suke yi ba, Ummah kuma ta dan girgiza kai. Itama bata sake mishi maganar ba sai ta cigaba da zana mishi lissafin abubuwan da take yi.

*

Karfe tara ya koma cikin falon bayan da suka gama sallar isha'i da kuma Tarawihi. Wannan karon Ammar kadai ya samu akan kujera yana barci. Ya gyara mishi kwanciya kafin ya wuce kan dinning kai tsaye. Ya zuba soyayyiyar shinkafa data sha naman sa zako-zako, ya hada da zobo ya zauna ya fara ci. Hankalinshi na kan TV inda ake hasko labaran duniya.

Anan Hajiya Ummah ta sauko kasa daga dakinta ta zauna itama tana kallon labaran da yake ma'abociyar kallonsu ce.

Ya ture kwanon abincin gefe guda, ko rabi bai samu ya iya ci ba. Ranshi a jagule yake kwarai da gaske, akwai wani abu dake mintsininshi a can kasan ranshi a cikin yan kwanakin. Ran nashi ya ki yi mishi dadi sam.

Ya taka a nutse ya karasa inda Ummah take, kafafunshi suna nutsewa cikin tattausan carpet da aka lullube tsakiyar falon da shi. Ya zauna a kasan carpet din kusa da kujerar Umman.

Haka suka cigaba da kallon, jifa-jifa su kan tattauna wani abu idan aka fada a cikin TV din, har dai aka gama shirin.

Ummah ta kira Lailah taje ta dauke Ammar ta kwantar da shi a dakinshi da yake anan bangaren Hajiya Ummah din yake da zama.

Shi kuma sai ya juya yana kallonta a nutse, yayi kasa da murya, yace, "Ummah dama cewa nayi ko wannan azumin a kai Ammar wajen Yadikko ne? Rashida tace tana son ganinshi saboda wancan zuwan da muka yi tana makaranta."

Nan da nan kuma sai tayi kici-kici da fuska, tace, "wani irin zuwa Makarfi kuma? Duka-duka kuma yaushe ne kuka je Makarfin har kuka kwana? Ina ce ko watanni biyu cikakku ba a rufa ba?"

Yayi kasa da kanshi yana jinjinawa, "haka ne Ummah. To zan fada musu hakan. In yaso ita Rashidar sai ta zo nan din, bayan sallah sai ta koma ko?"

Nan ma fuska babu walwala tace, "Allah Ya kawota lafiya!"

Daga haka suka dan yi shiru su dukansu. Zuwa can kuma ta kalleshi a tausashe, tace, "ka tashi kaje ka kwanta haka nan ko? Karfe nawa ne kace jirgin naku zai tashi?"

Yace, "sai jibi in Allah Ya kaimu, karfe goma na safe."

Tace, "ai nayi zaton gobene tafiyar. Allah Ya kaimu jibi din. Nima kwanciya zan je inyi."

Don haka yayi mata sai da safe. Ya jira har sai data haye sama kafin ya leka dakin Ammar ya samu yana barcinshi sosai, ya mishi addu'ar kwanciya barci kafin ya wuce sashenshi.

Ruwa ya watsa, ya fito daure da bathrobe ya tsaya a gaban mirror yana goge jikinshi. Bayan ya gama al'adar shafe-shafenshi daya saba, ya lalubi pyjamas ruwan madara masu taushi ya sanya. Ya sake bin jikinshi da turarenshi ya fesa.

Har ya nufi kan gado, sai kuma ya juya. Ya dauki wayarshi dake kan bedside drawer, ya fita daga bangaren nashi.

Gidan nasu babban gidane, an ginashi tun lokacin Mahaifinshi yana matsayin General ne. Wajene wanda yayi gadonshi tun Iyaye da Kakanni, daga baya kuma bayan rasuwarshi aka fadadashi aka hadeshi da wasu filaye. A yanzu kuma ya zama gida wanda za a iya cewa gari guda. Estate ce babba, wadda ta kunshi gidaje part-parts. Akwai bangarenshi, ga bangaren Ummah, ga bangaren Shukurah, bayan su ma akwai wasu parts din fiye da uku. Akwai waje na musamman da aka ware na motsa jiki, akwai wajen wasan yara, akwai babban garden da wajen shakatawa da shan iska, akwai madaidaicin masallaci a cikin gidan. Ga ma'aikata bila adadin da ko wane lokaci zaka samesu suna ta kaiwa da kawowa abinsu.

Ya wuce bangaren dake kusa da nashi, wanda kuma nan ne za a sauki Nadiya a cikinshi, ya shiga na kusa dana Ummah wanda na Shukurah ne.

Yanayin tsarin gine-ginen kusan duk daya ne da na sauran idan ka debe nashi da na Hajiya Umma.

Falon nata sai kamshin turaren wuta yake ga AC dake kara sanyaya dakin. Ya duba falon yaga bata nan, kai tsaye sai ya wuce dakinta.

Ya sameta tsaye tana kokarin ninke abin sallah, da alama sallah ta gama yi.

Ya wuce ciki kai tsaye ya zauna a gefen gado yana kallonta har ta gama ninkin, ta cire hijabin jikinta. Itama kayan barcin ne a jikinta, da alama ta gama shirin barci.

Ta haye gadon kai tsaye ba tare data tankashi ba, ta fara kokarin jan bargo ta rufa. Ya bita da kallo ranshi yana kara baci, yana kokarin dannewa.

Kawai ya kai hannu ya warci bargon yayi jifa dashi. Ya bita da kallo fuskar nan a hade, yace, "bar ganin wai ina binki kiyi zaton wannan guntun fushin da kike yi yana damuna ne Shukurah. Kawai ina kokarin sauke hakkinki ne dake kaina, tunda naga ke baki san sauke nawa hakkin dake kanki ba. Don zan kara aure shikenan sai in zama makiyi a wajenki, dama ana hakane Iye? To idan zaki sanyayawa ranki ki hakura, kiyi hakan. Idan kuma ba zaki iya ba, sai kije kiyi tayi. Aure dai ba zan fasa yi ba, ina ga ita kanta Ummah ai ta fada miki hakan ko? Ni dai kam ta bangarena, ba zan zauna ina bin kanki ba kamar yadda take yi. Jibi zan tafi Umarah kamar yadda kika ji ana fadi, kuma ba zan dawo ba har sai bayan sallah. Don haka ki zana min duk abubuwan da kike bukata inji, idan kuma har yanzu kina ganin bani da wannan matsayin a wajenki, sai ki fadawa Ummah."

Ya tashi tsaye yana kallonta, tayi zaune tana hararar waje daya idanunta sunyi rau-rau kamar zata yi kuka. Ganin ita yake kallo yasa ta daga baki da kyar tace mishi, "ni ba na bukatar komi!"

Ya tabe baki yace, "ba laifi!" ya juya abinshi.

Har ya kai bakin kofa yana kokarin budewa, ya ji an rungumoshi ta baya. Kawai sai ta fashe mishi da wani irin kuka mai sanyaya jiki. Tayi-tayi har ya isheta, bayan rigarshi ya jike da lema.

Yana da tausasawa, kuma in ta shi ne, mace ba zata yi kuka a gaban idonshi ba. Ko me yake ganin zai yi, zai yi kokarin yi wajen ganin hawaye bai kusanci idon kowace ya mace ba, balle matar da yake aure. Ya kuma san sanin hakan da tayi ne yasa take mishi kukan, bata san ko hawayenta karewa zasu yi ba akan maganar wannan sai dai su kare, amma ba zai fasa auren wannan ba. Ko ba don Ummah da burikanta ba, ko ba don sanin manufar wannan aure ba, to don kanshi kawai, ba zai iya fasa wannan auren ba.

Ya sanya hannu ya zagaya da ita gabanshi suna fuskantar juna. Abinka ga farar mace, fuskarta har tayi ja na kukan da tayi. Ya fara share mata hawayen idanunta yana kokarin tausarta, ta kama hannunshi ta rike kam, hawaye na kara cika idanunta.

"Honey, ba zan iya hadaka da wata ba, ba zan iya rabaka da wata ba, ba zan iya zuba ido in ga kana kulawa da wata kamar yadda kake kulawa da ni ba. Me nene bana maka? Menene baka so a tattare da ni? Zan iya canzawa, zan iya gyarawa. Don Allah Honey...!"

Sai ta sake rushewa da wani kukan tana kara rirrike mishi gaban riga.

Ya kama hannunta ya ja har zuwa bakin gado, suka zauna su duka.

Yace, "wai har sau nawa ne kike so in fada miki cewa babu ko daya daga cikin wadannan abubuwan? Ko baki ji me Ummah tace miki bane ranar nan wai? Ba tace miki kiyi hakuri ba? Me yasa wai ba zaki iya hakuri ki yarda da kaddara bane? Ina ce matan ma bayan ke an halatta min har guda uku matukar zan iya yin adalci? Kuma ina da yakinin zan iya daidaita adalcin. Me yasa ba zaki yarda da maganar Umma ba at least, idan baki yarda da maganata ba?"

Sai tayi shiru tana shessheka. Tace, "to naji, amma kayi min alkawarin koda ta zo, ba zaka taba daukar soyayyarka ka bata ba!"

Ya saki wani dan murmushi yana kare mata kallo, "kin taba jin irin wannan auren ne dama Shukurah?"

Taga dai kwata-kwata abinda take son samu ba zata sameshi ba, sai ta juya mishi ta wani bangaren. Tasan ta wannan bangaren, ba zai taba iya ce mata a'ah ba. Tunda sau nawa take cimma bukatunta ta wannan hanyar?

Ta fada jikinshi tana sanya hannunta cikin rigarshi inda boturan basu gama rufewa ba, ta fara yawo da hannun cikin salo na daukar hankali da kissa. Nan da nan kuma sai ta samo kanshi, abinka da mai neman kuka aka jefeshi da kashin awaki.

Sai data bari yayi nisa a can duniyar data kaishi, jikinshi ya gama dauka gabadaya har wani bari yake yi, sai kawai ta janye jikinta, ta ja bargo tana rufe jikinta.

Ya zuba mata idanu da suka shige ciki, suka fara rinewa cikin wani irin yanayi, bacin rai yasa ya ma kasa yi mata magana. Ta kalleshi tana yin wani takwa-takwa da fuska, "ni dai gaskiya ba zan iya hada jikina da naka ba bayan nasan cewa nan gaba kadan zaka taba jikin wata. Kayi min alkawarin jikinka ya zama nawa ni kadai, kayi min alkawarin ba zaka mallaka mata jikinka ba, ni kuma na maka alkawarin mallaka maka nawa jikin."

Ya lumshe idanu zuciyarshi na wani zafi, jikinshi ma kokarin daukar zafin yake yi. Lokaci mai tsayi ya dauka a haka, kafin ya tashi zaune ya dauki kayanshi da suka yi fatali da su ya sanya, kafin ya kalleta da idanunshi da suka yi mici-mici.

Yace, "mantawa kike yi, cewa daga lokacin dana bada sadakinki kuma shaidu suka shaida aurenmu, jikinki ya gama zama nawa. Zan kuma iya yin duk abinda nake so da shi a duk lokacin da naga dama, ke kanki baki isa ki hana ni ba. Don haka ki daina mistaking cewa kina da ikon hanani, bana son tursasa mutum, ba kuma zan kusanceki alhalin baki so ba shi yasa kika ga nake binki a hankali. A hakan kike so in miki alkawarin ba zan kusanci wata matar bayan ke ba? A hakan Shukurah? Kina hanani hakkin nawa a lokacin da nake so? Kina wancakali da duk wani lamari nawa kamar ba mijinki ba? Kina amfani da abinda yake hakkina ne kina blackmailing dina da sanyani yin abinda ban yi niyya ba bayan Allah ne Ya halasta min? A hakan Shukurah?!"

Kawai ya juya ya bar mata dakin. Saboda yasan idan ya cigaba da magana ma ranshi ne zai kara baci. Bai san ma ya aka yi har ya biye mata ba, bayan dama zuciyarshi sai data dinga mishi saka da wasi-wasin kada ya biye mata ya afka cikin dana sani.

Ya tura kofar dakinshi a zafafe ya shiga, kai tsaye bandaki ya fada ya sakarwa kanshi ruwan sanyi. Yayi shiru yana sauke wata irin ajiyar zuciya mai matukar nauyi. Ranshi ya kara dagulewa. Shekaru uku kenan tun bayan aurenshi da Shukurah. Har yau yana iya tuna lokacin da Ummah take fada mishi cewa ta samar mishi wata matar bayan da suka gama gano cewa wadda yake gab da aure ba son Allah da Annabi take mishi ba. Shi kuma ya amshi auren a take, ba tare da musu ba. Aka kuma daura auren cikin abinda bai gaza wata daya ba. Ita kanta Matar sau biyu kadai ya ganta kafin bikin nasu. A kuma duk ganin da zai mata, bai ga bambancinta da wadda suka rabu ba. Su duka arzikinshi da rayuwar dadi da zai samar musu suke so, ba shi a karan kanshi ba.

Lokuta da dama kuma yana zama ya tuhumi kanshi, me yasa bai ce a'ah ba? Me yasa bai ce a'ah ba?

Ya jima sosai a cikin bayin kafin ya fita, ya sake kimtsawa kafin ya kashe wuta ya lalubi gado. Har zuwa lokacin ranshi a jagule yake. Jikinshi kuma ya mutu murus. Yayinda a can kasan zuciyarshi wani sashe yake tambayarshi, 'me yasa wannan karon bai ce a'ah ba? Me yasa ba zai ce a'ah ba?'

23.

Washegari da yamma, ya shiga sashen Ummah sanye cikin dakakkiyar shadda fara, yana ta baza kamshin nan nashi.

Falon nata tuni ya gama rikicewa da kamshin kala-kalan abincin buda baki da ake hadawa.

Ummah ta kalleshi cike da mamaki, "ina zuwa ne haka Babangida da wannan yammaci?"

Yayi dan murmushi yana gyara zaman hular dake kanshi, "wai wata yar unguwa ce zan leka amma yanzun nan zan dawo."

Ta kalleshi cike da mamaki, "unguwa kuwa da wannan yammaci Babangida, ana gab da shan ruwa?"

Yace, "ehh. Abin gobe zan tafi, Matar abokina Mus'ab ta haihu shi yasa nace zan je in gano baby saboda da dare ina da wata tattaunawa da su Kawu Haruna to ba lallai in samu zuwa ba!"

Sai ta gyada kai cikin alamun gamsuwa, ta san shi da son yara sarai, duk inda yaji anyi haihuwa, to shi kuwa a tafe yake yaje ya ga baby. Baya da wannan kasa a gwiwa din.

Tace "to a dawo lafiya. Kayi kokari dai ka dawo da wuri kafin lokacin shan ruwan ya kure."

Ya amsa mata da, "to Ummah"

Ya fita.

A bakin kofa suka ci karo da Shukurah ita kuma zata shiga. Tana ganinshi ta wani dauke kai kamar bata ganshi ba. Shi kuwa ya ratsa ta gefenta ya wuce shima bai nuna alamun ya ganta ba.

Mota daya ya dauka, kuma shi kadai. Koda direba ya taso da securities dinshi biyu, sai yace musu su yi zamansu kawai saboda ba jimawa zai yi ba.

Aka bude mishi gate ya fita, kai tsaye ya dauki hanyar 'Diamond Ara Cakes and Snacks'

m

Farfajiyar wajen babu komi idan ka dauke ababen hawan ma'aikatan wajen. Yayi parking din motarshi, ya dakata daga ciki bai fita ba ganinta da yayi tana kokarin fitowa daga shagon.

Abaya ce a jikinta ruwan zuma da aka yiwa adon furanni ruwan madara. Tayi nadin gyalen a fuskarta inda ya fitar mata da fuskarta tayi round, kumatunta da lebunanta da suke a cike suka mayar da ita kamar wata Balarabiyar kasar Oman.

Ya kara gyara zamanshi yana kallonta, yadda take tafiya a nutse, hannunta daya dafe da wayarta a kunne tana kyalkyala dariya. Komi na Nadiya ya mishi. Bai san ta yaya, ko a wane lokaci Nadiyar tayi mishi irin wannan kamu na kazar kuku ba.

Ya bude murfin motar ganin tana kokarin wuceshi. Kawai ganin mutum tayi a gabanta sai kace wanda ya dira daga sama.

Tayi baya da sauri hannu dafe da kirjinta saboda yanda ya tsoratata. Da ta fahimci ko waye yayi mata wannan aika-aikar, sai ta ja fuska kawai tayi kokarin bi t gefenshi ta wuce, shi kuma yayi saurin sake shan gabanta. Ta sake juyawa ta daya bangaren, nan ma ya sake binta.

Sai ta cewa Rabi'ah da suke waya da ita, "zan sake kiranki Rabi'ah!"

Ta kashe wayar, shi kuma ta bi shi da wani irin kallo cike da kufula, tace, "lafiya?"

Ya langabar da kai gefe daya, "don Miji ya zo gaishe da Matarshi dama hakan ya taba zama laifi ne da za a ke tambayarshi lafiya?"

Ta ga idan tace ma zata tsaya bashi amsa rai kawai zai bata mata a banza, sai ta kankance idanu tace mishi, "ba ni hanya in wuce to!"

Yayi wani irin murmushi, "ko kuma ki shige mota mu tafi ko?!"

Ta ma rasa me zata ce mishi. Wannan abu na Habibun Hajiya Ummah nema yake yi ya wuce misali. Ta rasa ta ina zata bullo mishi kuma. Mutum a dinga yakiceka amma kana bin mutane sai kace wani guntun cingam?

Tace, "Malam ka bani hanya in wuce wallahi ko in tara maka jama'a a wajen nan!"

Yace, "kafin mu kai ga hakan ma zaki shige mota mu tafi..."

Ta daga baki zata mishi musu, ya hade fuska, "I am not asking Nadiya. Ki wuce muje kawai kafin in miki abinda ke zai tara miki jama'a anan wajen!"

Akwai wani abu can cikin idanunshi data hanga dake nuna mata cewa da gasken gaske yake, ba kamar ita dake cika baki ba da ban tsoro, shi kam idan ta kai ga hakan, zai aikata abinda yace din ba tare da bata lokaci ba.

Ta daga kafa ta nufi wajen motar tashi as if in a trance, kamar wadda wani maganadisu yake ja. Yayi murmushi cike da samun nasara, ya wuce ya bude mata gaban motar da kanshi ta shiga, ya mayar ya rufe.

Ya zagaya ya shiga, ba tare da bata lokaci ba ya ja motar suka dauki hanya.

Tuki yake yi cike da kwarewa da natsuwa a tattare dashi. Ta kurawa waje daya idanu tana kallo tun bayan shigarta motar. Shima kuma da yake tunda ya fara tukin bai sake nemanta da wani zancen ba sai abin yafi yi mata sauki.

Ya kaita har kofar gidansu yayi fakin. Ta bude motar ta fita abinta babu ko godi bare na gode. Tana jin lokacin da shima ya bude bangaren da yake ya fita, ya kira sunanta da wata irin murya mai sanyi da taushi data sanya ta dakata da tafiyar da take yi ta juya tana kallonshi ba tare da zuciyarta da gangar jikinta sun gama aminta da hakan ba.

Yace mata, "Gobe zan wuce Umarah, ba zan samu ko addu'ar Allah kiyaye bane a wajenki Nadiya?"

Tace, "idan kaje don Allah ka roka min Allah Ya yaye min wannan kidagar auren da aka kakaba min, ya koma kan mai so!"

Maimakon abin ya bata mishi rai kamar yadda taso, sai ma hakan ya bashi dariya. Yayi dan murmushi yace, "zan dai yi addu'ar Allah Ya baki ikon fito da wannan son nawa dake makale a cikin zuciyarki kina kokarin boyewa. Ya kuma kakaba miki son nawa ya zamana idan zan yi tafiya irin haka ba zaki taba iya jurewa ba!"

Tayi wani irin murmushi na bacin rai, tace, "son ka kuma? You wish!" Ta wuce gida abinta.

Shi kuwa har da komawa ya jingina da motarshi yana kara kallonta har ta shige gidan. Yayi ajiyar zuciya a hankali yana furzo da wani numfashin daga bakinshi.

Yara biyu matasa ya samu ya bude musu booth din motarshi yace su kwashi kayan su shigarwa Nadiya da su. Ya sallamesu kafin ya ja motarshi yayi gaba kafin ma su gama shigewa gidan don yasan kadan daga aikin Nadiya ne ta sanya su yo kwana da kayan nan.

Tuki yake yi wannan karon cike da tunani da sake-sake har ya karasa gida. A ranshi tunani yake ko ya Hajiya Umma zata ce idan taji cewa saboda Nadiya kadai ya daga tafiyar daya kamata ace yayi ta a yau? Da yanzu ya gama shan ruwa a Makkah. Amma idan ya tuna Nadiya, da yadda suka rabu da ita, sai ya tsinci kanshi da yin murmushi. Shi yasan ba zai taba damuwa ba idan ya kara daga tafiyar tashi ta yan kwanaki, batawa Nadiya rai da ganin tsiwar nan tata ma kadai sun isheshi debe kewa.

Tana ganin yara suna ajiye katan-katan din Maltina da madara peak ta ruwa da tarkacen kayan shayi har da su crates din kwai, duk kuma wai inji Habib, ta zabura tace musu su wuce su mayar mishi da kayanshi. AbdulBaqi yace mata ai tuni daya riga ya tafi. Ta rufe ido ta fara zazzaga musu masifar me yasa to suka amso kayan tun a farko? Tace musu tana bukata ne? Suka yi tsuru-tsuru a tsaye suka kasa gaba ko baya. Mama data ga haka tace musu su ajiye kayan anan. Ta dauki dari biyar ta basu, su kuwa suka ce mata ai tuni daya sallamesu suka wuce.

Ta kalli Nadiya da take jefawa kayan harara kamar su ne suka aikata mata laifin. Tace mata "sai ki dauke kayan ki kai daki ko?"

Ta wani turo baki gaba. Da kamar ba zata dauka din ba, sai kuma ta kira Amina suka fara jidar kayan suna kaiwa dakin.

Mama ta kalli yanda take ta guna-guni da bata fuska, tace, "Allah Ya kyauta miki Nadiya wallahi. Zan so in ga wannan zaman aure naki!"

Amarya dake aikin dama kokon da za a sha ruwa da shi tayi dariya, tace, "Mama ki kyale diyar nan taki da zurfin ciki, tana son kayanta ne kuma tana kaiwa kasuwa. Muna nan dake tsit zaki ji ta idan aka yi auren, ko motsinta ba zaki dinga ji ba. Watakila ma sai kin dinga nemanta da kanki ma sannan!"

Nadiya dake jinsu tayi caraf tace, "tab! Allah Ya tsareni wallahi!"

Mama da Amarya kam me zasu mata idan ba dariya ba?

Da aka nunawa Abba kayan da aka kai mata kuwa cewa yayi a kaisu dakinshi, haka aka sake jidarsu aka kai mishi. Ya dauki Maltinar nan da madara da ruwan gora ya kai kuryar daki ya ajiye, kwai yace matan su raba kowa ta dinga soyawa ita da 'ya'yanta idan an sha ruwa. Kayan shayin kuma yace a ba Nadiya ta dinga hada shayi tunda dama ma'abociyar shan shayin ce.

Daga fari ma da cewa tayi su Mama su raba ita da Amarya, sai da Mama din ta rufe idanu ta manna mata shirme sannan ta amshi kayan.

Washegari tana shago, ta dan bude datar wayarta tana duba halin da duniya ke ciki kafin su fara aiki.

A WhatsApp dinta ta kula wata sabuwar lamba ta tura mata sako. Ta bude cike da mamakin ko wanene? Sai ta ci karo da hoton mutumin nata, yana sauka daga jirgi. Yayi shigar wata bakar jallabiya wadda ta haska shi, gashin kanshi da sajenshi sun kwanta luf-luf gwanin sha'awa, ya dora farar hula a kanshi. A kasan hoton ya rubuta 'mun sauka lafiya. Nasan dai kina nan kina ta tunanina!'

Ta saki wani irin dogon tsaki har sai da Aramide ta juya ta kalleta tana tambayar lafiya? Ta girgiza kai.

Ta rasa abinda mutumin nan ke ji da yake da wannan confidence din. Ta fita daga WhatsApp din ma gabadaya. Tayi tunanin tayi blocking din lambar tashi ma gabadaya, sai kuma ta fasa daga baya.

Sai ta koma ta cikin messages ta zauna da kyau tana karanta dogon sakon da Abdullahi ya tura mata dazu da safe.

Sai jiya da dare sannan ta samu kwarin gwiwar kiranshi a waya ta sanar dashi abinda ake ciki tare da bashi hakuri. Saboda bata so yaji maganar a wani waje na daban. Ko babu komi sun yi alaka ta mutunci da shi, za kuma taso su rabu akan hakan.

Ya kuma saurareta da kunnuwan rahama, ya kuma nuna mata ya fahimta, ya kuma yarda da hukuncin Allah don haka ba shi data cewa. Hakan da yayi duk sai ya kara sanyaya mata gwiwa, har suka yi sallama dashi hakuri take bashi.

Shine ya sake tura mata sakon cewa kada ta damu kanta saboda shi dai tsakaninshi da Allah ya hakura da ita, ba don baya sonta ba sai don zai fi son ya tayata yiwa iyayenta biyayya. Shima har da kara yi mata nasiha da wa'azin muhimmancin yiwa iyaye biyayya da kuma biyayyar aure. Daga karshe yace mata ta tura mishi da account number dinta yana so ya bada gudummawarshi ta biki.

Tayi murmushi ranta cike da jindadin hakan. Ta tura mishi da sakon ta gode dai kwarai da gaske da fahimtar da yayi mata, amma yayi hakuri ta gode da addu'arshi ma a hakan kawai.

Ta kashe wayar tare da janyo Aramide ta zaunar da ita. Itama sai a lokacin take bata labarin auren da zata yi.

Don kuwa zuwa lokacin ta fara sakewa da lamarin gabadaya.

Aramide ta rungumota cikin murna, tace, "kai kawata! Amma na tayaki murna sosai da sosai wallahi! Amma shine baki fada min tun a lokacin ba?"

Ta dafe kumatunta tana kara jingina da kujerar da take kai. Tace, "to me kike so in ce Ara? Har ga Allah auren nan fin karfina aka yi. Kin sanni sarai bani da akidar wai dole sai auren soyayya zanyi, amma ko babu soyayyar dai at least ace an samu fahimtar juna da gamayyar hali. Amma wadannan dinma bamu dasu ni da shi. Kada kuma ayi zancen irin rigingimu da nake hangowa zasu iya faruwa anan gaba ta dalilin auren nan wallahi. Bana son abinda zai iya dawowa daga baya ya karasa bata dan guntun zumuncin dake tsakaninmu da Hajiya Ummah, dama ba wani mai kwari bane."

Ara ta dafa kafadarta, "ke wallahi kada ki wani sanyawa ranki damuwa, wannan fa ba komi bane. Don soyayya da fahimtar juna zasu biyo baya jazaman ne, kin ganki kuwa Nadiya? Wane namiji ne zai ce wai ba zai so ki ba? Ai karya ne. Zancen zumuncin su Madam kuwa ki barsu a yadda kika gansu kawai. Idan ma ta dawo ta cabe musu daga baya dai babu hannunki a ciki, shi tsuntsun da yaja ruwa dama ai shi ruwa kan doka. Ki cigaba da addu'a kawai. Wa ya sani kuma ta dalilinki zumuncin ya kara karfafa?!"

Nadiya ta ajiye gwauron numfashi, "I doubt. Amma don addu'a kam ina yi sosai!"

Tace, "yauwa, sai ki kara zage dantse abinki. Yanzu dai da me-da me ake shirya mana na bikin?"

Tace, "babu abinda za ayi, aure kawai za a daura shikenan. Hakan kuma ni yafi min dadi."

Ta dan turo baki alamun ba haka ta so ba, "to Allah Yasa hakan shi yafi alkhairi. Amma dai ai naso ace bikinki na cashe sosai da sosai!"

Ita kuwa ta tabe baki, tace, "ai bikin da ake so da doki shi ake cashewa!"

Ara tayi dariya tace, "lokaci ne ai. Lokacin da zaki yi naki casun saboda murnar auren wa zai sani?!"

Ta wuce ta cigaba da ayyukanta Nadiya na binta da kallo tana girgiza kai.

*

Sannu a hankali sai gashi azumi har an yi na goma sha daya kamar da wasa.

Ta fito zata tafi shago da misalin karfe biyu na rana. Kasancewar daren jiya an kwana ana yin ruwa yasa garin yayi luf-luf, ni'ima ta samu.

A kofar dakin Mama ta ci karo da Amarya da Mama din suna gyaran gero da barzar kwakwa. A gefe guda kuma su Fatima ne da Amina da Maryam, wata na bare dabino, wata na gyaran ganyayyaki da Nadiya ta rasa ko na menene, wata kuma na aikin daka mazarkwaila gata nan kifi-kifi, tana zubawa a cikin wani kwano.

Nadiya tayi turus tana kallonsu, "yau kuma aikin me ake yi ne haka?"

Amarya tace, "ai wannan aiki naki ne ke kadai, ki je ki dawo zaki sha mamaki!"

Tayi dariya, tace, "ni dai in tukudi ne zaku yi to a sanya kwakwa da dabino sosai a ciki fa, na fi son shi a haka!"

Mama tayi yar dariya, tace, "ai in dai tukudi ne har sai kin gaji da ci Nadiya, don kuwa wannan duk naki ne."

Tana shirin bata amsa sai ga AbdulBaqi yayi sallama ya shiga hannu riki-riki da leda, Amarya ta amsa ta bude tana ciro faifayen cukui da wasu karin ganyayyaki da itace. Nadiya ta kama baki, tace, "yanzu wannan tarkacen duk a cikin tukudi?"

Amarya tace, "wannan ai ba ma duka bane. Kin san mu da yake sana'ar gidanmu ce yin wannan tukudin musamman na matan aure da masu shayarwa da kuma amare, to duk nasan abubuwan da ake sanyawa. Ai gyaraki zamu yi da kyau amarya, sai kin amsa sunan naki na amarya da babbar murya!"

Ita sai lokacin ma ta fahimci ashe tukudin amare ne suke kokarin yi. Ta tabe baki ta musu sallama ta wuce.

Ta bar Lantana dake gefe daya tana bare gyada tana turo baki, "aikin banza aikin wofi! Allah sa uwar mai hada kayan mata ma za a ba mutum ya hadiya, aikin banza ne. Ita matar cushe ai bata daraja!"

Nadiya dai ta kada kai ta fita daga gidan abinta. Yadda bata tankata ba haka su ma babu wanda yace mata uffan.

Tayi tsaye a bakin titi tana jiran abin hawa. Sai kuma ta fito da wayarta daga jaka ta shiga WhatsApp. Kara dubawa take yi wai taga ko cingam din nata ya tura mata hotonshi daya saba tura mata a kowace rana.

Yawanci idan sun fita sallar la'asar a can yake tura mata, nan kuma din a Nigeria wajajen karfe biyu kenan lokacin da take tafiya wajen aiki. Sai ya tura mata hotonshi hade da maganganu na tsokana da neman magana, wasu lokutan kuma ya kan tura mata wani hadisi ko aya data dauki hankalinshi ne idan yana wajen tafsir.

Ko wanne ne dai daga ciki, bata taba tura mishi da amsa ba. Sai dai kuma a hankali, cikin rashin saninta balle yarjewarta, har ta fara sabawa da sakonnin nashi.

Lokuta da dama ta kan samu kanta da dariya ko murmusawa idan ya tura mata wasu hotunan da zai yatsine fuska, ko ya mata gwalo, ko ya kanne ido.

Gani take a girmanshi, da yadda ake fadinshi, kamar ba zai yi irin wadannan halaye ba. Amma sai ga shi yana yi mata hakan. Girman kan data fara ta'allakashi dashi sai ya fara wankewa daga ranta. Saboda wane mai girman kai ne zai iya yin abinda Habibun yake yi? Ta fara tunanin watakila duka

fahimtar data mishi a baya, akasari ne na dan Adam kawai da kuma 'bad first impression'

Yau dai babu abinda ya aika mata. Haka ta je shago, bini-bini sai ta daga waya ta duba. Aka sha ruwa nan ma bata ji daga gareshi ba. Ranta sai yaki yayi mata dadi, abin ya fara damunta. Ta fara tunanin anya lafiya kuwa?

Tana shan tukudin da aka dama mata, wanda ya hadu fiye ma da yadda tayi tunani, don kuwa ya sha kayan hadi, ya kuma hadu da nono mai kyau wajen damun. Ta bude chats dinsu tana bibiyar sakonninshi, ta samu kanta da murmusawa kawai. Wani abu mai kama da kewa ya fara ratsata. Kawai sai ta kashe wayar da sauri tayi jifa da ita gefe daya.

Ita abin ma nema yake ya fara bata tsoro. Ta yaya tun kafin aje ko'ina Habibu zai sanyata zubar da makaman yakinta ne?

Hakan kuma ba shi ya hanata jan wayarta da sauri ba ta daga bayan kamar mintuna ashirin. Ta duba sakon da aka tura mata, ta ga shi dinne dai da take jira.

Shigar larabawa yayi yau, har da su lullubin nan da manyansu ke yi. Fadar kuma irin kyawun da yayi ma bata baki ne. Ta samu kanta da zama tana karewa hoton kallo na fiye da mintuna goma. Kafin kuma ta fita daga cikin gallery dinta da taga ya tura mata wani sakon ta kasar hoton.

'Nasan ke ma kina kewata Nadiya! Ina jin hakan har a cikin raina da ruhina da gangar jikina.'

Kuma da yaga bata mayar da amsa ba na yan mintuna, sai ya kara tura mata da,

'kiyi ta kauce-kaucenki dai. Kwanaki ashirin da tara ne suka rage. Na miki alkawarin sai bakinki ya furta min hakan a cikin kunnuwana!"

Ta saki wani wata yar dariya kawai tana girgiza kai, kwana ashirin da tara yace ko? Sun zuba ita dashi kuwa!

Ta kashe wayar tayi kwanciyarta.

24

Wajen karfe goma na safe ta tashi tana nade abin sallar data hau tana yin lazumi da yake kwana biyu ta tashi da fashin sallah ne.

Maryam dake zaune akan kujera tana kallonta, tace, "Wallahi Anty kin ji dadi abinki ke kam. Kinga azumi rabi amma har kin sauke Al-Qur'ani Mai Girma kin juya. Dama ni ce ke!"

Tayi dan murmushi, "to Maryam in banda abinki ai zage dantse ne yake kawo hakan. Ke ma idan kinyi kokari sosai, sai kiga kin ma zo kin wuceni."

Tayi yar dariya tace, "Anty kenan!"

Mama ta shigo dakin a daidai wannan lokacin. Tace, "yauwa Nadiya, ga abu can na ajiye miki a firjin zaki gani cikin gallons na ruwa, ki tabbata kullum kin sha kofi biyu safe da dare."

Ta yamutsa fuska jin hakan. Ita fa abubuwan da ake bata dinnan sun fara ci mata tuwo a kwarya. Mama da Amarya sun dage tun karfinsu gyarata suke so suyi, su basu san cewa shi gyaran sai ana dokin miji da aure ba sannan ake yin shi ba? Ko kuwa fada musu aka yi cewa zaman auren take muradin yi da mijin ne da zasu dameta da wannan gyare-gyaren? Idan kuma kace ba zaka sha ba Mama ta hau fada.

Yanzu ma Mama tana ganin yadda take tabe fuska da mele baki tace mata, "saura kuma in ga baki sha ba ko kuma ba kya sha kamar yadda nace kiga abinda zai faru!"

Ita sai abin ma yaso bata dariya. Ta girgiza kai kawai, Allah sarki Mama. Tana ta kokarin tayi mata abinda mahaifiyarta ma wadda ta haifeta ta kasa yi mata shi.

Tunda zancen auren nan ya motsa sau biyu ta kirata. Na farko shine lokacin data kira ta tayata murna dinnan har ta bita da fada da gori. Na biyun kuma sake kiranta tayi da gargadi da fadan ta fa kama kanta ta kuma mike tsaye tun karfinta. Tayi kokari ta tsaya tsayin daka domin ganin ta zama ta farko a wajen mijin da zata aura.

Ta koma lallashinta da tausarta, akan ta kwantar da hankalinta, ta dangwali arziki ta sha romonshi tunda har yazo har inda take ba tare data nemeshi ba.

Nadiya dai bin ta ta dinga yi da 'to' kawai har suka kammala wayar. Shikenan ta kashe bayan nan tana mai kara jaddada mata lallai fa ta nacewa Habib, kiran safe daban, na rana da dare daban. Haka kuma kada ta sanyaya wajen aika mishi da sakonni da kalamai na kauna. Abinda ya hadasu kenan. Babu zance ko tambayar ya tsarinta yake? Me take tanada ta kuma shiryawa rayuwar auren da take kokarin sanyawa kafa?

*

Ranar bayan an sha ruwa, Hajiya Ummah tana dakinta wanda aka tanadeshi musamman saboda shan iska. Waya suke yi da Madam wadda take fada mata irin nasarori da maganganu masu dadi da suke samu a wajen mutanen da take tunkara da zancen Habib.

Don a halin yanzu ma haka ta samu nasarar zama da Jagoran jam'iyyar da ita Hajiya Ummah take ganin da ita zasu yi tafiyar, ya kuma tabbatar mata da cewa lallai Habibun shi zasu tsayar a matsayin dan takara.

Ta kuma kara da shaida mata da cewa a yanzu haka, ta tashi mutane bila adadin, suna shiga kauyuka suna bada tallafi iri-iri, duk da sunan shi Habib din. Juma'ar da zata yi kyawu tun daga Laraba ake ganeta, tana kuma ganin cewa lallai sun gama samun nasara a wannan tafiya.

Hajiya Ummah tayi murmushi cike da jindadi, "shi yasa dama tun farko banyi kokonto akanki ba Zahra'u. Nasan lallai-lallai sai kin kai hakarmu ya cimma ruwa."

Madam ta saki wata yar dariya, "ai Ummah ba yabon kai ba, amma ni nasan duk wani buri da zan sanya a gaba, to hakika sai na cimma nasara a cikinshi. Don haka ki kwantar da hankalinki, in Allah Ya yarda nan da dan kankanin lokaci, Kaduna sai ta zama tamu. Idan kika rike hannuna kuwa, na miki alkawarin har Nigeria ma baki daya sai na sanya ta durkusa a gabanki!"

Murmushi take saki sosai, jin maganar da Madam din take yi. "Hakika da babu abinda zai kai hakan faranta min rai Zahra'u. Allah Yayi mana jagoranci dai."

Madam tace, "ameen." Kafin kuma ta dan dakata.

Sai kuma ta nisa, tace, "to Ummah ina zancenmu kuma ya kwana?"

Tace, "Zahra'u baki da matsala game da wannan ko kadan. Kamar yadda na fada miki tun ba yau ba, bana magana biyu. Idan nace zan yi, to zan yi din babu mai canza min shawara. Fili naki ne, babu kuma wanda zai hanaki shi da yardar Allah. Nan da dan kankanin lokaci za a damka miki takardunshi da komi a hannu!"

Madam tayi tsallen murna, "nagode sosai Ummah, Allah Ya kara Girma da daukaka. Ai ni tuni na gama hada komi ta bangarena, go ahead kawai nake jira daga gareku muje mu fara gini."

Murnar da take ciki ta hanata sauraren maganganun da Hajiya Ummah take mata. Itama data fahimci hakan sai kawai ta mata sallama ta kashe wayar.

Suna gama wayar Madam ta tashi ta hau tikar rawa a dakinta cikin murna da farinciki.

Kamun kafar data samu a wajen Hajiya Ummah yasa ta bi wasu shaguna dake kusa da filinta inda take so tayi gini, ta siya domin ta kara fadada wajen. Duk wani abu da zata yi, tuni ta riga ta gama tattarawa, an fitar mata da tsarin wajen, an tanadi kamfanonin da zasu kai mata kayan aiki da kuma wadanda zasu yi aikin. Kai tsaye rana daya sai aka je mata da labarin ai wannan waje data saya ba a wajen ainihin mai wajen bane, don haka zance ya tashi. Don kuwa mai waje yace ba zai sayar da waje ba. Aka mayar mata da kudinta.

Ta nuna musu zata iya kaisu kara akan wannan maganar tunda ta riga ta gama sayen waje, kuskuren data yi a yarjejeniyar sayen wajen bata sanya idan an yi abu kamar wannan ba zata iya shigar da kara ba. Saboda bata taba sanin irin haka din zai faru ba

Da taga dai babu Sarki sai Allah sai ta koma bin kafa wajen Hajiya Ummah. Wadda cikin dan kankanin lokaci ta samo mai wajen, Alhaji Tijjani, da kuma sanyawar bakinta ne yace zai sayar da wajen amma sai yayi shawara. A hakan ma kuma sai da Madam ta kara mishi da wani gida flat da take dashi a Kinkinau bayan ainihin kudin data sayi shagunan dasu.

An fi sati biyu da yin hakan har yau kuma babu wani cikakken bayani data ji daga garesu. Amma maganar da suka yi da Hajiya Ummah sai ta karfafa mata gwiwa sosai da sosai.

Ta ci wa wannan waje da zata bude buri fiye da tunanin mai tunani. Akwai kuma mutane da dama da suma suke jiran budewar wannan waje. Saboda bayan shaguna da wajen wasanni da zata bude, akwai wani bangare na daban da zasu bude wanda wannan waje, na musamman ne. Na manyan kusoshin Gwamnati ne da suka ci suka tada kai da nera. Ba zata bari wani abu yazo ya gittawa wannan buri nata data kwashe shekara da shekaru tana ayyanawa ba.

*

Ita kuwa Hajiya Ummah suna kashe waya, wata wayar ta dauko daga cikin drawer ta kunna. Kai tsaye ta shiga cikin jerin contacts dinta, ta dannawa wata lamba kira.

Tana shiga aka daga babu bata lokaci, Alhaji Tijjani yace, "barka da dare Hajjaju, da fatan kun sha ruwa lafiya?"

Tayi wani murmushi cike da ginshira, "lafiya lau Alhaji. Ya Iyali?"

Suka gama gaisawa dashi cikin girmamawa, kafin ta fara mishi zancen daya sanya ta kirashi.

Tace, "ina aka kwana game da zancen shagunan nan ne?"

Yayi wata irin dariya, "zance ai yana nan a yadda muka barshi ne, ko kin canza shawara ne?"

Tace, "ko kadan! Ina so to zuwa satin da zai kama ka kawo min takardu da komi da komi, ka kuma bari sai satin ya kama ayi cike-cike saboda kada kwanan wata ya saba!"

Yace, "na gane Hajiya. To za a yi kamar yadda kika ce."

Tayi dan murmushi a hankali, "yauwa nagode, a gaida yara."

Shima yace, "mu ne da godiya Hajiya!"

Ta kashe wayar ta mayar da ita inda take. A karkashin wayar ta zaro wasu takardu, ta zauna akan kujera tana dubasu daya bayan daya tana sakin murmushi a tausashe, ranta fal da farinciki kamar an mata wata babbar kyauta.

Ta gama karancesu tsaf kafin ta ajiyesu a gefe, wani murmushin ya sake subuce mata. Ta jinjina kai a hankali wani tunani yana darsuwa a cikin ranta.

'Lallai yaro bai san wuta ba sai ya takata!'

****

Vibrating din da wayarta take ta yi ne babu kakkautawa ya tasheta daga barcin da bata jima da farawa ba. Nan da nan taji kanta ya fara sarawa, wannan shine bugu na uku kenan. Kafin ta kai ga dagawa har ya katse.

Ta sake yada kanta akan bargo tana kokarin komawa barcin, ba a dauki wasu mintuna masu yawa ba aka sake kiranta. Wannan karon har sai data zabura, kafin ta warci wayar ta daga. Karfe goma sha biyu saura na dare a dinga yiwa mutum irin wannan kiran sai kace wani yaki! Ta daga wayar rai a bace.

"Wai waye ne haka don Allah?!" Saboda bata ma tsaya ta ba lambar wayar data gani ba wani dogon tunani ba ta daga kiran tunda babu suna.

Sai taji shiru ba a amsa ba. Ta duba wayar don dai ta tabbatar mai kiran yana kan layi, taga dai kiran yana kai amsawa ce ba ayi. Ga kuma dai alamun kara nan ta background tana ji, balle tace ko network ne ya hana.

Ta sake cewa, "hello... waye wai?!"

Wannan karon da taji shiru sai data saki tsaki, tace, "in an san ba za a yi magana ba menene na yiwa mutane waya da wannan daren in banda rainin wayau?"

Ta tafi zata kashe wayar tana mita, "... kawai an katsewa mutane barci saboda wulakanci..!"

Sai kuma ta jiyoshi yana magana. Yace, "ki godewa Allah ke kin ma samu kinyi barcin. Bayan ni gani anan kin hanani!"

Ta mayar da wayar kunne tana jin abinda yake fada, sai ta kara hade fuska, "wai waye ne zai kira mutane cikin daren wannan a dinga musu wani zance maras kan gado?"

Yace, "oh, waye kike tunanin zai kiraki a daidai wannan lokacin ne kam? Ko kuwa dai dama kina da masu kiranki ne bila adadin?"

Tace, "don Allah idan baka da muhimmin dalilin da yasa ka kirani ka katse kiran nan. Kamar yadda nace, barci nake yi ka katse min!"

Ya ajiye numfashi, "Nadiya!" Ya ambaci sunan da wata irin murya data sanya taji wani abu ya tsirga mata tun daga tsakiyar kanta har tafin kafarta.

Bata san me ya kaita daga baki zata amsa ba, amma koda ta daga bakin sai taji bata ma iya hada kalma waje daya. Don haka ta maida bakin nata ta rufe.

Ya sake ambatar sunanta, yace, "Nadiya! Me yasa kike kokarin nesanta kanki da ni ne? Me yasa kike gujewa duk wani kusantoki da zan yi?!"

Tayi shiru kamar wadda ruwa ya cinye.

Bai tsaya sauraren amsarta ba shi kuwa ya cigaba da maganarshi. Yace, "kwanaki dai-daya har goma sha biyar Nadiya, baki ji muryata ba ban ji taki ba. Na nemeki a karo na farko amma kin bude baki wai kina ce min idan bani da magana mai muhimmanci in kashe waya. Anya kin dauko hanyar tsayar da adalci kuwa?"

Ta yatsine fuska kamar yana gabanta, a gefe daya kuma tana yin kasa da muryarta saboda kada ta damu su Mama dake barci.

Tace, "to ni don na shekara ma ban ganka ba ko naji muryarka meye nawa? Idan da kai kaso jin muryar tawa ai da kaji tun ba yau ba kuma ko?"

Ya saki wata yar dariya mai taushi, "okay, na ganoki! Wato ita kewar tawa da kika yi ma ba zaki iya fada kai tsaye ba sai kin dinga kewaye-kewaye? Nadiya, halin nan naki yana bani dariya!"

Ganin nemanta yake yi da tsokana yasa tayi shiru kawai ta kyaleshi.

Yace, "da ai nayi wayon wai in kyaleki ne zaki nemeni da kanki. Sai naga ke baki ma da wannan shirin sam. Shine nace to ni na ci girman, bari in kiraki. Ya kike ne? Naji ance garin yau an sha ruwa sosai har dare ko?"

Ta koma ta kwanta tana cewa "uhm!"

Yace, "muma yau yini guda ruwan aka yini yi tun safe, har yanzu ma kinga yayyafin ake yi. Garin kuwa ya dauki sanyi gwanin dadi, sai dai ni dazu da ruwan ya dakeni sosai kin ga ya sanya min zazzabi kuma. Yanzu haka kin ganni cikin bargo na rufa."

Haka kawai ta samu kanta da jin babu dadi, tace, "Subhanallahi, garin yaya ka bari ruwan ya tabaka ne haka?"

Yayi dan murmushi, "sallah na fita. Da zan dawo kuma sai ban sanya bazara ba ganin cewa ruwan ba mai karfi bane. Amma duk da haka sai daya tabani din."

Tace, "to Allah Ya sawwake. Ka sha magani?"

Yace, "sai dana sha sannan na kwanta. Da sauki ai, zazzabin ya fara sauka."

Tace, "to ka kwanta ka samu barci mana? Sai kaga ka wartsake idan ka tashi."

Yayi saurin ce mata, "a'ah! Ai nace miki da sauki. Besides... sauraron muryarki kadai ma yasa naji zazzabin ya sauka!"

Bata san lokacin data saki wata dariya ba marar amo, ta dinga kyalkyalawa kamar wata sabuwar kamu. Yayi zaune da waya a kunnenshi yana murmushi kamar wani zautacce.

Tace, "kaji wata magana sai kace a shirin film? Irin wannan zantukan dai yawanci a 'teen fiction' kake ji ana furtasu!"

Yayi dariya, yace, "ko babu komi dai ai na sanyaki dariya ko? That was a first!"

Sai kuma tayi shiru tana raba ido.

Yace, "in dai ni ne Nadiya, don dariya dai da farinciki da nishadi, zan sanyaki a cikinsu bila adadin. Na miki wannan alkawarin. Yanzu dai me da me kike shirya mana na aurenmu ne?"

Ta tabe baki, "wani shirin aure kuma? Shirin me kake nufi bayan kun ce amarya kawai kuke so a kawo muku sai kace wadda za a sayar?"

Yayi yar dariya, yace, "idan ma sayan za ayi ai nasan baki da matsala da hakan. Ke da kanki zaki dauko kanki ki zo inda nake! Zan kuma sayeki da madaukakiyar daraja!"

Tace, "tabdijam! Lallai kuwa kana yaudarar kanka!"

Suka raba wannan dare yana ta janta da hira da tsokana, har sai data saki jikinta dashi.

Bata san lokacin da barci ya dauketa wayar manne a kunnenta ba. Sai shi da yaji alamun tayi barci, sannan ya katse kiran yana murmushi.

Ranar shi ya tasheta sahur.

25.

Shikenan, tun daga wannan lokacin sai ya zamana shi yake tashinta sahur. Idan an sha ruwa zai kirata ya mata sannu da shan ruwa. Idan aka jima kuma zuwa wajen goma zai sake kiranta su sha hirarsu sosai. Haka a yini ma zai dinga kiranta akai-akai.

A hankali a hankali, sai gashi ita da kanta wani lokacin zata dauki waya ta kirashi ta mishi barka da shan ruwa.

Hirarrakinsu suka fara tsayi. Ta fara tunanin wai ma me yasa tun farko take kin shi ne? Me ya mata?

A karo na farko a rayuwarta take shaida menene kewar Mutum? Menene jin shaukin wani mutum?

Don kuwa a hankali Habibun yayi kokari ya shiga can cikin kasan ranta, inda ita a karan kanta bata san da wanzuwarshi ba.

Yayi wani kabe-kabe ya kanannade mata zuciya. Duk yadda take kokarin yakiceshi da banzatar dashi abin ya ci tura.

Ta fahimceshi sarai a mutum wanda yake matukar girmama duk wani abu daya shafi mahaifiyarshi, baya wasa da al'amarinta ko kadan. Duk wani abu da zai yi, duk wata shawara da zai yanke, sai Ummanshi taji. Magana daya, biyu, yace Ummah.

Nadiya tana girmama hakan, a gefe daya kuma tana mamakin wannan abu. Ta yaya babban mutum kamar Habib zai zamana bashi da wani sha'ani na kanshi kawai sai na Mahaifiyarshi? Ba aibun abun take gani ba, kawai tana mamakin hakan ne.

Daga baya ta fahimci hatta da siyasar da yake shirin sanya kafa a ciki, burin Hajiya Ummah dinne ba nashi ba. Bata manta tambayar data taba mishi wani dare, ranar sun kai azumi na ashirin kuwa.

Sun gama wayarsu zasu yi sallama, yake jaddada mata da cewa ta dage da yi mishi addu'a a wannan darare masu albarka. Allah Ya basu sa'a da nasarar siyasar da suke tunkara.

Tace mishi, "wai me yasa kake son siyasa ne sosai haka?"

Bai kuma tsaya dogon tunani ba yace, "saboda Ummah bata da burin daya wuce danta ya hau kujerar Gwamnan Kaduna!"

Har ga Allah tayi tunanin jin abu mai kama da, 'saboda taimakawa jama'a ko kawo cigaba a kasata' ko wani abu mai kama da haka. Sai taji akasin hakan kuma.

Ta gyada kai kamar yana gabanta ba don ta fahimceshi ba, tace, "to in shaa Allah kullum zan sanyaka a cikin addu'ata. Da aurenmu da siyasarka idan alkhairi ne, Allah Ya baka dukansu. Idan kuma duka ba alkhairi bane, to Allah Yayi maka canji da mafi alkhairi!"

Yayi dariya sosai, yace, "alkhairin ne ma in shaa Allahu, Love."

Ta samu kanta da murmusawa jin kalmar daya kirata da ita.

Ta tashi ta dukufa da addu'a babu kakkautawa, da auren da siyasar tashi, duka Allah Ya tabbatar da alkhairi a ciki.

*

Anyi azumi na ashirin da biyu aka kaiwa mutanen gidan kayan sallah. Yawanci idan sallah tazo Abbansu ya kan siyawa yaran gidan kayan sallah ne gwargwadon yanda hali ya bashi. Su kuma matan sai ya basu kudi yace su sayi duk abinda suka ga yayi musu.

Wannan karon kuma har matan duka ya hada ya sayawa Atamfofi masu matsakaicin kudi.

Lantana ta fito tsakar gida daga dakinshi, da atamfar a hannu shekeke tana kara dubawa, tsaki take ja tun karfinta ganin anko aka musu da Amarya.

Nadiya kuma tana raba ido taga ta ina nata kason zai fito.

Salame ita ma ta fito daga dakin nashi tana yatsine baki, suka koma gefe daya ita da Lantanar suna magana kasa-kasa.

"...Dama ai nace wannan karon dai mai farar kafa aka dauko mana. Yanzu banda tsabar ci baya, mutumin dake bada kudin leshi guda shine zai buge da sayen karamar atamfa? Ina cigaba anan?" Cewar Salame.

Lantana kuma ta tabe baki, tace, "ke ta kayan sallah ma kike yi, kina jin ko dan abin yankar sallah ma da ake mana fa cewa yayi ba zai yi ba saboda bashi da kudi. Ga wannan kaddararren aure da aka hadashi da shi!"

Salame tace, "ke! Ki kama bakinki to tun kafin ya ji ki. Kin kuwa san yadda yake ji da wannan auren? To wallahi a kanshi sai ya tafka miki rashin kirki kin dai san halin Malam sarai. Yadda yake fadin alkhairin da auren nan ya kawo mishi idan yaji kina wannan maganar ai wallahi sai ya bata miki rai!"

Tace, "yo wai ina albarka anan? Kina kallo ana zancen za ayi aure amma gida yana kara lalacewa da ja baya, ina alkhairin? Ai ya gode Allah ma sun ce kar ayi kayan daki, da yaji kunya sosai da sosai."

Salame tace, "yo jin kunya na nawa kuma? Ai sai dai kar a kuma. An zo neman aure ka dauka ka bada babu wani dogon bincike, an ce za a kaika Makkah ka bude baki kana godiya babu dan jan aji ko nuna wadatar zuciya. An zo an ce ba a bukatar kayan daki, nan ma ka hau godiya da murna, wannan ai salon kaja a rainaka ne. Ga wannan aure na wannan zamani da ake yi, an yiwa mace kaya ma bata yi daraja ba ina ga ba ayi ba?"

Lantana ta kwashe da dariya, "ina kika ga amarya tayi sati daya ta yo kwana don ba a kaita da kayan daki ba?!"

Suka sake fashewa da dariya har suna shewa.

Abba daya gama jinsu suna ta bayani, yace, "to ta Allah ba taku ba munafukan banza da wofi! Wato saboda kun ga yarinya tayi goshi ta samu gidan hutu, shine kuke mata bakin ciki da hassada. To dai hassada ga mai rabo taki ce, kuje kuyi ta maganganunku da iface-iface, bori dai baya hana mutuwa!"

Salame ta fitittike zata fara nade tabarmar kunya da bori, ya kakkabe rigarshi ya rufe dakinshi ya barsu anan.

Da taga haka ita kuma Nadiya sai ta rufa hijabi da dare ta sameshi da tambayar ina batun kayan sallarta? Saboda tayi tunanin ko ya manta da ita ne.

Yayi fici-fici da ido yana kallonta, yace, "kayan sallar me zan miki ke kuma bayan da anyi sallah zaki bar min gida? Ke ni fa ko ciyar dake da nake yi ma a yanzu, yi nake kawai don tsoron Allah ne ba don wani abu ba. Amma ni ai tuni na fiddaki daga jerin wadanda ke karkashina!"

Tace, "to amma dai Abba ai ko auren ma za ayi, ana dinkawa Amarya abinda zata yi fitar biki dashi ko?"

Amarya dake gefenta tayi caraf tace, "kwarai kuwa. Ai ko ni nan da kika ganni, sai da aka yi min kala hudu na fitar biki. Wannan jan leshin ma dana sa ranar da zan tare ai Babanmu ne ya dinka min shi!"

Ya kankance ido yana kallonta, "ita kuma nata lefen da zata je ta tarar fa? Mutane sun ce ba sai anyi taro ba, aure kawai za a daura akai musu mata. To kuma me kuke so inyi? Idan dai har ba bakincikin kayan da aka dinkawa yan'uwanki kike yi ba, to ki daina min maganar dinki anan wajen. Ki je ki samu mahaifiyarki ta miki mana, tunda ita tafi cin gajiyar auren ba ni ba! Sai kizo ni ki sanyani a gaba da wani zance na banza da wofi?!"

Ta daga kai a sanyaye ta kalleshi da idanunta da suka tara kwalla, tace, "babu zancen wani bakinciki anan Abba, kayi hakuri da zancen dinki da nace kayi mun kuma."

Ta tashi ta wuce dakin Mama abinta.

Ta rasa ma dalilin da yasa tayi mishi maganar ya mata dinkin fitar biki. Abinda da daga farko bata da niyar yi. Duk da cewa har yanzu ba wani taro za tayi ba, amma kuma ko yaya ai ya cancanci a zo a ga amarya cikin shiga mai kyau ko? Sai kuma ta girgiza kai, tana dan murmushi a tausashe cike da mamakin zuciya wadda take iya canzawa a cikin dan kankanin lokaci.

Ta kai zancen dinki can bayan ranta ta ajiye. Don kudi tana da su wadanda zata iya yiwa kanta dinki, amma tana tsentsenin taba kudin ne saboda kada wani abu mai girma ya fado mata wanda zata dawo daga baya kuma tana dana sani.

*

Anty Hauwa ta kirata take tambayarta wai me take yi na shirye-shiryen biki? Tace ita kuwa wani shiri zata yi ne? Tunda dai ba wani taro za ayi ba?

Tace mata, "duk da ba taro za ayi ba, ina maganar gyaran jiki da sauran al'amura ne. Kunyi su dilka ne da halawa? Kin san fa mu normally wata guda ake dauka ana yin wadannan abubuwan, saboda gyaran yayi sosai, kuma kamshi ya kama jikinki da kyau! Mun fara magana da Zahra'u kwanaki, to abin na dan yi tafiya ne kwana biyu shi yasa bamu karasa zancen ba."

Tace, "ai gaskiya ni dai Anty babu wani gyaran jiki da zanyi. A barni a yanda nake, tunda dai su suka ce sun gani suna so a hakan!"

Tace, "gidanku Nadiya! Ashe dama baki da wani wayon azo a gani nake kallonki a haka? To ki kiyayeni wallahi. Zahra'u bata taba yi miki zancen gyara ba tunda maganar auren nan ta taso?"

Ta girgiza kai, "gaskiya bamu taba yi ba. Amma fa Mama itama tana nata aikin." Ta fada mata abubuwan da Mama din take kan bata tana ci da sha da wankawa.

Tace, "amma gaskiya Mama ta kyauta, zan kira inyi mata godiya sosai. Sai dai nata gyaran daban, muma namu daban. Don haka dole ma zamu yi maganar da Zahra'u. In banda ma shirme irin nata, haka za a kaiki gidan kishiya ba tare da mun gama kimtsaki ba? Wannan ai ganganci ne!"

Ta kashe wayar tana korafi, Nadiya kuwa ta tabe baki. Don kuwa tuni ta gama gano Madam din, ba wadannan abubuwan ne a gabanta ba. Ita dai tunda zancen aure ya tabbata, to ta gama da Nadiya, Nadiya ta gama mata amfanin da zata mata. Inda za a kaita kuma, da irin rayuwar da zata yi, wannan ba damuwarta bace.

A daren ranar Anty Hauwa ta sake kiranta. Ta fada mata yanda suka yi da Madam din, cewa da anyi sallah za a zo a hau aikin gyaran jiki tunda suna da sauran lokaci.

Tace mata, "ni dai wallahi Anty da kun bar wannan maganar..."

Tun ma kafin ta karasa ta katseta, tace, "kin san Allah Nadiya sai in bata miki rai akan wannan zancen. An ce miki ne wai mu sakarkaru ne kamar ki? Ki bar ganin wai shi Habibun yana miki rawar kai da kafa da dadin baki. Wallahi kina shiga daga ciki ya fahimci ba daidai kike ba, ajiyeki zai yi a sukwane kamar wata tsumma wallahi. Kila sai lokacin zaki fahimci abinda rayuwa take ciki!"

Maganar tata ma sai taso ta ba Nadiya dariya, tace, "ni dai babu wani rawar kai da dadin baki da ake yi min!"

Tace, "ke dai kika sani ai. Kafin masu gyaran su zo zamu yi waya dake muji yadda abin zai kasance dai." Suka yi sallama da ita.

Washegari ta shiga shago suka sha aiki kamar ba gobe. Saboda sallah duka bata fi saura kwana biyu ba zuwa uku. Zasu fara aikin snacks na masu odar sallah, da wanda za ayi delivering har gida, da kuma wanda zasu sayar anan. Aiki ne ba karami ba saboda wannan sallar sun samu order sosai har sai da suka kai ga rufewa.

Kafin karfe biyar ta rufa, ta gama gajiya tikis kamar wadda aka yiwa dukan tsiya.

Tayi sallama da ma'aikatan da zata bari anan, ta fito daga shagon tana tafe kafafunta har suna hardewa.

Tana shirin fita, taga wata farar Elantra tana kokarin shigowa. Ta matsa gefe don ta bata hanya ta shiga. Sai kuma taji zuciyarta tana wani tsalle da daka a sukwane lokacin data fahimci lambar motar irinta gidansu Habib ce wadda ta fahimci duka motocin gidan suna da shigenta.

Ta fara tunanin ko dai Habibun ne ya dawo babu sanarwa?

Lokacin da taga an bude murfin motar za a fito, sai da taji har wani kadawa da rawa jikinta ya dauki yi kamar mai fama da masassara.

Madadin Habibu, sai taga Ammar ya fito. Gefenshi kuma wata matashiya ce da zata iya yin sa'ar Maryam. Kai daga gani babu tambaya kanwar Habibun ce saboda idan ka ganta yadda kasan yayi kaki ya tofar, basu da bambanci.

Tana yawan mamakin yadda aka yi Habib bai dauko kamannin Hajiya Ummah ba, amma sai tafi ba kanta uzirin watakila ko Babansu ya biyo.

Ta sauke ajiyar zuciya a hankali wadda bata san ta rike ba, ta nufi Ammar wanda ya ruga da gudu ya rungumeta.

Itama ta rungumeshi tana dariya, don kuwa duk da bata san yaron ba, dan zaman da suka yi dashi kwanaki taji kaunar yaron ta kamata sosai.

Budurwar da suke tare dashi ta dan duka tana gaisheta, ta amsa da murmushi akan fuskarta tana kallonta.

Ammar ne yake ce mata, "Anty Rashida ce tace in zo in rakota wajenki!"

Tayi dan murmushi, "aikuwa Allah Ya taimaka, da munyi sabani daku. Don kuwa fitowata kenan zan wuce gida."

Rashida itama tayi murmushin, "lallai fa. Tun dazu ma muka fito wallahi, sako muka tsaya amsa shi yasa muka dan jima. To ko zaki zo ne sai mu saukeki a gida?"

Ta girgiza kai da saurin "a'ah wallahi, nagode. Kada inje in tsayar daku."

Rashida tace, "laaa, babu fa inda zamu je. Musamman Yaya yace yau dai mu zo mu gaisheki!"

Tace, "to shikenan muje, kin ga ai sai ku tsaya ma a can gida ku sha ruwa."

Tace, "tab, ai gaskiya ba lallai ba. Saboda Ummah fada zata yi mana sosai."

Ta shiga mota direban daya daukosu ya ja suka wuce bayan ta fada mishi inda zai kaita.

Suna cikin motar ta kalli Rashida, tace, "amma dai ke kanwarshi ce ko?"

Tayi dariya, dogayen hakora jerarru suna bayyana, tace, "eh. Nasan ai da kyar idan ya taba fada miki hakan!"

Tace, "ko kadan. Kai ni ko wajen mutane ma ban taba sanin cewa Hajiya Ummah tana da wata diya ba. Duk munyi zaton ma ko shi kadai ne dan nata."

Rashida tace, "ai ba Hajiya Ummah ce Mahaifiyata ba fa, ni Ummana tana Makarfi."

Ta jinjina kai cikin mamaki da daurewar kai. Ganin kada ta dameta da tambaya yasa bata kara tambayarta ba.

Da suka karasa gida, ta bude mota ta fita Rashida tana binta a baya.

Tace mata, "to mu shiga ciki ku gaisa da yan gidan ko?"

Ta amsa mata da 'to.'

Sai kuma ta bude booth ta ciro wata leda mai dan fadi. Ta bi bayan Nadiya, Ammar kuma yana makale da ita yana ta zuba mata hira.

Matan gida duk aka zubawa Nadiya ido da Rashida kamar sun ga wasu sabin halittu. Mama na kofar kicin da amarya suna aiki, da Nadiya tace mata bakuwa ce kanwar Baban Ammar, sai ta ajiye aikin Amarya kuma ta amsa. Suka wuce dakin Mama, Rashida na gaida Salame dake aikin kulla lalle a leda wanda take sayarwa, tayi banza da ita ta kyaleta. Nadiya ta janye hannunta zuwa cikin daki ganin ta cigaba da auna mata gaisuwar ita kuma ta ki amsawa.

Rashida har kasa ta zube tana gaida Mama, ta amsa tana mata murmushi cike da jindadi.

Basu wani jima ba tace mata zasu tafi saboda Magriba ta matso.

Nadiya ta shiga uwar daka ta debo tarkacen kayan kwalliya da tayo guzirinsu tun bikin da taje Maiduguri. Ba wasu masu yawa bane ko tsada, amma haka Rashidar ta amsa tana godiya da nuna jindadinta kamar wata kyautar ban girma ce ta mata.

Sai kuma itama ta mika mata ledar hannunta, wai Yayansu yace a kai mata.

Ta amsa cike da mamaki, don kuwa ko da wasa bai fada mata hakan ba.

Ta rakasu har waje, suka shiga mota suka tafi. Ta daga jaka, ta ciro wata lafiyayyar shadda ruwan hanta ta sha wani irin surfani a hannu da wuya mai tsananin kyau. Nadiya bata san ya aikin surfani yake ba, amma dai wannan tasan daga gani ba karami bane. Ta kara ciro wani flat din takalmi da jaka na MK, ga agogo nan itama ruwan hanta da gyale mai yalwar fadi.

Ta zubawa kayan idanu da mamaki, Amarya data shigo ganin kaya, tayi guda tace, "Allah sarki, wani hanin ga Allah baiwa ne! Jiya har zancen wai ai wannan sallar haka nan zaki yi ta babu sabon dinki na tsinto ana yi a tsakar gida. Wai kina ta hura hanci da fankama na banza da wofi!"

Mama ta kama baki, tace, "kai! Ni da abin magana baya yiwa wadannan mutane kadan."

Nadiya kuwa tayi dan murmushi kawai. Ta maida kaya inda suke ta ajiyesu.

Da ya kirata suka yiwa juna barka da shan ruwa.

Tace mishi, "nagode da kayan da aka kawo. But you didn't have to!"

Yace, "duk abinki dai ba zaki hanani samun ladanki na zuwa idi ba Nadiya!"

Ta saki yar dariya, "ba abinda nake nufi ba kenan. Amma dai nagode!"

Yace, "anytime Nadiya!"

26.

Suna gama wayar da Nadiya sai ga kiran Hajiya Ummah ya shiga wayarshi kamar wadda take jira.

Ya tashi daga kishingide din da yake, ya dan runkufa yana gaidata bayan ya daga kiran.

Ta amsa a tausashe, "lafiya lau Babangida. Kun sha ruwa lafiya?"

Yace, "lafiya lau Ummah. Ya gida?"

Tace, "muna nan muna shan zafin Najeriya, kai dai ai ka gudo ka barmu!"

Yayi yar dariyar, yace, "Ummah ai ke kika ki zuwa, bayan har an kammala miki komi na tahowa."

Tace, "kai barni dai wannan karon kaji, nafi gane zamana cikin yan'uwa da dangi. Wannan na shiga wannan na fita."

Yace, "hakane kuma."

Ta gyara zama tana ambatar sunanshi a nutse, ta haka sai ya gane zancen nasu mai muhimmanci ne, sai shima ya gyara zama yana kara kashe kunne.

Tace, "me ya faru ne ga matarka nan tazo tace ka aikata mata rashin adalci."

Yace, "ni kuma Ummah? Me nayi mata ne bayan ba na ma garin?"

Tace, "cewa tayi ka dinkawa Amaryarka kayan sallah ka kai mata? Bayan kuma ita haka ka tafi ka barta zikal!"

Ya hade fuska kamar yana gabanta, "ita tace miki haka ne? To ki tambayeta kiji, da zan tafi nawa na bata na siyayyar kayan kamun azumi da kuma na sallah? Me take nufi da ni ne wai? Ko kuwa ba ita bace ta fada min iyaka adadin abinda take so ba, na kuma dauka na bata babu musu?"

Ummah tace, "duk da haka, gata nan tana korafin ita ai baka taba dinko kaya ka kai mata ba sai dai ka bata kace ta saya. Yanzu kuma ka dauki na wata daban, ka kai telan da yake mata dinki ya dinka mata. Anya ka so tsayar da zancen gaskiya anan Habibu?"

Ya shafa goshinshi da yaji yana shirin daukar zafi, yace, "Ummah, ni ban ma san ko wane tela ne yayi aikin ba. Sannan Shukurah ita da bakinta tace in daina yi mata dinki in dinga bata kudin. Saboda sau nawa ne zan kawo mata kayan tace kalarsu bata mata ba, watarana tace bata son design din, watarana ma haka zata ce kwata-kwata ba su take so ba. To ya zan yi mata ne? Ni Allan-musuru ne da zan san abinda ke cikin ranta? Ko kuwa a kanta zan kare ina bin kanta tana wulakantani? Wahayi aka min da ita ne?"

Ummah da taga ranshi yana neman baci sai ta jefawa Shukurah harara da tayi zaune tana sauraron hirar da suke yi. Tace mishi, "to naji, ta bangarenta dai bata kyauta ba kam. Amma duk da haka ka dinga kokarin daidaita adalci. Tunda dai kaga nauyi ne mai girma yake kokarin hawa kanka. Sannan daga yau na kashe zancen wai a ba mata kudi ta sayi tufafin sallah, ka sayo duk

abinda kaga yayi maka ka bata. Idan bata amsa ba kuma zata gamu da ni ne."

Ta karasa fadin hakan tana kallon Shukurah don ta fahimci gargadinta. Sai ta dauke kai.

Shikuwa yace, "to shikenan Ummah."

Har zata kashe wayar sai kuma ta dakata, tace, "da ba munyi da kai ba za a yiwa Nadiya komai ba tunda nan zata zo ta tarar da lefenta?"

Yace, "ai Ummah nima Mami ce ta kirani dazu tace ta bada dinkin da za a kaiwa Nadiya din tayi kwalliyar sallah dashi. Nayi tunanin ma ko kunyi maganar ai."

Tace, "ita Sumayyah din?"

Yace, "ehh."

Ta jinjina kai, "ok. Ai shikenan. Goben kake tafe dai ko?"

Yace, "in shaa Allah Ummah."

Tace, "to Allah Ya kawo mana ku lafiya. Allah tsare mana ku."

Yayi murmushi cikin jindadin addu'arta, "ameen ameen Ummah na!"

Suka yi sallama.

Ummah ta juya tana kallon Shukurah dake tabe baki, tace, "to ke kin dai ji da kunnenki ko? To wallahi idan zaki shiga taitayinki ki shiga Shukurah. Ina kula dake ai, tunda zancen auren Babangida ya tashi kika tsangwami kanki, kina neman ki tadawa mijinki hankali kema kuma ki hana kanki sukuni. An fada miki dama haka ake yi ne? Ko kuwa kin taba jin an ce ana yiwa namiji haka a zauna lafiya? To wallahi ki kula, don kinga yana binki a hankali yana miki yadda kike so, ba wai tsoronki yake ji bane. Lallabine yake miki, duk kuma ranar da ya gaji ke zaki kwan a ruwa!"

Shukurah ta zumburo baki, "to kuma Ummah sai a yiwa mutum rashin adalci amma ya kasa furtawa haka ake yi?"

Ta jefa mata harara, "zo ki fada min rashin adalcin da aka miki a wannan zance inji don Allah! Yanzu tunda Babangida ya bar kasar nan, sau nawa kika kirashi a waya?"

Tayi shiru tana hararar waje daya. Ummah kuma ta tabe baki, tace, "ke dai kika sani ai. Kada ta kara kwabe miki wallahi don kin bar hakarki tayi ruwa da gangan kuma kizo ki ce zaki sanya min ciwon kai Shukurah." Ta tashi ta barta anan.

Itama tashi tayi ta fita daga sashen Ummah din ta koma nata tana sake-sake a ranta.

⭐⭐⭐

Ranar sallah yan gida duk an zuba ido ana jiran a ga Nadiya ta fita da tsofin kaya zata je idi. Don Lantana tun da uwar safiya ta tashi ta ci kwalliya cikin sabin kayanta, ta je kofar dakin Salame ta nemi waje ta zauna. Fadi take tana karawa, "yau dai sai taga karyar masu karya!"

Sai ga Nadiya din ta fito ta ci kwalliyarta abinta tana ta bada kamshi. Salame da itama take ta saurin tayi tata kwalliyar ta fito sai ta koma tana lekenta ta taga. Musamman da su Maryam suma suka fito cikin shigarsu mai kyau wadda Mama ce tayi musu dinkin, suka tsaya a kofar dakinta suna kashe selfie abinsu. Da suka gama kuma suka dauki hanya suka tafi masallaci abinsu. Sai Lantana taja jiki ta koma daki kamar kazar da kwai ya fashewa a jiki.

Ranta fal bakinciki da takaici a cikinshi ya mata katutu.

Ana jimawa kuma sai ga Mama ta fito cikin rantsattsan leshinta da Yaya AbdulHadi ya dinka mata. Ta dinga kaiwa da kawowa a tsakar gida ita da amarya wadda ita ce da girki ranar, hankalinta kwance babu abinda ya

dameta. Sai suka bar su Salame da makalewa a daki suna lekensu, reshe ya juye da mujiya.

Don kuwa da so suka yi ranar su gallazawa Nadiya su tura mata haushi da takaici. Sai suka ga kuma lamarin bai je musu yadda suka so ba.

Ita kuwa Nadiya har ga Allah ma tuni data manta da abinda ya faru game da dinkin sallah da ba ayi mata ba. Kwalliyarta tayi tsakaninta da Allah ba don ta turawa kowa haushi ba.

Da suka taso daga Masallacin, suka biya ta shago ta dauki abubuwan motsa baki, saboda tasan ranar ba zasu rasa baki masu zuwa yawon sallah ba. Tasan kuma dasu zasu bude baki a gidan ranar tunda abincin da za a dafa ma sai a ranar aka kai gida, tasan ba a kai ga saukewa ba yanzu. Suka sake tarar abin hawa suka wuce gida.

Ta mikawa mai Napep din daya daukosu kudinshi, ta biyo bayan su Maryam da suka rigata fita tana mai gyara zaman gyalen dake jikinta.

Kamar an ce daga kanki, tayi kyakkyawan gani da wanda ya zame mata tauraro a halin yanzu.

Yana tsaye ta can bayan gidansu a jikin motarshi, shi kuma da waya a hannunshi yana kokarin kiranta sai suka hada ido.

Duniya da abinda ke cikinta suka dauke mata a wannan lokacin. Tsakanin ita da shi bata san wa ya fara takawa zuwa ga dan uwanshi ba, sun dai tsinci kansu a kofar gidansu Nadiya dinne a tsaye, sunyi carko-carko kamar wasu tsofin zakaru.

Kamshin nan nashi ya lullubeta yayi mata kawanya, akwai wani abu a can karkashin ranta dake kokarin janta zuwa gareshi, wanda ta rasa ko menene.

Wata daya kacal daya wuce, idan wani yace mata wai zata kalli fuskar Habibu taji kewarshi ko dadin ganinshi, wallahi sai tace mishi bashi da lafiya. Amma sai gata din, bakinta ba ma zai iya furta irin yadda taji dadin ganinshi ba. Ta kasa dauke idanu a kanshi da yake kallonta yana sakin wani tausassan murmushi.

Yace, "ba kallona zaki tsaya kina yi ba haka kawai Nadiya, idan kinyi kewata ne just tell me. Kin dai san ba zan iya karanta abinda ke cikin ranki a halin yanzu ba!"

Sai ta kawar da kanta gefe daya, tana dan gyara fuskarta don kada ya fara karantar irin abubuwan da zuciyarta ke fitarwa. Abin ma nema yake ya daure mata kai. Yaushe ne tayi sake har Habibun ya yiwa ranta wannan kamun kazar kukun? Har yaushe suka yi sabon da zata ke jin shi kamar wani tsohon masoyi da tayi shekara da shekaru bata gani ba?

Tayi kwafa cikin kokarin boye abinda ke cikin ranta, "wani kewa kuma ana zaman lafiya?"

Ya sake yin dan murmushi a hankali yana takawa zuwa inda motarshi take, itama tana binshi a baya.

"Ko baki fada da bakinki ba ai idanunki sun gama tona miki asiri Nadiya! Shi yasa ma ban fada miki zan zo yanzu ba kenan. Saboda ina son ganin abinda kike kokarin boye min ne da idanuna."

Ta dakata da tafiyar da take yi, suka koma suna fuskantar juna, "ban dai san me kake son cewa ba, amma ni dai nasan babu wani sirri dana boye a cikin raina!"

Bai bata amsa ba sai dan murmushi kawai da yayi, ya dauko kallo ya kare mata tun daga tafin kafarta har tsakiyar kanta. A gefe guda kuma ita satar kallonshi take yi, sai lokacin ta fahimci ashe ma ankon shadda suka yi ita dashi.

Yace, "wai ni amaryar nan tawa kullum wani kara fresh kike yi abinki, wai don Allah menene sirrin?"

Dariya sosai ta saki tana kallonshi a kaikaice. Ta dai fahimci tsokanarta kawai yake ji da neman magana. Don haka ta biye mishi.

Suka jima dashi anan suna hira kafin yayi mata sallama ya tafi. Saboda daga Masallaci nan ya zarce kai tsaye bai koma gida ba.

Itama ta wuce gida, data tarar an sauke abinci ma zuwa lokacin ta zauna ta ci kayanta.

Washegari gidansu ya cika da iyalan gidan yan yawon sallah. Su Basira da Zainab da Habiba duk sun je da yaransu, haka Anty Aisha matar Yaya Saminu. Ita Haulatu sai zuwa biki sannan zata zo.

Suka yiwa Nadiya caa da zancen me yasa bata fitar musu da anko ba? Ita dai nata bada uzirin su yi hakuri an ce babu taron da za ayi ne shi yasa.

Washegari ta fara zuwa gidan mai gyaran jikin da Anty Hauwa ta samar mata. Can ake mata turaren jiki dana gashi, a kuma yi dilka da halawa. Kullum nan take zuwa yini guda ana wannan aiki. Ita kanta duk korafin da take yi nan da nan sai gashi ta fara yin wani irin 'fresh' kamar yadda Habibun nata yace. Ta fara kilewa tana kara yin bul da ita. Kamshi kuwa duk inda ta ratsa sai ka ji shi, har sai ta bace ta barka kana shakarshi.

Bikin saura kwana uku, su Anty Hauwa da Anty Lima da wasu kannen Dada da yan'uwansu suka dira a Kaduna. Gida guda Madam ta ware musu inda nan ne itama zata yi nata taron bikin.

Sai ga Anty Lima ta dira da akwatu guda shake da kaya wai na fitar biki.

Ta kama baki tana kallon kayan cikin mamaki, tace, "wannan fa daga ina?"

Tace, "daga ina kuwa idan ba daga Angonki ba? Tun cikin azumi ya kirani yace in mishi estimating din abinda zai isa ayi miki dinkin kayan fitar biki, har da kudin kwalliya da na gyaran jiki. Na mishi calculations ya turo min kudina cas. Anty Hauwa ce tace kada a fada miki, don shi dinma cewa yayi kada a fadawa kowa."

Ta dinga daga kayan tana dubawa baki a dage, "wannan kayan ai sunyi yawa wai a fitar biki kawai gaskiya! Duk ya zanyi da wadannan ne kam?"

Anty Lima tace, "sai ki mishi kwalliyar da sauran idan kinje gidanshi. Don na fahimci dai mijin nan naki dan kwalliya ne sosai da son kyale-kyale. Shi yasa nima na kawo miki gudummawata ta musamman..."

Ta janyo wata jaka ta bude ta fara zarowa Nadiya wasu shegun night wears da underwears. Kallo daya ta musu ta kauda kai, ita kunya ma kayan suka bata.

Tace, "ki rasa abinda zaki bani yanzu sai wadannan yan iskan abubuwan? Kin dai san ba zan taba sanyasu ba ko?"

Anty Lima ta maida kayan inda suke tare da sanyasu a cikin akwatun kayan data kai mata.

Tace, "ke kika sani ai, ko ki sanya ko kada ki sanya duk ya rage naki. Ni dai ai nayi mai wuyar. Amma dai in fada miki gaskiya, yadda jikin nan naki yake daukar gyara yana kyalli da shekinnan, wallahi gwara kiyi amfani da damar nan. Ki dinga shiga ta raina sa'a!"

Tayi dariya, "Allah Ya kyauta miki wallahi Anty Lima. Kuma sai aka ce dole sai nayi shigar rashin kirki sannan ne ba za a raina ni ba?"

Tace, "ahaf! Zauna anan dai kina mamaki. Zaki fahimci tsarin abin nan ba da jimawa ba. Tashi mu tafi gidan gyaran nan kinji? Don nima gaskiya yau dai sai an dan shafa min dilkar nan na dan yi haske!"

Ta kyalkyale da dariya, "wato abin ma har da sharri kenan?!"

Ta hade kan kayan ta rufe akwatu ta ajiye, ta zari hijabinta suka fita.

27.

Madam taje da tawagarta mota guda, daya kuma tana binsu a baya shake da tarkacen souvenirs na biki. An bugo jakunkuna da mugs na shan shayi da abin turaren wuta. Kowanne dauke da sunan Nadiya din da Habibu ana tayasu murnar aure da fatan kasancewa karkashin inuwa daya har karshen rayuwarsu.

Basu kuma jima da zuwan ba sai ga masu hada waje suma sun karasa. Aka hau gyaran waje babu kakkautawa, nan da nan sai ga wajen taro mai kyau an hada.

Mai kwalliya taje har gida ta yiwa Nadiya kwalliya, aka shiryata cikin lafaya mai kyau ruwan zaiba, suka fita cikin yan'uwa da abokan arziki ana gaisawa. Duk yadda bata so a sanya kida ba, sai da Madam ta sha casunta ita da abokanta aka yi ta liken kudi kamar ba gobe. Sai can wajen karfe tara na dare kafin suka koma gida.

Can ma gidan cike yake da yan biki. Su Anty Haulatu da su Anty Jamilah duk sun je da iyalansu. Da suka zauna zaman hira duk ba su suka nemi makwanci ba sai wajen karfe daya na dare.

Washegari Juma'ah ranar daurin aure. Tunda Asubahi Abba ya tura aka kira Nadiya din, taje yayi mata nasiha daidai gwargwado, ya kara mata da gargadin kada ta kuskura tace zata taba taka kafarta cikin gidanshi da sunan yaji ma balle ayi zancen kaso aure. Daga nan kuma ya mata addu'ar samun zaman lafiya, yace taje ya sallameta.

Ta lallaba ta tashi da kyar, ta fita daga dakin cikin mutuwa da sanyin jiki. Haka ta wayi gari ranar gabadayanta jinta take kamar wata wadda aka yiwa mutuwa. Duk ta bi ta rasa duk wani kuzari nata.

Koda ta koma daki, kasa biyewa hirar da suka sake jonawa tayi, ta shige can dakin Mama tayi lamo a kan gado. Ko abinci sai da Mama din taje ta kai mata shi da kanta, sannan ta samu ta iya tsakurar kadan.

Da gari ya washe kuma, Anty Lima ta matsa mata tayi wanka, aka yi mata kwalliya madaidaiciya. Ta samu leshi fari mai kyau cikin kayan fitar bikinta ta sanya, ta fita tsakar gida aka hau hotuna da ita haka nan ba don ranta ya so ba.

Duk wannan abin da ake yi su Salame suna lafe a cikin dakunansu sun ki fitowa ko nan da can, kiran duniya babu wanda ba a yi musu ba akan su je a dauki hoto dasu amma suka ki fita. Sai Lantana ce ma daga baya da taji mutane suna maida magana, ta lallaba ta fito tana dariyar yake.

Zuwa lokacin da ake gab da daura aure, ta sake yin wata kwalliyar cikin atamfa holland abinta. Da bakin Madam yan Maiduguri suka je gidan nasu, aka hadu dasu aka cigaba da gudanar da hidimar biki.

A ranar ta Juma'ah bayan an fito daga sallar juma'ah a babban masallacin unguwarsu, aka daura auren na Nadiya Auwal Iko da Habibullahi Abdullahi Makama. Akan sadaki naira miliyan daya, lakadan ba ajalan ba.

Mata suka dauki guda da shewa, yara suka hau tafi da murna lokacin da sakon daura auren ya riskesu.

Tana can cikin zugar su Anty Lima da su Aramide da suke ta mata tsiya, ita kuwa gabadaya ta rasa sukunin biye musu ma kwata-kwata.

Aka shiga sanarwar ango zai shigo gida a gaisa da mutane. Nan ya shigo har cikin falon Mama cikin zugar abokanshi, ya sha shadda fara tas tana ta sheki. Suka kwashi gaisuwa tare da godiya suka juya suka tafi.

Tana jinsu har suka gama gaisawar, zuciyarta na aikin bugawa a gaggauce. Rabon data sanyashi a cikin idanunta tun ranar sallah da yaje. Da bikin ma ya kara matsowa sosai, sai wayar da suke yi ta ragu.

Tana dai jin su Anty Lima na gulmar irin kyawun da angon nata yayi, bata iya ce musu komai ba.

Aka cigaba da hada-hada da hidima a gidan. Anty Hauwa da Amarya su suke ta shige da ficen hada mata kayayyakin da masu kai amarya zasu wuce mata da su.

Ana yin sallar la'asar, taji ance wai a fara shirya amarya ga motocin daukar amarya nan sun taho. Sai idanunta duk suka raina fata, hawayen da tun safiyar ranar suke son zubo mata tana makalesu, suka hau kwarara. Jin abin da take yi kamar a mafarki, sai a yanzu ta fara yarda da lallai gidansu zata bari.

Anty Hauwa ta ja ta bayi, ta hada mata wani irin ruwa tayi wanka dashi mai tsananin kamshi da sanya fata laushi. Data fito kuma ta tareta da turare kala-kala, tayi na tsuguni, aka yi na jiki, aka yi na gashi, aka yi na kaya. Abu fa sai gata ta zama kamar wata gidan kamshi. Duk inda ta motsa sai kamshi ya watsu.

Wani swiss lace aka sanya mata riga da skirt, rigar ta sha adon stones da net, idan ka gani sai kayi tunanin ko inji ne yayi dinkin ba mutum ba.

Gashin nan nata da ya sha gyara yana ta kamshi, aka sakar mata shi ya sauka har baya, saboda ta hana a fiddo wani ya zuba a gaban goshinta. Aka kai bakar Alkyabba aka dora mata.

Da aka kaita gaban Mama tayi mata nasiha, kawai sai ta dora kanta akan cinyar Mama din ta fashe da kuka sosai. Baiwar Allah itama Mama din sai ta kasa cewa komi, ta dora hannunta a gadon bayan Nadiya din tana shafawa a tausashe, daya hannun kuma tana share mata hawayen.

Da za a fita da ita har dakinsu Salame da Lantana aka shiga da ita son suyi bankwana, Salame dai cewa take, "ayi hakuri, zaman aure dan hakuri ne."

Lantana kuma na aikin amsawa da "kwarai kuwa. Hakane kam!"

A haka su Anty Jamilah suka ja ta aka fita da ita zuwa inda motoci suke jiransu.

Ba wasu mutane aka dauka da yawa ba, daga Anty Jamilah din, sai Anty Hauwa da Maryam da Anty Lima da Amarya. Da suka tsaya gidan Madam itama ta mata nasihar da zata musu, sai abokiyarta daya ta bi bayansu.

*

Gidansu Habibun gidane ba kamar sauran gidaje da suka sani ba, haka ba irin gidan da Nadiya tayi tunanin tararwa bane.

Kanta a kasa yake tunda aka fara tafiya, jifa-jifa hawaye kan diga daga cikin idanunta tasa hannu ta share.

Daga bakin mutanen cikin motar take jin irin hirar da suke game da haduwa da tsaruwar gidan.

Masu jan motar suka kaita har kofar sashen da Nadiya din zata zauna, acan suka samu Rashida a tsaye tana jiransu. Ita tayi musu jagoranci har zuwa ciki.

Suka shiga ta wani lafiyayyen falo, ya sha leather seats jajaye, suka ratsa ta wani karamin corridor suka karasa dakin Nadiya din.

Dakin madaidaicine, gado ne sambal dan kasar Italy ya sha lullubi da zanin gado mai taushi, aka kama hannunta aka zaunar da ita a gefen gadon.

Su Anty Lima sune masu karade gida don ganin me ya kunsa? Kuma kowannensu ya yaba, ya kuma gamsu da abinda ya gani. Don kuwa tsayawa fadar irin daula da aka narkar a wannan waje ma bata baki ne. Aka shigar musu da abinci a cikin kuloli da lemuka.

Da suka gama zagaye da yan gyare-gyaren da zasu yi, Rashida ta musu jagoranci har wajen Hajiya Ummah. Ta musu tara ta girmamawa, ta bisu daya bayan daya ta runguma, fara'a fal fuskarta da nuna jindadi. Da ta yiwa Nadiya nasiha game da hakuri da rayuwar aure, sai ta bisu da godiya da ban

gajiya. Ta kuma bi yan kawo amarya da dubu ashirin-ashirin, kafin tace a kaita sashen Uwargida don tayi mata maraba. Haka suka tafi ransu fal farinciki da jindadin wannan mutunci da karamci na Hajiya Ummah.

Zuwanau sashen Shukurah kuma sai ya sage musu gwiwoyi. Sun samesu su uku ne kadai a falon. Suka yi sallama aka amsa, sauran gaisuwa kuma data biyo baya babu wanda ya taga musu. Su Anty Jamilah suka karaci maganganunsu suka gama, in bango yayi magana to sun tanka. Don Uwargida ma ana cikin bada amanar ta shuri takalminta tayi cikin daki abinta. Suma da suka ga haka sai suka lallaba suka juya.

A dakin Nadiya Anty Jamilah ce take kara yiwa Nadiya fada da wa'azantarwa, zaman aure dan hakuri ne musamman gida na kishiya, wanda kuma za a zauna tare da suruka. Tace tasan dai ba zata samu wata matsala daga Hajiya Ummah ba, itama kishiyar tata tayi kokari ta fahimceta, ta bata girma da hakkinta, don ta taimakawa mijinta kwatanta adalci a tsakaninsu.

Miji kuma tsakaninta dashi yi, na yi. Bari, na bari. Matukar hakan bai sabawa addini ba. Ta girmamashi, ta girmama mahaifiyarshi. Ta kaunacesu tsakaninta da Allah, ta kuma kiyaye hakkinshi dake kanta.

Da suka gama nasihar, lokacin har an fara kiran Magriba, suka mata sallama zasu tafi.

Anty Jamila tace mata, "na cewa Yaya AbdulHadi ya amshi sadakinki ya ajiye miki, bayan biki zan mishi magana sai ya turo miki su ko kuma a duba wani abu a saya da su."

Ta gyada kai tana sharar hawaye. Bata yi mamakin jin hakan ba. Don duk yanmatan gidan da za a aurar a gidansu to Abbansu idan ya amshi sadaki baya badawa, idan kuma an mishi magana yace hidimar biki yayi dasu. Don haka daga baya sai Yayunsu maza suke amsa da kansu, in yaso daga baya sai a ba amaryar tayi abinda zata yi da su.

Haka tana ji tana gani su Anty Lima suka tafi. Ta zauna tsuru ita kadai anan. Kadaici da tunane-tunane suka dameta. Daga karshe dai ta mike a hankali ta shiga bayi.

Bata tsaya duba abubuwan ciki ba da yabawa yadda aka tsara wajen, aka wadatashi da duk wasu abubuwan da za a bukata a bayi. Kawai tayi alwala ta fita.

Kofar da taji ana cewa nan wardrobe take ta bude, sai ta tarar da walk-in closet. Nan kam tsayawa tayi baki a bude kawai tana karewa komi kallo. Duk wata sutura, babu wadda babu. Sashen komi kuma daban. Sashen atamfofi da lesuka gasu nan, shaddodi gasu nan, ga jakunkuna da takalma suma ba su kirguwa. Ga mirror da itama aka shake samanta da kayan shafa da turaruka, a kusa da ita kuma wani dogon show glass ne da aka shakeshi da humrori da turarukan wuta da mayukan shafa hadin hannu, tasan wannan aikin su Anty Hauwa ne.

Ta samo hijabi mai tsayi ta sanya, ta fuskanci alkibla ta tayar da sallah. Koda ta gama bata tashi ba, ta cigaba da zama akan abin sallar tana lazumi har aka kira isha'i, ta yi. Ta daga hannunta sama tana addu'a, duk akan Allah Ya jibanci lamuranta game da wannan sabuwar rayuwa data shiga.

Bayan lokaci mai tsayi ta tashi tana nade abin sallar da hijabin jikinta, sai taji an yi knocking, kafin aka turo kofar dakin aka shigo. Ta juya a hankali tana kallon angon nata dake saye da doguwar farar jallabiya, shi kuma ya karasa shiga cikin dakin tare da maida kofar ya rufe.

Kallonta yake, in appreciation. Kayan sun matukar yi mata kyau fiye da tunani, haka sun fitar mata da kirarta kwarai da gaske. Musamman da yake babu kallabi a kanta sai gashinta da yayi baya ya kwanta, hakan sai ya kara kayatata a gareshi sosai.

Ya tsaya a gabanta yana cigaba da kallonta, ita kuma haka kawai ta tsinci kanta da rawar jiki da sagewar gwiwa. Yasa hannu ya karbe hijabin hannunta ya ajiye a gefe.

Yayi murmushi ganin yanda tayi wani tsuru-tsuru tana muzurai kamar wadda aka kama ta yiwa sarki karya.

Yace, "Tubarkallah Amarya. Ma shaa Allah. You look so breathtaking wallahi Nadiya! Anya zan iya jumurin bari wani ya kalle min ke kuwa, ba zan kulleki a dakina inyi ta kallonki ni kadai ba?!"

Ta rasa kalar amsar da zata bashi, kawai sai ta buge da gaidashi, tace, "ina yini?"

Yayi dariya sosai, ba zato kuma sai tsintar kanta tayi cikin jikinshi. Kanta saman kirjinshi tana iya jiyo bugun da zuciyarshi take yi, yace, "lafiya lau Love. Ya bakunta?"

Ita ai tuni bakinta ya gama macewa, abubuwan da kusancin da suka yi suke haddasa mata a jikinta suna da yawa. Bugun da zuciyarta yake yi shi kanshi sai daya jiyo shi. Yayi dan murmushi, "to, tun kafin a kai ga zuwa ko'ina har na kashe bakin tsanyar? Ko kuwa dai saduda ce kika yi tun yanzu?"

Ita dai ta kasa ce mishi komi, yadda kasan wadda aka cirewa duk wata laka ta jikinta.

Yace, "ki zo muje Ummah take nemanmu, idan mun dawo sai ki fada min dalilin wannan shan kamshi da ake min. Da kuma tukuicin yabawa kwalliyarki da nayi, tunda ni na cire tawa kafin ki kai ga yaba min din."

Yadda kasan wata mutum-mutumi, haka ta tsaya ya taimaka mata ta sanya hijabi. Sannan shi da kanshi ya lalubo mata takalmi flat mara nauyi ta sanya, kafin ya kama hannunta suka fita.

Har sai daya daga kofa zasu fita, sai kuma ya mayar da ita. Ya juya ga Nadiya dake jefa mishi kallo mai dauke da alamar tambaya, sai dai kafin ta kai ga tambayar, ya hade bakinsu waje daya.

Zuciyarta ta hau daka da lugude a kirjinta cikin wata dimuwa data ziyarceta. Wani al'amarine yake faruwa da ita wanda bata taba tsintar kanta a cikinshi ba tunda take.

Habibu kam bai ma san abinda ke wakana da ita ba, bidirinshi kawai yake yi. Don kuwa lebunanta sun jima suna tsole mishi idanu. Sai daya gama shanye duk wani janbaki da wet lips dake bakinta kafin ya saketa, ya hade goshinsu waje daya idanunshi a lumshe yana sauke wani irin numfashi. 'Da ba don Ummah bace me kiransu...' Sai kuma ya girgiza kai.

Ya bude idanunshi a hankali yana kallon yadda nata idanun suke a rufe itama, numfashi take ja tana fesarwa a sukwane kamar mai fama da cutar numfashi.

Ya kai hannu a tausashe yana goge gefen bakinta inda ya damalmale da janbaki, sai daya goge mata shi tsaf kafin ya kalleta da rinannun idanunshi. Data kasa daukar kallon nashi sai tayi kasa da nata idanun. Murmushi ya saki mai sauti, yace, "bari dai muje mu dawo, zan fayyace miki wasu sirrika na musamman Nadiya! Na ga alamun dai ke baki san kalar wainar da nake toyawa bane a cikin raina!"

Ya sake bude kofa suka fita, ya rufe kofar da makulli ya damka mata a hannu kafin suka wuce sashin Hajiya Ummah kai tsaye.

Sun sameta a zaune a falo ita da Shukurah akan kujera. Ya wuce kusa da ita kai tsaye, ya zauna a kasan kujerar da take kai kusa da kafafunta. Da Nadiya taga haka, itama sai ta bi sahunshi. Ta zauna a gefenta na dama tana mai dan bada nisa dasu kadan.

Hajiya Ummah ta hadesu waje daya. Nasiha tayi musu sosai wadda yawancinta maimaicin abinda ake ta fadawa Nadiya ne tun da garin ranar ya waye. Bayan nan kuma sai dokar gidan da take a kafe tun ba yau ba, ana haduwa anan sashenta duk safiya a karya, haka ma abincin dare a can ake ci. Don haka ko kina girki ko ba kya yi, dole sai kin halarta. Idan ma kaga zaka iya, har da rana zaka iya zuwa ka ci abinci. Idan kuma kaga dama, zaka iya hada naka a bangarenka, tare da maigidan idan kaine da girki ranar. Ta tambayesu sun fahimta? Duk suka ce mata ehh.

Sai kuma ta juya ga Habibu tana tambayarshi kwanaki nawa ya debar musu na girki? Ya amsa da bai kai ga yanke wannan hukunci ba. Don haka tace musu to bayan Nadiya tayi kwanakinta bakwai kamar yadda al'ada da addini suka zartar, zasu cigaba da yin kwanaki bi-biyu a tsakaninsu. Da suka yi na'am da hakan, sai tace to kowace ta wuce sashenta sai da safe.

Nadiya da Shukurah suka tashi suka fita. Suna fita Shukurah ta daga kafa ta wuce abinta kamar dama mintsininta ake yi. Nadiya kuwa ta tabe baki ta wuce sashenta itama.

Suna bada baya Hajiya Ummah ta kalleshi, tace, "Habibu ka bani hankalinka nan, akwai magana mai muhimmanci da zamu yi da kai!"

Sai ya mayar da hankalinshi gabadaya kanta.

Tace, "amarya dai gata nan an kawo maka. Na gode maka da biyayyarka a gareni, Allah Yayi maka albarka!"

Yayi murmushin jindadi, "Ameen ameen Ummah!"

Tana shiru tana kallonshi a hankali kafin ta nisa, tace, "abu daya nake so kayi min Habibu. Ni nasan ba zan hanaka zama da matarka ba, sai dai ka fahimci cewa, auren nan naku na wucin gadi ne!"

Ya daga idanu da sauri, a birkice yana kallonta. Yace, "wucin gadi kuma Ummah?!"

Ta gyada kai, "kwarai! Dogon labari ne, wanda ba zai yiwu a gama shi da wuri ba idan nace mu fara. Saboda haka nake so, ka takaita yawan haduwa da ita. Bana son abinda zai dawo daga baya ya bata maka rai shi yasa nake fada maka wannan yanzu. Da zarar lokaci yayi, zaka sallameta ne. Saboda bata dace da kai ba ko kadan. Akwai mata da yawa a ciki da wajen Kadunar nan. Zan kuma yi kokari in mayar maka da wadda ta fita a komi. Ta zauna dai da sunan tana a matsayin matarka, amma hada jini da ita shine abinda

ban amince ba. Ba zama tazo yi ba, don haka ban ga amfanin hada zuri'a da ita ba. Ka na jina?"

Ya gyada kai a matukar sanyaye. Duk wani buri da kudiri na duniya, babu wanda bai dauka ya ta'allaka ya dora akan wannan dare ba. Me ya faru ne haka? Ya shirinshi yake kokarin shan ruwa ne?

Tace, "yauwa. Kayi kokari ka kiyaye hakan. Ka kuma dinga tunawa da cewa kana da wata Matar a gefe, wadda zata iya baka duk wani abu da zaka bukata a wajen mace. Mace ai macece, menene zata nunawa yar uwarta mace? Don haka ka tashi abinka, kaje ka kwanta. Gobe kuna da muhimmin meeting kai da Maigirma Gwamna da Mai Martaba Sarki. Karfe tara ne na safe bana so kayi kuskuren makara... Ka wuce sashenka kai tsaye, ban amince da wai ka kwanta a sashenta ba kana ji na?"

Maganar ta karshe ta dira a cikin kunnen Nadiya wadda ta manta makullin dakinta ta koma don ta dauka. Tayi sallama a nutse, kamar dai babu abinda taji. Tunda tun asali ma dai bata fahimci inda zancen nasu ya sa gaba ba.

Suka amsa mata, murya a shake tace, "makulli na manta."

Hajiya Ummah ta mata nuni da inda ta zauna, "aikuwa gashi nan, muma bamu kula dashi ba ai da an kai miki. Ko gajiya ce ta sa kika fara mance-mance ne?" Tayi mata tambayar cike da tsokana.

Nadiya dai dan murmushi kawai tayi ta dauki makullin ta juya, don bata son katse musu hirar da suke yi.

Sai da ta fita kafin ta kalleshi, "ka fahimci me nake fada maka ai ko?"

Murya a matukar shake yace, "ehh Ummah!"

Ta gyada kai, "to madallah. Tashi kaje. Allah Yayi maka albarka!"

Ya tashi babu musu ya wuce. Ranshi cike fal da tambayoyi da daurewar kai, sai dai ya kasa daga baki ya furtasu.

Hajiya Ummah ta bishi da kallo har ya fita. Tausayinshi ya darsu a cikin ranta. Saboda duk yadda ya so ya boye yadda abin yaje mishi, fuskarshi ta kasa boye hakan. Sai dai saboda wannan kadai, ba zata iya bari wannan dama ta subuce mata ba. Ba zata yi kuskuren hada zuriya da su ba. Wannan ma da suka hada da ita ta isa. Ta san ma idan ta gama sauke abubuwan data kudirta a kansu, zasu rabu ne rabuwa ta har abada. Don haka babu zancen ma sake kawo wani lamari da zai kara dagula mata shiri.

Da wannan tunani ta gyada kai cike da gamsuwa da wannan shawara, ta tashi ta wuce dakinta.

Shiru-shiru Amarya har ta kammala shirin kwanciya barci cikin fargaba da taraddadin alkawarin da Habibun ya daukar mata. Tsoron haduwarsu dashi take yi tsakaninta da Allah. Tsoron ya fayyace mata wadannan sirrika take yi. Bata tunanin ta shiryawa hakan.

Ta lalubi waje ta kwanta tana zaman jira, har dai daga karshe dai ta yanke wannan dai ba zuwan zai yi ba. Ga yunwa da take nanikarta kamar me, tana tunanin rabonta da abinci tun karin safe da tayi. Shi din ma ba wani abu na azo a gani bane ta ci.

Ta tashi ta shiga kicin da shima yake a shake da kayan kawa. Ga mamakinta sai ta tsinci kaza a cikin microwave wadda ta sha gashi tana ta tashin kamshi. Bata san lokacin data watsawa kazar harara ba, ta kara duba agogon wayarta taga har karfe goma saura. Babu kira daga angonta babu sako a rubuce. Sai tayi kwafa kawai.

Sauran abincin da su Anty Jamilah suka yi ta bude ta zuba dan kadan ta ci, ta hada shayi mai kauri ta sha. Ta koma dakinta tayi kwanciyarta.

Har barci ya fara daukarta, ta bude idanunta tarwai wani tunani yana darsuwa a cikin ranta; 'ko dai ita ce ake cewa ba a yarda a kwana a sashenta ba?!'

28.

Ranar dai barci ga su duka biyun sai barawo. Duk da gajiya da barcin dake tattare da Nadiya, amma haka tayi ta juye-juye da sake-sake har dare ya raba. Lokacin data samu barcin ya kwasheta da kyar, tuni duniyar ta gama kwanciya barci.

Shi yasa ta makara a washegari. Bata tashi farkawa ba sai can da gari ya fara yin haske. Ta tashi da sauri ta dauro alwala tayi sallah.

Da ta gama sai bata koma barci ba saboda tasan koda ta koma ma ba lallai ta iya yin ba, ta shiga bandaki ta bata lokaci mai tsayi cikin ruwan dumi dake tashin kamshin lemun tsami da citruss kafin ta fita, ta tsane jikinta da kyau kafin ta dauki lotion mai kyau na Dove ta shafe jikinta dashi.

Ta zaro wata doguwar rigar atamfa da aka yi dinkin rabi da net da bakin lace ta sanya. Data gyara gashinta ta nade, sai kawai ta dora karamin gyale a saman kanta bata dora dankwali ba. Data kai turare ta fesa, sai ta fito sak a amaryarta.

Ta zare wayarta a caji, ta kunnata kafin ta fita zuwa falo. Ta zauna kan luntsumemiyar kujera tana kara karewa wajen kallo cike da burgewa, lallai fa wanda ya samu ya huta. Waje sai kace fadar wata matar Gwamna ko First Lady? Sai kuma ta dan saki yar dariya kawai, data tuna ashe angon nata fa Gwamnan yake son zama.

Ta hau duba wayarta tana laluben missed call daga angon ko kuma text message, amma babu abinda ta tarar sai sakon Anty Lima dake bata labarin wai ta tabbata ta shiga ruwan zafi da kyau, kuma ta samu man zaitun mai kyau ta dinga amfani dashi. Taja wani dogon tsaki tana fita daga cikin message din.

Ba wai rashin kwanan da bai yi da ita bane yake bata mata rai, rashin sanin dalilin faruwar hakan ne ke bata mata rai. A da kam, watakila da babu abinda zai dameta. Da kila ma babu wanda zai kai ta farinciki idan Habibun ya gujeta. Amma yanzu fa? Abubuwa sun canza. Ta fara sabo da shi da

alakanta kanta dashi cikin sani da kuma rashin saninta. Bayan hakan ma, wace mace ce zata so ayi mata fashin darenta? Amarya ma kuma a haka? Tasan cewa koda tayi ikirarin bata damu ba, karya kawai take yiwa kanta.

Tana nan zaune tana wadannan tunane-tunane taji an buga kofa, ta tashi taje ta bude saboda jiya sai data kulle kafin ta kwanta.

Kamshinshi kadai ya sanar da ita ko wanene a bayan kofar. Ta dakata, tana tunanin ko da wace irin fuska zata tare shi? Sai kuma ta bude kofar fuska kadaran-kadahan. Bata so ta nuna zakewarta a abinda bai kai ya kawo ba. Sai me ma wai don bai kwana a dakinta ba? Watakila yana da wani daliline ko uziri na daban.

Fuskarshi zane take baro-baro da alamun laifi da yasan yayi, idanunshi kuma sun nuna alamun rashin barci da shima bai samu ba.

Ta dan duka a nutse ta gaisheshi kafin ta bashi hanya alamun ya wuce ciki. Bai shiga ba, sai kafa daya daya zura cikin dakin. Ya kai hannu ya kamo nata cikin nashi yana shafawa da dayan hannun a tausashe, kallon da yake mata na tausayi da rashin abin cewa yasa taji hawaye na alamun cika mata idanu. Ta dai yi kokari ta danne su.

Yace, "I'm sorry Nadiya! Kiyi hakuri na bace miki jiya ba tare da wani uziri ba, wani abu na gaggawa ne ya taso min kai tsaye. Kiyi hakuri!"

Ta girgiza kai tana kokarin kakaro murmushin yake wanda yaki fita daga bakin nata, murya a shake take ce mishi, "babu komi. It's okay ai."

Ya girgiza kai da sauri, "no, it's not! Ba ni da wani abin cewa wanda ya wuce kiyi hakuri dinne kawai, amma nasan ban kyauta ba!"

Sai kawai ta gyada kai, saboda babu wani abu a bakinta a lokacin.

Kallonta yake da wasu abubuwa a cikin idanunshi, ji yake kamar ya hadiyeta danyar ta. Amma ba lokaci, sauri yake yi saboda zaman da yake dashi da karfe tara.

Yace, "fatan dai babu matsalar komi ko? Akwai wani abu da kike bukata ko wanda bai yi miki ba?"

Ta dan daga kafada tana girgiza kai alamun babu.

Yace, "ok, good. Fita zanyi yanzun ana jirana, ki wuce sashen Ummah ki gaisheta sai ki karya ko? Idan da wani abu da zaki bukata in taho miki dashi kuma sai ki kirani ko ki tura min sako. Yayi?"

Tace, "to. Allah Ya kiyaye, Allah Ya dawo da ku lafiya!"

Yayi murmushi a hankali, fuskarshi na nuna alamun jin dadin addu'arta. "ameen ameen Nadiya, nagode."

Ya jata cikin jikinshi ya rungume tare da nutsa kanshi a gefen wuyanta inda wani daddadan kamshin humra da oil perfume ke fita. Ya jima yana shakar kamshin kafin ya saketa yana sakin wani dogon numfashi, ya yi dan murmushi ganin yadda tayi wani sak! ta kafe a waje daya kamar wata sakago. Yace, "kamshinki gwanin dadi Nadiya. Kamar dai mu dawwama dake a hakan."

Ya karasa fadin hakan yana kallon agogon dake daure a tsintsiyar hannunshi, lokaci yana kokarin kure mishi. Don haka ya manna mata sumba a goshi, ya juya baya yana daga mata hannu. "Sai na dawo, Love!"

Ya barta anan tana binshi da kallo. A ranta take ayyana, 'ta haka kuma wai yake cewa tayi hakuri? Bayan shi ne yake tura mata wadannan alamu da signals, daga baya kuma ya janye babu wani kwakkwaran dalili ko hujja?'

Ta sauke numfashi a hankali. Ta rufe dakin ta wuce sashin Hajiya Ummah.

Tayi sallama cikin falon daya gama daukar sanyin ac yana ta tashin kamshin turaren wuta da freshener.

Ammar da Hajiya Ummah ta hanga akan teburi suna cin abinci, don haka ta taka ta karasa wajensu.

Ta duka har kasa a kusa da kujerar da Hajiya Ummah take zaune, tace, "Ummah Ina kwana?"

Ta kalleta a kaikaice, ta amsa da, "lafiya!" fuska babu yabo babu fallasa. Tun anan sai taji jikinta yayi sanyi. Ta samu kanta da mamakin ko ina fara'a da kulawar dake tattare da ita a jiya suka nufa? Ta dai tashi ta fara kokarin jan kujera kusa da Ammar itama ta zauna.

"Nadiya!"

Hajiya Ummah ta ambaci sunan nata a kausashe. Sai ta dakata da abinda take yi ta amsa tare da juyawa tana kallonta.

Tace mata, "daga yau zaki dinga kirana da Hajiya Ummah ne, ko Hajiya. Not Ummah. Wannan sunan na wasu ne ba naki ba, kina ji na?"

Ta gyada kai a sanyaye kirjinta yana bugawa cikin fargaba da wani taraddadi. Me take nufi ne?

Ammar daya tashi ya rungumeta cikin murna shi ya katseta daga tunanin da taso fadawa, ta rungumeshi itama tana murmushi tare da amsa gaisuwar da yake yi mata.

Ta zauna itama tana jan plate tare da fara bude warmers da aka zuba abinci a ciki. Chips din dankalin turawa ta zuba da farfesun kaza. Ta zauna tana cin abincin a nutse tana kokarin jan Ammar da hira.

Bata jima da zama ba Rashida itama ta fito, ta duka ta gaidata tare da Hajiya Ummah, kafin itama ta zauna ta fara karin.

Ta kalli Ammar tace mishi, "lokacin tafiyarka makaranta fa ya wuce."

Don haka ya musu sallama ya tafi tunda ya gama cin abincin nashi.

Hajiya Ummah tana gama cin abincin ta tashi ta haye sama. Ita da Rashida jifa-jifa suke hira. Ta kula yarinyar tana da sanyin hali, kuma bata da yawan magana da zantuka barkatai.

Suma suna gamawa, mai aikin gidan ta fita ta kwashe kwanukan da suka yi amfani dasu, ta koma kicin.

Rashida itama ta koma dakinta, sai aka bar Nadiyar ita kadai zaune a falo tana kallon TV ba don tana jin dadinshi ba.

Wajen karfe goma kuma sai ga Shukurah ta shiga, kai tsaye ta wuce kan dinning abinta ba tare da ta kalli inda Nadiya take ba wadda take kokarin gaisheta.

Taje ta zuba abinda zata zuba, ta dauki kwanon ta dawo kan kujera ta zauna. Kai tsaye ta dauki remote control ta sauya tashar da Nadiya take kallo zuwa Boom TV.

Hakan bai dameta ba, bata kuma yi kasa a gwiwa ba ta sake juyawa ta kalleta ta gaisheta.

Ta wani sha kamshi, ta dauki fiye da sakan goma idanunta akan TV din kafin ta amsa da kyar kamar wadda ake tursasawa. Da Nadiya taga haka sai ta tabe baki, a ranta tace, 'kinyi da yar halak!'

Da dai taga zaman jugum-jugum din da suke yi ba zai musu ba, sai ta tashi ta koma sashenta.

Ta kira yan gida suka gaisa, har su Abba da su Anty Jamilah ta musu ban gajiya da yake a ranar suka koma gida don har sun karasa Kanon take ce mata tunda fitar safe suka yi.

Da ta gama wayar kuma sai tayi komawarta ta kwanta, cikin ikon Allah wannan karon barci ya dauketa mai nauyi. Ba ita ta tashi ba sai bayan Azzuhur.

Ta cigaba da zama a bangarenta bata fita ba, saboda taraddadin fitar take yi. Hajiya Ummah ta nufi wani bangare da Nadiya din bata fahimci ko ina bane balle ta san ta yadda zata iya ji da shi. Shukurah kuma bata bata fuskar zuwa inda take ba balle ta ce zata je wajenta hira.

Tana nan sai ga Rashida da Ammar sun je bangaren nata. Ta nuna jin dadinta da zuwansu sosai, suka zauna suna kallo da hira. Ganin ta fara jin yunwa sai ta tambayesu ko sun ci abinci? Suka ce 'a'ah'

Don haka ta shiga kicin ta fara dube-duben abinda zata samar musu. Store din akwai danyun kayan abinci sosai, haka freezer cike take da kayan miya har da danyen nama da kifi.

Ta ji ance garar da Yayunta suka hada mata ce aka ajiye a store dinta, babu laifi kuma gaskiya sunyi kokari sosai da sosai.

Ta fara daga bokitai da aka zuba mata dubulan da alkaki da nakiya ta deba ta kaiwa su Rashida. Kafin ta koma kicin ta ciro kayan miya ta fara grating.

Rashida ta shiga wai zata tayata, tace mata ta koma wajen Ammar su yi kallonsu kawai tunda ba wani aiki ne na a zo a gani ba take yi.

Macaroni ta dafa musu da sauce din kwai. Ta hada musu a kwano daya suka zauna a tsakiyar falonta suka ci suka yi nak. Ta wanke komi da tayi amfani dashi ta mayar inda yake, ta koma ta zauna suka cigaba da hirarsu.

Haka ta biye musu yadda kasan wasu sa'anninta suka yi ta wasa da raha har aka kira la'asar. Rashida ta tafi ta taya Ammar ya shirya ta tafi makaranta, ita kuma ta tafi tayi sallah.

Wajajen karfe biyar lokacin ta sake yin wanka ta yi wani shirin cikin jan leshi. Anty Lima ta kirata a waya, ta daga da murnarta saboda dazu da safe bata nan lokacin data kira su Madam, bata kuma kirata ba don haka basu gaisa ba.

Tace mata, "Nadiya kin ganmu nan a bakin gate an hana mu shigowa wai ba a san da zuwanmu ba!"

Tace, "kamar yaya? Baku fada musu wajena kuka zo ba?"

Tace, "mun fada ya fi cikin carbi, amma sun ce sai Hajiya ta kirasu da kanta ta fada musu sannan ne zasu barmu!"

Tace mata "to bari in zo!"

Ta zura takalmi ta fita bakin gate din da kanta, amma wadannan masu gadi suka yi kememe suka hanasu shiga. Ta cije lebe ranta a bace, don kuwa abin ya bata mata rai. Kai da bakinka Amma sai an maka katanga da su? Ta juya ta wuce sashen Hajiya Ummah da kanta.

Ta sameta a falo tana latse-latsen waya da gilashi a idanunta. Ta duka kusa da ita ta gaisheta kafin tace, "Ummah baki nayi a waje amma an hanasu shigowa saboda wai baki fadawa masu gadi ba."

Tace mata, "kwarai kuwa. Haka dokar gudannan take. Ba a shigowa sai an san da zuwan mutum. Idan kin san wani zai zo miki tun farko, ki dinga fada da wuri ne saboda a dinga sanar da masu tsaron."

Ta hadiye wani yawu daya kafe mata a wuya, wannan abin nema yake ya fara isarta kuma. An yiwa mutum iyaka da mijinshi, an mishi iyaka da sunan da zai ambaci mutum dashi, yan uwanshi ma sai an sanya shamaki a tsakaninsu ne?

Ta daure tayi kasa da murya, "to kiyi hakuri Ummah, bamu san da hakan ba amma zamu kiyaye nan gaba in shaa Allah. Don Allah ayi mana wannan uzirin."

Tayi shiru tana cigaba da latsa wayar ta kamar bata ji abinda Nadiyar tace ba. Sai can an kwashe wasu kyawawan mintuna hudu, kafin ta kara wayarta a kunne, ta bada umarnin a bar baki su shigo.

Nadiya ta runkufa tana mata godiya.

Tana kokarin tashi ta dakatar da ita, "ba ke na cewa ki daina kirana da Ummah ba Nadiya?"

Tayi kasa da kanta, tace, "kiyi hakuri."

Hannu kawai ta daga mata alamun zata iya tafiya. Ta juya ta fita cikin salubewar gwiwa.

A waje suka ci karo da Anty Lima, da Maryam da Fatima da kuma Iya Lami wata kanwar Dada da taje bikin.

Ta musu maraba sosai ta kai su bangarenta, bata bari damuwar fuskarta ta bayyana ba. Sai hakuri data basu akan zaman jira da suka sha, ta nuna musu cewa matsala ce aka samu saboda umarni da aka basu na hana baki shiga gidan sai da izini.

Ta kai musu ruwa da lemu suka sha, suka zauna anan falonta suna ta hirarsu ana dariya.

Sai da suka kebe a dakinta ita da Anty Lima sannan take nuna mata bacin ranta game da abinda ya faru. Tana mata korafin Anty Lima ta dakatar da ita ta hanyar dafa kafadarta.

Tace mata, "Nadiya, kada ki bari hakan ya bata miki rai ko yasa kiyi kasa a gwiwa. Su dama mutane kowa da tsarinsu, kuma kowa da irin halinshi. Dole zaki yi hakuri, ki bi dokokin da aka kafa miki don a samu zaman lafiya. Ni ina ga ma hakan yayi ai, kin san akwai mutane da dama da zasu yi ta zuwa gulma da kinibibi, amma ta haka kinga sai a samu saukinsu. Kawai daga yanzu duk wanda zai zo gidanki ya fada miki da wuri, sai ki sanar dasu. It's not a big deal Nadiya, kada ki bari hakan ya bata miki rai..."

Ta samu da kalami masu dadi ta tausheta har ta dan sauko. Ta kula hankalin nata ma ba a waje daya yake ba, amma bata takura mata da son sanin ko me ke damunta ba.

Sallame suka je yi mata, saboda dukansu washegari zasu wuce. Itama Anty Lima zata je ta fara shirin nata bikin ne da za ayi bayan sallah Babba.

Ta jido musu kayan kwalliya ta rarraba musu. Iya Lami kuma cikin kayanta da ba a kai ga dinkawa ba ta dauko atamfa super Holland guda biyu aka bata tare da Tatuwa, dayar dattijuwar da suka je bikin da ita.

Sai da suka yi sallar Magriba anan kafin suka tafi. Wannan karon ta musu rakiya har gaban motarsu. Anty Lima take mata rada a kunne, "wai ya bata ga tana tafiyar amare ba?" Tasan abinda take nufi sarai. Ta jefa mata harara a kaikaice ba tare data bata amsa ba, a gefe daya kuma a ranta take cewa 'amaryar da bata kwan da ango ba?!'

Bayan tafiyarsu ta juya ta koma sashenta inda ta bude Al-Qur'ani ta fara karantawa.

Zaman ya isheta haka nan ita kadai muku, don haka tana gama sallar isha'i ta wuce sashen Hajiya Ummah don cin abincin dare.

Su dukansu ta samesu suna cin abinci. Don haka itama ta bi sahunsu ta zauna. Jollop din taliya ce aka yi spaghetti da hadin salad. Da yake ma ba wata yunwa take ji ba, kuma dai ba ma'abociyar cin taliya bace musamman jollop, sai ta zuba kadan. Ta zuba salad din da yawa tana ci.

Hayaniyar Rashida da Ammar kadai take tashi a falon, sai Shukurah da ke taba Ummah da hira jifa-jifa.

Zuwa can sai ga shi shima ya shiga falon. Saye yake da wandon pants baki da farar rigar shirt. Ya wuce kai tsaye inda suke shima ya zauna, ya gaida Ummah ta amsa cikin kulawa, Rashida da Ammar da ita Nadiya kuma suka gaidashi kusan a lokaci daya, ya amsa hankalinshi akan Ammar.

Yana zama yar aiki taje zata zuba mishi abinci, Nadiya ta fuskanci kamar hakan al'adar gidan ce. Don itama Hajiya Ummah sai dai ta cewa yar aiki ta zuba mata abinda zata ci. Ya dakatar da ita alamun ta barshi, ya tsakuri taliyar shima ya zauna yana ci.

Zaman ya isheta, tuni abincin ya fita kanta. Ta kasa fahimtar abinda ke faruwa a wannan gida da kuma ma'anar abubuwan dake faruwa.

Babu jimawa ta tashi ta musu sai da safe ta wuce sashenta.

29.

Ranar ma haka ta kwana ita kadai. Washegari kuwa da basu ko hadu a wajen kari ba sai itama bata bi ta kanshi ba. Sai zuwa can da yamma ya lekata, da alama ma dawowarshi gidan kenan don yayi wani wujiga-wujiga dashi.

Da daren kuma ya sameta ita kadai akan dinning tana cin faten dankalin turawa da yaji hanta da naman kaza a ciki, ga hadin zobo a gefenta tana sha.

Ya ja kujera a kusa da ita ya zauna, kamshin turaren nan nashi yana ta kai mata karo. Yace, "kaji manya manya inji kanana, Hajiya Nadiya ikon Allah! Abinci ake ci?"

Tayi dan murmushi kawai wanda bai kai zuci ba, don kuwa bata so hirar ta su tayi tsayi. Haushinshi take ji wasa-wasa, bata son yin wani yunkuri kuma na nuna mishi abinda yake mata yana sukan zuciyarta. Abinda take ji a lokacin kuma, tasan cewa zata iya bare baki ta tambayeshi dalilin da yasa yake mata haka. Idan tayi hakan kuma ai tasan ta barar da kanta a gabanshi.

Yace, "to! Yau kuma yan sarautar ne a kusa kenan? To madallah. Fara da zuba min abinci dai yanzu."

Ta tashi babu musu ta zuba mishi abincin. Farar shinkafa ce aka yi da miya, sai kuma faten dankalin da lemun zobo, ga kuma shayi ga mai son hadawa.

Ya fara ci ka'in da na'in, kamar wanda yayi yini guda bai ci abinci ba. Ita ma tayi gaggawar kammala cinye na cikin kwanonta, ta tashi tana kokarin wucewa. Yayi saurin kallonta,

"a'ah! Ina zuwa kuma haka? Har kin gama cin abincin ne?"

Tace, "ehh, dama a koshe nake. Dakina zan wuce saboda kwanciya zan yi saboda na gaji da yawa."

Ya dan watsa mata hararar wasa, "aikin me kika yi ne haka da har za ki gaji? Zauna ki tayani hira please!"

Ta girgiza kai a hankali, "sorry, maybe next time!"

Kokarin daga baki yake yi don ya mayar mata da amsa, sai ga Ummah da Ammar suna saukowa kasa.

Ammar ya ruga wajen mahaifinshi ya rungumeshi yana murnar ganinshi, Hajiya Ummah kuma ta ja kujera ta zauna tana tambayarshi, 'har ya shigo?'

Ya amsa mata da 'ehh!' cike da girmamawa.

Nadiya tayi amfani da wannan dama ta silale ta koma dakinta abinta.

Ta fito daga wanka tana tsane jikinta, taji alamun an tura mata sako. Wai tambayarta yake yi, 'shine ta tafi ta kyaleshi bayan yace ta tsaya ko? Zai rama kuwa!'

Tayi kwafa tayi jifa da wayar ba tare data damu akan ta mayar mishi da amsa ba.

Ta gama shirinta tsaf na kwanciya ta kwanta abinta.

Washegari Rashida ta shirya zata koma gida saboda makaranta da suka koma. Nadiya bata ji dadin tafiyar tata ba, saboda yarinyar ita ce take dauke mata kewa ita da Ammar a gidan. Tana tunanin irin yanayin da zata shiga idan babu ita a yanzu. Saboda daga ganin take-taken Habibun, ba zata samu hakan a wajenshi ba.

Ta jata zuwa dakinta suka shiga wajen kayan kwalliyarta, tace mata ta zabi duk abinda take so a ciki. To da yake ma Nadiyar ta girmeta nesa ba kusa ba, kayan nata duk sun yiwa Rashidar yawa. Sai tarkacen janbaki da hoda

data bata da danginsu turare da humrori. Ta kuma dauko atamfa babba ta bata tace ta kaiwa Mamansu. Ta amsa tayi ta mata godiya.

Tace, "to kuma Rabi'ah sai zuwa yaushe?"

Yarinyar tayi yar dariya, tace, "to Aunty, kawai dai sai dai in ce sai na zagayo. Saboda gaskiya ban cika zuwa Kaduna ba sai ta kama."

Tace, "to ai shikenan. Idan ma ke din baki zo ba, mu sai mu je ai."

Rashida ta yada kai gefe, tace, "to Allah Yasa Ummah ta bari!"

Anan sai wani abu ya darsu a cikin ranta. Ta kama hannun Rashida suka zauna a gefen gado. Tace mata, "Rashida don Allah dan fahimtar da ni wani abu mana. Shin wai, menene alakarki da Baban Ammar? Kin ce min Yayanki ne, amma kuma ba mahaifiyarku daya ba. Kuma Babanku daya, sannan kuna kama. Ki fada min don Allah."

Rashida tayi kasa da kanta tana kokarin tauna abinda zai fita daga bakinta. Kafin ta kalli Nadiyar tana dan taune lebe alamun nervousness, "to amma dai ba zaki fadawa kowa ba ko?"

Ta gyada kai da sauri, "in Allah Ya yarda babu wanda zai ji."

Tace, "uhmm... Dama dai gaskiya Hajiya Ummah ba ita ta haifi Yaya ba fa, Mahaifiyarmu daya dashi. Ita kuma tana Makarfi ne a halin yanzu."

Ta kama baki cikin tsananin tu'ajjibi da mamaki, "wai kina nufin dama ba Hajiya Ummah ce mahaifiyar Habibu ba?!"

Ta gyada kai.

Sai Nadiya taji tana fahimtar wasu abubuwa da suka jima suna daure mata kai.

Alakar ta Hajiya Ummah da Habibu tsurar alaka ce ta 'Da da Mahaifiya ziryan. Ba ta tunanin akwai wani dalili da suka taba bata na tayi zargin akasin haka. Amma a yan kwanakin ta fara zargi da tambayar kanta, anya dai babu wata a kasa kuwa?

A ganinta, wata Uwa ce ta gari zata yi hani da danta tarawa da Matarshi ta Sunnah kawai saboda wani ra'ayi nata na daban? Anan sai ta samo amsar tambayar data dade tana mata yawo a ka, me yasa ne Hajiya Ummah din ta dage sai ta hada iri da Madam duk da daddadar gaba da kiyayyar da take a tsakaninsu? Ta jima tana zargin ba wai saboda a tallafawa Habibu a fannin siyasarshi bane kadai ya assassa aurensu ba.

Kada dai ace akwai wata magana ta daban dake faruwa a wannan lamari?

Ta tashi gwiwa a salube ta yiwa Rashida din rakiya zuwa inda direba yake jiranta zai mayar da ita.

Ita kadai ce a yan rakiyar, babu kyallin Hajiya Ummah balle na Shukurah. Shi dama Habibun tunda safe da zai fita ya damka mata kudaden da zata yi guziri da su. Ta samu kanta da tambayar, 'shin ko Shukurah ta san ko wacece ainihin mahaifiyar Habibun? Kuma a wane matsayi take a cikin wannan gida a halin yanzu?'

Ta yini cikin wannan tunani da saka da warwara. Da kyar ta iya tashi tayi sallah lokacin da aka kira Azzuhur. Barci ya dauketa anan, sai can wajen karfe uku ta tashi. Shima yunwa ce ta dinga nanikarta shi yasa ta tashi babu shiri.

Tayi tunanin ko taje bangaren Hajiya Ummah ne ta ci abincin acan kawai? Sai kuma ta canza shawara saboda bata san abinda suka dafa ba a ranar.

Ita kuma kayan kwadayi kawai take bukata saboda a yan kwanakin kwadayin take ji. Ta kula idan tana kusa da fara period tana yawan yin wadannan kwadaye-kwadaye kamar wata mai laulayi. Sau tari kuma sai ta haddasa mata kasala da yawan gajiya.

Ta samu ta lallaba ta fara yin sallah kafin ta fada kicin kai tsaye, ta lalubi fulawa ta hau kwabin wainar fulawa. Ta yanka su kabeji, cucumber, karas, albasa a ciki. Data tashi soyawa Kuna sai ta soya da manja.

Tana cikin aikin shi kuma ya fado kicin din. Ya shaki numfashi yana leka abinda take yi, "lalalaaa... Menene haka kike yi Nadiya, kuma ba zaki laluboni kiyi mun tayi ba?"

Ta dan juya ta na kallonshi. Sweat pant ne a jikinshi ash color da farar riga, da alama tun dawowarshi bai fita ba. Tace, "ni kuwa ina zan ganka da har zan yi maka tayi?"

Magana ce ta danna mishi a kaikaice. Ko ya fahimta ko bai fahimta ba? Ya basar da zancen ta hanyar ce mata,

"to ai ga ni nazo yanzu. Sai a zuba min in ci."

Ta kama baki da mamaki, "wainar fulawa ce fa?!"

Yace, "eh, ita din. Kin kuwa san yadda nake son wannan abin?"

Shi da kanshi ya dauko faranti, ya lalubi waje ya coge, duk wadda ta dauke a wuta sai ta zuba mishi ya lamushe abinshi, ga yajinta mai dadi da amarya ta daka mata yana dangwalawa.

Sai ga shi ita mai aikin ta tashi da yar kadan. Ta zauna itama ta ci bayan ta kammala, tana sauraronshi yana zuba mata santin wainar.

Ta hada kwanukan ta wanke, duk yana coge a kicin din ya ki matsawa ko nan da can. Data gama ta koma falonta, nan ma sai ya bi bayanta.

Ta lalubi kujera ta zauna tana canza tashar da ake haskawa a jikin TV.

Ba zato kawai sai jin mutum tayi ya kwanta a kan kujerar da take, kanshi akan cinyarta.

Tayi sauri ta zabura zata tashi, sai ya sanya hannu ya sakalo kugunta, ya nutsa kanshi a ruwan jikinta yana shaka da fesar da numfashi.

Tace, "wai meye hakan kake yi don Allah? Ka tada ni!"

Yace, "ni da jikina ma sai anyi min iyaka ne Nadiya?"

Tace, "ni dai gaskiya ka kyaleni, idan kwanciya zaka yi sai in bar maka wannan kujerar in koma karama."

Yace, "babu ruwanki da inda zan kwanta, nan din dai nayi niyar kwanciya. Bani minti ashirin kawai in dan runtsa, barci nake ji wallahi sosai da sosai!"

Ganin dai tsayawa ja-in-ja da shi ba zai mata ba, sai ta kyaleshi din. Ya gyara kwanciyarshi da kyau ya lumshe idanunshi kamar mai barcin da gaske. Ta ci gaba da kallonta, sai dai ta kasa tsayar da hankalinta waje daya ta fahimci abinda ake yi. Kusancinta da shi ya fara sanya mata wata kadawar jiki data 'ya'yan hanji data kasa fahimta.

Wayarshi ta hau kara a dai-dai wannan lokaci, Ya tashi a kasalance, da alama har barcin ya fara daukarshi. In da ba don Ummah bace mai kiran bama da zai daga ba saboda yaji dadin kwanciyar.

Ya daga kiran yana mai yin sallama. Kasancewar a kusa da Nadiya yake zaune, tana tsintar abinda Ummah din take ce mishi.

Wai tambayarshi take yi ina ya shiga ne tana ta nemanshi tun dazu, har sashenshi an je baya nan?

Yace, "Ummah Ina cikin gidan ai. Akwai wani abu ne?"

Tace, "ehh, kayi maza-maza kazo ina son yin magana da kai ne."

Yace, "to gani nan."

Ya kashe wayar ya mike da kyar yana kallon Nadiya, "bari in je Ummah tana son ganina."

Ta gyada mishi kai.

Yace, "idan kina da Groundnut paste ki dama min kunun gyada mana, zuwa dare zan zo in amsa."

Tace, "to bari in duba in gani."

Ya fita ita kuma ta shiga kicin.

Babu kullin a kicin dinta, sai ta yanke shawarar ta duba ko akwai a bangaren Hajiya Ummah tunda itama ma'abociyar shan kunun ce.

Bata samu kowa a falon ba, don haka ta wuce kicin. Ta samu Lailah mai dafa abinci tana ta aikin dafe-dafe, suka gaisa da ita ta tambayeta ko suna da kullin gyada zata yi kunu? Ta dauko mata shi a bokiti ta debi iyaka wanda zai isheta, ta koma sashenta.

Suka ci karo da Ammar ya dawo daga makaranta. Sai ta ja shi suka wuce sashenta. Ta tayashi ma yayi bitar karatunshi da assignment da aka basu, sai da aka kira Magriba sannan ya tafi.

Zuwa karfe takwas ta gama hada mishi kunun yadda ta saba hadawa.

Itama data samu ta shanye kofi daya, sai taji cikinta a cike. Don haka bata ma fita wajen cin abincin ba. Koda Lailah taje kiranta sai tace mata yau a koshe take.

Ta kwanta akan kujera two-seater tana chatting a wayarta. Karfe tara taje ta shige goma na shirin kawo kai, amma babu alamun Habibu.

Data gaji kawai sai ta tashi ta wuce daki ta kwanta.

Wani irin suya da juyi ranta yake mata. Wannan wace irin rayuwace wai take yi ne haka? Abu sai kace a almara ko tatsuniya? Abinda yafi bata mata rai shine yadda duk kokarin da take wajen ganin kada ta bari hakan ya dameta, amma kuma dai abin yana damunta.

Da Asubahi koda ta tashi yin sallah ta ga ta samu rashin tsarki, sai kawai ta kimtsa jikinta ta koma tayi kwanciyarta tunda dama barcin ba isarta yayi ba.

Wajen karfe goma ta fita zuwa bangaren Ummah. Bakar Abaya ce a jikinta, tayi nadi da gyalen a kanta. Wayarta a hannunta tana laluben kiran su Maryam don su gaisa ta fita daga sashen nata.

A bangaren Hajiya Ummah ta samu Shukurah akan dinning itama tana kari. Ta ja kujera ta zauna tare da gaisheta.

A yan kwanakin ta gama fahimtar ba lallai su yi zaman mutunta juna ba ita da Shukurah din. Ta dauke kanta kamar bata ganta ba, bata kuma amsa sallamar tata ba.Don haka itama bata kara gaisheta ba. Tana cikin zuba abinci kuma ta ga ta dauke plate dinta ta koma tsakiyar falo ta zauna. Haka yake faruwa duk lokacin da Nadiya ta sameta tana cin abinci, sai tashi ta koma falo. Idan kuma ita ta samu Nadiya din, to sai dai ta debi abincin ta tafi wani wajen ta ci, amma bata zama waje daya da ita.

Shi cin abincin ma a falon ta kula Shukurah din ce kadai take ci, saboda babu wanda Ummah take bari yayi mata wannan aika-aikar. Hatta da Ammar bata bari.

Nadiya ta tabe baki, ta zauna ta ci abincinta tayi nak.

Da taga ta gama Ummah bata sauko kasa ba, sai ita ta haya saman da kanta. Wannan shine karo na farko tun zuwanta gidan data hau saman.

Wani madaidaicin falon ta ci karo dashi da kujeru masu fadi irin na shan iska dinnan, a kasa kuma akan kafet Ummah ce a zaune ta mike kafafunta akan filo.

Nadiya ta durkusa a gabanta tana gaisheta, "Ina kwana Ummah? An tashi lafiya?"

Kullum ta Allah, bata fasa kiranta da Ummah din da bata so ba. Haka itama kullum ne sai ta gyara mata, tayi mamaki yau da bata taga mata ba. Ta amsa ciki-ciki kamar yadda ta saba.

Yanayin zaman nata sai ya ba Nadiya mamaki, tace, "Ummah ko baki jin dadi ne?"

Da kamar ba zata amsa ba, amma kuma sai tace mata, "lafiyata lau. Kafafuna ne suka dan motsa kawai."

Tace, "assha, sannu. Ya jikin? Kin sha magani? Ko kuma akwai na shafawa ne sai in shafa miki?"

Tace, "bar shi kawai kije kiyi karinki kinji?"

Tayi caraf tace, "ai yanzu na gama shirin. Idan akwai na shafawar kawo in shafa miki mana."

Ta nuna mata kwalbar maganin neurogesic, tace "ga shi nan."

Ta tashi da saurinta ta dauko maganin. Kafin ta shafa mata din sai data dauko ruwa a tasa da dan karamin towel, ta je ta goge mata kafafun tas kamar yadda taga Dada tana yi itama saboda tana da ciwon kafafu. Sannan ta bi ta shafesu da man wannan tas, ta kuma bi ta dinga massaging dinsu tun daga gwiwoyi har zuwa tafin kafarta.

Ta dauke kwanon ruwan ta shanya towel din, ta zubar da ruwan.

Komawa tayi tana tambayarta ko da akwai abinda take bukata kuma?

Tace mata 'babu komi'

Tace, "abinci fa? Kin karya ne?"

Tace mata, "na karya Nadiya, ki je kawai."

Tace "to, Allah Ya sawwake."

Ta tashi ta tasamma komawa kasa, sai kuma ta ji Ummah din na kiranta. Ta juya tana kallonta, tace, "ki dama min kunu a zuba a flask. Idan na sauko anjima sai in sha."

Ta amsa da "to"

Ta sauka kasa din ta shiga kicin, ta mata damun mai kyau da kauri. Na Habibun ma da yasa ta dama mishi ya ki zuwa ya dauka yana cikin flask. Data gama hadawa ta dauka da wasu kofuna biyu, ta kai wa Ummah din. Sannan ta wuce sashenta itama.

30.

Kwanaki uku suka zo suka shude a haka. Sai ga shi tana kirgan washegari Habibun zai fita daga dakinta, duk da cewa ba kwanan yake yi ba har yanzu. Kai a takaice ma rabon data sanya shi a kwayar idanunta tun ranar da yace ta dama mishi kunu bai koma ba. Ko a bangaren Hajiya Ummah ba sa haduwa, bata san ko arashi bane hakan ko kuma shi ne yake gudunta.

A daren kuma kamar da kiranye, sai ga shi ya diro dakin nata. Lokacin har ta gama shirin kwanciya ta kwanta amma ba ta kai ga fara yin barci ba.

Ya karasa har gefen gadonta ya zauna yana kallonta ta cikin dim light data kunna lokacin daya shiga dakin.

Yace, "har kin kwanta ne Nadiya?"

Ta gyada mishi kai ba tare data bashi amsa ba.

Yayi shiru din shima yana kallonta cikin wani yanayi da ta kasa fassarawa. A hankali ya kai hannu cikin tattausan gashin kanta daya kwanta har baya yana shafawa. Suka dauki lokaci mai tsayi a haka, cikinsu babu mai cewa wani abu.

Zuwa can kuma sai ya tattagota kamar wata karamar yarinya, ya zaunar da ita a tsakiyar gadon. Maganganu da yawa a cikin zuciyarshi, amma ya rasa da wane harshe zai iya furtasu. Idan ya daga bakin sai ya gaza cewa komi. Tausayinta da ma kanshi ya lullubeshi. Dalilin da yasa a duka yan kwanakin ya ma kasa zuwa inda take kenan balle ya nemeta. Kunyarta yake yi kwarai da gaske, ya rasa da wane ido zai kalleta, balle bakin da zai mata bayanin abinda ke faruwa.

Bai san dalilin Ummah na aikata hakan ba, amma shi kanshi dai yasan hakan bai dace ba, kuma yasan babu ta yadda za ayi ace Nadiya itama tana jin dadin hakan. Haka kawai saboda wani dalili na daban da ba shi da ruwa da tsaki akai, an yiwa kwanakin amarcinsu dirar fataken dare. Robbed, just like that!

Wani abu kamshin turaren jikinta ke haddasa mishi. Ga purple din rigar data sanya yau, gabadaya saman rigar net ne da kuma siririn hannu. Dan hasken daya rage a cikin dakin bai yi wani abu ba wajen boye kafatanin kirjinta.

Wani irin kallo ya koma yana watsa mata ba tare da yasan yana yin hakan ba.

Akwai lokuta da dama da yake rasa kalmomi a cikin bakinshi na neman afuwa ko uziri, a wadannan lokuta sai ya fi aikatawa da nunawa a jiki, cewa lallai yasan yayi laifi. A wannan lokacin kam, yasan cewa sai dai ya nuna mata a aikace. Wani aiki kuma yafi wanda yake kokarin nuna mata a halin yanzu?

Ya duka ya fara shinshinar wuyanta kamar wani tsohon puppy, kafin ya fara lasa da bin ko'ina na wuyanta zuwa fuskarta da ruwan kisses. Abubuwan da yake mata nema suke su dilmiyata a wata nahiya ta daban. Ta fara kokarin kwatar kanta, amma Habibun ya hana hakan ta faru.

Zuwa lokacin da tayi nasarar zamewa daga jikinshi da kyar, yar rigar tata da ta tsokane mishi ido an rabata biyu, ta zube akan cinyoyinta.

Idanu a lumshe cike da wata rigima da ta girmami tunaninta. Murya a dusashe yake ce mata, "why?!"

Itama tata muryar a shaken take, sai data hadiye miyau ta dan jika makoshinta sannan ta iya ce mishi, "fashin sallah nake."

Jin haka sai ya dora kanshi akan kafadarta ya lumshe idanu yana sakin numfashi a wahalce. Hakika da ba don wannan ba, bai ga abinda zai hanashi tabbatar da yiwuwar aurensu ba. Ummah sai dai tayi hakuri.

Sun kwashe fiye da mintuna sha biyar a haka kafin taga ya zame ya kwanta da kyau akan gadon.

Tayi zaune tana kallonshi a matukar tsorace. Ganin yanda take ta zare ido yasa ya kalleta yace, "me kike jira ne? Taho mu kwanta mana!"

Tayi jim kamar ba zata kwanta din ba, sai kuma ta lallaba ta gyara rigarta da aka wulakanta, ta kwanta itama, amma ta matsa can nesa dashi ta kuma bashi baya.

Babu wanda ya sake cewa dayansu uffan. Ita kam har barci ya daukeshi bata iya runtsawa ba. Sai zuwa can kafin barci barawo ya silale ya dauketa.

Da Asubahi tana jin motsinshi lokacin daya tashi zai wuce masallaci, har da gyara mata zaman bargo a jikinta. Ta kara gyara kwanciyarta abinta.

Ita kanta tasan cewa farincikin data tashi dashi na musamman ne ranar. Ko banza tasan cewa abinda take ta sakawa a cikin ranta ba haka bane. Habibu ya damu da ita, ko babu komi dai abinda ya faru a daren jiya hakan yake nuna mata.

Tayi kwalliyarta kamar yadda ta saba, kafin ta fita bangaren Hajiya Ummah don tayi kari. Yau ma sai data je har sama ta gaishe da Hajiya Ummah din, ta

kuma tambayeta ko yau ma zata bukaci kunu ta dama mata ne? Ciwon kafar tata yayi sauki cikin ikon Allah. A kwanakin da suka biyo baya kuma kullum Nadiya ta kan je bangaren nata ta dama mata kunu ta kai mata. Har sai da ita da kanta tace mata ta dakata, idan tana bukata za tayi mata magana. Ta amsa gaisuwar tata sama-sama, tace a'ah bata bukatar komi. Sai ta sauka ta koma kasa don tayi kari.

Suka yi karo da Shukurah ita kuma za ta hau sama din. Kokarin bangajeta taga tana yi, don haka tayi gaggawar matsawa gefe ta lafe a jikin bango gudun kada tayi abinda za a ce tayi. Amma duk da haka sai da Shukurah din ta gogeta da kafadarta.

Wai kuma maimakon ta amsa gaisuwar da Nadiyar take mata, sai ta watsa mata wani sakaren kallo. Murya cike da hargagi take ce mata, "ke ni kike bangajewa?!"

Ita abin ma sai yaso ya bata dariya, ta nuna kanta da dan allinta, "ni kuma? To ki yi hakuri. Ina ga ban kula bane."

Maimakon amsar tata ta gamsheta kuma sai ta kara tunzurata, ta wani kama kugu tana nuna Nadiyar da dan yatsanta, "an ki ayi hakurin kinji? Bani son iskanci da rashin mutunci fa kina ji na? Wallahi ba karamin aikina bane in sameki anan inyi ta jibga, kuma wallahi na daki banza! Sakarai kawai wadda miji yake gudunta tana manne mai!"

Daga farko abubuwan da take fadi dariya ma suka dinga ba Nadiya saboda taga rigima ce take nema da ita haka kawai ba tare da ta yi mata wani abu ba. Amma yanzu kuma da taji abinda ta fadi, sai taji wani irin bacin rai ya ziyarceta. Wato ashe dai duk abinda ke faruwa ana kula da su?

Ta gyara tsayuwarta da kyau don ma kada Shukurah din taga alamar raini a tattare da ita, tace, "ba da kashi dai kam wannan kin ci uwar raini wallahi, don kaf duniya ban ga wanda ya isa ya daga hannu ya dakeni ba yace wai ya ci a bilis! Wallahi ba a haifeshi ba tukun. Shi kuwa miji da kike wani gori a kanshi da babatu da daga jijiyar wuya, ban sa a ka ba, don haka bai dameni

ba. Ke din da ya dama har kike sanyawa rayuwar wasu ido, sai kije kiyi ta fama dashi!"

Kawai sai ta nufi Nadiya gadan-gadan, wai wallahi sai ta bata kashin tsiya taga shegen daya tsaye mata.

Ita kuwa ta kara gyara tsayuwarta tana jiran ko-ta-kwana. Don kuwa tasan a bugu dai, tsaf zata make Shukurah din ta barta anan. Ko a zubi da dirin halitta, ta ninka Shukurah din nesa ba kusa ba. Haka take yar yaloluwa da ita babu kiba sai tsayi, sai dai itama tana da nata zubi da dirin daidai-wa-daida. Kana ganinta kuma kasan ka ga yar gidan hutu. Irin sangartattun yaran masu kudin nan ne da suka tashi cikin kudi da wadata, suka kuma raina kurar data kwaso sauran mutane.

Gyaran muryar Ummah ne ya katse musu shagalin da suke yi, ta tsaya daga saman steps din bene tana kallonsu, "ku kuma lafiyarku, me yake faruwa ne?"

Nadiya ta daga baki za ta amsa mata, kawai sai Shukurah ta fashe da kuka. Ta ruga sama wajen Ummah ta rungumeta, wai fada mata take yi Nadiya ce ta bangajeta, kuma ma take cewa sai ta bata kashin tsiya.

Nadiya tayi saurin cewa, "wallahi Ummah karya take yi! Ita ce fa ta so bangajeni ma na matsa, amma kuma duk da hakan shine ta dinga zagina har da ce min banza."

Ummah ta kalleta fuska a hade, "wato zaman lafiya ne ba ki so ko? Haka kawai zata kama bangajeki da fadin maganganu ba tare da kin mata wani abu ba? Ai in bera da sata, to daddawa da warinta! Ke dai kika san me kika mata!"

Wasu hawayen takaici suka cika mata ido. Wannan fa shine a dakeka a hanaka kukan. Tace, "wallahi, wallahi Ummah ni ban san me na mata ba!"

Tace, "to tunda baki san me kika mata ba, da kika ga haka ba sai ki bata hakuri ba? Shukurah dai ta girmeki, anan gidan kuma matsayin babba take a wajenki. Dole ki bata girmanta yadda yakamata. Saboda haka nan gaba, kada ki kuskura inji abu makamancin hakan ya faru a tsakaninku. Kina ji na ko?"

Hawayen nata suka karasa dirowa kan kumatunta. Abu goma da ashirin ya mata rubdugu. Dannewa dai tayi ta gyada mata kai. Ta wuce ta fita daga wajen nasu jiki a sanyaye ko karyawa bata yi ba. Wannan tsagwaron rashin adalci har ina? Ga gaskiya kiri-kiri amma a danne don kawai ba a son mutum?

Haka ta koma sashenta tana ta wannan mitar a ranta. Sai da yunwa ta isheta ne sannan ta hada custard ta sha.

Da dare da kamar ba zata koma sashen na Ummah ba saboda har zuwa lokacin abinda ya faru dazun bata mata rai yake yi idan ta tuna. Ta dai daure ba don ranta ya so ba, ta tafi.

Tana kallon Shukurah akan dinning da ta sha kwalliya kamar zata je wajen gasar kyau, ita ala dole ga mai girki a ranar, ta ki gaisheta. Saboda dai ta mata magana ne ai har take binta da sharri ko? To babu kari. Nan gaba sai ta ga da abinda kuma zata kakaba mata wani abin.

Ta zuba abinci ta zauna tana ci, da wayarta a hannu tana chatting.

Data gama sai ta koma falo ta zauna tana kallo don ta rage dare. Ta shafa kan Ammar da yake faman yin assignment. Daga karshe ma sai ta buge da taya shi tunda taga yana kakarewa a wani wajen.

A haka gogan ya shiga ya samesu. Kai tsaye shima dinning din ya wuce ya zauna. Bata san ya aka yi ba, bayan wani dogon lokaci da ta kai kallonta wajen da yake, sai ta tsinci Shukurah kusan zaune akan cinyarshi. Tana ta wani kissa da abubuwa. Tayi saurin dauke kanta ta mayar gefe daya, tana kokarin dauke hankalin Ammar daga kallonsu don bata ga tsari a abin nasu ba.

Zuwa can kuma sai Shukurah din ta taso, ta wuceta tana wani taku dai-daya. Da taje dai-dai inda take sai ta juya tana ce mishi, "baby ina jiranka fa!" Ta karasa fita, takalmin kafarta yana 'kwaras-kwaras!' akan tiles din falon.

Ta kalli gogan ta ga ko waiwayenta bai yi ba, sai kawai ta girgiza kai abinta. Ta cigaba da taya Ammar da zanen gida da motoci da yake yi, don kuwa abin na Shukurah bai wani dadata da kasa ba.

Da ya gama cin abincin fita yayi daga sashen. Ita kam tana nan har sai da Ummah ta sauko kasa, ta gama cin abincinta ba tare da wata magana ta hadasu da ita ba bayan gaisuwar da ta mata.

Ammar da zai yi barci ta rakashi dakinshi da kanta, anan saman yake kusa da na Hajiya Ummah. Ta taimaka mishi ya wanke baki tare da canza kayan barci, ta mishi addu'ar kwanciya barci kafin ta sauka kasa. Ta yiwa Ummah sai da safe, ta koma sashenta itama tayi shirin barci.

Har karfe sha daya ta gota, lokacin shima ya gama tura wasu takardu can Kasar Indiya game da wani project da yake yi akan siyasa da kuma tsarkin muhalli, yana kokarin kwanciya sai ga kiran Ummah ya shiga wayarshi.

Wai tambayarshi take yi 'me ya hanashi zuwa dakin Shukurah?'

Yayi jim na wani lokaci mai dan tsayi. Ba ya so maganganu irin haka na ratsawa a tsakaninsu, shi yasa tun farko bai tsaya yin wani dogon jayayya da ita ba a game da hukuncin data zartar a tsakaninshi da Nadiya.

Yana da alkunya da girmamawa ga duk wani wanda zai mu'amalanta. Personal zance irin wannan ba da kowa yake yi ba.

Dalili kenan da yasa bai taba daga baki ya kai mata karar Shukurah ba, wadda ta maida kwanciyar aure da shi wani kasuwanci na musamman. Ba ta ba shi hakkinshi har sai ta san da akwai wani abu da zata samu a gareshi ko wata bukatarta ta kanta da zata biya sannan. Wai a hakanma kuma ba koda yaushe ba, ba kuma zama za tayi ta tarairayeshi ba kamar yadda yake so. Sai dai kawai ta mishi kim, ya gama kidanshi da rawarshi ya kara gaba. A hakanma sa'a ce ya ci idan bata ce mishi ta gaji ba ta tashi ta barshi.

Duk wannan abu, bai taba daga baki koda sau daya ya furtawa Hajiya Ummah ko wani na kusa da shi ba. Saboda a ganinshi zance irin haka yayi tsauri da nauyi a tsakaninshi da Ummah din. Amma sai yaga kuma ita tana nuna hakan ba komi bane a wajenta.

Duk da hakan, sai ya daga baki yace, "Ummah ita me ya hanata zuwa?"

Tace, "ka rufe min baki anan, bana son wata doguwar magana. Iyalinka ce ai, ita in bata zo inda kake ba kai sai ka je gareta ai. Ko baka san mata yan lallashi bane? Tana ganin yadda kayi mata kishiya dama ai dole ta ja baya da kai, kai ne zaka yi kokari har ka ja ta a jikinka!"

Yana so ya tambayeta, 'to ita kuma Nadiya ba Iyalina bace kenan da kike umartata da in gujeta?!' amma sai ya kame bakinshi.

Yace mata, "kiyi hakuri Ummah. Zan tafi yanzu in shaa Allah."

Tace, "yauwa!" tare da kashe wayar abinta.

Yayi jim zaune a gefen gado cikin zuzzurfan tunani. Bai manta abinda Shukurah din ta mishi ba kwanaki, shi yasa shima yayi niyar shareta. Tunda dai dama ba wani abu yake mata ba, haka itama ba wani abin kirkin take tsinana mishi ba.

Shi kanshi yayi mamakin tarairayar data dinga mishi dazu, sai da yayi tsam da ranshi sannan ya fahimci saboda ganin idon Nadiya ne take yin hakan. To ina amfanin abinda ba don yaji dadi aka yi ba sai don a kuntatawa wani?

Har ga Allah Ya so ace Ummah bata shiga cikin zancen ba. Don kuwa ya sha alwashin shi da Shukurah dai, sai dai idan ita ta je gareshi. Amma ba dai ya kai kanshi gareta ba.

Da kyar ya iya tashi ya wuce bangaren nata.

Wannan fita da yayi karaf a idon Nadiya kamar an ce ta daga kanta. Da yake tagar kicin dinta tana fuskantar bangaren Shukurah din da na Hajiya

Ummah. Tana kallo ya bude kofar dakin ya shige. Tayi kwafa rai na suya. To! Ashe dai da gasken gudunta yake yi?

Shi kuwa Asubahin fari ya bar wajen. Bayan mita da yada kananun maganganu babu abinda ya tsinta a wajen Shukurah din. Ita ala dole ya ci zalinta tunda ya mata kishiya. Daga baya kuma ta koma nuna mishi tasan dai baya kwana tare da amarya har yanzu, idan ya yarda tafiyar tasu ta dore to zai iya duk abinda ya ga dama da ita. Wato dai har yanzu tana kan bakanta.

Ya kalleta a wulakance, yace, "me kike yi min ne wai? Me kuma kike bani wanda ba sai kin wulakanta ni ba? In dai don wannan ne, ki rike kayanki. Ki kwadashi kiyi duk abinda kika ga zaki iya Shukurah! Ba na so!"

Sai ta fashe mishi da kuka. Shi kuwa ya juya mata baya ya kyaleta tayi ta gama.

31.

Zuwan su Amarya ganin daki washegari shi ya dauke mata damuwa da ta kwana da ita. Don kuwa barci gagararta yayi a daren daya gabata. Ta kwana tana tunani da tambayar kanta, wai shin menene matsalar? Kuma ta ina za ta tattago wannan al'amari?

Suka mata yini guda ita da sauran yaran gidan da suka je. Amarya sai binta take da kallo tana murmushi, ce mata take yi tana karawa, 'ai lallai wannan amarci ya karbeta!' Nadiya dai dariya kawai take binta da ita. Sai zuwa can yamma suka shirya tafiya, da suka je yiwa Hajiya Ummah bankwana, haka ta musu sha tara ta arziki, ta kuma hadasu da direba tace ya mayarsu gida.

Amarya ta ja Nadiya gefe tana kara mata nasihar lallai ta kama Surukarta hannu bi-biyu, ta mata biyayya ta girmamata. Tunda tana sonta, itama ta kaunaceta don Allah. Nadiya ta yi shiru ita dai tana jinta, don kuwa bata tunanin shawarar da zata cigaba da bata kenan idan taji abinda ke faruwa a gidan. A haka dai direba ya ja su suka tafi tana daga musu hannu.

Da dare suka hadu da mutumin nata a wajen cin abinci, kasa ko daga ido ta kalleshi tayi a lokacin saboda tsabar yadda yake bata haushi. Ita kanta bata san tana da irin wannan kishin ba sai a yanzu. A da gani take yi ita Allah bai dora mata wannan abun ba, a da, gani take yi koda Allah zai sa ta shiga yanayi kamar wannan to ba zata taba damuwa ba. A yanzu kuma sai ga shi labari ya sha bambam. Kishin Habibun take ji yana nanikarta har a cikin kokon kanta, ta kasa daga ido ta kalleshi daga shi har Shukurah din saboda dukansu haushinsu ma take ji.

Ta gaisheshi a kaikaice, da ya zauna a kujerar kusa da ita kuma sai ta juya mishi baya. Ta dinga tura abincin ma da kyar saboda ji tayi cikinta ma ya cushe gabadaya.

Ai tana gamawa ta musu sai da safe ta tsere sashenta.

Abin daren jiya bata samu barci da yawa ba, tana kwanciya cikin ikon Allah sai barcin yayi awon gaba da ita. Shi yasa sanda ya bi sahunta ya buga mata kofar falo bata ji ba, waya kuma da yake a silent ta sanyata ko da ya kira bata ji ba.

Washegari shima tunda farar safiya ya bar gidan don haka basu hadu ba. Ita dadin hakan ma ta ji. Don kuwa duk da bata ga shigarshi bangaren Shukurah ba jiya, amma zuciya da sake-sake haka suka dinga auna mata ai a can dinma ya kwana. Yau ma haka ta tashi rai a cunkushe.

Taje ta gaida Hajiya Ummah wadda itama ta sameta tana shiri da alama dai fita zata yi. Shayi kadai ta iya hadawa mai dan kauri ta sha, ta wuce dakinta.

Kasancewar ranar Public Holiday ce, Ammar bai je makaranta ba. Sai Ummah ta fita da shi. Gida ya rage daga ita sai Shukurah kadai.

Wajajen karfe sha daya ta shiga kicin da niyar dora abinci saboda yunwar data fara nanikarta. Ta samu shinkafarta ta barza, ta dora rigana ta hau aikin dambun shinkafa.

Nan da nan gidan ya kacame da kamshi mai dadi. Kafin ta gama kuma sai ta dora farfesun kaji. Aikin da dan yawa tayi saboda yau ta kudurta har Ummah za ta kaiwa abincin. Ta ga abinda zata ce mata kafin kuma daga nan taga ko idan za ta cigaba da kai mata.

Da ta sauke dambun ta zuba cikin mazubai masu kyau guda biyu, sai ta bar farfesun under low heat don ya karasa dahuwa. Kunun ayar data hada kuma ta sanya a cikin firjin don ya kara sanyi kafin ta tashi sha.

Ta wuce dakinta ta fara watsa ruwa kafin ta dauro alwala ta je tayi sallar Azzuhur.

Tana tahiyar karshe taji alamun an bude kofa an shiga dakin tare da maidawa aka rufe. Kafin ta fara mamakin ko wanene kamshinshi ya bayyanashi.

Ta sallame sallar ta zauna tayi tasbihai da ladubban da take gudanarwa a duk sallar da ta yi. Ta mike tsaye tana nade abin sallar hannunta tana kallonshi yana zaune ta gefen gadonta yana latsa wayarshi. Tayi tsaye bayan nan tana kallonshi ba tare data cire doguwar hijabin jikinta ba. Don kuwa bayan wankan da tayi bata maida wasu kayan kirki jikinta ba. Karamar rigar shan iska ce a jikinta da bata gama rufe mata cinyoyinta ba, sai ta dora zani a kai. Ganin ita kadai ce a sashen nata ba wani yake je mata ba.

Ya bita da kallo tun daga sama har kasa yana lura da yadda take kaucewa hada ido da shi.

Yace, "wai ni wannan shan mur din da ake mun na menene? Na lura tun jiya kina wani jin haushina da kin yi mun magana. Akwai abinda na miki da ban sani ba ne?"

Ta dan tabe baki tana kallon can gefe daya, "ni kuwa me kayi mun? Yaushe ma muka hadu da kai da har za kayi mun abinda raina ba zai so ba?!"

Yayi murmushi yana kallonta kamar abinda tace din dadada mishi rai yake yi, yace, "to idan haka ne, zo nan ki zauna kiji wani abu."

Ya fadi hakan yana daddabar kusa da shi alamun nan za ta zauna.

Tayi tsaye cak tana kallonshi ta ki motsawa, maimakon ta je din sai tace mishi, "abinci nake son ci idan hakan babu damuwa."

Ba shi take kallo ba, shi yasa bata ma san lokacin daya tashi daga inda yake ba har ya karasa gabanta. Sai data ganshi gab da ita sannan tayi kokarin juyawa, ya kama gefen hijabin nata ya rike gam, ya hanata matsawa ko nan da can.

Yace, "to wai me yasa ne idan zaki yi magana ba za ki kalleni ba Nadiya? Kuma na tambayeki kin ce wai ba kya fushi da ni? A haka kike so in yarda dake?"

Kokarin ya sake mata hijabi take yi, "to tunda nace babu wani abu ka kyaleni mana! Nace maka yunwa nake ji!"

Ji tayi kawai ya zame mata hijabin ya yar, ta daga hannu a sukwane ta kare kirjinta tana kokarin durkusawa kasa. Ya sanya hannu ya jata cikin jikinshi ya rukunkume. Kanshi a cikin gashinta yake ce mata, "know what? Nima yunwar nake ji Nadiya, amma daga ni har ke yau ba zamu bar dakin wannan ba har sai kin fada min abinda na miki sannan!"

Ganin babu Sarki sai Allah yasa ta sauko daga tsinin data hau ba shiri, ta hau magiya da kankan da kai. "Na rantse da Allah babu abinda ka min. Ka wa girman Allah ka kyaleni, don Allah. Yau fa ranar girkin Anty Shukurah ne ko ka manta?!"

Ya kai hannu bayan wuyanta yana shafawa zuwa gadon bayanta, wasu abubuwa suka fara mata yawo a jiki da jijiyoyi. Jikin nata gabadaya sai ya dauki wata irin rawa kamar wadda lantarki take ja.

Idanunshi a rufe, tunaninshi da kwalwarshi ba lokaci daya suke tafiya ba, shi yasa ma ya fara rasa zaren tunaninshi gabadaya. Wasu abubuwan yi yake, amma shi kanshi ya fara rasa sanin abinda yake aikatawa din. Sunbatarta yake, shafata yake, komi ma yi mata yake, amma duk da haka ji yake yi it's not enough.

Cikin hakan yake ce mata, "kin manta cewa ku dukanku da zarar an gama karin safe shikenan kun gama fita daga girki? Yanzu kuwa lokacin Azzuhur ya shiga Nadiya, lokacinki ne. Don haka ki barni in fanshe takaicin kwanakin da na rasa na amarcina!"

Maganar tashi ta so ta bata haushi ma, ta bude baki tace, "to ni na hanaka cin amarcin? Ko kuma ni ce na sabbaba maka hakan?"

Sai ya dakata, ya kalleta da kyau da murmushi akan fatar bakinshi, "ai dama nace hakan yana damunki amma kika ce ba haka ba. Ana son mutum amma ana kaiwa kasuwa! Nadiya wannan hali naki sai ke. Amma dai a hakan kike burgeni."

Ya juyata ta fuskanci gado, kafin ta ankare sai ta tsinceta tsamo-tsamo akan gadon shi kuma ya bi ta yayi mata rumfa.

Abubuwan nashi neman wuce gona da iri suke, tuni sai ta hau magiya da neman hanyar tsira. Fadi take tana karawa, "don Allah don Annabi ka taimaka min kayi hakuri ka kyaleni. Wallahi Tallahi yunwa nake ji!"

Yace, "ai mai rabani da ke yau Nadiya, sai ikon Allah. Ko kin yi zaton jiya ban ga irin hararar da kika dinga auna min bane? Kuma nasan duk cikin jin haushin rashin kwana a dakinki ne, don haka yau dai sai na wanke kaina a wajenki tas!"

Sai hawaye shar! sharr!! Suka hau zarya a fuskarta, tace, "ka rufa min asiri, don Allah kayi hakuri. Wallahi ni ban harareka ba, in ma na harareka din cikin rashin sanine, don Allah kayi hakuri Abban Ammar!"

Tana ta magiyarta da neman hanyar guduwa shi tuni ya gama yin nisa a al'amuranshi. Yace, "kin ji ma Abban Ammar kike ce min kai tsaye, ba Angon Nadiya ba! Ai wallahi yau dai sai na amsa sunan nan!"

Daga wannan magana bai kara bata damar yin wata maganar ba, ya kara zafafa al'amuran nashi a gareta.

Da ta samu ya saki bakinta daya damka da nashi cikin yanayi na fitar hayyaci, sai ta bare baki ta hau kwala mishi ihu. Da taga abin ba kanta sai ta fara hadawa da bugu. Abin dai nashi yaki raguwa sai ma kara kaimi da yake. Idanunta suka gama raina fata, ta saki wani irin kuka mai cike da tashin hankali da wata azaba ta musamman da taji tana ratsata.

Sai ga ta ta hau kiran su Madam da Mama, a je a ceceta Habibu zai kasheta. Shi ai bai ma san kalar wainar da take toyawa ba.

Ta yi Ala-wadai da yarda da maganganun Anty Lima da tayi, da take ce mata wai ai idan budurwa ta jima bata yi aure ba fatar budircinta na budewa ne ta yadda ba zata ji zafi ba sosai a first night dinta. Ashe duk kanzon kuregene? Ita kuma ta hau kan magana ta zauna daram, a ganinta bulis zata ci. Ashe Habibu shi zai kwashi bagas! Gashi nan yanzu yana bambance mata tsakanin aya da tsakuwa.

Lokacin da yaji shi da kanshi yana neman wuce makadi da rawa, ya dakata, saboda tausayawa irin halin da yaga ta shiga ne na galabaita.

Ya lumshe idanu wani irin murmushi mai tattare da sanyi da salamar jiki data zuciya daya dade bai samu a tattare da shi ba kwance akan fuskarshi. A haka barci ya daukeshi mai nauyi. Ita kanta tana ta jan shessheka da auna mishi harara barcin yayi awon gaba da ita bata ankara ba.

Kiran sallar la'asar ya katse mishi barcin, ya tashi da sauri yana duba agogo. Allah Ya taimakeshi ranar baya da wani abu mai muhimmanci da yammacin, da lallai ya makara.

Ya juya yana kallon yadda ta kanannade a cikin bargo ta rufa gabadayanta, fuskarta ce kadai a waje. Barci take a nutse tana sakin ajiyar zuciya akai-akai. Ga sawun hawaye nan a fuskarta da suka bushe.

Yayi murmushi a tausashe yana girgiza kai, tunano irin rigimar daya san za su kwasa idan ta tashi. Ya lallaba ya shiga bayi cikin taka-tsantsan din kada ya tasheta. A gurguje yayi abinda zai yi ya fita.

Lema-lema da sanyin ruwa da ta dinga ji a fuskarta ya sanya ta fara bude idanunta a hankali da suka yi mata nauyi.

Suka yi face-to-face da shi, ya duka a kasan gadon yana kallonta.

Wata irin kwalla ta ciko mata ido a take, ta mele baki da fuska tana shirin fara kuka, yayi saurin tashi tsaye yana kokarin boye dariyar data ciwo shi. Yace mata, "Masallaci zan je. Ga ruwa can a bayi na hada miki kiyi sauri ki yi wanka kafin ya huce."

Ya bar dakin cikin sauri kafin ta kai ga mayar mishi da amsa.

Sai data jima tana kara jinjina abinda ya faru a cikin ranta kafin ta tashi a hankali, ta lallaba da kyar ta shiga bandakin.

Ta fito tayi sallah ta gama. Yunwa take ji matuka har wani jiri-jiri take gani. Ta samu riga doguwa marar nauyi ta sanya. Ta fita falon tana jin jikinta babu karfi ko kadan. Tafiyar kanta sai take nema ta zame mata wani aiki na daban.

Sai ta sameshi already a falon, ya zuba dambun nan cike da faranti da farfesun kazar nan a gabanshi yana ta aikin durawa a ciki babu kakkautawa.

Haushinshi kifi da kifi ya lullubeta. Ji tayi kamar ta kwace kwanon hannunshi ta hanashi cin abincin. Ta dai daurewa ranta bata aikata hakan ba, ta wuce kicin itama. Yace mata, "zo nan mu ci wannan da na zuba mana? Idan mun cinye sai ki karo."

Tayi kunnen uwar shegu dashi.

Anan cikin kicin din ta zauna ta ci kayanta don tsakaninta da Allah ko ganinshi ma bata son yi.

Tana cikin cin abincin ya shiga da empty plates, ya ajiyesu a cikin sink. Ya daga firjin ya tsiyaya kunun aya ya kafa kai yana sha har da wani lumshe idanu. Harara kawai take jefa mishi, karaf suka hada ido da shi lokacin daya juya.

Yayi murmushi yana ajiye kofin hannunshi, "wato harara ta ma kike yi ko? Lallai ma ashe ban gama goge rainin da kika yi mun ba har yanzu. Da alama ina da sauran aiki kenan."

Ganin yana nufarta gadan-gadan sai ta mike tsaye sukwane tana shirin tserewa. Shi kuwa me zai yi in ba dariya ba?

Yace, "farar kura! Ga tsoro ga ban tsoro. Dawo ki ci abincinki babu abinda zan miki. Lokacin da zan damkeki a hannuna Allah na tuba ai you wouldn't even see it coming. Besides, ke din ai amaryace da bata laifi. Don kin harareni ai ba wani abu bane!"

Ta koma ta zauna din a darare, amma ta kasa sakin jiki ta ci abincin yadda ya kamata. Saboda ya sanyata a gaba yayi kikam, sai taji duk ta takura.

Ta kalleshi a kaikaice tace mishi, "ni fa gaskiya ban cika son ina cin abinci ba ana kallona. Ai sai ka sa in shake!"

Bai ce mata komi ba, taga yayi hanyar fita kamar tafiyar zai yi. Kafin ta sakankance ta ji ta a cikin jikinshi ya rungumota ta baya.

Ya lalubi kunnenta yana rada mata, "madallah da ke Nadiya. You've made my day! Allah Yayi miki albarka, Allah Yasa munyi dacen samun yan biyu..." da wasu zantukan da suka yiwa kunnuwan nata nauyin ji.

Ita dai tayi turus a zaune tana sauraronshi har ya gama fadin abinda zai fada, ya juya ya fita yana fada mata wajen tafsir da ake yi na yammaci a Masallacin dake makale da gidansu zai je.

Ita dai bata samu sakewa ba sai data ji da gaske din ya fita, sannan ta saki ajiyar zuciya. Ta zauna ta ci abincin sosai da sosai.

Data gama ta hade kwanukan ta wankesu duka. Sauran dambun da suka rage kuma ta barshi a cikin kular tunda dama ba wani na azo a gani ne tayi ba, wanda za ta ci da wanda zata kaiwa Ummah kawai ne. To kuma ga shi Habibun nata ya bi ta kanshi.

Sauran yammacin ranar a kwance tayi shi tana jinyar jikinta. Don kuwa sai a lokacin ma take gane kalar ta'asar da Habibun yayi mata ashe ba karama bace. Ko motsin kirki tayi sai taji a jikinta.

Sai can wajen Magriba sannan taji dawowar Ummah. Amma bata shiga bangaren nata ba sai da aka yi sallar isha'i.

Data shiga tayi mata barka da zuwa, sai ta ja Ammar gefe suka zauna tana tayashi yin assignment kamar yanda ta saba. Ta kula yaron yana da rauni sosai ta bangaren lissafi, haka kuma fannin addini ma yana da mas'aloli da dama. Ganin kuma babu wani tsayayye dake bibiyar lamuran makarantar tashi yasa ita ta azawa kanta wannan nauyin. Tana taimaka mishi da spelling, da kira'a, har ma da haddar abubuwan da ake yi musu a duka Islamiya da makarantar boko. Da suka gama suka cigaba da kallon Fina-finan yara da ake nunawa a tashar Mbc 3.

Kasancewar cikinta a cike yake tun bayan dambun da ta ci, bata ma tunkari teburin cin abincin ba.

Tana nan Shukurah itama ta shiga falon, ta zauna a dan nesa dasu kusa da Hajiya Ummah. Magana take mata kasa-kasa duk don kada Nadiya din taji me suke cewa, ta tabe baki a kaikaice ta kara dauke kanta daga garesu don kuwa itama ba son jin abinda suke cewa take yi ba.

Kamar ba zata gaisheta ba, daga karshe dai ta daga baki da kyar ta gaidata din, itama ta amsa a fuzge kamar wadda aka takurawa. Tasan ganin idon Ummah ne yasa ma ta amsa.

Wajajen karfe tara ta musu sai da safe ta koma bangarenta. Sauran farfesun data rage ta cinye da kunun aya. Ta shiga bayi ta watsa ruwa kafin tayi shirin barci cikin pyjamas masu dan nauyi pink masu digon fari a jiki. Hadari ne a garin sosai ta san ba dadewa ruwa zai sauka.

Sai da taje ta kulle sashenta kafin ta kwanta saboda kada Habibu ya mamayeta irin na dazu.

Ila kuwa tana kwanciya ba jimawa, aka tsage da ruwa kamar da bakin kwarya. Ta kara shigewa cikin bargo barci mai dadi yayi awon gaba da ita.

Kamar cikin mafarki kuma ta dinga jin wani abu na faruwa da jikinta. Ta fara bude idanu cike da magagin barci, tana kokarin fahimtar me ke faruwa.

Fahimtar da tayi mutum ne kwance kusa da ita yana mata wasu abubuwa yasa tayi baya tana kare jikinta da sai lokacin ta fahimci ashe babu kaya a jiki.

Ya kai hannu yana kokarin kamota, ta fashe da kuka tun karfinta. Ita ta ma rasa ta yadda aka yi har ya bude dakin nata ya shiga.

Tace, "kasan Allah ka tashi ka fita ka kyaleni. Haba wannan wane irin abu ne haka? Ba za a bar mutum ya huta bane?"

Kallonta yake yi kasa-kasa, "Nadiya dama akwai hutu a cikin rayuwar aure ne?"

Tace, "ban sani ba! Ni dai wallahi ko ka fitar min anan, ko ni in fita. Amma wallahi ba zan iya ba!"

Ganin yadda ta hakikance tana kuka bilhakki, yasa ya dauki kayanta ya mika mata, yace, "to naji, shikenan. Yi hakuri ki daina kukan."

Ta amsa cikin sauri ta sanya, ta tsaya tana kallonshi cikin alamun rashin yarda.

Ya kwanta tare da tapping din kusa da shi, yace, "taho ki kwanta kin ji? I promise babu abinda zan miki. For now."

Duk da haka dai kasa yarda dashi tayi din. Shi kuwa ganin haka sai ya juya mata baya yayi kwanciyarshi.

Ita kam sai da ta jima sosai a hakan, ta tabbatar da yayi barcin sannan ta silala kamar barauniya ta kwanta. Gunaguni take yi kasa-kasa, duk bata san lamo yayi mata ba sai da Asubahi tayi yaje yayi sallah ya dawo. Yayi ram da ita yana neman sake maimaita yar gidan jiya. Ta hau magiya da rokon ya daga mata kafa, yace, "a'ah, ba kin ce na dameki da kwarzaba da bita zaizai ba? Ai baki ga komi ba ma Nadiya, don kuwa ko farawa ma ban yi ba."

Tace, "to kayi hakuri ka bari in gama warkewa tukun. Wallahi bana jin dadi ko kadan."

Yace mata, "muna da magunguna ai a gidan."

Bai kuma kara barin ta furta wani abu ba sai daya karasa gudanar da abinda ya kudurta sannan.

32.

Cikin yan kwanakin amarcinsu suke ci ka-in da na-in, ko kuwa tace Habibu amarcinshi yake ci babu kakkautawa. Don kuwa tana ganin kwarzaba da bita-zai-zai din da yace mata zata gani, sai daya zamana har bata son girkinta ya juyo kanta ko kadan. Idan kuwa ta ganshi har wani faduwar gaba take ji tana ziyartarta.

Babu yadda baya yi da ita akan ta saki jiki, amma wannan din ya gagareta.

Wannan sabon kusancin da suka yi yasa ta kara fahimtar ainihin wanene Habibu Abdullahi Makama, Babangidan Hajiya Ummah.

Bawa ne ga duk abinda yake so da kauna, mai fahimta ga abinda baya ma kauna. Yana da kyautatawa da son kyauta ba kuma don a gani a yaba ba. Ga matanshi da Iyalanshi, mutum ne mai taka-tsantsan da gudun bacin ransu. Mutum ne mai saka alkhairi da alkhairi, sharri ma a wajen Habibu da alkhairin yake maidashi. Bakin kokarinshi yana yi don ganin ya kyautata musu, yana musu uziri a duk al'amuransu, haka yana da fahimta. Lokuta da dama idan suna tare da Nadiya ya kan maida kanshi kamar wani karamin yaro ne ko matashi, baya da girman kai kuma baya cikin mutane masu amfani da ikon dake kansu don su hanawa matansu motsin kirki. Abu daya da Nadiya ta fahimta a tare da shi shine wannan abu daya da bata so, zai iya hakuri akan komi ma, zai kuma yi uziri da fahimta, amma fa yau yace mata zo gyara shimfida tace a'a, anan ne kam take ganin rashin uziri da fahimta. Don kuwa baya mata wannan hakurin.

Shi yasa ma wani lokacin sauran kawaicin nashi baya burgeta.

Haka tsananin biyayyar da yake yiwa Ummah wani lokacin har tsoro take bawa Nadiya, saboda baya taba iya ce mata a'ah a duk wani umarni da zata bashi. Haka yana matukar kambama abubuwanta da yin taka tsantsan wajen gudun bacin ranta. Tana lura da yadda yake ta boye-boye da kokarin kada abinda ke tsakaninsu ya bayyana a wajen Ummah din. Saboda da aka kwana biyu ma sai ya zamana baya shiga bangarenta ranar girkinta sai can cikin dare ko kuma tunda Asubahi. Sai dai a ranta tasan da kyar idan Ummah bata

gama ramfoshi ba a yadda dai idanunta suke a kansu a kodayaushe kamar wata mikiya.

Tun karon farko daya fita daga dakin Shukurah ya koma nata, ya sameta da rana a bangarenta da zancen ta bashi abincin rana. Ta kalli plate kwaya daya tal da ta yi roasted macaroni don ta ci, tace mishi bata dafa da shi ba.

Ya dauke plate din tana kallonshi ya tadashi a gabanta, ya gama ya kora da ruwa ya tashi tana kallonta, yace, "banda ma rashin kara irin naki, ranar girkin naki ma sai na dinga rokonki da barar kiyi mun abinci kenan? Idan kin ga dama ma gobe kada ki sa girkin da ni!" ya fita ya barta anan.

Tun daga nan ita kuma ta kan zauna ta tsara girki mai rai da lafiya ta ajiye mishi ranar girkinta da rana.

Daya dauko hanyar ranar girkin Shukurah ya je da rana yace wai ta bashi abinci, sai tayi saurin taka mishi burki tun kafin hakan ya kai ga kara janyo mata bakin jini a wajen Ummahn da Shukurah. Don kuwa ta kula hatta da abincin ranar da yake ci a bangarenta su dukansu ba son hakan suke yi ba.

Wani hali nashi dake kara burgeta shine yadda baya da halayyar korafin wata a wajen wata. Duk yadda Shukurah zata bata mishi rai, koda wasa bai taba yiwa Nadiya korafin hakan a wajenta ba. Hasalima kullum kokarin boye wata baraka ko matsala dake faruwa a tsakaninsu da Shukurah din yake yi. Hakan ita kuma sai yake kwantar mata da hankali, tunda tasan ba zai taba kai maganarta wajen abokiyar zamanta ba.

A haka kuma sai ta fahimci wani abu, zama a matsayin matar Habibu abu ne mai dadi da kuma wahala a lokaci daya.

Dadi saboda duk macen data samu miji kamar Habibu dai, to ta huta. Mutum ne mai saukin kai da tarin alkhairori, haka kuma yana matukar kokari wajen sauke nauyin iyalinshi daya rataya a kanshi.

Wuyarshi kuma shine ba kowace mace bace zata iya hakurin barin wadannan halaye nashi ya dinga rabasu a tsakaninshi da wata ba. A

bangarensu kam, har Ummah ta shiga ciki. Tunda kuwa babu abinda yake zartarwa ba tare da hukuncinta ba. A gefen Nadiya kuma, ta kula Ummah din duk wani kokari nata, to shine na ganin bai kyautatawa Nadiya ba. Wadannan abubuwa dama wasu, suka sa dole sai data kara koyawa ranta hakuri da kawaici da kawar da kai akan wasu al'amuran. Saboda tasan idan tace akan komi sai tayi magana, ba lallai hakan ya haifar musu da da mai ido ba.

Ta cinye wata guda a hakan, tana so taje gida ta gaidasu amma fir hakan ya ki ya yiwu. Duk lokacin da tace tana so taje gida sai yace mata ta dan dakata, ba zai kara yi mata maganar ba kuma sai ta sake mishi. Daga baya ta gano umarnin Hajiya Ummah yake jira, don kuwa ta taba tsintar hirar tasu bisa kuskure inda taji Ummah din na mitar, 'ita Nadiya din me zata je yi ne a gidan nasu yanzu? Me ake yi? Ita fa bata son yawace-yawace marasa kan gado!'

Taga wani irin yawo ne a cikin zuwa ganin danginka? Tunda ga Shukurah nan ita ba zaman gidan take yi ba, babu ruwanta ma ita fita sai ta gama shirinta sannan take sanar da ita. Akwai lokuta da dama ma sai dai kawai ta fadawa Ummah din zata fita, Nadiya bata tunanin tana fadawa Habibun, amma da wasa bata taba jin Ummah tayi mata fadan yawo ba. Sai ita? Akan wane dalili? Me tayi mata? Don haka ta bar maganar fita ta hakura.

Iyaka tunani ita dai tayi akan ta gano menene wai ta yiwa Hajiya Ummah haka? Amma ta kasa gano dalili. Don haka sai ta kudirci wata aniya a ranta, ita zata kyautata, ba zata gaji ba kuma har sai ta ga abinda ya turewa buzu nadi. Hajiya Ummah za tayi ta shareta da kokarin hanata rabar jikinta, amma ba zata bata wannan damar ba.

Kullum idan tayi abincin rana to sai ta sanya da Hajiya Ummah ta kai mata nata, bata taba tsayawa ta ga ta ci ko bata ci ba, ita dai aikinta ta hada girki mai kyau mai cike da ganyayyaki na karin lafiya, hadin abinci kuma ya zamana irin wadannan tsofi zasu ji dadinshi ne sosai.

Haka kuma idan taje sashen nata ta kan yi mata gyare-gyare da goge-gogen falo da falon sama duk da cewa akwai masu yi, kuma itama Ummah din tana hanata amma bata bari ba.

Yau ba ita ke da girki ba. Zaman kadaici ya fara isarta da takurata, kwarai take bukatar fita ko yaya ne ko don ta samu ta ga gari. Bata saba zama a gida har haka ba, musamman wajen da idan ba kai kaso ganin mutane ba zaka iya share sati ma ko fi baka ga wani yaje inda kake ba.

Ta fito cikin doguwar rigar atamfa anyi mata freestyle, ta yafa dan karami gyale a kanta. Sashen Hajiya Ummah ta wuce kai tsaye, so take yi ta ji ko tana da wani abu da take bukatar ayi mata. Ta kudiri niyar idan ta samu Habibun zata tambayeshi izinin ya barta da yamma ta dan zaga koda cikin unguwar ne kawai ko gidajen makotansu ko ta dan warware daga yanayin kadaici da take ji yana ratsata.

Ta samu Hajiya Ummah din da Lailah a kicin, da alamu tsarin wani abu ne suke yi don ga takarda nan da biro a gabansu suna yin list.

Ta duka ta gaidata, ta amsa hankalinta gabadaya akan lissafin da take yi, itama Lailah ta gaisheta ta amsa. Sau tari anan wajen Lailah din take zuwa su sha hira abinsu, saboda ta kula yarinyar bata da rawar kai. Abinda ya kaita gidan shi kawai take yi, ba kamar sauran yan aikin gidan ba data kula kusan dukansu hadiman Shukurah ne. Duk wani motsi nata suna kula dashi ta kuma san suna kai mata rahoto, don haka take taka tsantsan a gabansu.

Ta tsaya bata tafi ba tana tsintar maganganun da suke yi jifa-jifa, daga karshe dai ta fahimci cewa Ummah din baki ne zata yi daga Riyadh, Saudi Arabia. Ita kuma Lailah za tayi musu girki ne na tararsu.

Sai ta matsa kusa da ita, tace, "aikuwa Ummah na iya Arabian girki sosai, idan babu damuwa ki bari inyi ko kuma in taya Lailah muyi tare."

Ta kalleta a nutse tace, "kin tabbata?"

Ta gyada kai da sauri tana dan murmushi, "sosai ma. Ai ina yawan yin girke-girkensu. Saboda kafin in bar wajen aikina ma ai da muna tunanin gabatar

da daya daga cikin abincinsu da yayi shura ne a wajen, kuma nima shi nafi iyawa."

Ummah ta kalli Lailah, ta juya tana kara kallon takardar gabanta cikin dogon tunani, sai kuma ta gyada kai, tace, "to tunda hakane, sai ku hadu din kuyi saboda dama Lailah tace bata kware ba a harkar girke-girkensu. Bakine zamu yi masu muhimmanci Nadiya, kada ki dauki aikin da ba zaki iya ba fa!"

Tace, "in shaa Allah Ummah zan iya, babu matsala!"

Ta gyada kai, "ok. Tunda hakane, ga Lailah nan ki rubuta abubuwan da zaki bukata duka, a duba wadanda muke da su anan, wadanda babu sai ta fita ta sayo. Gobe zasu zo, don haka a tanadi komi yau. Kin gane?"

Tace, "to Ummah!"

Ta fita ta basu waje, ita kuma ta nemi waje ta zauna suka hau sabon list. Yinin ranar hankalinta sai ya karkata gun irin abincin da zata yi, duk suka hada komi a ranar kamar yadda Ummah din tace. Bata koma sashenta ba sai can bayan isha'i, hakan sai ya yaye mata kadaicin data jima tana yawo dashi a ranta.

Washegari kuwa tunda safe taje suka hau dafe-dafe. Ba su suka gama komi ba sai can wajen karfe uku na yamma, ta koma sashenta domin tayi wanka. Tana jin lokacin da bakin Hajiya Ummah din suka karasa, amma bata yi gigin zuwa ba sai ta zauna a sashenta. Gudun ruwansu take so ta gani.

Zuwa can wajen karfe biyar da rabi sai ga Lailah taje tace mata Ummah ce tace taje su gaisa da bakinta. Dama a shiryenta take tsaf cikin wani maroon din swiss lace, ta yafa gyalenta ta zura takalmi ta bi bayan Lailah.

Bakin na Hajiya Ummah mata biyu ne manya, zasu iya yin sa'annin Hajiya Ummah din, sai wata matashiya da zata iya girmar Nadiya da yan shekaru.

Ta duka ta gaishesu cikin dan larabcin data iya, tunda babu laifi ta iya gaishe-gaishen Larabci. Ga mamakinta Hajiya Ummah ce take tadata a inda ta karkare, sai taji ita larabcin take yi sosai kamar dama can yarenta ne.

Take ce mata sun ci abincin nan sosai sun kuma yaba, saboda daya a cikinsu ma cewa tayi wai yafi wanda suke ci a can dadi. Shine tace bari ta kira wadda ta musu girkin su ganta. Tayi kasa da kanta tana dan murmushi cikin jin dadin hakan. Ko babu komi Ummah ta bata mutuncin daya dace da ita, ayi acknowledging abinda kayi na bajinta ba tare da boye-boye ba ai abin dadine. Ba kamar yadda Madam ta taba yi mata ba.

Ta zauna anan har bayan isha'i kafin aka raka bakin Hajiya Ummah bangaren baki suka kwanta.

Kwanansu biyu a gidan, Nadiya kuma bata gajiya wajen dawainiyarsu ba ta bangaren abinci da abubuwan sha dana motsa baki. Hakan kadai sai daya kara kankaro mata mutunci sosai a wajen Habibu, bata san ta bangaren Hajiya Ummah ba dai.

Da bakin zasu tafi suka yiwa Nadiya kyauta ta musamman, kudi suka bata masu yawa, daloli na kasar America. Wadanda idan aka canzasu ba kananun kudi bane. Koda ta nunawa Hajiya Ummah sai tace ai nata ne. Me zata mata da su? Ta sake yin godiya sosai, amma data tashi sai ta raba kudin biyu ta ba Lailah. Tunda itama tana tayata a wasu abubuwan a kokarinta na son ganin itama hannunta ya fada a girkin.

Wai hakan kuma sai ya bakanta ran Shukurah, har sai da taso tayar da rigima. Wai akan wane dalili aka zabi Nadiya? Ita yanzu kenan nema ake a mayarta saniyar ware? Ana so a nuna mata karfin yan'uwantaka kenan?

Ta yiwa Habibun korafin haka lokacin suna kan dinning da dare suna cin abinci. Tun tana maganganunta bai tankata ba har dai ya kai ga ajiye cokalin da yake tsakurar abinci dashi tana kallonta. Wasa-wasa girkin Nadiya ya fara shagwabar da shi, ya sanyashi fara raina duk wani abu da zai kai cikin bakinshi matukar ba ita ta girka ba.

Ya ambaci sunanta a kausashe kafin yace, "yanzu me kike so ayi akai kenan?"

Ta tabe baki, "oho! Ni ai ina fada maka ne don kasan matakin da zaka dauka ko? A matsayina na babba kuma wadda tazo ta tarar a gidannan, ai ya cancanci ace duk wani abu da zai faru a gidannan ni ce zan fara sani. Kuma koda ma bakin ne zasu zo, ai kamata yayi ace ni ce ke da masaukinsu. Lailah wannan da kake gani shahararriyar chef ce, matar tsohon shugaban kasa ma daya sauka ita take mata girki kafin ta dawo nan gidan. Don haka ban ga abinda za a gwada mata ba a fannin girki na kowace kasa ma balle kasashen larabawa. Amma don daurewa karya wani gu, shine za ayi mun danwaken zagaye wai ace Lailah bata iya girki ba?"

Ya gyara zama da kyau yana kallonta, "ke me yasa ba zaki tsaya da kanki kiyi girkin ba sai dai ki sanya wata? Kin fara fahimtar bambancin naku tun yanzu?"

Ta tsaya tana kallonshi, "ok! Yanzu goyon bayanta ma kake yi kenan? Ina maka korafi amma kana fada min wai bambancin dake tsakanina da ita? Kaga tun anan ma ka gama nuna min kaima kalar naka rashin adalcin ko?"

Dai-dai lokacin Hajiya Ummah ta karaso wajen da Ammar yana binta a baya. Ya daga baki zai bata amsa sai ga zuwan Ummah din, sai yace mata, "yauwa, ki tambayi Ummah sai ta fada miki dalili ko?"

Ummah tace, "dalilin me?"

Daya fada mata abinda ke faruwa, Ummah baki ta tabe, ta harari Shukurah da itama take turo baki saboda tasan fada ne zata sha a wajenta. Tunda ita ta fara yiwa korafin amma tace mata ta bar maganar.

Tace, "wai ke a wajenki magana bata mutuwa ne Shukurah? Ba a isa ace miki ki bar magana ba ki bari? Sai kije kiyi tayi ai, ni dai ko fitar ni daga cikin wannan maganar!"

Ta tashi ma ta bar musu teburin gabadaya.

Amma duk da haka dai maganar bata mutu ba a wajen Shukurah.

33.

Sai da tayi kwana hamsin a gidan sannan Ummah ta yarda taje ganin gida. Ranar dai murna a wajen Nadiya kamar tayi me, shi gogan daya bata albishir sai gefe ya koma yana kallonta yana sakin murmushin yadda take ta shigi da ficin laluben kayan da zata sanya. Tayi kewarsu Mama fiye da misali, su kansu yaran gidan tun bayan da aka kaita sau biyu kadai suka koma. Tasan kuma babu mamaki Mama ce zata hanasu zuwa saboda kada ace sun cika zarya.

Tayi shirinta tsaf, Habibun da kanshi ya kaita gidan nasu tare da Ammar data bukaci a bata shi ya mata rakiya tunda babu makaranta ranar.

Gida ya kacame da iface-ifacen murnar ganin Nadiya. Fadar irin murnar da Mama tayi ma ba karama bace, duk inda Nadiya din ta juya idanunta na kanta tana dan murmushi cike da jindadin yadda alamun hutu da jindadi suka bayyana a jikinta.

Ta samu Amarya bata nan taje duba kaninta da bashi da lafiya. Ta bi su Salame da Lantana har dakunansu ta gaidasu. Sai taga alamun duk sunyi sanyi a jikinsu, ko kuwa don ta kwana biyu bata ji duriyarsu bane yasa? Ta koma dakin Mama ta bude jakar tsaraba da tayo musu a hanya, tarkacen su sabulan wanka ne dana wanki, yara kuma alewowi da biskits da cakuleti. Haka duk ta bi ta raba musu, har su Salame dinma sai da aka kaiwa sabulai.

Ranar ta yini a gaban Mama tana ta tattalinta, duk abinda ta kai hannu ta dauko na ci, ta mikawa Nadiya. Ita kam ranar ranta wasai.

Tana nan har dare da Abba ya dawo. Taje suka gaisa tare da yi mishi sallama, saboda yana ta shirye-shiryen tafiyarshi aikin Hajji wanda za a fara kwasar mahajjata nan ba da jimawa ba.

Suka gaisa dashi yana tambayarta mai gidanta da iyayenshi, ta amsa mishi suna nan lafiya lau. Ya kara da yi mata nasihar zaman lafiya da bin miji sau da kafa, kafin ta yi sallama da yan gidan baki daya suka tafi saboda direban da aka aika ya dauketa ya karasa. Ta koma gidan Hajiya Ummah rayuwa ta cigaba da tafiya a haka.

*

Watanni suka shiga suka shude. Nadiya ta kasa gama fahimtar wata irin rayuwar aure take yi. Ta kasa gano kan matsalar dake tsakaninta da Ummah wadda take kamar Uwa ce ga mijinta. Balle tasan irin takun da zata yi da ita.

Hajiya Ummah baudaddiyar macece mai wani irin baudadden hali da daga ita sai Allahn daya halicceta suka san iyakarshi. Abu daya data gama fahimta da ita shine cewa tana da riko, kuma fushinta baya da iyaka ko kadan. Idan mutum ya kuskura tayi fushi da shi, to akwai matsala.

Habibu ya fara fita zuwa yawon kamfen dinshi, zaben da ake sa mishi rai nan da abinda bai gaza shekara ba. Wannan dalili yasa gabadayanshi yayi wahalar gani, ko ta waya bai cika samuwa ba. Saboda tafiye-tafiyen nashi wani lokacin har kwana suke sanyawa yayi ko fi, ko kuma idan ya fita tun safe sau tari sai cikin dare yake komawa.

Ta gefen Hajiya Ummah da Shukurah su ma suna tayashi nasu kalar kamfen din. Ita kanta Shukurah din tana yawan fita kamfen din ko ma ta bi bayanshi a matsayinta na matarshi. Da rana daya basu taba sanya Nadiya a cikin

sabgar su ba, itama da taga haka sai ta koma gefe tana kallonsu. Bata taba musu magana ba, kuma bata taba nuna musu sha'awar tana son zuwan ba. Tana jin Shukurah watarana tana waya tana fadawa wanda suke wayar mutanen data tanada wadanda zata yi aiki da su idan ta shiga ofishinta na Matar Gwamna. Tana ta daga murya da hayagaga da sakin habaici duk don Nadiya ta ji ta ne wadda a lokacin tana falon a zaune tana chatting da Anty Lima wadda bikinta yake ta matsowa. Tayi banza ta kyaleta ta nuna kamar bata ji abinda take cewa ba. Harkar siyasar Habibu ta kula idan ma tace zata sanya abun a ranta, ita za a dinga bari da bacin rai.

Akan wannan maganar har sai da Madam ta kirata wata rana cike da bacin rai, take tambayarta 'wai me yasa bata taba ganinta a kafar yada labarai ko daya ba game da siyasar Habibu? Me yasa har yanzu babu wanda ya santa a matsayin matar Habibu?'

Nadiya tace mata, "to Mommy tunda ba a gayyaceni ba ba sai in kama kaina ba kada in sayowa kaina cin mutunci da kaina?"

Madam din cike da mamaki take tambayarta, "yanzu ita Hajiya Ummah din ce bata taba sanyaki cikin harkokin siyasarsu ba?"

Nadiya tace, "basu taba ba Mommy. Don haka kema da kin kyalesu, kada ki musu magana don Allah!"

Madam sai ta hau fada, tace, "ashe ma ke baki da hankali Nadiya? A tunaninki wai duk don saboda wa nake wannan hakilon ne? Ba don ke bane?! Kuma sai a zo ace wai an wareki a harkar wannan? To ni duk bautar da nake yi a yaya take kenan? Ai wallahi ba zata sabu ba! Idan aka hau mulkin wannan a haka ai ban ga abinda auren naku zai tsinana min ba!" Ta kashe wayar tana cigaba da fadanta.

Bata san ko ya suka kwashe da Hajiya Ummah ba, ta dai ga Madam bata kara yi mata zancen ba, don haka itama sai ta watsar da maganar.

Ranar wata Laraba tunda safe sai ga kiran Rashida, take fada mata tana nan hanya yau. Nadiya tayi murnar jin hakan sosai, saboda wasa-wasa tayi kewar Rashida kwarai da gaske.

Ta taba yiwa Habibu maganar sau daya watarana da taga yana cikin nishadi, take ce mishi tana son zuwa ta ga Rashida, yakamata dai ranar da yake free ya kaita ita da Ammar su gansu. Yayi shiru kamar bai ji ta ba, daga karshe ya basar da zancen. Fahimtar da tayi cewa baya son zancen yasa sai bata sake yi mishi ba itama.

Duk da cewa ranar ba girkinta bane, sai ta shiga kicin a bangaren Hajiya Ummah da kanta ita da Lailah suka yi girki ranar.

Rashida din bata karasa gidan ba sai bayan la'asar, da taje kuma sai Nadiya taga ashe ba ita kadai bace. Tare suke da wata dattijuwar mata, wadda ko ba a fada ba kasan cewa mahaifiyarsu ce. Saboda kamarta da Habibu har ta baci.

A falon Hajiya Ummah taje ta samesu, ta zube har kasa tana gaishe da ita cike da girmamawa. Girmanta da nauyinta suka kamata a take, ta rasa wace irin tarba zata mata? Nan da nan sai ta hau fito da kayan abinci daga kicin da lemuka tana shiryawa akan dinning.

Jikinta sai yayi sanyi lakwas ganin irin tarbar da Hajiya Ummah tayi mata. Ta sauko daga kan bene tana takunta daya bisa daya, ta nemi kujera ta zauna a hakimce, Rashida na gaisheta tana amsawa da kyar. Hajiya Hadiza, wadda Nadiya taji Rashida na kira da Yakumbo, ita ta dinga gaishe da Hajiya Ummah. Ita dinma cike da wata irin ginshira ta dinga amsawa, babu ya hanya ko ya bayan rabuwa ko tayi kokarin jan ta da hira, sai kiraye-kirayen de waya data hau yi. Zuwa can kuma sai ta kalli Nadiya tana tambayarta wai an kaiwa baki ruwa? Ita data coge a kusa da teburin cin abinci tana kallon wannan abin mamaki sai lokacin ta iya motsawar kirki. Ta matsa tana yiwa Yakumbo tayin abincin da ta gama shirya musu.

Tayi murmushinta mai cike da kamala da rashin jin haushin abinda Hajiya Ummah din tayi mata, ta cewa Nadiya, "Alhamdulillah, a koshe muke wallahi.

Rasuwa aka yi cikin family dinmu muka zo gaisuwa, shine nace Rashida ta rakoni in ga matar Habibu. Har anyi biki an gama bamu samu mun leko ba."

A ranta taji babu dadi sosai da wannan abu dake faruwa, amma sai bata nuna hakan a fuskarta ba. Ta dauko lemuka da snacks ta kai mata, ta koma kusa da Rashida ta zauna. Yadda take yi idan Ummah tana falo bata zaman kan kujera, yanzun ma a kasan kafet ta zauna suna hirarsu ita da Rashida kasa-kasa.

Wajajen karfe biyar sai ga Shukurah ta shigo falon shajaran-majaran a matukar gajiye, wasu mata biyu suna take mata baya da alama yan kanzaginta ne.

Kai tsaye wajen Ummah ta wuce yadda kasan ita kadai ce a falon, tayi briefing dinta a tsaitsaye akan abinda ya wakana a yawon kamfen data je yau. Sai data gama ne tana shirin juyawa ta tafi sannan Rashida ta gaisheta. Ta dubesu a karo na farko tun shigarta falon, ta wani yatsine fuska, "lafiya lau... Yakumbo sannu da zuwa!"

Ta dauke hankalinta daga kansu bayan wannan ta mayar ga matan da suka je dasu tana kara jaddada musu lallai-lallai su tabbata kudaden data bada a rabawa mutanen da taje wajensu yau, sun isa hannun kowa. Daga haka ta wuce abinta cikin rigar bubu data sanya tana yawo a ciki ta wuce.

Ba Yakumbo din ba, hatta da Nadiya kanta sai da wannan abu yayi mata zafi. Bata ji dadi ba, amma wa ya isa ya tanka?

Babu jimawa da fitar Shukurah din Yakumbo ta mike tana cewa Hajiya Ummah, "to Hajiya za mu koma. Mun ga mata, Allah Ya sanya alkhairi, Ya kuma bada zaman lafiya!"

Hajiya Ummah tace, "ameen. Ku gaida gida!"

Ta tashi zata koma sama abinta.

Nadiya sai ta kalli Yakumbo, tace, "Yakumbo ba zaki yi hakuri ki jira Baban Ammar ya dawo ba? Yanzun nan zaku ganshi ya dawo in shaa Allah."

Yakumbo tayi dan murmushin manya, "a'ah Nadiya, sauri muke yi saboda a yau nake sa ran komawa Makarfi in shaa Allah. Idan ya so ganina ai zai je har inda nake ne!"

Ta fita Rashida na binta a baya, daga ganin yanayinta itama kasan cewa hakan bai yi mata dadi ba.

Nadiya tace, "to Yakumbo, muje sashena ki gani mana?"

Tayi yar dariya a tausashe, tace, "to muje Nadiya!"

Ta mata rakiya har bangaren nata, ta zagaya ta ga komi tana mai sanya albarka da yabawa. Tace mata, "Yakumbo ba zaki bar Rashida tayi mana ko kwana biyu bane?"

Tayi murmushi sosai tana kallon Rashida da itama take murmushi, tace, "Rashida makaranta ai take zuwa, amma in shaa Allah idan sun yi hutu, zata zo muku!"

Da zasu tafi ta shiga kicin ta cika musu leda da doughnut da tayi a jiya da cin-cin. Habibun yana yawan mata korafin idan ya fita ko yaje office yunwa tana takurashi a lokuta da dama, shi dama gashi ba ma'abocin cin abincin waje bane. Na gidan kanshi da yan aiki suke dafawa ma don dolene yake ci, yanzu kuwa tunda Nadiya tayi uwa tayi makarbiya da girke-girkenta, sai ya fara kauracewa abincin restaurants koda ya fita. Ita kuma sai take hada mishi snacks na ciye-ciye wadanda tasan zai ji dadinshi kuma zasu cika mishi ciki, idan zai fita sai yayi guzirinsu.

Ta cika musu leda taf tace sun ci a hanya. Haka ta rakasu har wajen motar da direba ya tuko Yakumbo a cikinta. Da zata shiga mota ta juya tana kallon Nadiya, ta kama hannunta ta rike tana murmushi wanda ya ke nuna wani abu na bacin rai dake dankara a can cikin ranta wanda take kokarin dannewa. Tace, "nagode sosai da sosai 'ya ta, Allah Yayi miki albarka. Allah baku zaman lafiya a cikin rayuwar aurenku. Don Allah a gaishe min da Ammar, hopefully shima idan sun samu hutu a kawo min shi. Shima Baban nashi a mika min sakon gaisuwata izuwa gareshi."

Tayi murmushi na yake tana jinjina kai, "in shaa Allah duk zasu ji Yakumbo. Ku gaida gida. Kuma in shaa Allahu ni da kaina zan kawo miki Ammar din idan sun samu hutu."

Ta sake yin murmushi wannan karon mai nuna jindadinta, tace, "to Allah Ya amince Nadiya!"

Ta shiga mota direba ya ja suka tafi.

Ta juya ta wuce sashen Hajiya Ummah da niyar dauke abubuwan data jera akan dinning kafin masu shirya abincin dare su kai ga zuwa. A ranta tana ta saka da warwarar wannan abu dake faruwa mai daure kai.

Sai ta samu Hajiya Ummah tana falon har a lokacin, tana shiga ta ambaci sunanta cikin wata murya dake nuna koma menene zata fada ba wanda Nadiya zata ji dadinshi bane.

Tace mata, "gargadi daya ne zan yi miki a yanzu wanda nake so ya zama na karshe a wajenki, kina ji na?"

Nadiya ta gyada kai da sauri, tana kallonta gabanta na faduwa, a ranta take tambayar me ya faru ne yanzu-yanzu ba tare data sani ba?

Hajiya Ummah tace, "kada ki kuskura, in sake yin baki a cikin gidannan ki shiga cikin harkarsu ba tare da ni na bada wannan izinin ba. Nan din gidana ne, ni kadai nake da hurumin tarar wani idan yazo nan gidan da mutuntawa ko akasin haka, babu ruwanki, babu abinda ya hadaki da kowa da zaki dinga wani bare-bare da rawar jiki akan wasu daban. Wannan shine gargadi na farko da karshe, kada ki kara maimaita min hakan!"

Kanta ya daure da wannan abu, ta daga kai tana kallon Ummah din da mamakin kalaman dake fita daga bakinta, tace, "amma Ummah.... Yakumbo fa mahaifiyar Baban Ammar ce!!"

Ta daga kafada, "and? Sai me? Hakan ba shi ya goge cewar nan gidana ne inda nake da iko dashi, nake da damar yin duk abinda naga dama ba. Tana amsa sunan mahaifiyarshi ne kawai, amma ba wai tana da wannan girma da kimar bane ko iko. Don haka idan zaki sauke wannan giringidishin dake kanki tun wuri ma ki sauke saboda wannan hanyar da kika dauko ba zata bullar dake hanya mai kyau ba! Ki kwashe min wadancan kayan da kika baza min a kan teburi ki san inda zaki yi dasu." Ta haye sama ta bar Nadiya anan.

Ta jima anan tana sakar zuci, kafin dai daga karshe ta ja kafafunta ta wuce ta kwashe kayan ta kai kicin, ta koma bangarenta jikinta kamar an watsa ruwa.

Ta kasa ganewa kanta abinda ke faruwa, sai dai ko kusa bata tunanin zata iya biyewa umarnin Hajiya Ummah a wannan karon. Wace riba ce ma ita Ummah din zata ci idan ta raba 'da da Uwa? Kuma menene ribarta idan ta hana Nadiya bata girman daya dace? Ta sanya a ranta, idan har ta samu hali, ita kam sai ta kusanta Habibu da mahaifiyarshi.

34.

Ranar da girki ya juya kanta, ta tareshi kamar yadda ta saba a sauran ranaku. Ranar da wuri ya shiga bangaren nata, yana ta wani irin rawar jiki da bare-baren jiki yadda kasan dai shekara ce yayi rabonshi da ita. Har kullum hakan bai daina ba Nadiya mamaki ba, rawar jikin nashi tana yin yawa a lokuta da dama da har baya iya boyewa a gaban Ummah yanzu. Tana tsoron ranar da Ummah din kuma za tayi magana a kan haka don ga dukkan alamu idanu ne ta zuba mishi don taga iyaka gudun ruwanshi.

Duk da dai a kullum kuma sai ya mata korafin., 'ban san me zan miki ki saki jiki da ni ba Nadiya. Har yau kina boye min kanki, har yanzu baki gama

mallaka min kanki ba Nadiya. Ban kuma san me zan yi ba, for you to give me all of you. Heart, body and soul!"

Ko a daren yau abinda ya gama fada mata kenan cikin yanayi na contentment da yake a ciki. Shi kanshi yasan cewa yana korafi da yawa da neman takura mata, but he can't help it. Daga yanayin da take karbarshi kadai, yasan cewa ba wai don ta bashi kanta bane dari bisa dari yasa take ziyartar shimfidarshi, sai don kawai sauke hakki wanda ya rataya a kanta. To in banda abinshi ma, har yaushe ne yake da wani iko ko katabus a kan matarshi? A tsayin shekarunsu na uku da aure shi da Shukurah, ba zai ce ga rana daya wadda ya gayyaceta zuwa shimfidarshi ba taje kai tsaye ba tare da korafi ko ta kai mishi wani excuse ba na daban. Sai ita Nadiya din mai kokarin yi zai takurawa? Wani lokaci haka zai zauna yana tuhumar kanshi.

Rayuwar aurenshi da Hidaya mahaifiyar Ammar rayuwace ta mutunta juna da kaunar juna mai tsafta wadda suka jima suna shimfidata tun kafin auransu, sun hadu da ita ne a Jami'ar Ahmadu Bello University dake Zariya, lokacin yana kokarin hada degree dinshi na farko. Babu jimawa da kammala karatun nashi aka daura musu aure da ita, da niyar bayan auren nasu zata karasa nata karatun saboda ita a lokacin tana shekara ta biyu ne kawai. Haifaffiyar cikin Zariya ce a unguwar Palladan.

Ba wani cin amarci suka yi ba na azo a gani, saboda ana yin auren Allah Ya hadata da wani irin ciki mai zafin laulayi. Ya zamana bata ko son ya kusanci inda take ma balle zancen auratayya ya shiga. Shi kuwa kasancewarshi mutum mai hakuri da tausayawa, yayi kokari sosai ya danne urges dinshi har zuwa lokacin da cikin nata yayi kwari da girma sosai. Ba jimawa da samun wannan lafiyar kuma ta haihu, cikin ikon Allah kuma tun bayan haihuwar bata samu wata cikakkiyar lafiya ba. Watanta uku da haihuwar Ammar Allah Yayi mata rasuwa. Mutuwar ta bugeshi kwarai da gaske, ya dauki son duniya ya dorawa Ammar. Bai kara bibiyar lamarin aure ba bayan nan har sai da Ummah da kanta taga dacewar ta shiga cikin zancen sannan.

Bayan kuma bin dogon layin yanmata da dama da suka wucewa tantacewar Ummah, rabon ya fada kan Shukurah. Sai gashi a wajenta bai samu abinda yake so din ba.

A yanzu daya samu Nadiya din gabadaya sai ya juye ya koma phase din cin amarcin sabon aure wanda bai ci ba a wancan lokacin. Amarcin da ko a wancan lokacin baya yi mishi wannan rawar kan da giringidishi.

Wani abu ne a tattare da Nadiya din na musamman, wanda shi kadai yasan irin halin da yake tsintar kanshi a ciki idan yana tare da ita. Shi yasa zuciya da sake-sake suke saka mishi, wai a hakan ma bata gama sakar mishi jiki ba. Me zai faru kenan idan ta mallaka mishi kanta dari bisa dari? Watakila dai ranar sai ya kai ga shidewa.

Shi yasa ya takura din, ba kuma wai don ta gaza mishi a komi ba. Wani lokacin shi da kanshi zai dawo daga baya yace mata ai ko a haka ta barshi, shi kam hakan ya isheshi.

Ta gama sauraronshi yana ta zuba korafinshi, idan ta itane ta riga ta gama sabawa da hakan. Ita dai kam, iyaka tunani da wasa kwakwalwa, tayi akan ta gano me Habibun ke nufi da kin mallaka mishi jiki amma ta kasa fahimta. Shi yasa ta ke kyaleshi kawai yayi ya gama. At the end of the day dai, a hakan zai sake dawo mata.

Ta kalleshi a nutse ta cikin dan hasken dake ratsawa dakin, tace mishi, "Ummansu Rashida ta zo ranar nan. Nasan kila ma kunyi magana da ita ko Rashida din, amma dai na ari bakinka na ci maka albasa. Nace mata idan su Ammar sun samu hutu zan kai mata shi har gida su gaisa. Don Allah kada kace min a'ah! Ka bari in cika wannan alkawarin."

Yayi shiru a kwance kamar bai ji abinda tace ba. Lokacin yana rigingine ne a kwance, ita kuma ta dan kishingida tana kallonshi. Sai ta dora tafin hannunta a saman kirjinshi wanda babu riga a jiki, ita a karan kanta ba zata ce ga lokaci na karshe da ta kai hannu ta taba jikinshi ba willingly, watakila ma zata iya cewa hakan shine na farko.

Ta kara yin kasa da murya cikin son janyo hankalinshi, tace, "Daddyn Ammar magana fa nake yi maka, kaji?!"

Ya dan bude idanu yana kallonta da idanu kasa-kasa, tsigar jikinshi har tashi take yi. Kamar dai ba yanzu bane babu dadewa ya gama sauke mata tarin rigingimunshi ba.

Yace, "to me kike so in ce miki ne Nadiya? Tunda kin gama are min baki kin ci albasa?"

Tayi dan murmushi a tausashe, "to kayi hakuri idan hakan ya bata maka rai."

Ya kai hannu ya dora saman nata inda take wasa dashi a kirjinshi ba tare da tasan tana yi ba, yace, "babu laifin da kika yi Nadiya. Sai dai wannan karon tuni an yiwa Kakanninshi dake Zaria alkawarin kaishi yayi musu hutunshi. Kinga babu dadi kai tsaye kuma ace musu an fasa ko? Amma mu jira zuwa lokacin sai mu ga idan hutun nasu da tsayi, daga can sai a kaishi Makarfi din. Hakan yayi?"

Tayi murmushi sosai cike da jindadin abinda yace, ko babu komi dai ai ta samu positive reaction. Tace, "to amma dai har da ni din za a je ko? Kuma dai kaga bikin Anty Lima ma nan da sati uku ne fa, ina so in je in tafi a week to bikin saboda bana so inyi missing din komi. Ka dai san yadda muke da ita."

Ya kalleta da baki a dage kamar wadda ta tsiro da wani sabon kai daga jikinta, yace, "ke yanzu idan nace miki ki tafi a week to bikin kuma sai ki tafi? Kusan sati biyu fa kenan kike fada min zaki yi!"

Tace, "to ai kaga ta hakan zan samu damar zuwa in ga dangi suma su ganni sosai ko? Itama da bikina ba haka ta yi mun ba?"

A ranshi yake raya, 'Allah tsareshi da ganin wannan rana shikuwa. Haka kawai sai ya bar matarshi ta dauki hanya wai ta tafi biki fiye da sati biyu? God forbid!'

Amma a fili kuma sai ya jata cikin jikinshi daya hango zai iya yin amfani da wannan damar ya tafi zagaye na biyu. Yace, "to bari dai lokacin yayi sai mu gani!"

Jin haka ita kuma sai ta bada kai bori ya hau, duk da tarin gajiya da barci dake tattare da ita.

Washegari tafiya ta kamashi ta gaggawa ya tafi wadda zai kwana a can. Yayi sallama da su cike da kewa ya tafi, wani taro ne aka kira na gaggawa a can Abuja. Tafiyar tasu ma sai tayi tsayi ta daukesu har kwanaki biyu.

Ranar da zai dawo Nadiya ta san zai karasa mata cikon kwana dayanta da bai yi ba ne, don haka ta shirya tarbarshi ta musamman ta hanyar da tafi gwanancewa, wato girki. Don tunda ya tafi, kullum korafinshi abinci ne. Don haka ta shiga kicin dinta ta gasa mishi kaza gashi mai kyau da ruwa-ruwa, ta barta a cikin microwave. Ta san shi gwanine wajen cin abincin tsakiyar dare, sau tari sai dai ta farka ta ga baya gado, da safe kuma ta shiga kicin ta samu ya cinye mata snacks da kayan motsa baki da bata rabuwa dasu. Wannan dalilin yasa ita kuma ta himmantu wajen ganin cewa ta bar mishi wani abu da zai ci koda ya tashi cikin dare a bangarenta.

Shigowar yamma yayi, tana can bangarenta tana wanka bayan girkin data gama, duk da kasancewar bata da tsarki hakan bai hanata dauro alwala ba, saboda a kodayaushe ba zaka rasata da ita ba a jiki.

Ta sanya doguwar rigar shadda ruwan goro da aka yiwa surfani a wuya da hannuwan rigar da green din zare mai kyau. A fatar Nadiya da take ta kara tumbatsa da yin fari da yin kyal-kyal a lokacin kamar ka taba jini ya fita, Nadiya ba karamin kyau tayi ba. Ga jikinta dake kara wani budewa yana direwa waje daya. Saboda tana matukar kula da jikinta da cimar da take ci mai kyau da karawa jiki kyau, shi yasa a kullum take ta kara rikita maigidan nata kamar wata sabuwar amarya.

Ta jira aka yi sallar isha'i, kafin ta dora dan siririn gyale green a saman gashinta da ya sha gyara. Ita da kanta ta zauna ta wankeshi tayi steaming din kayanta dazu, sai ya kara yin luwai yana tashin kamshi mai tsananin dadi. Yadda gashinta ke kamshi daban, haka jikinta yake fitar da wani kamshin na daban, haka ma kayan jikinta nasu kalar kamshin daban. Ta dauki wayarta ta fita daga falon tana taku dai-daya abinta.

Suka ci karo da shi a corridor wanda zai sadaka da bangaren Hajiya Ummah. Bakar Jallabiya ce a jikinshi, yana ta tashin kamshin turarenshi na gado.

Ya tsaya yana kallon yadda take tafiyarta a nutse, jikin nan yana rangaji sai kace bishiyar icen turare da iska yake kadawa a sanyaye. Ya shagala da kallon nata har sai data karasa inda yake, tayi diddige saboda yanayin tsayi daya fita, ta hura mishi iska a idanu.

Yayi firgigit yana dan ja da baya, sai ta saki wata tattausar dariya ganin yadda yayi.

Yace, "wato ma ni kike tsokana ko Nadiya?"

Tace, "to ai kai dinne naga kana ta kallona kamar ba zaka daina ba, kallon na nawa ne ma wai da?"

Ya kamo hannunta yana dan murmushi, taushin fatarta da santsin da take yi tana kai mishi har tsakiyar kanshi. Yace, "ki bari in muka hadu anjima zan fada miki ko na nawa ne!"

Ta fizgi hannunta ta wuceshi tana yar dariya, "lallai ma na ki wayon!"

Ya bita suka jera yana jifanta da kallo cikin burgewa, "ina gab da hanaki yin kwalliya a gidannan Nadiya! Saboda gaskiya na fara kyashin wadannan ma'aikatan dake kaiwa da kawowa a gidan suna gane min ke fa!"

Ganin sun shiga tsakiyar falon Hajiya Ummah kuma ga Hajiya Ummah din da Shukurah a zaune suna magana, sai bata mayar mishi da amsa ba.

Mazauna falon suka zuba musu ido suna kallonsu yadda suka jera dinnan. Ai ko hasidin iza hasada dai a wannan lokacin idan ya ga Nadiya da Habibullahi, sai ya kara juyawa ya kallesu, sai kuma ya yaba. Saboda tsabar haduwa da suka da dacewa. Wani abu ya daki kirjin Shukurah a lokacin har take jin numfashinta yana yin sama kamar wadda take fama da athma.

Hajiya Ummah ta samu kanta da yin tasbihi a cikin ranta saboda ba karamin kwasarta suka yi ba. A ran nata tace, 'wannan shine ma'anar match well made!'

Suka karasa wajensu a nutse. Ya zauna a kusa da Hajiya Ummah kamar yadda ya saba, Shukurah a gefenshi na hagu. Ita kuma sai ta zauna a tana mai fuskantarshi kusa da Hajiya Ummah kenan. Ta fara gaishe da Hajiya Ummah din, ta kuma fara zuba mishi abinci kafin ta nemi waje ta zauna. Don tun ranar daya ce ta zuba mishi abinci da kanta, bata kara fashin zuba mishi abincin ba matukar ranar girkinta ce.

Fried rice aka yi da taji kaji da hanta da nama a ciki. Ta zauna ta ci sosai, saboda da rana bata samu sukunin yin abinci ba saboda shirin tarar Maigidan data yini yi. Tana kula da yadda ya dinga tsakurar abincin shikuma kamar a koshe yake.

Falon ya kaure da hira a tsakaninsu wadda rabinta game da taron da yaje ne, da kuma irin nasarori da suke gani a yawace-yawacen kamfen dinsu. Ganin ba a sanyata a ciki ba, sai itama bata tsoma musu baki ba.

Ta tashi a nutse lokacin data gama cin abincin, tayi musu sai da safe da niyar wucewa bangarenta.

Shi kuma kamar wanda yake jira dama, sai yayi fatali da cokalin hannunshi shima ya fara musu sai da safe.

Hajiya Ummah ta bishi da kallo na bacin rai da takaicin wannan abu na Babangida. Tun yana kokarin boye mata dai har ta kai yanzu bata baya ma shayi ko jin kunyar idanunta ko kadan. Shukurah kuma ta mike tsaye yana kallonshi cikin kunar rai. Su dukansu kasa boye wannan doki da yayi a yau dai ya bakanta musu rai. Amma Shukurah sai tayi kokarin dannewa cikin kissa da kisisina.

Ta kamo hannunshi babu ko kunyar Hajiya Ummah dake kallonsu, tace, "Honey ina zaka je ne kake gaggagawa haka? Ko ka manta yau girkina ne?"

Jin haka Nadiya sai ta dakata da tafiyar da take yi ta waiwaya tana kallonsu, ita bata ma san Habibu ya tashi tana shirin bin bayanta ba.

Ya kalleta yace, "me kike fada ne haka Shukurah? Hala kin manta cewa kwana daya nayi a wajenta kafin tafiyar nan ta sameni ko?"

Tayi caraf tace, "to ai ka cinye kwananka shekaranjiya, jiya da yau kuma ni ce da miji. Ita ai sai gobe zata karbeka."

Yayi maza yace, "wannan wane irin zancene wai kike yi haka marar kan gado? Ai a doka da tsari da ka'ida na Islama, sai na karashe mata kwananta daya sannan zan dawo wajenki!"

Amma Shukurah ta rufe ido tace bata san wannan zancen ba, Nadiya da mamaki ya kamata ma ita sai ta kasa magana. Kawai tayi tsaye dososo! Tana kallonsu kamar wadda aka kafe a wajen, wannan fa shi ake kira karfin hali barawo da sallama!

Ummah da taga zancen nasu ya ki ci ya ki cinyewa sai ta tsoma musu baki, tace, "kaima Babangida dai so kake yi ka ja zancen da tsayi. Tunda dai wancan lissafin ya riga ya gama karewa ba sai kawai ku jona wani sabo ba? Ni ma dai naga kyawun tsarin da Shukurah ta fitar. Ka hakura kawai ka karasa kwanan yau a wajenta, in yaso gobe sai ku zuba sabon lissafi!"

Nadiya ta daga kai ta kalli Ummah a hankali, kafin ta mayar da kallonta ga shi Habibun don taji me zai ce. He was dumbfounded. Ya ma rasa abin cewa saboda tsabar mamakin wannan abu na Hajiya Ummah. Ta gaskiya kiri-kiri amma ki take saboda wani abu na daban? A iyaka saninshi da Ummanshi, macece ita mai tsayawa akan gaskiyarta. Duk inda karya da rashin adalci suke, to bata wajen. Amma yan kwanakinnan duk ta aro wani hali na daban,

wanda bai santa dashi ba ta yafa. Wadanda ya rasa dalilin wannan sabuwar halayya tata.

Nadiya ta kulu matuka, rashin maganar da bai yi ba ya tunzurata, tasan tunda har Ummah ta furta hakan, shikenan ta zauna daram. Maganarta a gidan ai kamar tawwada CE da aka yi rubutu da ita ta bushe akan takarda, babu ja balle zancen ja-in-ja.

Ta juya ta fita daga falon da sassarfa, ranat cike da dana sanin shigowa wajen wannan dare. Da tasan irin bakin cikin da za a kunsa mata kenan, da bata tako kafa tazo ba.

Shi kuma sai bayan fitarta ne ya iya samu bakinshi daya rike ya bude, ya kalli Ummah din cike da mamaki, yace, "amma dai Ummah kin fi ni sanin cewa hakan ba dai-dai bane? Shiga hakki ne da rashin tsayar da adalci, wanda ke kike yi mun hani da hakan. Amma yanzu kuma sai kice inyi abinda baki dorani akan tarbiyarshi ba?!"

Wannan amsa daya bata sai ta tunzura Ummah. Wai yau Babangidanta ne take magana yake tsaga tsakiyar idanunta yana mayar mata da amsa. Saboda mace!

Ta kalleshi cike da bacin rai. Tace, "idan baka yi hakan ba ai ba zaka tabbatar min da cewa na auro mace na kawo maka ba ta mallakeka! Yaro ka dawo sai kace wani sha-ka-tafi! Ka duba irin rawar jikin da kake yi akan yarinya karama Babangida, sai kace a kanka aka fara yin aure!"

Maganar tayi mishi nauyi kwarai da gaske. Sai ya kasa bata amsa. Ya juya ya kalli Shukurah data coge tana sauraronsu, ranta fal da farinciki. Ya maida kallonshi ga Ummah, yace, "kiyi hakuri Ummah. Amma zai fi mun idan kina so in nesanta kaina da Nadiya ne ki fada min, zan iya yin hakan. Amma ba zan iya shiga hakkin wata ba a cikin iyalaina, bayan ba a kan wannan tarbiyar kika tada ni. Zan wuce sashena in kwanta, sai da safe!"

Ya juya ya fita, yana taku rai cike da bacin rai. Yadda ya fita din sai kace wata giwa. Ummah ta bishi da kallo na mamaki fal a cikin ranta. Har yaushe ne Babangida ya fara yi mata gardama har da hadawa da wa'azi? Lallai tayi sake kwabarta tayi ruwa.

Ya fita yayi tsaye a tsakiyar gida yana furzar da wani numfashi cike da bacin rai, ranshi idan yayi dubu to a bace yake. Shukurah ita ce ummul-a-ba-isin haddasa wannan fitinar ta yau, duk wani budget daya dauko ta wargaza mishi shi a kasa war-was! Yayi alkawarin idonshi-idonta a gidannan, sai ta yabawa aya zakinta. Don sai ya sauke mata kwandon rashin kirki iri-iri tunda abinda ta zaba kenan.

Bai yi niyar kwana dakin Nadiya ba, amma duk da haka sai ya wuce bangaren nata ganin yadda ta fita dazu cike da bacin rai.

Ya sameta ta shige daki ta kulle, ya sanya makulli ya bude kofar falo, amma bathroom dinta ta sanya sakata daga ciki. Yayi bugun duniya da magiyar ta bude, amma tayi biris dashi taki tashi.

Ta zauna a gefen gado tana ta sharbar kuka cike da takaici da bacin ran wannan rayuwa. Yau ga abinda tafi tsana da kyama a cikin rayuwar gidansu, wato daukar kwanan wata a kaiwa wata, ya faru da ita kiri-kiri tana gani, amma bata da halin tankawa. Shin dama haka mata suke ji ne?

35.

Yana dawowa sallar Asubahi kai tsaye dakinta ya wuce. Cikin sa'a ya samu ta bude dakin amma tana kwance tana barci. Da kamar ya tadata saboda yasan bata yi sallah ba, sai kuma yayi tunanin watakila ko tana fashi tunda yana kirge da kwanakinta dama. A yadda kuma ya san ta da rashin wasa da sallah, yasan mawuyacine ta makara da gan-gan. Don haka ya juya ya tafi

nashi bangaren don shima ya kara dan runtsawa. Daren jiya kwana yayi yana saka da warwara ta inda yakamata ya bullowa wannan al'amari. Don ya kula maimakon abin ya fara yin kasa sai ma kara hawa da hau-hawa yake yi.

Sai wajajen karfe goma ya baro sashenshi ya fito. A farfajiyar gidan ya ci karo da motoci da escorts suna jiranshi saboda fita zasu yi da karfe goma din. Sai yace musu su dan dakata, ya shiga bangaren Hajiya Ummah ya gaisheta kamar yadda ya saba. Ta amsa mishi kamar kullum, kamar dai babu abinda ya faru daren jiya. Yayi mata sallama tana ta mishi fatan alkhairi.

Ya samu Nadiyar a zaune akan abin sallah tana lazumi. Kasancewar ta riga ta saba da gudanar da sallar walaha a dai-dai wannan lokaci a duk ranakun duniya, shi yasa koda bata sallah to sau tari ta kan nemi waje mai kyau tayi lazumi ko karatun Al Qur'ani mai Girma

Ta shafa addu'ar data gama yi, sai ta juya daga zaune din da take tana fuskantarshi. Murya a shake cike da rashin sukuni har zuwa lokacin a tattare da ita ta gaisheshi. Gabadaya sai ta kara bashi tausayi, ya taka da sassarfarshi ya karasa gareta, gabadayanta ya jata zuwa cikin jikinshi ya rungume a tsanake.

A haka din yake furta mata kalmomin, "tayi hakuri ta yafeshi, hakan ba zai sake faruwa ba yayi mata alkawari!"

Tayi kokari ta janye daga jikinshi a hankali tana ja da baya tare da girgiza mishi kai. Ya kyaleta din, amma duk da haka sai daya kama hannuwanta ya rike.

Tace, "kayi hakuri Abban Ammar. Amma ba zan iya yarda da kai ba a wannan gabar!"

Zuciyarshi ta karye, amma duk da haka sai ya dake. Yace mata, "kada ki ce haka Nadiya. Please have a little faith in me, ko yaya yake. Nasan cewa ban

baki dalilai masu karfin da zasu sanya ki yarda da ni a take ba, amma don Allah wannan karon, ina rokon ki yarda da ni. Ki bani dama in gyara komi. Nasan ni nayi saken da har muka zo kan wannan gabar, amma zan gyara Nadiya. I promise!"

Hawaye suka shiga zarya akan fuskarta, tace, "ta yaya? Ta yaya zaka gyara iye? Tun ran gini tun ran Zane. Tun a farkon fari daya kamata ka yiwa tufkar hanci, baka yi ba. A yanzu da aka kawo kan wannan gabar kuma bana tunanin zaka iya yin wani katabus. Don Allah kaje kawai, wallahi a yanzu haka ganinka munana raina yake yi. Amma kaje na yafe maka hakkina da kuka shiga, ko babu komi ba zan so ka tashi a gaban Ubangiji ba a matsayin mutum marar tsayar da adalci a tsakanin iyalinshi!"

Ta juya da sauri ta shige cikin closet dinta tana kokarin rufewa, ya bi bayanta da sauri shima tare da rungumota ta baya.

Yace, "ina so ki san cewa duk duniya Nadiya, ba ni da wanda ya kai Ummah. Saboda a duk duniya, babu wani mutum mai karamci dana sani irin nata. Ta so ni, tana kuma so na fiye da yadda ni kaina nake son kan nawa Nadiya. Abinda zai sanya inyi musu da ita ba karami bane Nadiya, amma a kanki nayi, ina kuma kan yi. Saboda so da biyayyar da nake mata ba zasu sanya ni take miki hakki ba. Wanda nayi a baya ma ban ji dadinshi ba, kuma ina neman afuwarki akan hakan. Kuma abinda kike zargi bai faru ba, ban je ga wata ba a daren jiya, ban kuma dauki kwananki na kaiwa wata ba. Ba kuma zan taba yin hakan ba...!"

Ya juyo da ita suna fuskantar juna shi da ita, yayi kasa da muryarshi yana kallon yadda idanunta duk suka yi luhu-luhu.

Yace, "kiyi mun alfarma daya don Allah, kada ki kullaci Ummah a wannan abin. Don Allah ki tayani sonta da girmamata da yi mata biyayya. Na shaku da ita fiye da yadda na shaku da mahaifiyar data haifeni, zan kuma iya ce miki duk duniya babu wanda yasan halinta kamar ni din nan. Mugunta ba a jininta yake ba, all these abubuwan da take yi I promise you zata daina cikin dan kankanin lokaci. Idan kuma ta tashi son ki Nadiya, na tabbatar miki sai ta so ki fiye da ni dinnan a karan kaina!"

Anan sai ya sosa mata inda ya jima yana yi mata kaikayi, sai ta kalleshi a tsakiyar idanu tace mishi, "Abban Ammar duk kusancinku da ita da shakuwarku, ba zai taba kamo na wanda kake dashi da mahaifiyarka ba. Saboda wannan bond din Allah ne kadai yake sanyashi a tsakanin uwa da da kadai, shi kadai kuma yasan adadinshi. To ko ita din, ba huruminta bane ta sanyaka taka shari'ah da hakkin addini ba. Idan ma kuma tayi hakan, kana da damar taka kafa ka take umarninta, kuma ko a wajen Allah baka da laifi!"

Ya dan lumshe idanu yana dan girgiza kai, "I know, na sani Nadiya. Kiyi hakuri don Allah!"

Ta girgiza kai, "baka yi mun laifin komi ba ni, kawai ina tunasar da kai abinda na tabbata mantawa kayi. Iyayenmu wasu muhimman figures ne a cikin rayuwarmu da babu wani abu da zamu iya musanyasu dasu. A zance na gaskiya kuma kana shakulatin-bangaro da al'amarin Mahaifiyarka. Don Allah, don Allah Abban Ammar, ka daina hakan. Wallahi you've no idea yadda abinnan yake sanyani a cikin damuwa da tunanin me hakan zai zama makomarka? Ba lallai sai ka guji daya a cikinsu bane dayar zata san lallai kana sonta da girmamata ba, you can love and respect them both, a lokaci guda. Don Allah do this for us..."

Ta karashe maganar kwalla tana taruwa a cikin idanunta. Kallonta kawai yake tunda take magana ba tare daya iya cewa komi ba. Tsakaninta da Allah magana take saboda ta damu da shi, da halin da duniyarshi da lahirarshi take ciki. Yaji wani irin abu a tattare da ita irin wanda bai taba ji ba. Girmanta da so da kaunarta suka ninku a cikin ranshi ninkin-ba-ninkin, har ya rasa ina zai kai su.

Tunda yake a rayuwarshi, bayan Mami, baya tunanin akwai wani daya taba nuna damuwarshi akan halin da yake ciki da mahaifiyarshi. A kalaman Nadiya a yanzu kuma, sai ya dinga tsintar traces din maganganunsu shi da Mami din idan tana yi mishi nata zancen da nasiha cikin hikima irin tata da ribata.

Ya gyada kai a hankali, yace, "Allah Yayi miki albarka Nadiya, nagode da wannan tunatarwa taki. In Allah Ya yarda kuma, zan yi aiki da ita. Ina kuma fatan abinda ya faru a jiya shima ya wuce a wajenki?"

Tace, "ni ai na fada maka babu laifin da kayi mun."

Yace, yana matsawa jikinta sosai, "to idan hakane, dan bani lebbanki kadan mana inji ya suka kwana?"

Tayi baya da sauri tana kawar da kanta gefe daya, "kayi hakuri don Allah. Amma ba zan iya aikatawa wata abinda nasan idan ni ka min ba zan ji dadi ba!"

Sai ya saketa shima, ya ja da baya yana sauke ajiyar zuciya a hankali. Barin nata shi zai fi a daidai wannan lokaci. Don kuwa shi kanshi yasan idan har ya sumbaceta din a yanzu, to fa ba zai iya barinta ba don wasa.

Yace, "shikenan Nadiya, na hakura. Bari inje. A sanyamu cikin addu'a please!"

A fili tace, "in shaa Allahu!"

A ranta kuma cewa take, 'addu'a ai kullum cikin yin ta nake, sai dai idan ban daga hannuna sama da sunan yin addu'ar ba!'

Ta bishi da kallo har ya fita daga dakin, kafin ta sauke ajiyar zuciya a hankali.

Ta sanya takalmi a kafarta kasancewar bata cire hijabin jikinta ba. Bangaren Hajiya Ummah taje ta gaisheta, cike da girmamawa da mutuntawa kamar yadda ta saba a kullum. Bata bari fuskarta ta nuna wani abu na daban ba, har ma ta hada da tambayarta ko tana bukatar ayi mata wani abu ne?

Ita gabadaya ma sai taji kunyar yarinyar ta rufeta. Tana so ta daga baki ta bata hakurin rashin kyautawar da ta yi mata jiya, tunda ita a karan kanta tasan ba dai-dai ta aikata ba, amma girman kai ya hanata cewa komi. Sai kawai ta ce mata bata bukatar komi, ta tashi ta haye sama.

Nadiya ta hau dinning ta zuba soyayyar doya da kwai da sauce din hanta, ta hada shayi ta sanya ciyawar shayin Victoria ta strawberry. Ta zauna ta ci

abinda zata iya a nutse, ta kwashe kayan duka ta kai kicin inda masu aiki ke faman wanke-wanke da kokarin fara shirin dora abincin rana.

Don ta samu ta rage yawan tunane-tunane da take yi sai ta hau sama, ta shiga dakin Ammar ta shareshi ta gyara tare da fitar da kayan dattinshi ta ba masu wanki da guda. Ta sake dawowa falo nan ma ta kara gyarawa duka na sama da kasan, sannan ta wuce sashenta ta kwanta domin samun barcin da bai gama isarta ba.

***

Madam Zarah ta shiga gidanta a yammacin ranar Lahdi afujajan da ita. Hannu daya rike da jaka, dayan kuma ya sangalo gyalenta. Kitson attachment da aka mata ya sauka har gadon bayanta. Pencil skirt ne aka yi mata na kamfala da riga half bubu, amma duk da hakan bai hanata shiga falon ba a sukwane cikin sauri kamar wadda ake bibiya.

Sai kuma ta dan ja tayi turus ganin mijinta Alhaji Shehu da waya a hannunshi yana dannawa. Watanni fiye da uku kenan baya cikin Najeriyar gabadaya, ita dashi sai a waya kawai suke haduwa. Bai kuma sanar da ita zuwan nashi ba duk da cewa sunyi magana dashi a daren jiya.

Ta karasa wajenshi ta dan duka ta sumbaceshi a gefen kumatu kafin ta zauna kusa dashi.

"Yallabai, what a surprise! Ai ban san da dawowarka ba yau, da ban fita ba sam!"

Yayi dan murmushi, "afuwan my dear, tafiyar ce nima ta zo min kai tsaye shi yasa kika ganni yanzu din. Wannan sabon kamfanin da nake fada miki zan

bude na energy drink aka samu wasu yan matsaloli, shi yasa na taho domin mu samu muyi tackling din matsalar da wuri."

Tace, "da gaskiyarka kam. Kana bukatar wani abu ne? Ban yini a gida ba don haka ko abinci ban samu damar yi ba. Amma zan iya sama maka wani abun da gaggawa."

Tun wani lokaci data kama mijin nata da yar aikinsu dumu-dumu akan gadon barcinshi, ta manna mishi hauka mai lasisi har da dauko wuka da cewa zata yanke mishi mazantakar tashi taga da abinda zai ke bin mata. Ya dai samu da kyar ta shawo kanta da bata hakuri kan cewa tsautsayine, bata kara daukar yar aiki ba.

Sai data sanya gardawa suka yiwa yar aikin data kasance wata Bakaniya lilis kafin ta sallameta. Ta gwammace gwara ta dinga yin girki da kanta, yan aiki kuma sai dai a kullum suje suyi mata ayyukan da za ayi mata su tafi, amma babu masu kwana.

Duk a dabararta na kada mijinta ya kyalla ido ya kara ganin wata a cikinsu ne. To in ma banda hayyata da jaraba irin ta namiji, mutum me mata kamar Madam Zarah me zai nema a wajen matan banza?

Yadda take kulawa da kanta da lafiyarta, duk watan duniya akwai ranaku na musamman da take warewa na zuwa spa kawai, ga gyara cikinta da wajenta da bata gajiya dashi. Shi yasa har kullum idan ka ganta sai kayi zaton bata kai adadin shekarun da take dasu ba. Musamman idan mijin nata yana gari, har soke harkokinta take yi gabadaya ta kasance a tare dashi. Duk dai don kada yaji kewar wani abu balle har ya kai ga kissima fita ya nema a wajen wata.

Bata san cewa namiji ba in dai mai halin bunsuru ne, mace ko uwar gyara da kayan mata za ta hadiya, su ko a jikinsu.

Don kuwa fitar nan da yake yi kasashen ketare babu abinda yake yi sai sheke ayarshi da matan banza yadda yake so.

Ya girgiza mata kai yace, "noo... Ban jima da sauka ba ai. Kuma na ci abinci a jirgi. Dinner kuma ki shirya sai mu fita mu ci a waje ko? Amma me ke faruwa ne? Naga alamun kamar kin shigo cikin damuwa."

Tayi ajiyar numfashi mai nauyi, "ka bari kawai Darling. Ina wannan arena da nake fada maka zan gina a Kaduna? Ina ta cin karo da matsaloli ne wallahi, ina tunanin kamar akwai wata a kasa, amma kuma ban san ta ina zan duba lamarin ba. A halin yanzu kuma ma ni Investors nake nema saboda budget din dana dauko babba ne. But I don't know who to trust."

Yayi shiru yana tunani, yace mata, "me zai hana ki barni inyi investing? Kinga hakan sai ya saukaka mana damar gabatar da sabon drink dinmu idan ya shiga kasuwa. Tunda akwai wajen events da kwallo a can, sai kiga mutane sun san shi nan da nan."

Ta saki murmushi cike da jindadi, "dadina da kai Yallabai, ba dai iya warware matsala ba cikin dan kankanin lokaci. Wannan shawarar taka na ji dadinta sosai da sosai fa! Bari inyi sauri in watsa ruwa, zan fito maka da duk tsarukanmu da muke yi, sai muyi maganar over dinner, yayi?"

Ya gyada kai, "of course!"

Ta duka ta kara sumbatarshi a kunci kafin ta wuce dakinta, wannan karon da kuzarinta.

Ya maida kallonshi ga wayarshi daya ajiye bayan shigarta falon, chat din da suke yi da yarinyar daya baro a kasar London ya bude yana kallon watsattsun hotunan data tura mishi yana sakin murmushi.

36.

Cikin yan kwanakin kewa duk ta bi ta dabaibayeta a cikin gidan nan kamar dai ita kadai take rayuwa. Habibun ya fita zagayen kamfen dinshi a Kauyukan dake kusa dasu fiye da kwanaki hudu kenan, Alhamdulillah kuma suna ganin nasara. Social media da su gidajen radio duk sun karade da zancenshi, duk inda ya sanya kafa kuma ya shiga jama'a ne ta kowane bangare ke dako da bibiyarshi suna nuna mishi kauna.

Ita da take a gida ba fita ba take yi, tana ta binshi da addu'o'in data saba yi a kowace rana.

Ranar Juma'ah bayan an fito Masallaci, ta shiga sashen Hajiya Ummah da kanta ta kamo hannun Ammar ta wuce bangarenta dashi. Gurasa tayi da rana, ta kuma fahimci daga Ammar din har Babanshi suna son ta sosai. Don haka ne in dai tayi, to ko bata ajiyewa Baban nashi ba shi sai ta ajiye mishi.

Suka zauna ita dashi suna ci a kwano daya, tana tambayarshi game da rayuwar karatunshi da mu'amalarshi da sauran yara cikin hikima da dabara. A ta haka ta tsinci zancen akwai wani yaro daya takura mishi a makarantar saboda ya fishi kokari, yana hanashi sukuni ta hanyar muzguna mishi tare da fara janye mishi abokanshi. Ranar nan har littafinshi ya yaga mishi.

A ranta ta yanke shawarar zata tuntubi mahaifin nashi game da zancen, in ta kama ma ita zata iya bin kanun zancen domin ta yiwa tufkar hanci tunda wuri kafin lokaci ya kure. Cases irin haka a hankali suke juyawa su koma bullying, sai kaga yaro mai kokari ya dawo dakiki saboda rashin samun sukuni a makaranta da kuma takurarwar abokai. Wanda hakan kan iya affecting dinshi emotionally, sai kaga yaro ya kasa yin abokai, ya zama socially inept.

Suna cikin yin hirar wannan sai ga mai aiki taje kiran Ammar din inji Hajiya Ummah. Nadiya ta dan bata fuska cikin rashin jin dadin hakan, shima Ammar din ga dukkan alamu bai ji dadin kiran ba. Amma bai yi musu ba ya tashi ya bi bayan mai aikin.

Ta bisu da kallo cike da taraddadi. Ba tun yau ba ta fahimci kokari ake yi a janye yaron daga jikinta, a hanasu mu'amala.

Yanzu haka kiri-kiri hirar da suke zama su yi da bitar karatu da suke yi an soketa saboda da sun zauna ne, zaka ga yar aiki a saman kansu, 'Hajiya tace lokacin kwanciya barcin Ammar yayi' ko 'Hajiya tace Ammar yaje tana son ganinshi'

Ita dai ta kasa fahimta dalili da manufar yin hakan. Idan Ummah ta rabata da Ammar ribar me zata ci ne? Saboda me?

Wadannan tunane-tunane da take yi sai taji ranta ya fara baci. Al'amarin nasu ya fara kaita bango kuma. Tun zuwanta gidan bata ga wani abu marar kyau ko na assha da tayi ba, amma kuma duk da hakan kullum yadda ake treating dinta kenan. Kamar wata wadda ta aikata wani gagarumin laifi.

Zuciyarta take tambayarta, to haka zata cigaba da zama ne? Ana takata duk yadda ake so, alhalin babu wani takamaiman dalili?

Abu daya Nadiya ta rike akida a cikin ranta, shine, hukunci kowane irine zata iya dauka matukar tana da laifi a cikinshi. Tana kuma yiwa mutum uziri idan taga yana hukuntata din.

A inda kuma tasan bata da kuskure kuma taga ana hukuntata, nan ne fa bata iya dauka. Don kuwa ko sama da kasa zata hade, ba zata dauki laifin wani ta kakaba a kanta ba. Ko ta karbi hukunci akan abinda bata aikata ba.

Shi yasa zaman gidansu ya wahalar da ita kwarai. Saboda a can, da gangan ake tsokanarta kuma daga baya azo a lakana mata laifin da ba nata ba. Ita kuma ga rashin iya daukar laifin da ba nata ba, ga rashin iya bada hakuri shima a laifin da bata aikata ba.

Ganin tunanikan nata suna neman jefata cikin wani yanayin na daban sai kawai ta dauki waya ta kira su Mama.

Abba ya dawo daga aikin Hajji lafiya. Gida ya cika dankam da mutane yan sannu da zuwa, kwana biyu da dawowar tashi amma har yanzu gidan da

sauran yan sannu da zuwa basu tafi ba. Maryam ta hadasu da shi ta sake yi mishi sannu da zuwa, kafin ta kirata ta vedio call ta hadata da kowa da kowa dake gidan suka gaisa suka kuma ga juna.

Lallai da ake cewa lokaci babu abinda ya bari. A yan watannin baya har alwashi take sha iri-iri, akan cewa idan har ta samu damar barin gidan wannan, da ba don su Mama ba da sai ta shekare bata waiwayesu ba. Sai gashi a yau, babu abinda take so kamar ta bude idanu ta tsinci kanta a tsakiyar gidansu da dandazon yara da matan gidan.

Da zasu yi sallama ta cewa Maryam ta samu su ware rana ita da yaran gidan su je suyi mata yini kafin ta fara zuwa makaranta. Sun rubuta jamb cikin ikon Allah ta cinye. Yanzu Post utme zata yi sai kuma jiran admission.

Ta mata alkawarin in shaa Allah za tayi hakan, sai suka yi sallama daga nan.

Ta karashe yinin ranar cikin kiraye-kirayen waya da gaisawa da yan'uwa, da Anty Lima suka yi waya ta karshe. Ta ajiye wayar kan center table a nutse, ta koma ta zauna tana bin wayar da kallo.

Rabon da suyi waya da Maigidan yau kwana biyu kenan. Ta kira shi har sau biyu, amma tarin uzirirrika sun hanashi iya daga wayar. Balle ya samu damar dawo mata da kiran. Don haka itama sai bata sanyawa ranta lallai-lallai sai ya daga wayar ba, ta koma gefe abinta. Shawara take yi da canki-cankar ko ta sake kiranshi ne? Daga karshe dai ta tashi taje tayi sallar la'asar.

Ta karashe yinin ranar akan abin sallah tana karatun Al Qur'ani da yin lazumi. Kasancewar karshen sa'ar ranar Juma'ah lokacine mai tsananin falala, Nadiya bata bari ya kufce mata ba tare da tayi addu'o'i ba.

Cikin kwanaki biyun da suka biyo baya ta fara fahimtar kamar Hajiya Ummah bata jin dadin jikinta.

Ta fara lura da rashin cin abinci da take yi yanzu, sannan ta rage yawan yin zirga-zirga kamar yadda ta saba. Yanwancin lokuta zaka sameta ne a kwance ko a shingide, ga shi cikin dan lokacin har ta fara rama a fuskarta. Ubangidan ya dawo ranar Asabar da yamma a gurguje, ya sake juyawa ranar Lahdi

tunda safe, don haka Nadiya bata tunanin ya kula da halin da Ummah din take ciki.

Ita kuma bata son shisshigi da tura kanta inda ba a yinta, ko don gudun kada a gwasaleta. Don haka ta rasa confidence din tambayar Ummah din ko bata da lafiya? Amma ta damu kwarai da gaske a cikin ranta.

Ranar Litinin ta tashi da azumi a bakinta kamar yadda ta saba. Ya jima da fada mata matsayarshi akan azuminta na nafila, yace ba zai hanata samun lada ba da neman yardar Allah. Amma dai bai amince mata da yin azumi ba ranar da take dashi, don kuwa bai yi mata alkawarin zai kauda kanshi daga gareta ba. Amma duk da cewa ranar girkinta ne, sai ta tashi da azuminta tunda dai ai baya gari.

Tayi sallama bangaren Ummah din da misalin karfe goma da rabi na safe, falon babu kowa sai TV da take ta aiki.

Tayi kokarin hayawa sama don su gaisa da Ummah, sai ta ganta tana kokarin saukowa.

A hankali take tako steps din tana sauka kamar marar laka. Daga yanayin tafiyar tata kadai ma zaka san cewa lallai bata da cikakkiyar lafiya. A kullum tafiyarta cike take da isa da takama mai dauke da wata irin haiba. Hajiya Ummah bata tafiyar salo-salo, kodayaushe zaka ji tana tafiya ne cike da sassarfa, mai dauke da nutsuwa da kuma alamun karfi. Amma yau duk babu wadannan a tattare da ita.

Data sauko, Nadiya ta tareta a tsakiyar falo tana gaisheta, ta amsa mata cikin yar karamar murya. Sai ta tsinci muryarta na tashi a cikin falon, tana furta, "Ummah ko ba kya jin dadi ne?"

Ba tare data gama tauna hakan a cikin ranta ba.

Tace mata, "lafiya lau" kawai, ta wuce kan dinning.

Ita kuma ta koma kan kujera ta zauna tana jan tasbahar hannunta cikin yin zikiri tana ambaton Allah. Lokaci zuwa lokaci kuma tana satar kallon Ummah data hada shayi baki ta sha. Ta ture kofin ta tashi, taje ta wuce Nadiya zata sake hawa sama.

Sai ga Hajiya Shukurah ta fado falon kamar wadda aka jefo. Ta ci kwalliya cikin doguwar riga ta leshi, don kyau kam tayi shi har ta gaji. Gashin nan an tamkeshi a keya da yake babu laifi tana da yalwar sumar kai, an daura kallabi a samanshi yadda ya fito da kyau. Dan gyalen nan ta yafo shi a kafadarta yadda kasan wata budurwace. Ita dai tasan ko Maryam ba zata yafa wannan dan gyalen ba.

Ganin Ummah tana kokarin hawa sama yasa ta karasa da dan saurinta tana kiranta, "Ummah! Ummah!!"

Sai ta juya tana kallonta a nutse. Ta ja tunga a gabanta kafin tace, "Ummah ina bukatar wasu kudine yanzu-yanzu, saboda abubuwan da muka saya jiya na kayan masarufi basu isa ba don haka dole yau sai mun kara sayen wasu."

Ta daga baki da kyar tace, "ki yiwa Zakari magana Shukurah."

Shukurah tace, "ok! Sannan jiya na fara miki maganar wata women leader da nake zargin fa kamar tana cin duga-duginmu ne. Ina bincike a kanta ne don in tabbatar, amma akwai yiwuwar tare take da kungiyar adawa, don naji daga bakin mutane da dama suna cewa bata aikin komai sai na zaginmu da yi mana batanci. Ina so ne idan har hakan ta faru, ki barta a hannuna. Don kuwa wallahi sai na sanyata yin dana sanin abinda tayi mana!"

Magana take ta zubawa, hankalinta ko bai kai ga yadda Ummah din take layi bane daga tsaye? Idanunta na budewa da kyar suna kara komawa su rufe. Nadiya tayi wuf ta tashi da sauri, nufinta ta karasa wajen ta fadawa Shukurah tayi hakuri da zancen wannan tukun, sai Ummah din ta samu zama ta huta.

Tana karasawa wajen, Ummah tana silalewa zata fadi, Nadiya tayi azamar tareta, suka tafi su duka suka fadi a kasan tiles din wajen. Allah Ya taimaka duk basu yi wata buguwa ba, amma dai da alamun Ummah ko dai ta suma, ko kuma tana kan hanya.

Tayi gaggawar tallabota tana kallon Shukurah da tayi tsaye cikin kidemewa tana kallonsu ta rasa me za tayi. Tace, "me kike jira ne?! Ki kira mana likita ko ki kama min ita mu kaita asibiti!"

Sannan ne ta zaro waya a jaka da sauri ta dannawa likitan gidan kira. Aka yi sa'a yana kusa dasu. Don haka yace ta bashi mintuna goma gashi nan.

Kafin zuwan nashi Nadiya ta sanyata a gaba tana yi mata firfitu da tofa mata duk addu'ar da taje bakinta. Shukurah tayi tsaye a kansu tana kaiwa da kawowa, lokaci zuwa lokaci ta kan kai dubanta da latsetsiyar agogo dake daure a tsintsiyar hannunta. A gefe daya kuma ga kiran waya da ake ta jera mata amma ta ki dagawa.

Cikin abinda bai gaza mintuna goman daya ambata ba kuwa sai gashi, ya shiga hannu rike da first aid kit. Ya dukufa a kanta yana aikinshi, sai gashi cikin dan kankanin lokaci ya samu kanta. Ta bude idanu tarr tana kallonsu, numfashinta dake hawa da sauka da sauri ya dawo ya daidaita. Sannan ne da taimakon Nadiya suka samu suka haura sama da ita zuwa dakinta. Inda anan ne ya hau dubata da kyau. Ya manna mata drip din ruwa da wasu allurai, sai gashi nan da nan ta yi barci.

Ya juya yana yiwa su Nadiya din bayani da suka yi cirko-cirko suna kallonshi kamar wasu zakaru,

"hawan jininta ne ya motsa, sai alamu na mura data kamata. Akwai sauran tests da zan je inyi yanzu, zan dauki jininta saboda akwai wasu abubuwa da nake tunani amma ba zan tabbatar ba har sai nayi mata test. Ta ci wani abu ne?"

Nadiya tace, "ehh, ta sha kofin shayi daya yanzu babu jimawa."

Yace, "Ok! Zan je inyi mata sauran test din zan dawo zuwa anjima, sai a kula sosai da ita kafin in dawo please. Ga magunguna na rubuta yanzu zan bada a kawosu, don haka idan ta farka a tabbata ta ci wani abun mai dan ruwa-ruwa, marar tsami kuma da yaji. Sannan a kiyaye yi mata amfani da gishiri a abinci. Allah Ya sauwake!"

Ya dauki sample din jinin nata tare da yi mata fatan samun lafiya kafin ya hada kan yan kayanshi ya wuce.

Nadiya ta bi Ummah da kallo ranta duk a jagule cike da tausayin yadda lokaci daya ta yi wani fiyat da ita.

Shukurah kuma ta mike tana makala wayarta a kunne, ta cewa Nadiya, "yauwa ni bari inje wajen taron da zamu je saboda ga mutane can sunyi gangami suna jirana."

Ta bita da kallo kamar tace, 'taron ba zai yi hakuri ba zuwa na wani lokaci ko kuma ki sanya wani ya wakilceki ba?' amma sai ta yiwa bakinta fada, ta bita da kallo kawai tana jinjina kai. Ta juya ta fita daga dakin tana magana da Zakari akan kudaden da take bukata a tura mata yanzu-yanzu.

Babu jimawa da fitarta aka kai magungunan da likita yace za a kai. Da yake kowanne da prescription dinshi a jiki, sai ta zauna ta dubasu a nutse. Ruwan da ake zubawa a hankali yake tafiya, don haka karewarshi ba yanzu ba.

Sai ta kara gyara dakin, kafin ta sauka kasa a nutse ta shiga kicin.

Lailah da sauran masu tayata aiki har sun nabba'a a falo zasu fara aikin abincin rana, sai ta fada musu yau kada suyi abinci da yawa a gidan saboda ba lallai a bukace shi ba.

Ta bude firiza ta fara ciro abubuwan da zata bukata na girki, ta kunna gas ta hau aiki.

Farfesun talo-talo tayi, ta dafeshi ya dahu luguf, ta wadatashi da kayan kamshi da yar daddawa saboda ta fahimci Ummah din tana son farfesu da daddawa. Sai ta fere irish potato shima tayi fatenshi. Ta zuba kayan lambu irinsu alayyahu, green beans, peas da danginsu kabeji a ciki. Ta kuma hada mata kunun gyada yadda take so.

Data gama ta sauye komi a cikin kwanuka masu kyau, ta jerasu a karamin trolley na abinci, ta garashi ta koma sama.

Ta samu ruwan ya kusa karewa, don haka ta dauro alwala ta nufi yin sallar Azzuhur. Tana gamawa ta cire mata ruwan tunda dai babu laifi ta iya wannan aikin.

Ta cigaba da zama anan dakin zaune akan sallaya da casbaharta tana lazumi har lokaci mai tsayi, Ummah din ta farka daga dogon barcin daya dauketa.

Sai ta karasa wajenta da sauri, tana jera mata sannu cike da kulawa da tausasawa. Kallonta take yi kamar Mama ce take a kwance a lokacin, saboda haka damuwarta ta kasa boyuwa.

Ta taimaka mata ta tashi zaune tare da jingina mata filo a bayanta yadda zata ji dadin zama. Sai ta gara trolley dinnan gabanta tana fada ga abubuwan data dafa saboda likita yace a bata abu mai dan ruwa idan ta farka, wanne zata ci?

Tace ta fara bata kunu. Ta zuba mata shi a kofi mai dan yawa, ta mika mata ta amsa tana sha a hankali. Sai ta janyo bowl ta zubo farfesun nan shima ta mika mata, ta amshi kofin kunun da ta sha rabi.

Ta girgiza kai, "bari haka nan Nadiya, na koshi."

Sai ta dan marairaice, tace, "Ummah kiyi hakuri ko kadan ne ki dan sha haka nan. Naga magungunan da aka rubuta fa suna da karfi, idan kika ce zaki dinga shan su hakanan kuma babu abinci sai kiga suna daukarki!"

Tace, "zuciyata ce take tashi ai sosai, ji nake kamar zanyi amai."

Sai tace, "to bari in zo."

Ta sauka kasa da sauri, ta shige kicin ta samu danyar citta ta bare bayanta ta markada a blender nan da nan, ta matse lemon tsami a juicer ta hadesu waje daya ta tace ta juye a cikin wani madaidaicin jug na glass, ta zuba zuma da kankara ta motsa da kyau ta koma sama din.

Tace mata, "ga wannan juice din, idan kina sha in shaa Allah zai rage miki tashin zuciyar."

Ta sake mika mata bowl din, wannan karon ta amsa babu musu ta fara ci, ita kuma ta tsiyaya mata lemun a kofi ta ajiye mata. Tana cin farfesun tana korawa da lemun, sai nan da nan ta cinyeshi duka. Nadiya taji dadi sosai, ta dauko magungunan tana balla tana bata tana sha da ruwa har ta gama sha duka. Ta kwashi yan mintuna a zaunen kafin Nadiya ta shawarceta data koma ta kwanta saboda alamun gajiya daya fara bayyana a jikinta. Sai tace mata bari ta fara lallabawa tayi sallah tukun.

Ta taimaka mata har zuwa bayi ta dauro alwala, ta shimfida mata abin sallah tayi daga zaune. Sannan ne ta koma ta kwanta. Babu jimawa barci ya sake daukarta.

Sam-sam ta manta da wata aba wai ita waya data baro a jikin caji a bangarenta da zata fito, balle tayi tunanin sanar da Babangidan halin da Ummah take ciki.

Tana kokarin janye kayayyakin abincin ne taji an turo kofa, wannan unique kamshin nashi ya fara bazowa cikin dakin kafin ya shigo gabadayanshi cikin farar kaftan, kanshi babu hula.

37.

Ta juya tana kallonshi a nutse, shi kam kai tsaye gefen gadon Hajiya Ummah ya wuce ya zauna. Ya kama hannunta ya ninke a cikin hannuwanshi damuwar shi karara tana bayyana.

Sai ta dan kara tausasa muryarta tana mai yi mishi sannu da zuwa, ya amsa a tausashe yana kara kallonta cikin wani yanayi na daban.

"Lafiya lau Nadiya, ya mai jikin?"

A hakan sai taji dan dadi a ranta, ya alakantata da Ummah har yana tambayarta jikinta. Lallai zuciya da bure-bure. Sai ta samu kanta da dan murmusawa ba tare da yasan dalilin hakan ba, tace, "jiki da sauki Alhamdulillah. An cire mata drip din yanzu babu jimawa, kuma ta ci abinci ta sha magani har ma tayi sallah kafin ta kwanta din."

Ya jinjina kai, "ok, sannunki da kokari. Nima likitan ne ya kira ni yake fada min halin da ake ciki. Luckily bamu yi nisa da Kadunar ba sosai."

Ya kara mayar da hankalinshi ga Ummah din dai, ita kuma sai ta fara gara trolley din da tayi niyar fita dashi.

Ya dakatar da ita ta hanyar cewa, "akwai sauran abincin ne?"

Tace mishi, "eh, akwai."

Ya kuwa gyara zama yana kallonta, "to zubo min ki gani."

Da alama dai yunwa ce ya kwaso ba karama ba.

Ta juye mishi duka sauran abincin ta ajiye mishi. Sai ta sauka kasa ta mayar da kayan kicin. Kafin ta gama abinda zata yi ta koma saman, tuni har ya gama cinyewa tas. Ta kalleshi da dan mamaki a ranta da kuma tausayi. Bata dai ce mishi komi ba sai kwanukan data kwashe.

Tace mishi zata je falon sama ta dan shingida haka nan kafin lokacin la'asar yayi. Idan Ummah din ta farka yayi mata magana. Ta juya ta fita da kwanukan hannunta. Gajiya da rashin barci da kuzari har sun fara tambayarta, ko don ta jima bata yi azumin ba? Sai kawai ta ajiye kwanukan anan sama, ta samu doguwar kujera mai laushi ta kwanta akai.

Babu jimawa barci ya kwasheta. Bata san lokacin daya fito daga dakin Ummah din ba, ya maida mata kofar ya rufe kafin ya karasa gareta a hankali. Yayi durkuso a gabanta yana karewa yadda take barcin nata a nutse kamar wata baby.

Ya shagala a kallon nata har ya fara manta a inda suke. Komai na Nadiya na daban ne. Halayenta daban suke da na sauran mutane, haka dabi'unta na daban ne da ba kasafai aka cika samunsu a cikin zamanin wannan ba.

Kasa ya sauka yana tambayar Lailah ina Ammar? Ta sanar mishi sai karfe hudu suke dawowa yanzu saboda an jima da yi musu canjin aji. Shi a karan kanshi sai yaji yar kunya ta kamashi, saboda tunda harkar siyasar nan ta tashi, ya rage ba yaron da al'amuranshi lokacinshi da hankalinshi. Kai ba yaron kadai ba, har iyalinshi da shi a karan kanshi ma. Sai kawai ya juya ya koma saman, yana fada mata kada a bari kowa ya hau saman nan har sai an sanar dashi, saboda Ummah bata jin dadi. Ta amsa mishi da 'to, Yallabai!'

Hannu ya sanya yana shafa fuskarta dake smooth sosai, Nadiya ba dai kula da iya kyalkyale jiki ba. Koda bata yi kwalliya ta sanya su foundation da tarkacen concealer ba, a kullum zaka samu jikinta laushi tubus, yana santsi da wani asirtaccen kamshi da yake hargitsa kwanyar mutum.

Ta fara bude idanunta a hankali, ganin shine a durkushe a gabanta, sai tayi tunanin ko Ummah ce ta farka. Ta tashi da sauri tana lalubar gyalenta daya salube ya fadi kasa, "Ummah din har ta tashi ne?"

Hannu ya sanya da sauri ya zaunar da ita daga mikewar da take shirin yi, yace, "wannan farkawarta ba yanzu ba. Don akwai magungunan sanya barci a magungunanta."

Ta dan ajiye zuciya a hankali, "oh!! Ta kuma koma ta zauna tana kallonshi kasa-kasa.

Wani irin murmushi ya saki, Nadiya da gulmarta! Kallon ma ba za ayi mishi yasan ana kallonshi ba sai dai a dinga satar kallonshi.

Yace, "idan kin yaba kwalliyar tawa ne, baki zaki daga da kyau ki yabani din ai in san na burgeki, ba wai ki dinga satar kallona ba kina wani basarwa!"

Ta ji kunyar kamata din da yayi tana kallonshi, sai ta dauke kanta da sauri. Shi kuwa ya kara sa hannu ya juyo da fuskarta suna kallon juna, "to wai shi kallon nawa haramun ne Nadiya? Ko kuma shi shakulatin-bangaro da kike yi da ni da al'amurana ladarsu kike samu?!"

A ranta tace, 'to! Yau kuma?!'

Amma a fili sai ta dan kalleshi a kaikaice, wani kallo daya tsirga mishi tun daga tsakiyar kanshi har tafin kafarshi, leaving goosebumps a duka sassan jikinshi.

Ta buda baki da kyar tace, "ni kuma me nayi maka?"

Bata san tuni ta gama kassara mishi gabbai da wannan kallon nata ba. Ya hau kan kujerar da kyau ya jata cikin jikinshi. Wannan kamshi nata da babu abinda yake so da marmari kamarshi yana mishi oyoyo, sai kawai fara nuna ma'anar kalaman nashi a aikace ba tare daya furta ba.

Ko daga urgency na yadda yake gudanar da al'amuranshi yau, tasan cewa ba karamin kewarta yayi ba. A kuma matukar bukace yake.

Ta fara kici-kici da kokarin janye jikinta gabanta yana faduwa a tsorace ganin cewa a saman bangaren Ummah suke. Ga azuminta dake makale a bakinta.

Ya kalleta da wasu idanu da suka fara canzawa, tsabar mutuwar da jikinshi yayi ma ya kasa iya daga baki ya tambayeta dalili. Musamman da yaga kwalla tana taruwa a cikin idanunta.

Sai itace tace cikin rawar murya, "don Allah kayi hakuri ka rufa min asiri Abban Ammar. Ka manta a inda muke ne?"

Kawai ya kara janyota, ya cigaba da bin fatar ilahirin wuyanta da kafadarta da butterfly kisses a yunwace, wani abu da Nadiya ta gama fahimtar

weakness dinshi ne. Shi yasa ta himmantu da gyaran wuyanta sosai da bayan kunnenta. Tana amfani da sabulai masu kyau wajen wanke fatar jikinta wadanda yawanci ma ita take hadasu da kanta da sinadarai masu gyaran fata. Haka kullum ba ka raba wajen da kamshin nau'in turaruka masu kyau, irin nasu na asalin Bare-bare da tuni har ya gama kama fatar jikinta. Ta hakane a kodayaushe, a kowane hali ya sameta, kamshin nan dai nata yana nan.

Bai fasa abinda yake yi ba, yace mata, "in dai don Ummah ne, ba yanzu zata tashi ba!"

Sai tayi kundunbala tace, "azumin tadauwu'i fa nake yi!"

Ya dan dakata yana kallonta, "it has nothing to do with me Nadiya, ai na fada miki matsayata akan hakan ko?"

Tayi rau-rau da idanu, "to kayi hakuri don Allah, kaga ai baka nan ne shi yasa."

Ya jinjina kai, humming softly kamar ya yarda da abinda take fada, sai kuma ya cigaba da gudanar da abubuwanshi alamun dai ba zai yarda din ba dai.

Sai kawai ta saki wani irin kuka a tausashe, tana shessheka a hankali hawaye na diga a kan fuskarta zuwa jikinshi, dis-dis. Da dai tasan abinda kukan nan nata ke haddasa mishi, to da ko da kudi ba zata yi shi ba. A dai halin da yake ciki.

Tace mishi, "to kuma a bangaren na Ummah? Kana kallon tsakaninmu da ita bai wuce wani taki na azo a gani ba, anan din?"

Wannan sai ya dan dakatar dashi, ya zuba mata shanyayyun idanunshi, "hakane kuma gaskiya. To taso mu koma can wajenki kafin ta tashi. Kinga dai ai bata jima da kwanciya ba."

Ta wawuri gyalenta ta dake mayarwa ta rufe kanta, ta gyara zip din rigarta da aka zuge shima. Ta fara goge hawayenta kafin cikin tausasa murya, tace, "to ka fara yin gaba dai sai in biyoka a baya!'

Ya tashi yana daukar rigarshi da itama yayi wancakali da ita, ya sanyata a jikinshi duk tayi squeezing kamar an cirota a bakin kura. Yace mata, "to kiyi sauri fa!"

Ya juya ya fita da sassarfa, tana binshi da kallo har ya sauka. Bata san lokacin da murmushi ya subuce mata ba bayan ya sauka din. Lallai yau da drama a gidan nan idan ya gano aika-aikar da take shirin aikata mishi.

Ta shige dakin Ummah da har lokacin barcinta kawai take shaka, oblivious to all abubuwan dake faruwa. Ta shige toilet dinta ta kulle har da karawa da sakata duk da dai tasan cewa ai ba zai zo har nan yace sai ta je ta karfi ba.

Shi kam zuwa lokacin daya fahimci Nadiya dai kafa ta bashi ya wuce falau, tuni wasu masallatan har an fara kiran sallah.

Ya daure yayi sallah din, kai tsaye daga masallaci sashen Ummah din yayi niyar wucewa, ko a kafada ne sai sabota. Abinda ya kudurta a ranshi kenan. Sai suka yi clashing da motar da taje dauko Ammar daga makaranta, don haka ya dakata har yaron ya fito hannunshi rike da jakarshi da food flask dinshi. Ya daukeshi a hannunshi suka wuce tare, a ranshi yana fadin idan ya damketa a hannunshi, sai ta ba yan garin Maiduguri labari.

Suka zaune a gefen gadon Ummah bayan itama ta kammala sallah. Da taga shigarsu dakin sai ta tashi tsaye, ta mayar da hankalinta ga Ammar daya ruga wajenta ta tareshi da murna itama. Duk yadda yaso su hada idanu ta ki bashi damar hakan.

Daga karshe ma sai ta kama hannunshi suka fita don ta shiryashi da gaggawa ya wuce Islamiya.

Ya bisu da kallo, duk yadda yaso yaji bacin ran abinda ta aikata mishi, ya kasa ji. Yayi murmushi jin tambayar da Ammar yake jefa mata, 'wai gobe ma ita zata hada mishi lunch flask dinshi? saboda yau har saura yayi, kuma tare da abokanshi suka co suna ta cewa Mamanshi ta iya girki!'

Ita kuma tana dariya tana ce mishi zata hada mishi din.

Sai wajajen karfe biyar ta farka, shi da kanshi ya taimaka mata tayi sallah. Nadiya ta kai mata fura da ta sha nono ta sha da kyau. Cikin ikon Allah tuni har ta fara girgijewa. Amma ko bayan fitar Babangidan don gabatar da wasu kiraye-kirayen waya, kasa tafiya tayi ta barta ita kadai. Duk inda zata motsa to idanun Nadiya suna biye da ita, tana tsoron kada jiri ya dauketa ta sake faduwa. Ita a karan kanta Ummah din sai data fahimci tsoron Nadiya din. Tace mata, "wai ba azumi kike yi bane ba Nadiya? Ba zaki je kiyi shirin shan ruwa bane?"

Sai tace mata, kanta a kasa, "Ummah ai ba wasu abubuwa ne nake hadawa ba dama na shan ruwan. Idan na tashi zan dama kunu kawai!"

Don haka ta kyaleta.

Tana falo akan dinning tana shan ruwa, kunun tsamiya ne ta dama kadai take sha, sai fruits da aka yanka mata sun dau sanyi.

Shukurah ta shigo falon a lokacin, da alama ta dan jima da dawowa. Don ta canza shiga daga ta dazu da safe zuwa wata doguwar rigar cotton din material ruwan makuba.

Ta ja kujera ta zauna tana kokarin zuba abincin dare da har an gama shiryawa, yanzu an samu cigaba tunda tana zama akan dinning idan Nadiya tana nan ta ci abinci, ba kamar da ba.

Yadda bata yi mata magana ba, haka itama Nadiya bata yi mata magana ba. Tunda ai ko a ka'ida ma ai ita da ta tarar ya kamata ta fara yiwa sallama.

Ta zuba white rice and beans, da sauce din kayan miya da coleslaw. Ta ci abincinta tayi nak, ta kara da lemu mai sanyi. Sannan ta ja kujera, sauran abincin data bari ko rufewa bata yi ba ta barshi anan. Har flask din data debi abincin a ciki haka ta barshi bata rufe ba, sai Nadiya dince ta rufe don kada ya huce.

Ta haye sama da alama Ummah zata gaisar.

Ita dai ta zauna anan falo din har aka yi Isha'i tayi, sannan ne ta haura saman domin ta yiwa Ummah sai da safe, jikinta hutu yake bukata sosai da sosai.

A falo ma ta samu Ummah din zaune akan kujera, sauran furar data dama mata dazu a gabanta a cikin bowl mai fadi tana sha.

Ta duka a gefenta, yayinda Shukurah take zaune a kujerar kusa da ita tana aikin latse-latsen waya abinta, ga cingam nan a bakinta tana ta aikin tauna kas-kas! kamar yakin duniya.

Tace mata, "Ummah kina bukatar wani abu ne? Zan je in kwanta yanzu."

Tace mata, "babu abinda nake bukata Nadiya, jikin nawa ai ya warware Alhamdulillah, zan iya yiwa kaina komi yanzu. Kije ji huta da kyau tunda yau baki samu yin barcin ba. Allah Yayi miki albarka!"

Kawai sai taji wasu irin hawaye sun cika mata idanu. Bata taba zaton jin wannan kalmar daga bakinta ba. Mahaifinsu dai shi dama ba ma'abocin sanya albarka bane, haka Madam. Ita kam zata ma iya cewa tunda take da Madam din bata taba jin ta sanya mata albarka ba. Wannan sai Mama da kuma Dada. Sai kuwa Babangida. Shi wannan kullum cikin sanyawar albarkarshi take, duk kankanin abu idan ta mishi ya burgeshi, sai ya kalleta yace 'Allah Yayi miki albarka Nadiya!' Shi yasa take ta dagewa da zage dantsen kyautata mishi koda bata son yin abu kuwa, idan har ta kula yana so to kuwa itama zata so shi.

Muryarta tayi nauyi, ta kasa amsawa da 'ameen' sai kai kawai data iya gyada mata. Ta tashi cikin wata irin mutuwar jiki tace mata, "sai da Ummah, Allah Ya kara lafiya!"

Tace mata, "sai da safe Nadiya!"

Data sauka kasa sai da taji kamar ta kwala ihu don murna. Ta dai daure ta fuske ta tunkari kofar fita.

Tana kokarin bude kofa ta fita, shi kuma yana turo kofar. Tayi kokarin ja da baya da sauri, sai kafarta ta dan gurde ta yi baya zata fadi. Ya sanya hannu da sauri ya tarota cikin jikinshi, yace mata, "what's with you da kai min karo duk sanda zamu hadu ne Nadiya?"

Ta janye daga jikin nashi tana turo baki, "dadinta dai kullum kaine kake ture ni, ka zubar min da abu a jiki, ko ka fasa min waya, ko kuma kayi kokarin kayar da ni!"

Yayi murmushinshi mai kayatarwa, "ni me yasa baki taba tambayata illar da kike min idan kin kai min karon ba?"

Ta dan bude idanu tar akanshi, tace, "ni illar me zan maka ne?"

Ya dan sumbaci bakinta, "yanzu dai barka da shan ruwa. Kije ki shirya Nadiya, yau har dakina zaki zo ki sameni. Bashin da kika ci yau sai kin biyani da tsada!"

Tayi yar dariya ta bi ta gefenshi ta karasa fita. Sannan shima ya karasa shiga falon domin ya duba Ummah.

38.

Ba tayi tunanin da gaske yake da zancen taje dakinshi ta sameshi ba, tayi zamanta a daki bayan ta gama shirin kwanciya. Shiru-shiru lokaci ya ja bai je ba, kuma bai tuntubeta ba ko a waya. Tana tunanin kila ko wani aikine ya rikeshi ko wani abu, barci yayi awon gaba da ita.

Ba ita ta farka ba sai da Asubahi, ta sauka daga kan gadon da kyar, gabadaya jikinta yayi wani irin nauyi ji take kamar wata tirela ta bi ta kanta.

Ta duba wayarta da taga tana blinking alamun an bar mata sako ko missed call. Tana dagawa ta ga sakon daga shi ne, 'kin kyauta!' kadai ya tura mata. Amma sai da taji jikinta yayi kamar an watsa mata ruwan sanyi saboda yadda sakon ya daketa.

A ranta taji babu dadi, kuma tasan bata kyauta ba ko kadan. Ya daga baki da kanshi yace mata ga abinda za ayi amma ta mayar da abun wasa! Anya ta kyauta? Ta tura mishi, 'I'm so sorry dear, barcine ya daukeni'

Gwanda ta tsaya a barci dinne ya saceta akan gaskiyar abinda ya faru. Ta kudira a ranta idan sun hadu zata bashi hakuri da kyau ta fatar baki, kafin sauran su biyo baya.

Tayi sallah ta sake komawa ta kwanta. Sai wajen karfe takwas ta farka. Ta watsa ruwan dumi a jikinta ta dan ji karfi sosai, ta zura riga da siket na atamfa a jikinta, tayi daurin kallabi simple ta fita. Kai tsaye sashenshi ta wuce da niyar bashi hakurin da tayi niyya. Sai ta samu bangaren nashi a rufe, tasan babu mamaki yana can wajen Ummah. Sai ta wuce can.

A can din kuwa ta sameshi, a zaune a gabanta a falon kasa suna hirarsu a nutse, da alama jikin nata ya samu sauki sosai. Itama ta duka a gefenshi ta gaishe da Ummah din kafin shima ta gaida shi, ya kalleta sau daya, ya amsa a tsaitsaye, ya kuma mayar da hankalinshi ga Ummah din ba tare daya kara tankata ba. Duk da cewa dama a gaban Ummah din bai cika yi mata zakalkalewar daya saba yi mata ba, amma ko yaya ya kan amsa mata gaisuwa da salama da kuma taushi a tattare dashi. Sai jikinta yayi sanyi ganin yadda ya amsa ta din yanzu cikin daure fuska da harhadewa.

Sai ta mayar da kanta ga Ummah tana tambayarta, "ya karin karfin jiki?"

Ummah ta amsata, "jiki da sauki Alhamdulillah Nadiya."

Tace, "kin sha magani ne kam?"

Tace, "ehh, yanzu na sha."

Itama Ummah yadda take amsa mata tambayar tana wani ciccijewa da dan yatsine fuska, sai abin duk yayi mata wani iri. Taji zama a wajen dai kamar

she's not welcomed. Don haka ta koma kasa ta zuba abinci tana tsakura ba don tana jin dadin abincin ba.

Tana nan a zaune ya sauko kasa cikin takun nan nashi na nutsuwa da kamala.

Ganin yana shirin fita ne yasa ta tashi da sauri ta tareshi, tace, "Abban Ammar kayi hakuri don Allah!"

Ya tsaya yana kallonta, "hakurin me kike bani ne Nadiya? Kinyi min wani laifi ne?"

Yayi tambayar cikin wani kwantaccen bacin rai. Sai tayi kasa da kai, ta fara motsa baki cikin rashin sanin abin cewa. Da kyar ta iya cewa, "uhmm... Dama jiyan... Barci ne ya daukeni shi yasa."

Ya dan tabe baki, "eh, ai ban ce wani abu ba dama, or did I complain? Shi mutum dama ai sai ka damu dashi da al'amuranshi sannan ne baka mantawa da shi ko kuma sanyashi as a priority. Excuse me please ina da wajen zuwa!"

Ya zagayeta ya fita daga falon. Ta bishi da kallo rai a jagule, lallai yau ta tsokano ran manya.

Ganin har a wajen Ummah dinma dai babu wajen zama, sai ta lallaba ta koma dakinta.

Ta zauna a gefen gadonta tare da bude wayarta, ta rubuta message dogo mai cike da alamu na ban hakuri da neman afuwa ta tura mishi. Tana fatan Allah Ya sassauto da wannan fushi nashi.

Bata yi tunanin fushin na shi zai dugunzuma mata hankali har haka ba, sai taji gabadaya gidan ma yana wani sire mata daga rai.

Amma har aka kwashe awanni masu dama bata ga amsa daga gareshi ba. Sai kawai ta shiga kicin dinta, ta fara hada mishi lafiyayyen abinci mai kyau, watakila ta samu ta janyoshi da wannan.

Tana nan sashen nata har wajen karfe biyu cikin taraddadi da tunanin ya zata yi? Don kuwa ko keyar Babangida bata kara gani ba.

Yadda ya saba kuwa a duk ranar girkinta in dai yana gari to yana fita sallar Azzuhur wajenta zai nufa ya ci abinci da kyau, watarana ma anan zai shantake har bayan la'asar don sau tari shi yake jansu sallar la'asar din. Idan kuma yasan ma ba zai samu damar cin abincin ba to sai yayi mata waya ya fada mata don kada ta sanya girkin da shi.

Ta sake komawa bangaren Ummah domin taga ko yana can, ta kuma duba ko Ummah din itama ta sha maganinta na rana.

Kafin ta karasa taga an bude gate, aka turo hancin bakar Hummer Jeep da Babangida din ke fita a cikinta, tasan babu mamaki shine. Don haka taja tunga, tana jiran ya fito ya sameta, suyi duk wadda zasu yi ita dashi kawai su wuce wajen.

Security dake tare dashi ya fita daga gaban mota ya bude gidan baya, kamar yadda tayi kintace din, shi dinne ya zuro kafa ya fito. Sai kuma ta tsaya da mamaki ganin an bude dayan gefen da yake, wata mata ta fito hannunta jaye da hannun wata yarinya karama, amma zata girmi Ammar. Suka jero suna tafiya ita da shi din suna hirarsu, direba yana binsu a baya jaye da tarin trolleys kusan guda uku.

Sai dai tun kafin su karasa inda take, ranta ya gama bata wannan Mami ce, Sumayya kanwar Hajiya Ummah. Wadda duk a cikin danginsu bata tunanin wani ya sake ganinta tun bayan barinsu gida bayan rasuwar mahaifiyarsu. Kamanninsu ita da Ummah din sak, yadda kasan wasu identical twins. Abinda ya bambantasu da juna kawai shine ita Ummah zata nunawa Mami shekaru ne kawai da yanayin girman jiki.

Nadiya tana jin zancenta a bakin Babangida sosai, sai dai ko a hoto bata taba ganinta ba. Ya dai sha fada mata cewa a Jordan take da zama ita da mijinta

da 'ya'yanta, yana kuma cewa zai hadasu koda ta waya ne su dinga magana amma kuma sai Allah bai taba bashi dama da ikon yin hakan ba.

Har suka karasa kusa da ita tana tsilla-tsilla da tunanin wace irin tarba zata yi mata ne? Tunda ga matakin da suke da Hajiya Ummah kadai ma wadda har zuwa lokacin bata gama sakar mata jiki ba, ita kuma ko da wacce ta zo?

Mami ta tsaya a gabanta tana dan murmushi tana duban inda Babangida din yake, tace mishi, "ko da ban tambaya ba dai wannan ce Nadiya ko?"

Ya ki bata amsa sai kafada daya daga mata, ganin haka ita sai ta rusuna, tace mata, "Mami sannu da zuwa, ya hanya?"

Kawai sai ji tayi ta rungumota kai tsaye tana yar dariya, "come on Daughter, kada kiyi mun gaisuwar kauyawa mana! Ni da kike ganina ba sarakuta ko jika da kaka zanyi da ke ba, 'ya ce a wajena kinji?"

Sai ta samu kanta da dan murmusawa cikin samun salamar zuci, don kuwa bata san ya zata yi ba idan ta mata karbar wasa-re-re irin na Ummah.

Ta kama hannun yarinyar dake tattare da ita ta bi bayansu ita da Babangida din inda suke tattaunawa game da rashin lafiyar Hajiya Ummah din da kuma sakamakon da likita ya fitar a ranar. Sai a lokacin take jin cewa ciwon sugar ne ta fara kamuwa da shi duk da dai ya fara shigarta ne kawai bai yi karfi ba, sai kuma jininta da ya hau sosai, ga kuma karin ulcer. A ranta take jinjina wannan abu, da kuma kara yarda da zancen Mama can wani lokaci da take ce mata ai yanzu Ulcer ba cutar yunwa bace, cutar zamani ce kawai.

Suka shiga falon a haka, suka samu Hajiya Ummah a kasan bene a tsaye, da alamu su take jira. Shukurah kuma tana zaune a tsakiyar falo akan kujera tana kallo.

Mami da saurinta ta karasa wajen Hajiya Ummah ta rungumota cike da doki da murna, sai Ummah din ce ta dinga kokarin janyeta daga jikinta tana mata fadan, "Ni kada ki kada ni don Allah! Wai ke ba zaki taba girma bane Sumayyah? Kullum ke baki taba yin abu na girmanki da shekarunki?"

Mami tayi yar dariya cike da farinciki, tace, "haba Ummanmu? Kina ganin tsawon lokacin dana dauka ba tare dana ganki ba, yanzu kuma sai ki hanani yin murna?"

Tace mata, "ke dai kika sani. Taho muje dakinki dai tukun kuyi wanka ku huta sai ku ci abinci."

Shukurah ta karasa wajen nasu itama tana yiwa Mami sannu da zuwa, "Mami sannu fa... Kun iso lafiya? Ya hanya?"

Mami din ta amsa, kafin suka runkuta zuwa sama inda aka gyarawa Mami din dakin da take sauka. Ita dai data samu ta rakata dakin taga ta shiga wanka, sai ta silale ta bi sawun Babangida daya sauka kasa din yana ce musu zai je ne ya dan kwanta zuwa la'asar. Itama Mami din tace mishi ai da ta fito wanka ko abinci ba zasu ci ba ita da Farida, diyarta, kwanciyar zata yi saboda sun kwaso gajiya sosai, kuma sun ci abinci a jirgi.

Ta wuce ta gaban Shukurah da tun bayan gaisawarsu da Mami ta koma inda take zaune ta zauna. Harara ta watsawa Nadiya din data bata baya, hakan duk bai isheta ba sai data kara da jan tsaki. Kiri-kiri yarinyar nema take yi ta dinga shigar mata hanci da kudundune. Ta fara bin mutanen gidan tana shige musu jiki sai kace wata mai aiki da asiri. Da can tana zaman-zamanta, hankalinta kwance. Duk abinda tayi a gidan dai-dai ne, babu mai daga kai ya kalleta balle a kai ga zancen ce mata ba haka ba. Amma yanzu daga zuwan wannan figaggar abar, wai ita ce har aka fara comparing dinta da ita. Ita kam me yayi ma hadinta da ita ne? Hanyar jirgi daban, ta mota daban. Ita dai ba zata iya cusa kanta jikin mutane ba, mutane ita suke cusawa kai suna kokari da son ta mu'amalancesu. Balle akai ga wani kula da dora dawainiyar da ba tata ba. Ita duka yaushe ma ta fara daukar dawainiyar kanta da kanta? Ita da tun tasowarta a gidansu bata san tayi abu da kanta ba sai dai ayi mata!

Ta sake jan wani tsakin tuno da yadda jiya wai Habib yake tuhumarta da tafiya yawon kamfen alhalin Ummah na kwance babu lafiya. Har da fada mata cewa da mahaifiyarta ce a wannan halin ita zata je ne? Ya kuma kara da fada mata wai ta duba dai yadda Nadiya ta dinga nan-nan da ita da kula da ita a jiyan. Wannan abu ya haddasa musu hawa sama shi da ita a gaban Ummah, don kuwa rufe ido tayi tace mishi kada ya sake hada sunanta dana

Nadiya a cikin kalma daya, don kuwa ta fi karfinta. Wutsiyar rakumi tayi nesa da kasa. Kuma kamfen din da yake ihun taje, tana cewa dai don shi taje da kuma Ummah din? Shi kuwa budar bakinshi sai yace mata ta dai kara nazari, don kuwa yasan don kanta take yi. Idan ma don shi dinne, shi ya taba daga baki ne yace yana bukatarta?

Sai da Ummah ta gaji da fadan nasu ne sannan tace musu duk su tashi su bar mata wajen ta sallamesu, sannan ne suka bari.

Ta sake jan wani tsakin a karo na barkatai. Tana so ta ji zafin maganganun daya dankara mata ma amma abubuwan dake gabanta suna janye hankalinta. Don haka ta watsar da komi, a ranta tana fadin idan ta jajirce da kyau, ta samu da taimakonta Habib ya ciwo kujerar Gwamnan Kaduna, ai wannan ma kadai ya isa ya sayo mata girma da mutunci a wajenshi da na Mami din tashi data kula tun ba yau ba dama ba sonta da Babangida din take yi ba. Bata ma raba dayan-biyu akan cewa da sanya hannunta aka auro mai wancan farin irin na yayan zabiya da idanu sai kace na yan maye! Ita kadai dai take ta wannan gulmar a cikin ranta.

✿✿✧✧✿✿

Can ta iskoshi a dakinshi tsaye a gaban mirror, har ya cire rigar jikinshi ya rage sai farar singileti kawai daya bari.

Kallo daya yayi mata tun shigarta dakin, ya dauke kai ya cigaba da maganar da yake yi a waya dake manne a kunnenshi.

Ta maida kofar dakin ta rufe tare da karasawa inda yake, kafarta tana nutsewa cikin tattausan carpet yadda kasan katifa. Dakin na Babangida madaidaicine dai-dai shi dai, lafiyayyun Turkish Royal set ne royal blue a jere a dakin. Kusan komi na dakin royal blue ne sai su labulaye da fentin dakin da suka kasance grey.

Ta amshi karamin comb a hannunshi da yake taje kanshi dashi, ta fara taje mishi sumar da kanta har zuwa sajenshi. A ranta take cewa 'wai mutumin da zai kwanta ne yake fama da gyaran suma' amma dai ta kame bakinta bata ce komi ba.

Har ta gama, ta dauki mai ta shafa mishi a sumar, wayarshi yake yi abinshi, yana ta yaryara yaren turanci tare da wanda yake yin wayar kai kace rainon kasar Amurka ne.

Ganin baya da niyyar barin wayar tashi, sai ta zagaya ta bayanshi ta rungumoshi da kyau. Ta kai hannuwanta saman faffadan kirjinshi tana shafawa a hankali cikin yanayi na son daukar hankalinshi.

Ta kuwa dauki hankalin, don kuwa tun yana iya fahimtar me ake fada mishi ta daya bangaren da kokarin jan zancen nasu, har yazo ya fara rasa zaren kamawa. Don kuwa Nadiya aikin damalmala mishi lissafi kawai take yi.

Babu shiri yayi sallama da wanda suke wayar, ya ajiye wayar tare da kama hannunta da ke ta yawo a ko'ina na sassan kirjinshi. Idan ya kyaleta tuni zata sanya ya manta da zancen fushin da yake yi da ita.

Ta zagaya tana kallonshi tana wani lankwashe murya da kai gefe daya, "haba Yallabai, Abban Ammar, ango a wajen Shukurah da Nadiya! Babangidan Ummah ikon Allah! Laifin nawa yayi girman da ba za a iya yafe min shi bane kuma?!"

39.

Kirarin nata ya so ya bashi dariya, amma sai ya fuske ya ki bari ko dan murmushine ya bayyana a fuskarshi. Don ya fuskanci dai idan ba ta haka ba, Nadiya ba a samo kanta ta sauki.

Ya janyeta daga jikinshi, ya wuce gefen gado ya zauna abinshi, tana biye da shi a baya itama.

Yace, "wane irin ango kike magana? Dama haka anguna suke ne? Suna bibiyar matansu suna yakicesu, wai har suna mantawa da zuwa kiran angunan nasu barci ya daukesu? Wannan ai ba ango bane, wanda ba a so ne!"

Tayi murmushi, ita rigimar tashi ma dariya ta koma bata kuma. Tace, "to ai nace kayi hakuri fa, kuma in Allah Ya yarda hakan ba zata sake faruwa ba."

Sai ya gyara zamanshi da kyau yana kallonta a nutse, yace, "ai dama tun ba yau ba tara ki nake yi in ga iyaka gudun ruwanki Nadiya. Shi kenan ni kullum bini-bini ina tafe kan hanyar dakinki wai na zo kwana, saboda nine makale mata ko me? Ko kuwa don na fi ki son yin abin? Shikenan ke dai in an zo inda kike kin iya ki dinga lankwashewa mutane murya da kanne idanu, amma in ba a zo inda kike ba kuma dai ko oho! Ai ba haka sauran mata suke yiwa mazajensu ba."

Tayi kasa da kanta cike da jin kunya, tace, "to shikenan ni kuma sai dai a dinga ganina ina tafe a sashenka kullum? Wannan abin kunyar har ina!"

Aikuwa ya jefa mata harara da duka idanunshi, "ok! Abin kunya ne kenan don ki faranta ran mijinki?"

Ganin yadda yake neman juya maganar sai tayi saurin ce mishi, "a'ah! Kayi hakuri na daina."

A lokacin dai zama yayi ya mata bayani daki-daki, duk wani abu da yasan tana mishi wanda baya so, kamar dai rashin zuwa kwana dakin nan nashi, da yadda yake fadin bata fifita al'amuran da suka shafeshi. Har gyaran dakinshi

a ranar sai daya lankaya mata ya koma kanta. Tace taji ta amsa duka, zata gyara inda ta kuskure.

Sai ya ja ta jikinshi ya fara kokarin hade bakinsu waje daya, tunda dai ya gama neman fadan da ita yanzu.

Ta janye tana kallonshi, "abinci fa yana bangarena na ajiye, kada ya huce."

Yace, "bar zancen wannan abincin yanzu Nadiya!"

Ya mata rumfa da jikinshi yana fanshe bashin da yace sai ta biyashi. Ta kuwa biyashi da tsada sosai.

Ba ita ta samu sukunin komawa bangaren Ummah ba sai bayan Magriba. Ta shantake a can har dare ya tsala, suna ta hirarsu da Mami kamar irin ta 'yan'uwan da suka jima basu hadu ba.

Sai wajajen karfe goma ta yi mata sallama, ta tayata tashin Farida da Ammar da suka yi barci anan falon, suka rakasu zuwa sama. Sannan ta leka Hajiya Ummah tayi mata sai da safe da kuma fatan Allah Ya kara saukaka mata jikinta.

Ta wuce sashenta kai tsaye, ta cancada wanka tayi kwalliya da kayan barci masu daukar hankali, sai ta dora hijabi doguwa a saman kayan ta kulle bangarenta ta nufi turaka.

Tafe take har ta karasa, zuciyarta na cike da wasi-wasi da sake-sake. Wani abu ya tsaya mata a rai ya ki fita, ta rasa dalilin da yasa take kasa sakewa da Babangida kwata-kwata a shimfidarshi. Dazun nan duk irin burika data dinga dauka a kanshi da yadda zata sake dashi ta faranta mishi da kyau don ta wanke kanta a wajenshi, amma ta rasa dalilin da yasa kawai daya tabata sai taji ta kasa aiwatar da komi. Sai dai kawai ta sakar mishi ragamar komi.

Tana maida kofar dakin ta rufe, taji an janyota ta baya an rungume. Ya sanya fuskarshi a saitin kunnenta yana rada mata, "you are late."

Ba kuma tare daya bari ta amsa mishi ba, ya fara salube hijabin nata yana janta zuwa bedroom dinshi.

✷✷✷✷✷✷

Kwana biyu da yin hakan, Mami tayi sallama dakin Ummah bayan itama ta kammala nata shirin na kwanciya. Zaune ta sameta a gefen gado, ta tsiyaya shayin Chamomile a dan karamin mug tana kurba, da kuma takardu a gefenta tana dubawa.

Ta dauki wani mug din itama ta tsiyaya shayin ta zauna a gefenta, don kuwa yau hira ce zasu sha ba karama ba ta yaushe rabo, wadda tun zuwanta basu samu damar yi ba.

Kasa-kasa take kallonta tana ta dube-dubenta har ta kammala, ta bude drawer ta gefen gado ta sanya takardun. Ta daga kai tana kallon Mami da dan murmushi akan fuskarta, "wai wannan kallon na menene? Tun dazu kin sanyani a gaba kina ta kallo, kuma baki ce komi ba."

Mami ba mutum bace mai boye-boye. Halinta frank ne, kai tsaye take fadin magana gadan-gadan ba tare da tsoron abinda zai biyo baya ba, haka gaskiya komi dacinta ta kan zauna ta tsarge maka ita ne kai tsaye. In yaso daga baya ta yi dealing da abinda hakan zai haifar.

Tayi karatu a bangarori da dama na likitanci da ilimin halayyar dan Adam wato Psychology. A halin yanzu ita din Licensed Mental Health Therapist ce, wadda tafi kwarewa a Trauma and Family Therapy. Sai ta juye gabadayanta a lokacin, ta dauko rigar Therapist dinta ta sanya. Ta tunkari Hajiya Ummah din a matsayin therapist.

Tace, "ina mamakin irin kallon da naga kina watsawa surukarki ne Ummah. It's not like you sam. Ko kuwa dai tayi miki wani laifi ne?"

Ummah ta yamutse fuska a take, "don Allah kada ki janyo min zancen da zai bata min rai da wannan daren har in zo in gaza barci. Idan ba hirar yaushe gamo ko ta su Fu'ad zaki yi min ba, to don Allah hada naki-i-naki ki bani waje in kwanta."

Ta gyara zama da kyau tana kallonta, tace, "wannan hirar ma ai ta shafemu. Kuma ni dama koda kika ji ina dokin zuwa nan to saboda wannan ne kawai. Don nasan idan ma nace zamu yi ta a waya ne ba yarda zaki yi ba. Shi yasa nace zan jira sai mun zauna ni dake ido-da-ido."

Ta nisa tana kallon Hajiya Ummah din a nutse tana karantar yanayin da take ciki, kafin ta sauke numfashi, tace mata, "tun kafin ayi auren wannan, sai da na fada miki. Idan kin san ba zaki iya jurewa ba ki manta komi dake ranki, kada ayi auren nan. Maganin kada ayi, kada a fara. Amma kika nace. Yanzu kuma ki duba abinda ke faruwa, kwanaki biyu kacal nayi a gidan nan, amma tuni har na gama karantar yadda baki sakewa yarinyar wannan ko kadan. Kina ganin kuma yadda bata iya sakewa a cikin gidan aurenta saboda ke kawai. Wallahi ina jiye miki tsoron hakkinta da kike dauka, da tarin zunuban da kike karawa kanki saboda riko da mummunar gaba irin taki!"

A wannan gabar a fusace Ummah ta kalleta, tace, "yanzu Sumayyah har kina manta ko ita din tsatson wacece?"

Tace, "na sani sarai, tsatson makiyinki ce Alhaji Laminu! Sai dai abinda kike mantawa shine, duk ta inda aka shiga aka fita dai, tsatsonmu ce. Tsatson Alhaji Nalado ce. Don haka ko kin ki ko kin so, jininki ce. Tunda dai ba a canzawa tuwo suna. Wai ba Allahn da Ya haliccemu bane ya horemu da mu yi hakuri ba? Ba Shi bane ya mana alkawarin saka mana da rahama mai dumbin yawa ba a lokacin da muka yi hakuri a lokacin da aka zalunce mu? Me yasa ke ba zaki yi hakurin ba? Ke me yasa ba zaki manta da abinda ya riga ya faru ba? Lokaci ya ja, kwanaki sun tafi da yawa. Me rikon naki yake haifar miki a halin yanzu? Bayan cuta daya barki da ita da threat din kamuwa da cutar shanyewar barin jiki?!"

Hajiya Ummah tayi shiru tana sauraronta, hawaye suna cika mata idanu. "To ya kike so inyi? Ba zan taba iya barin wanda ya cuceni ba wallahi! Ba zan iya ba!"

Mami ta tari nunfashinta tun ma kafin ta dasa aya, tace, "shi din yana ina yanzu to? Da shi da Baban namu suna ina ne? Suna can sun koma ga Ubangijinsu, tuni sun manta da abinda ke kike fama dashi a ranki shekara da shekaru, kina sauke fushinki akan mutanen da basu ji ba basu gani ba. Saboda Allah menene laifin Nadiya a wannan abin? Lokacin da abin nan ya faru, ko uwarta ba a haifa ba. Balle ita kanta. To meye ruwanta anan? In fada miki gaskiya, ba fansa bace kike dauka anan, wallahi hakkine da tarawa kai dumbin zunubi kawai. Zan kuma so kiyi nadamar hakan tun kafin lokaci ya kure miki Ummah!"

Kawai sai ta saki wani kuka mai cin rai, Mami ta rungumota a jikinta tana kokarin tausarta da kalamai masu dadi.

"Yaya don Allah, ina rokonki ba don ni ba, ki manta da duk abinda ya faru haka nan. Don Allah ki samawa ranki salama, ko muma da muke damuwa da halin da kike ciki zamu samu salamar rai. Ita daukar fansar ma wai menene fa'idarta musamman akan wanda bai san kina yi ba? Zan so ki hakura haka nan, ki yarda duk abinda yake faruwa da bawa dama can rubutaccene tun kafin ma a samar dashi a allon kaddarar mu. Mu su wanene da zamu ja da hukuncin Allah? Bayan ita kaddara din ita take shaping dinmu zuwa wasu mutane na daban, masu iya hakuri da jurewa duk wani yanayi da zasu shiga a rayuwarsu?"

Ummah ta lumshe ido hawaye yana kwarara daga cikin idanunta, "ta yaya zan yafe mishi Sumayyah? Ta yaya zan iya yafe mishi?!"

☆☆☆☆☆

HAJIYA UMMULKHAIRI KACHALLA!

Sun taso cikin tsananin kulawa da kaunar iyayensu, musamman ita din da tazo a farko kafin haihuwar Sumayyah. Soyayya dai da gata, babu irin wanda bata gani ba a rayuwarta. Har kuwa bayan da aka haifi Sumayya, Ummulkhairi ita ce yar gaban goshin iyayenta musamman ma dai Alhaji Kachalla.

Tun kafin su girma, Alhaji ya gama shirya musu feature dinsu. Su dukansu karatun likitanci ya zabar musu, ya kuma dauki alkawarin zai kashe musu kudi komi yawansu don su cimma wannan buri nashi. Kasancewar bashi da d'a namiji, ya dauki Lamin tamkar wani babban dan shi, ya kuma yi burin tunda su matane babu ruwansu da kasuwanci, to zai damka harkokin kasuwancinshi ne a hannun Lamin din domin ya ci gaba da kula mishi da komi.

A wancan lokacin mutane sun fi gane su yi ta tattala kudinsu a hannunsu da dai su je banki ko wani waje su zuba hannun jari. Sai ya fi karkata hankalinshi wajen sayen filaye da gidaje kawai, da kudirin zasu amfani su Ummulkhairi a gaba.

Daga shi har su din babu wanda ya taba kawo Lamin zai yaudaresu haka. Su dukansu kuma babu wanda ya taba tunanin zai tafi ya barsu a cikin wannan duniya mai cike da rikici da mutane maha'inta, masu saka alkhairi da sharri.

Mahaifinsu ya kwanta jinya a gaban idonsu, Ummulkhairi da wayonta a lokacin, tunda har ta shiga aji hudu na gaba da firamare. Don haka duk wani abu dake faruwa ta sani. Mahaifinsu yazo ya rasu, kudinsu dake mallakinsu, suka nutse a hannun Lamin.

Lokacin da Mamansu suka shigar da kara kotu, ya bi dare ya dauki wasu yan tasha, suka je gidansu cikin dare da wukake da adduna. A gaban idonsu, aka dorawa Ummansu wuka a wuya. Yace mata idan bata janye wannan karar ba, wallahi sai ya sa sun daddatsata. Su kuma su Ummulkhairi zai sanya wannan gardawan su rabasu da martabarsu. Wannan abu shi ya tsoratata, ta janye karar ba tare da ko yan'uwanta sun san musabbabin hakan ba. Ta kuma hanesu da suma su fadawa kowa saboda tsoron abinda Lamin din zai iya aikatawa. Don kuwa yace matukar suka kuskura yaji zancen nan a waje to zasu dawo.

Sai gashi cikin dan kankanin lokaci suka koma yin wata irin wahalalliyar rayuwa. Basu taba sanin ana yini a kwana da yunwa ba, sai a wannan dan takin. Gidansu da a kullum abinci sai dai a ba almajirai, don ma Mamansu bata kasance mai almubazzaranci ba, sai gashi su ne suke kwashe fiye da sati ma ba tare da an dora sanwar abinci mai suna abinci a gidan ba. Kullum sai gamje-gamje kawai suke yi. Suna kuma ji suna gani dangi suka watsar da su. Kalilan ne kadai suke dan zagayasu ko su dan aika musu da wani abu na masarufi. Sai da ta kai ta sayar da kayan dakinta tsaf, ta fara sana'ar sayar da abinci anan cikin gidanta.

A haka cuta ta kama Mamansu, ta dauki lokaci mai tsayi tana yin ta a tsaitsaye. A hankali sai kudaden sana'ar suka fara lumewa wajen sayen magani da zaryar asibiti. Daga baya sai gashi ta kwanta jinya warwas itama, zuwa lokacin da suka ankara suka je asibiti, ta kamu da matsanancin ciwon koda har ya kai stage 4.

Kafin ma a kai ga tunani da shawarar ta ina za a bullowa al'amarin? Allah Ya karbi abinshi.

Fadin irin kukan da su Ummulkhairi suka yi ba kadan bane, a kullum idan ta tuna yadda Mamansu ta mutu akan gadon asibiti, yadda ta kade ta rame kafin rasuwar tata, gabadaya kamanninta suka sauya saboda tsabar cuta. Sai data yi kwanaki uku a gadon asibiti ko ruwa bata iya hadiyawa, sai karin ruwa da jini da ake mata ne kadai suke tallafa mata.

Duk kuma wannan zaman jinya da suka yi, a cikin danginsu aka rasa wanda zai iya tsayawa tsayin daka a kan maganar har dai ta Allah ta kasance. Idan Ummulkhairi ta tuna hakan sai tayi ta kuka.

Haka aka basu gawa suka tafi gida da ita, kafin su je gida zancen rasuwar ya zagaya dangi. Wai sai lokacin ne duk kuma suka hadu, suka je suka yi ta matse-matsen hawayen da ta kira na munafurci.

Lamin yaje da kayan abinci ya jibge musu bayan an dawo daga janazarta. A lokacin ne ta tashi ta musu wani dan karamin bori, ta musu tatas daga shi har dangin nashi akan banzatar da su da suka yi. Ta kuma ce a fitar musu da wannan kayan abincin na haram, ko ta konasu. Bata san ya aka yi da kayan ba, don shi Lamin din da tayi hakan dominshi ma tuni ya dade da barin gidan. Bai san tayi ba.

Yayan mahaifiyarsu wanda ya kasance shi kadai ne shakikinta, ya yanke shawara da mahaifiyarsu cewa zai sayar da gidan da suke ciki kawai tunda dai yanzu ya zama na magada, ya daukesu a mayar dasu gabansu kawai. Don basu san irin halin da zasu shiga ba idan suka barsu anan.

Ita kuma tayi na'am da hakan, sai ta bashi shawarar kada su sanar da kowa amma. Gudun kada su sake hanasu tafiya da su kamar yadda suka yi a bayan rasuwar Alhaji Kabiru. Kafin zagayowar bakwai kuwa aka sayar da gida, suka hade kan kayansu tas, ba tare da sunyi sallama da kowa ba suka koma Kaduna.

Ummulkhairi ta tafi zuciyarta cike da matsananciyar tsanar Lamin wadda bata iya misaltuwa. Ta kuma yi alkawari ta maya, komi daren dadewa, sai ta rabashi da duk wani farinciki na shi. Kamar yadda ya kwace musu nasu farincikin!

40.

Komawarsu Kaduna da zama yaje musu da wani irin sauyi wanda basu saba da shi ba. Dangin Mahaifiyarta mutanene su masu matsakaicin karfi, amma kuma suna da wadatar zuciya.

Dama can Hajiya Uwale ce take kula da su musamman mahaifiyarta Nenne wadda karfinta ya fara ja, har ma da Yayanta Tasi'u wanda shi har yau baya da wata tsayayyar sana'a sai tsilla-tsilla da kame-kame kawai. Bayan iftila'in daya sameta kuma sai suka koma yar gidan jiya.

Ga kuma karin su Ummah din da Sumayya da suka tare a wajen Nenne saboda dama ita kadai ce a gidan. Shi gidan Kawu Tasi'un kusa da na Nenne yake, don da duka gidan a hade yake kasancewarshi na gado, daga baya ne

ya rabashi da nata din saboda iyalinshi. Yana da 'ya'ya shida maza da mata, don haka dawainiyar kanshi data yaranshi ta isheshi.

Amma duk da haka sai da yayi iyaka bakin kokarinshi wajen jansu a jikinshi. Wadannan kudi da aka sayar da gida da su yayi amfani su dukansu ya maidasu makaranta, Ummah ta shiga aji shida kai tsaye, yayinda Sumayya ta shiga aji uku don haka duk jarabawar fita zasu zana. Ya biya kudin, ya kuma yi musu yan saye-sayen kayan masarufi wadanda zasu amfana. Sauran kuma ya damkawa Ummah a hannunta yace ta kama sana'ar da zata rikesu da su.

Ta shiga tunani da taraddadin ya zata yi? Don kuwa zama bai kamata ba. A haka suka yi jarabawar NECO da WAEC duk bata gama yanke shawara ba. Ga kayan abincinsu sun ja baya sosai, kudaden hannunsu sun tasamma karewa. Don haka ta yanke shawarar fara sayar da abinci kawai.

Ta kuwa fara da hannun dama, shinkafa take yi da wake da kuma doya da miya. Ta yanka salad da albasa da kabeji da tumatir. Sai ta fita can bakin titi kusa da wani gareji inda ake gyaran mota. Kawu Tasi'u ya rokar mata alfarma a wajen mai garejin har aka fitar mata da yar rumfa take sana'arta hankali a kwance.

Abinka da farar mace da masu iya magana suka ce alkyabbar mata, ga ta budurwa danya shataf, kyawun jikinta da sura duk sun gama bayyana a lokacin. Duk da cewa ba kwalliya take yi ba idan zata fita, amma tana gyara jikinta da kyau. Don kuwa macece ita mai tsananin tsafta. Komi take yi cikin nutsuwa ne da tsentseni, wasu a wajen duk suna cewa girman kai ne da jan aji, amma ita haka tsarin halittarta yake. Da dama wasu mutanen basu san da zamanta ba sai data fara tallar wannan. Aikuwa nan manema suka yi mata caaa kamar kudaje, ita kuma ta ki kula kowa a cikinsu. A ganinta idan tayi aure yanzu, ya zata yi da Sumayyah?

Tafi-tafi likkafa tayi gaba, kullum kara yawan abinci take yi don kuwa yanzu har daga wasu wajajen zuwa saye ake yi don Allah Yayi ta da zakin hannu.

Ga tsaftarta da tafi burge mutane. Ta kuma fara hadawa da zobo da kunun kanwa.

Da Sumayya ta gama tata jarabawar, itama sai ta fara binta tana taimaka mata da wasu abubuwan. Ita take wanke mata kwanuka idan masu saya sun gama ci, ita kuma take kaiwa wadanda suke tsallake dasu. Amma suka wannan cikin kulawar yar uwar tata, bata bari ta nufi bangaren da idanunta ba zasu hango ba saboda gudun abinda zai iya zuwa ya zo a wannan zamani da amana tayi karanci.

*

Doguwar tafiya suka yo tun daga Nasarawa a mota. Yana daga cikin wadanda suka yiwa Gwamnan Kaduna rakiya zuwa tattaunawa da gaisuwar ban Girma ga Maigirma Gwamnan Nasarawa din. Suna shiga garin Kaduna aka sanar dasu Gwamna kai tsaye zai wuce gidan sarautar Zazzau ne tare da securities dinshi, su kuma anyi releasing dinsu a nasu aikin, za su tafi da wasu sojojin. Su dukansu dama hutun suke bukata. Aikin tsaro musamman na manyan figures irinsu Gwamnoni, ba abu bane mai sauki. Kowa ya matsu ya dangana da gidanshi don ya samu ya huta kafin kuma su ga inda za a sake jefasu zuwa gobe.

Sun kusa karasawa Shagari Low cost inda nan ne main house dinsu yake za a saukeshi, motar tasu ta fara hayaki da rawa akan hanya, ala dole suka gangara gefen titi suka kasheta. Signboard da suka gani na wani gareji anan kusa da su yasa suka tura motar zuwa garejin shi da sauran abokan tafiyarshi su uku. Daya motar da suke tare da ita kuma ta wuce can Jaji.

First Lieutenant I. A Makama (Abdullahi Ibrahim) ya fito daga cikin garejin da suka kai gyaran motarsu bayan yayi sallama da abokanshi, niyarshi ya samu acaba ya karasa dashi gidansu ko kuma ya lallaba da kafa tunda babu nisa sosai. Saye yake da kakinshi na sojoji, ya cire rigarshi ta sama mai dauke da insignia dinshi a kafada wato l aligned silver stars guda biyu. Ya rage daga shi sai dogon wandon na kakinshi da bakar riga.

Lokacin shigarsu bai kula da mai sayar da abincin ba sam, sai bayan daya fito ya tsaya a bakin titi sannan ya ankare da ita zaune a cikin rumfa tana ta aikin zubawa kwastomominta abinci.

Kallo daya tak! Yaji ya samu matar aure yanzu-yanzu.

Yana da matarshi daya da aka yi musu auren lalle, zabin iyayenshi ce a gareshi daya karba da hannu biyu da biyayyar daya saba yi musu a kodayaushe. Amma ya fada mata, su ma iyayen ya fada musu, zai kara aure a gaba idan har ya samu wadda ta kwanta mishi a rai. Suka kuma yi na'am da hakan.

Ba mai kyalle-kyallen kallon mata bane shi, shi yasa ma yake tantamar anya zai ma iya daga ido ya kalli mace har ya samo mata? Sai gashi a yau kwatsam ya sameta.

Ya koma gefe daya yana kare mata kallo a nutse, yadda take gudanar da komi nata cikin nutsuwa da rashin rawar kai. Wani mai azababben surutu ne a kusa da ita kadan, an zuba mishi abinci yana ci yana ta zuba mata surutu kamar an bude kan famfo. Amma bata ce mishi komi ba, sai dan murmushi kawai da take yi.

Allah kadai Yasan iya adadin lokacin daya dauka anan kawai yana aikin kallonta, har aka gama gyaran motarsu abokan nashi suka fito. Itama nata abincin ya kare ta fara tattara kayanta waje daya.

Sai ganinsu yayi sun tsaya a gabanshi, Al-Ameen Tukur ya kalleshi da mamaki, "Abokina, naji kamar kace gida zaka wuce tun dazu? Ko jiranmu kake yi?"

Sai yaji yar kunya ta rufeshi, ya hau kame-kame cikin rashin sanin abin cewa. Bai iya karya ba, Allah Ya gani kuma ba zai iya yinta a yanzu ba.

Shi kuwa daya duba wajen da idanunshi suke, ya kula da yar kyakkyawar yarinyar daya tsurawa idanu, sai ya kyalkyale da dariya.

Yace, "Allahu Akbar! Lallai yau Allah Ya kama wani!Duk fadin ran naka da ihun baka ga macen da ta isa ka yiwa kallo biyu ba, ka tsaya kana kallon

wata for hours? Lallai da labari ashe!" Suka ja mota abinsu suka tafi suna kyalkyala mishi dariyar shakiyanci.

Shi kuma ya ci gaba da tsayuwa nan har ta gama kwashe kayanta, almajirai biyu suka daukar mata wasu, itama da karamar yarinyar dake tare da ita suka dauki wasu.

Ya daga kafa as if in a trance, yana binsu a baya har suka gangara suka tsallaka titi, suka shiga gida. Ya kira daya daga cikin almajiran da suka kai mata kaya yana tambayarshi ko nan ne gidansu budurwar nan? Kuma ya sunanta? Yace mishi, 'gidansu ne. Kuma sunanta Ummulkhairi.'

Ya dauki kudi ya ba yaron kafin ya juya ya wuce gidansu.

Ummah na zaune da dare bayan an gama sallar isha'i tana gyaran kayan miya da za a kai mata markade na miyar gobe, yaro yayi sallama ya shiga, yace, "an ce Ummah ta zo ana kiranta."

Ta jefi yaron da harara, "kaje kace ba zata zo ba!"

Saboda duk a tunaninta Nasiru ne. Wani nataccen saurayine tayi anan cikin garejin yake aiki, ta fada mishi bata son shi, amma ko a jikinshi wai an mintsini kakkausa. Kullum cikin zarya yake gidansu, a wajen sana'ar tata ma baya barinta. Bini-bini yana nan yana ta zuba aikin surutu yadda kasan wani aku kuturu.

Nenne ta lallaba ta fito daga dakinta tana dafa bango, "kai kaje kace tana zuwa."

Ta kuma juya tana hararar Ummah, "ki tashi ki fita tun kafin kiga bacin raina wallahi. Ni na taba ganin haka? Yarinya ana binki amma kina wulakanta mutane? Idan baki tsaya kin saurari samari ba ta yaya za ayi auren kenan?"

Ta turo baki, "ni Nenne nace ina son yin aurene dama?"

Ta mata dakuwa, "aikuwa karyarki ta sha karya wallahi! Ba ido zan zuba miki ba kina abinda kika ga dama ba sai kace wata marar aikin yi. Bari kawunki ya shigo gidannan wallahi, cikin maneman naki ya cewa daya ya fito kawai mu aurar dake mu huta!"

Ta tabe baki, "tab! Allah Ya tsareni wallahi!"

Da haka dai ba da son ranta ba ta zari hijabinta ta fita, da niyar ta wankeshi tatas wankin babban bargo. Yadda ko a hanya ba zai yi fatan Allah Ya sake hadashi da ita ba.

Sai ta tarar da abinda bata yi tsammani ba. Don kuwa ba Nasiru bane. Wani kyakkyawan matashi ne da bata taba ganin mutum mai zati da kamala irin tashi ba. Duk yawan samarin dake zuwa wajenta, bata taba ganin wanda ya kama kafarshi a komi ba. Ga iya gayu. Ya sha kaftan dinshi fara tas, ya dora hula a kanshi yana ta bulbula kamshi.

Sai ta karasa wajenshi a nutse tayi mishi sallama.

Abdullahi ya sanya mata idanu yana kallonta cike da wata kauna da sanyayyar soyayya. Wannan yammaci da yayi, da kyar ya iya bari gari yayi duhu ya zo gareta. Wani abu ne da bai taba dandana ba a cikin tarihin kuriciyarshi har zuwa girmanshi da yin aurenshi, wai shi soyayya. Ya daga baki da kyar ya iya amsa mata sallamar yadda ta kashe mishi jiki.

Ya gabatar mata da kanshi a matsayin masoyi, wanda yaje da kokon barar aurenta. Bai boye mata ba, ya fada mata cewa yana da mata har da dansu wanda bai wuce shekaru shida ba. Kuma shi aurenta yake son yi da gasken-gaske idan ta amince.

Mutum ne smart, wanda yake da kwazo da naci, duk abinda ya sanyawa rai to fa sai ya ga abinda ya turewa buzu nadi. Yaje mata da zance wanda ba zata iya kwabar da zancen aure daya mata ba, na cewa zai hada daga ita har Sumayya ya rika tamkar kanwarshi. Saboda a dan tsayuwar da yayi a dazu ya karanceta tsaf, koda bata sonshi, ba zata taba kin zancen kulawa da Sumayyah ba. Don kuwa ya karanci kaunarta da kulawarta zuwa ga yarinyar.

Ta mishi sallama akan cewa zata yi tunani, ta kuma kwana tana tunanin. Daga karshe taga me zata rasa ne a wannan auren idan anyi?

Don haka washegari daya dawo ta furta mishi ta amince. Yayi murna ya kuma ji dadi sosai da sosai.

Cikin dan kankanin lokaci sai ga iyayenshi sun je wajen su Nenne da zancen aure. Bangaren su Nenne sun yi bincike, suka samu gamsasshen bayani game da iyalan gidan Ibrahim Makama. Mutum mai tawali'u da wadatar zuciya kenan. Abdullahi shine babban dan shi, bayan nan yana da kani Hashim wanda shima aikin damara yake yi, Custom ne. Bayan su iyayensu basu kara haihuwa ba. An shaidi zuriyarsu da girmama mutane da bin na gaba, iyayensu mutanene masu tausayi da taimakawa na kasa dasu. Mahaifinsu ba mai arziki can-can bane, amma yana da rufin asirinshi dai-dai gwargwado. Tsohon malamin makaranta ne wanda yayi ritaya. Da suka gamsu da duk bayanan da suka samo, sai kawai suka sanya ranar aure kamar yadda suka bukata, yan kwanaki kalilan.

Aka sha hidimar aure sosai, dangin Uwale sunyi musu kara kwarai da gaske. Mutanen Maiduguri kuwa ko keyar wani basu gani ba, dama dai tuni ta ciresu daga cikin ranta. Don haka bata damu da rashin zuwansu ba.

Amarya ta tareta a gidanta dake Shagari Low cost, tazarar dake tsakaninsu da surukanta ba mai yawa bace, tare da kishiyarta Hadiza.

Hadiza da tabi ta tashi hankalinta ganin irin kudaden da Abdullahi yake kashewa amarya, duk da cewa dai itama yana yi mata bakin gwargwado, amma ba haka take so ba. Ta hau kan zugar yan'uwanta da abokai, kodayake dama can da halinta, ta shiga harkar malaman tsubbu da bokaye hankali tashe, bata so auren ya yiwu. Amma duk abinta sai da aka daura auren, aka kuma kai mata amaryar gidanta. Hakan bai sanyaya gwiwarta ba, tayi rantsuwa ta maya, in zata yi yawo tsirara, to sai ta raba wannan aure. Don kuwa gidan Abdullahi gidanta ne ita kadai, ba gidan da za a raba da wasu ba.

Don haka zancen zaman lafiya ma da Ummulkhairi bai tashi ba. Gaba ta dauka da ita sosai da sosai.

Ita dai tunda aka kaita take zaune da kowa lafiya, daga mijin har iyayenshi da yan'uwansu da ita kanta kishiyar, da zuciya daya take zaune dasu. Don haka duk abinda Hadiza take yi, bata taba tankata ba.

Mutanen unguwa data tsince wadanda suke son zaman mutunci da ita, sai ta kamasu. Ta zubar da masu kai mata zuga da gulma da kuma wadanda dama can a bayan Hadiza suke a gefe.

Abdullahi aka yi posting dinshi anan gidan Gwamnati a Kaduna din, don haka yana gida a zaune. Ya kuma cika alkawari inda tana cika wata daya a gidan, yaje ya dauko Sumayyah da kanshi da kayanta duka, ya maida ita hannunsu da zama tare da sama mata transfer din makaranta zuwa wadda tafi kusa da gidansu.

Wannan abu shi ya kara rura wutar tsanarta a wajen Hadiza. Duk kuma yadda Ummah ta so da su zauna lafiya, abu ya gagara. Danta daya tilo dake gidan, bata bari ya rabeta. Haka bata bari Sumayyah ta rabesu. Don haka Ummah ta kama kanta, ta daina shiga harkarta amma tana bata girmanta a matsayinta na babba.

Anyi auren nasu babu jimawa Allah Ya dauke Nenne. Sunyi kuka kwarai da gaske, don kuwa sai a lokacin ne suka tabbata marayu na gaske. Don ma dai Abdullahi a tsaye yake a kansu tsayin-daka, daga ita har Sumayyah din.

Hadiza dai tana gefe daya, shiga da fita gidajen malaman tsubbu kawai take yi. Sai gashi ta fara nasara da cimma burinta. A sanyawa Abdullahin tsanar Ummah, ko ita taji ta tsaneshi, a sanya ya dinga wulakantasu, a sanya ya hanasu abinci, abubuwa dai iri-iri babu wanda basu gani ba. Amma da yake Ummah din mai kara ce da hakuri, ko iyayenshi basu taba sani ba. Ta dukufa da addu'a babu dare babu rana tana neman tsari.

Akwai ranar da Abdullahi ya shiga dakinta cikin dare yayi mata dukan tsiya, ya kuma ce ta hada kayanta ta bar mishi gidanshi a wannan dare. Ta ci kuka har ta gode Allah a wannan rana, tunanin ina zata nufa cikin tsakiyar daren wannan ita da Sumayya ya rufeta, amma dole zata tafi din. Don ba zata iya irin wannan zama ba.

Haka ta tashi jiki duk yayi tsami, daga ita har Sumayyan kuka suke yi, ta dauki hijabi kadai ta sanya da yan kudaden da yake bata tana tarawa. Ta gama kudirawa a ranta idan ta fita daga wannan gidan, to ita da Kaduna sai labari. Don kuwa garin ma zata bari kwata-kwata ta huta. Yadda kasan wadda ake tunzurawa ko ake ja, haka suka nufi kofa su duka zasu fita.

Tana kokarin bude kyauren gidan ta fita kuma sai taji ya biyosu a sukwane. Da fari tsorata tayi, tayi tunanin ko bugun nata zai sake yi ya karasata. Sai taji ya kamota ya rungume, ya hau bata hakuri da magiyar don Allah kada ta tafi tayi hakuri, bai san me ya hau kanshi ba har yayi mata wannan danyen aikin.

Da kyar da jibin goshi ya jata ya maidata dakinta don itama kakarewa tayi tace kawai ya kyaleta ta bi duniya, abinda bata taba yi mishi ba kenan a tarihin aurensu wato musu.

Shi da kanshi ya hau kikiniyar dora tukunya a risho, ya dafa ruwan zafi yana gasa mata jiki. Ranar ita kuka, shi kuka haka suka kwana.

Tun kuma daga wannan rana ta dage da addu'o'i na kariya, da wanka maganin tsari irinsu ganyen magarya da kaikayi.

41.

Cikin ikon Allah kuma daga ranar ne suka sake daidaitawa ita da angon nata, suka koma tamkar tif da taya saboda tsananin kauna da kyakkyawar zamantakewa.

Suna cikin hakan kuma sai ga ciki ya bayyana a jikin Ummah. Wayyo, ina wuta in saka ki! Hadiza taji kamar ta shaketa ta mutu. Shi kuwa Abdullahi da Iyayenshi suna ta murnarsu, suka fara shirin karbar yaro ko yarinya.

Kulawa ta musamman suke bata kamar su dauketa su goyata. Babu abinda zata ce da iyayen Abdullahi a wannan lokaci sai godiya ga Allah kawai, domin kuwa sun rike amanarsu da suka dauka. Abdullahi ya zame mata mijin marainiya ita da Sumayyah.

Tunda cikin nan ya samu ita kuma Hadiza babu irin kokarin da bata yi ba don ta zubar dashi, amma fa abu ya gagara. Akwai ranar da ta dafa faten masara da wake yadda ta saba ci kusan kullum, ta barshi akan wuta ta shiga daki ta fito, ta juye fate a kwano ta sha. Shikenan jiki ya hautsine, ciki ya hau murdawa yadda kasan mai nakuda. Lokacin Abdullahin baya nan, Sumayyan kuma tana makaranta. Ta fito tsakar gida tana kuka rike da ciki, amma kiran duniya Hadiza tana jin ta a daki ta ki fitowa. Haka ta lallaba da kyar ta shiga makota, su ka tarairayeta aka nufi asibiti da ita. Likitoci suka hau kanta da kyar aka samu aka ceto abinda ke cikin. Suka ce akwai abinda ta ci wanda yayi yunkurin zubar mata da ciki, bata son doguwar magana da yin tashin-tashina, shi yasa bata ma fadi musu tana zargin wani abu ba. Shima Abdullahin da yaje sai kawai tace mishi ciwon ciki ne ba wani abu ba. Aka basu sallama da dokoki da aka kafa mata, suka koma gida.

Sai dai fa tun daga nan, ta kiyaye kanta da yin girki ta bari akan wuta ta fita. Musamman bayan hakan da kamar sati biyu data kama Hadiza din kiri-kiri tana zuba mata abu a cikin tukunyar miya data bari tana simmering ta dan zagaya bayi. Sai ta hau mata kame-kame da kokarin nade tabarmar kunya da bori. Bata ce mata komi ba, amma dai haka wannan miya ta zama haramiyarta. Wannan dalilin ne yasa ta dinga taka-tsantsan da duk abinda zata ci ko sha a wannan gida.

A haka cikinta ya dinga girma cikin kulawa da tattali. Kusan kullum Hadiza sai ta takaleta da fada, ta dinga yada mata kananun maganganu da habaici iri-iri, duk tayi kunnen uwar shegu da ita bata taba tankata ba. Don ta kula so take yi ta tanka din ta kai mata duka, motsi kadan sai tayi kamar zata kaiwa cikinta hari.

Cikinta ya fita wata na takwas, watarana da yammaci ta fito daga bayi tana tafiya da kyar. Duk ta kumbura, ga cikin nata ya fito sosai yayi mata kyau. Duk abinda yake tsone idon Hadiza kenan tana kara tsanarta da cikin jikinta.

Ta wuce Hadiza din zata shiga dakinta sai taji ta saki tsaki, tace, "matsiyaciyar kawai, mayya! Wadanda idan suka kama kurwar mazan mutane ba su saki. Ai wallahi sai nayi maganin dan iska anan gidan! An gama karuwanci wajen sai da abinci an yayimo cikin shege an likawa mijina don maita!"

Maganganun nata suka bata ran Ummah sosai, amma ta dakewa ranta bata tanka ba. Ta wuceta kamar kullum.

Kawai sai ji tayi an shakota ta baya, kafin ta ankare me ke faruwa taji an fara naushin cikinta ta ko'ina. Garin neman ta warci kanta tayi wani irin juyi, Hadiza kuma ta tunkudata. Sai gata ta fadi kasa yummm! akan ruwan cikinta.

Wata irin azaba ta ratsata da tunda take bata taba jin makamanciyarta ba, gabadaya kasa ko mosti tayi balle tayi ihu saboda yadda azabar ta fitar da ita daga hayyacinta. Jini ya tsinke mata a take, kamar an yanka rago.

Amma Hadiza bata sadara ba, sai ma gyara tsayuwa da tayi tana jiran ta ga ta tashi, ta kara mata da wani dukan.

Allah ne Ya jefoshi a dai-dai wannan lokaci, don kuwa yawanci sai dare yake komawa gida.

Ganin abinda yake faruwa yasa ya nufi kan Ummah cikin wani irin kidima da tashin hankali, musamman jinin da yaga yana malala daga jikinta.

Ya daga ido ya kalli Hadiza da bacin rai wanda bai fasaltuwa akan fuskarshi, "wallahi, Tallahi Hadiza. Idan wani abu ya samu da na ko matata, ki kuka da kanki. Ni kaina ban san irin hukuncin da zan dauka a kanki ba!"

Ya sungumeta yayi waje a sukwane.

Sabuwar mota da yayi awo tun daga Kwatano aka kawo mishi yau yaje ya amsa. Wannan ne musabbabin dawowarshi gida, ya dauki Iyalanshi a ciki ya zaga dasu su sanya mishi albarka. Sai kuma ya tarar da wannan tashin hankali. Haka ya sanyata a bayan mota, ya fuzgi mota a sukwane yayi asibiti.

Kakin jikinshi ya ceceshi a ranar, don kuwa da ba za su amsheta bama sai da yan sanda. Haka aka garata zuwa dakin tiyata cikin gaggawa yana ji yana gani, ya dawo yana ta safa da marwa a kofar dakin, addu'a iri-iri a bakinshi. A cikin haka ne ya tuna da Iyayenshi, sannan ne ya dauki waya ya kira ya sanar dasu halin da ake ciki, sai gasu nan da nan sun je sun sameshi a asibitin. Suna nan har zuwa lokacin da aka fito da ita bayan an kwashe kwararan awanni biyu.

"Kuyi hakuri, mun samu mun ceto uwar da kyar, amma bamu iya ceton dan ba. Kafin ku kai ga zuwa ma ya riga ya rasu saboda rashin isasshen oxygen a cikin cikin. Amma ita yanzu uwar tana lafiya, zamu yi mata sauran gwaje-gwaje idan ta tashi zuwa gobe!"

Abinda likita yace dashi kenan, aka mika mishi dan shi lullube a cikin zani. Ya amsheshi fuskarshi na bayyana rauni kwarai da gaske, duk karfin halin da yaso ya nuna sai da hakan ya gagara, ya zauna akan kujera dabar! Hawaye na cika mishi idanu. Ga d'a nan Tubarkallah kamar ka mishi magana ya amsa.

Innarshi ta amshi dan ganin yadda jikinshi yake rawa sosai, yayinda mahaifinshi ya dafa shi yana tausarshi. A haka jiki a sanyaye duk suka kwashi jiki suka koma gida, aka yiwa yaro sutura aka je aka binneshi kafin suka koma asibitin.

Mutane suka fara zaryar zuwa dubiya kamar su ci kansu, don kuwa Ummah macece mai mutane kwarai da gaske, yadda ta kama danginshi ta rike da hannu bibiyu kamar nata yasa suke matukar girmamata. Ga ta dama abin hannunta bai rufe mata ido ba sam.

Sai da ta kwana ta yini sannan ta farfado. Sumayyah ce a kanta da Abdullahin, su duka sunyi wani zuru-zuru da su kamar wadanda suka kwana suna jinya.

Suka shiga nan-nan da ita, amma cikinsu aka rasa mai kwarin gwiwar sanar da ita halin da ake ciki.

Likita yaje ya duba jikinta da kyau, nan ya zaunar da ita yana yi mata bayanin halin da take ciki...

Saboda mummunar faduwar da tayi kuma akan cikinta, da karin naushin da aka dinga yiwa cikin nata, uwa wadda take rike da d'a a ciki, ta rabu da mahaifarta (ana kiran hakan a turance Placental Abruption) wanda dalilin haka ne yaron cikinta ya rasa numfashi da nutrients da ake samu daga jikin mahaifa, saboda haka ne kafin su kai asibiti ya rasu. A yanzu dai komai nata normal bayan jininta da ya hau, don haka sun rubuta mata magunguna da allurai, za su cigaba da monitoring dinta kuma su ga abinda zai biyo baya.

Ta kwantar da kanta akan filo ta lumshe idanunta hawaye na tsiyaya akan fuskarta. Kuka take so ta fashe dashi, ta zagi duk duniya da mutanen cikinta ko zata ji dadin bakin cikin dake tukuki a ranta. Da zata iya tashi a lokacin, da zata je har inda Hadiza din take ta kamota, itama ta mata abinda tayi mata. Amma ba damar haka.

Wata zuciyar dake tausarta da likitan daya dage yana yi mata wa'azi da kara tausarta, yasa ta fara jan 'Innalillahi wa Inna ilaihi rajiun, Allahumma ajirni fi musibati wa aklifni khairan minha!'

Kafin wani irin kuka mai karfi da daci ya kwace mata. Ta kokawa kanta a wannan rana, na maraicinta, da rashin iyayenta, da rashin Nenenta, da rashin da daya tilo da bata ko samu ganin kamanninshi ba balle ta dauka da hannunta. Wa ya sani ko zata sake ganin wani dan na kanta bayan shi? Likita ya fita ya barta tana wannan kuka na tausayawa kai.

Da Abdullahi suka shiga suka sameta, ta gama kukan ta share hawayenta. Idanunta sun yi ras kamar an soya gyada, amma daga ganinta babu tambaya an san ta sha kuka.

Ta yanke shawara daga wannan kuka, ta gama! Ta gama bari a takata, ta gama bari a dauki hakkinta, ta gama bari wani ya kwace mata abinda yake nata ne. Daga wannan rana, ta kulla bakar aniya da duk wani wanda zai nufeta da sharri. Ba kuma zata daina ba har sai taga karshen mutum!

Har tayi zaman jinyarta na kwanaki goma a asibiti, Hadiza ko a leke. Tana gida abinta ta mike kafa tana jiransu. Duk da ta dan sha jinin jikinta game da alwashin da Abdullahi ya dauka a kanta, amma gwiwarta bata yi sanyi ba. Saboda tasan a irin aikin da wani sabon bokanta yake mata akan Abdullahi, duk abinda zata mishi ba zai taba rabuwa da ita ba.

Shi kuwa da ba don ban hakuri daya sha ba a wajen iyayenshi, to da tun a washegarin ranar da abin ya faru ma zai sallameta. Amma suka tausheshi da kalamai masu kyau, suka ce yayi hakuri. Don haka yayi, amma shi kadai yasan kudirin daya dauka a cikin ranshi.

Aka sallameta ta warke dakau abinta, sai rama da tayi da rashin karfin jiki.

Ya daukesu su duka har iyayenshi dake tsaye a kanta da hidimarta kamar nata iyayen ne, da kuma Haule matar Kawu Tasi'u. Suka dauki kayansu yayi gidanshi dasu su duka.

A tsakar gida duk aka baza babbar tabarma aka zauna. Aka kira Hadiza taje, suka yi mata fada da nasiha kwarai da gaske, suka nuna mata rashin jindadin abinda ta aikata. Amma yadda fadan ke shiga ta kunnen dama, haka yake fita ta hagu. Da suka ce ta ba Ummah hakuri, ganin idonsu ne kadai yasa ta kalleta a kaikaice ta furta kalmar, 'yi hakuri!' da kyar.

Ta taune harshenta tana danne bacin ranta, amma ta kasa iya daga baki ta amsa ta.

A haka dai suka kara hadasu har shi Abdullahi din suka kara yi musu nasiha da kara nusar dasu akan zamantakewa da kuma yin hakuri da juna.

Yana jinsu har suka gama, kawai sai ganinshi suka yi ya tashi ya shiga dakin Hadiza. Ya fito sungume da dansu dake barci, a lokacin shekarunshi ba zasu haura shida ba, yana primary 1 a makarantar firamare, hannunshi daya kuma jaka ce shake da kayan yaron.

Kai tsaye ya kwantar da yaron a kusa da Ummah, ya dora kanshi akan cinyarta.

Ya juya ya kalli wadanda ke wajen, yace musu, "ina so ku zama shaida, daga yau, na mallakawa Ummah da na Habibu halak malak, na damka duk wata fada-aji nashi a hannunta. Daga yau kuma, ita kadai zata yanke hukunci irin na Uwa a kanshi! Ko Hadiza ban bata wannan damar ba. Ina kuma so in fada muku cewa, daga ranar da Hadiza tace zata tsallake wannan sharadi nawa, to wallahi a bakin aurenta! Kuma ko bayan nan gaba Umma ta sake haihuwa, ban yarda tayi zancen a bata dan ta ba. Allah Ya bata wani, Ya kuma sanya musu albarka."

Mutanen wajen suka yi shiru suna kallonshi jiki a sanyaye, Hadiza kuwa cikin kaduwar jiki ta mike tsaye tana ihu hannu a ka. Ta rantse ta maya wallahi bai isa ba, ai ba wani shege ya mata jinyar cikin ba har ta haihu, don haka wallahi ba zata sabu ba!

Ya tashi cikin tsananin bacin rai, dama tarata yake yi, yace, "ita da kika yi mata sanadin nata cikin, bata ce komi ba sai ke? Ba doguwar magana zan yi da ke ba Hadiza, wallahi ba don darajar iyayena ba, wallahi Allah da tuni na datse duk wata alaka dake tsakanina dake. Zabi daya ne zaki yi a cikin biyu, ko dai ki zauna a gidannan da hukuncin dana yanke miki, ko kuma in sallameki ki bar min gidana, shine kawai."

Da taga hatta iyayen nashi yau goyon bayanshi suke yi, sai kawai ta warci gyale ta bar gidan tana kuka. Ya tabe baki yace ta fi nono fari.

Cikinsu babu wanda yayi musun hukuncin daya yanke, sai sabuwar nasiha da suka yiwa Ummah na ta kara yin hakuri da yarda da kaddara, da kuma kulawa da amanar da aka damka mata. Daga nan kuma suka yi mata sallama suka tafi.

Ta dauki yaro da kayanshi, ta kama hannun Sumayyah suka shige dakinta Abdullahi yana binsu a baya.

Ba tare da an je biko ba ko wani abu, sai ga Hadiza ta koma gidan ita kadai da dare, ta shige daki ta kulle.

Shi kuwa Habibu koda ya farka ya ganshi dakin Ummah sai bai tanka ba, yayi zamanshi anan saboda dama can Hadiza din ke hanashi zuwa wajenta. Amma idan bata gidan a wajenta yake yini da Sumayyah. Ga zaman wajen Ummah da yafi na wajen Hadiza din dadi da sakewa, komi yake so shi za a bashi. Da yana wajen Babarshi ko kayan makaranta bata wanke mishi balle ayi zancen guga, kayan nan da zai je dasu ranar litinin haka zai yi ta sanyasu har zuwa juma'a, haka na Islamiya dinshi. Ga babu zancen duba mishi yadda karatunshi ke tafiya, babu kudin makaranta saboda duk sati Uban ita yake damkawa na satin, ta dinga bashi kullum. Amma bata bashi sai dai ta ce mishi ya tafi haka nan.

Amma da komawarshi wajen Ummah sai komi ya canza, kullum kaga yaro kal-kal dashi ya dau wanka. Kulawa take yi da shi kamar wani kwai.

Da yake ita kanta Hadizar bata zauna ba a gidan cikin satin, sai duk bai wani sanya kulaficinta a cikin ranshi ba. Kullum idan ta dau gyale tayi asubanci ta fita, to sai dare take dawowa. Gidajen malamai kala-kala take zuwa, ita ala dole sai an raba tsakanin Ummah da Habibu.

Ranar farko data zauna a gidan, ta tafi dakin Ummah kai tsaye lokacin su biyu ne kawai a gidan, shi ya fita, yara kuma suna makaranta.

Za ta shiga dakin, Ummah ta tareta fuska a murtuke, tace, "Malama lafiya?!"

Itama ta sha kunu, "dalla can munafuka ba ni waje! Ki fito min da kayan da na daga wannan matsiyacin dakin naki tun kafin in sake lakada miki na jaki wallahi!"

Ummah ta saki wani irin murmushi, tace mata, "an ki a fiddo kayan, na kwata ne!"

Wai sai ta kamata da dambe, kici-kici kafin ta ankare Ummah ta dagata sama ta maidata kasa ta kifar. Ta haye ruwan cikinta ta sameta ta dinga naushi da mari, sai data mata lilis.

Tace mata, "karyar iskanci ai kike yi dama, kinyi zaton haka zan zauna ki dinga buguna saboda ga ni jakar gidanku? Wallahi wannan kadan ne na miki, duk ranar da kika kara takalata a gidan nan wallahi sai an zo kwatarki a hannuna!"

Ta tashi ta barta anan, da kyar ta iya rarrafawa ta koma dakinta tana ta kukan zuci, a cikin ranta tana ta kara daukar alwashi akanta iri-iri.

42.

Daga ranar dai ta daina takalarta da fada. Habibullahi kuwa tunda ta fahimci yadda ya kwarewa Ummah kun san d'a da mai kyautata mishi ba dama, shima sai ta dauki duk wata tsanar duniya ta dora mishi. Ba damar taga ya tunkareta sai ta hau zaginshi da hantara da kyara, wani lokacin har da bugu.

Akwai wata rana data kamashi da duka saboda yace mata, 'Mama'

Ta daki yaron nan kamar wadda ta samu sa'anta tana bugu, zagi da alkaba'i kuwa iri-iri.

Ummah tana bayi tana wanka ta dinga jiyo kukanshi kamar wanda ake yankawa, babu shiri ta fito a sukwane, jiki duk kumfa taje ta kwaci yaron nan a hannunta. Ta daga hannu zata mareta, sai taga ma ai bata lokaci ne, halin Hadiza wanne ne bata sani ba? Kawai ta kama hannunshi suka wuce dakinta ta samu ta lallasheshi. Shima dai tun daga ranar nan da ya sha kashin wannan, sai ya fara baya-baya da ita, tsoronta ya shigeshi sosai da sosai.

Suka cigaba da lallaba rayuwa a haka, Ummah tana ta kara warwarewa jiki na kyau. Sumayya ta shiga aji na shida na sakandare zata zauna waec. Abdullahi da kanshi ya kaita ta cike Jamb, ta cike Medicine a Usman Danfodio University, babu yadda Ummah bata yi da ita ba akan ta cike makarantu na nan kusa dasu mana. Amma tace ita kawai Makarantar ce tayi mata. Don haka bata tsawwala ba, sai tayi mata fatan alkhairi kawai.

Suna nan ranar nan sai suka wayi gari ta dinga jiyo hayaniya kamar fada-fada a dakin Hadiza. Ta riga ta saba da hakan, don tunda aka maida Habibu wajenta bata tunanin an sake zaman lafiya tsakanin Hadizar da Abdullahi. Kullum cikin fada suke da tashin hankali. Don haka bata sanyasu a kanta ba.

Ta ci gaba da tatar kunun aya da take anan gidan, ana kai mata wani shago anan cikin unguwar, daga gidaje ma kuma ana aikawa a saya.

Sai ga shi ya fito daga dakin nata, ya gama shirin fita wajen aikinshi.

Ta biyo shi a sukwane, yadda taga Hadizar tayi wani firi-firi kamar mahaukaciya sabon kamu sai da hakan ya tsoratata. Ta dakata tana kallonsu cike da mamaki, a ranta tana tambayar me ke faruwa ne?

Hadiza ta sha gabanshi dai-dai zai sa kanshi a soro ya fita, "wai gidan wa zaka tafi Malam baka sallameni ba? Wallahi sai ka sakeni yau zaka bar gidan nan, idan kuma ba haka to ni da kai da duk jama'ar gidannan babu zaman lafiya!"

Tsaye take, amma ilahirin jikinta rawa yake yi gabadayanshi. Gashin kanta duk ya cuccure ya wani cukurkude, Ummah ta tsaya tana kare musu kallo jikinta itama yana dan rawa.

Ya kalleta yace, "wai ke wani irin bala'ine wannan da ba zaki bar ni in huta ba? Saki kike so ko? To ki je na sakeki saki daya!"

Amma maimakon tayi murna ko ta hakura, kawai sai ta kamo kwalar rigarshi, idanunta har wani tartsatsi suke yi, "Malam saki uku zaka yi min wallahi, sai ka karasa sakina!"

Abin nata sai kace mai fama da aljanu, shi kanshi kamar wanda ake tunkudawa. Bashi da niyar sakin mace idan ya aureta, shi yasa tun farko bai tashi yin aure ba sai daya ji cewa ehh lallai zuciyarshi ta nutsu da Ummah sosai. Itama kuma Hadiza din dalili kenan da yasa yake matukar yin hakuri da al'amuranta.

A ranar dai a haka ya furta mata ya saketa saki ukun da ta bukata. Ta sakeshi ta shige dakinta, kafin kace me! Ta zauna hade kan kayanta. Dama can ba wasu kaya bane na azo a gani, duk sun kare a yawon bin Malamai.

Kafin zuwan Azzuhur, Hadiza ta bar gidan kamar ba ta taba wanzuwa ba. Babu ko allurarta, ta kwashe komi.

Shima ya kada kai ya tafi aikinshi, Ummah ta tsaya nan tana ta rawar jiki. Jin furta kalmar saki ba karamin abu bane. Daga baya ta tabe baki itama ta cigaba da gudanar da harkokinta.

Tun bayan barin Hadiza gidannan sai rayuwa tayi musu dadi ta kara dadada a garesu.

Shekaru biyu bayan nan, ya biya musu aikin Hajji ita dashi, aka bar Habibu a wajen Inna. A dan tsakanin Allah Ya yiwa Malam Ibrahim rasuwa.

Suka je suka yi Hajjinsu suka sauke farali cikin dadin rai.

Kudi masu kauri ya bata domin tayi tsaraba dasu, itama kuma da nata kudin na sana'arta da take yi.

Kafin a fara aikin Hajji suka shiga kasuwa da niyar fara sayayyar tsaraba, kawai sai wata dabara ta fado mata.

Yana da aboki da yake Agent ne na Alhazawa anan garin Makkah din, sai kawai ta nemi shawararshi akan tana so ta sari kaya a auna mata su gida ta jirgin ruwa. Yace wannan ai karamin abu ne.

Sai kawai ta kwashi takalma, jakunkuna, turarukan wuta, kayan ado na mata da yara iri-iri. Aka kira yan dauri suka daure kayan nan, aka badasu aka kai aka dora a jirgi ta biya komi.

Suna komawa gida ba dadewa suma kayan suka sauka a Kano, Agent din ya hadata da wani anan Kano din yaje ya amso mata kayan aka yi clearing, aka doro mata su motar Kaduna.

Ta bude wannan kaya da wata irin nasara da sa'a mai ban mamaki. Aka yi dafifi akan wannan kaya kafin kace me! Sai ga kudadenta cas a hannu, ta samu riba mai matukar yawa.

Daga wannan lokaci sai ta fara wannan harka, a sayo mata kaya daga Makkah, a auno mata su. Idan an kawo gida Nigeria kuma taje ta amso ko kuma aje a amso mata, ta fasa ta sayar.

Cikin dan kankanin lokaci sai gashi ta zama Hajiya ta kanta, don kuwa ba karamin samu take yi ba.

Shi kanshi Abdullahin a cikin wannan shekarun ya samu karin matsayin fiye da biyu a wajen aikinshi. Don haka rayuwa tana mika musu cikin jin dadi da godiyar Allah. Har zuwa lokacin dai Ummah ko batan wata bata taba yi ba. A

shekarun baya ta sanyawa ranta damuwar rashin haihuwa, shima kuma Abdullahi din duk da cewa dai yana matukar kokari wajen ganin bai nuna mata hakan ba. Ta ziyarci likitoci da dama domin son samun tabbaci akan rashin haihuwarta, kusan duk abu daya suke mata; Mahaifarta lafiyarta lau, rashin haihuwarta kuma baya da nasaba da faduwar data taba yi. Kawai dai Allah ne bai kawo haihuwar yanzu ba. Su dorata akan magunguna ta koma gida.

Don hakane ta sake kama Habibu da Sumayyah ta rike kakam.

A wani zuwa Birnin Lagos da tayi akan wata matsala da aka samu da kayan da aka aika mata daga China, ta ci karo da wani abu daya bata mamaki.

Kasancewar Hashim a Lagos din yake, Chief Superintendent Customs Officer ne a lokacin, a ofishinshi ta tsinci file mai dauke da takardun kayan Laminu Nalado. Ta yi matukar mamaki da ganin hakan, ta samu kanta da tambayarshi, "shin me wadannan kayan suke yi ne anan?

Sai yace mata, 'ai sun rike kwantainonin ne guda biyu wadanda ke dauke da kayan Laminun da na sauran mutane fiye da watanni uku da suka wuce, saboda basu cika ka'idar da aka bada ba. Kuma suna tunanin ana smuggling abubuwan da kasa bata yarda da shigarsu ba. Amma fa hakan ba matsala bane, idan ta san mai kayan zai iya musu hanya su amshi kayansu salin-alin! Tunda a yanzu haka wadanda suka san manyanshi da dama an riga an basu nasu kayan.'

Tayi dan murmushi, ranta na wani irin suya na bacin rai da bakinciki. Tace mishi, 'ban san ko wanene ba!'

Amma bacin ran dake kwance akan fuskarta ya nuna akasin hakan. Har tayi cike-ciken da zata yi ta gama, zuciyarta cikin sake-sake take. Zuciya da shaidan suna kara kissima mata bakinciki da bakin talauci da Lameen ya sanyasu a ciki bayan daya cucesu.

Da ta gama komi tsaf, sai ta juya ta kalli Hashim, tace mishi, "ni da zaka bi shawarata ma da ka kara rike wadannan kaya ka sanya musu tsauri da kyau. Ka min alfarmar kada su koma hannun mai shi!"

Da wannan ta kulla da Hashim, aka hana Lamin kayanshi.

Koda ta koma gida bata zauna ba, zuciya ta cigaba da auna mata da ta dauki fansa, ta rama abinda Lamin ya mata. Ta nuna mishi itama fa yanzu ta zama wani figure a duniya da zata iya taka wanda ta so, a kuma zauna lafiya.

Kai tsaye ta kira Uwargidan Sarkin Bornu ta wancan lokacin, kawarta ce wadda zumuncinsu ya dore har zuwa yau. Ta roki alfarmar ta sanya ayi mata bincike akan Lamin. Cikin yan kwanakin komi daya faru dashi sai da aka sanar mata, tun daga kan arzikinshi da kuma siyasa daya shiga kai tsaye da iftila'in daya auka mishi.

Amma maimakon zuciyarta tayi sanyi tunda ga shi nan Allah Ya nunawa Lamin karshenshi tun a duniya, amma ina! Zuciya da shaidan sun gama rinjayarta. So take yi kawai ta karasa shi, kai ba shi ba ma, har 'ya'yanshi da tattaba kunnenshi. So take yi suma ta dandana musu abinda Lamin ya dandana musu.

Don haka ta cigaba da bibiyarsu da rayuwarsu har zuwa lokacin da aka sanar da ita bikin Zahra'u.

A shekarar ne Sumayyah ta gama samun kwalinta na degree akan Psychology, aka tura gidansu neman aurenta daga wani wanda suka yi UDUS dashi, Engineering yayi. Cikin ikon Allah kuma ya samu aiki da kamfanin Jordan Petroleum Refinery a Jordan, yana rokon a daura musu aure ya tafi da ita, itama kuma za ta jona second degree dinta a can.

Ummah bata so wannan aure ba, amma ganin daga Sumayya din har Fahad suna son junansu, sai ta hakurarwa ranta. Aka daura aure suka tafi.

Ba ayi wata daya da bikin Sumayyah ba aka tashi yin na Zahra'u, ta shirya tsaf ta tafi. Yadda dangi suka dinga rawar jiki a kanta duk bai burgeta ba, hasalima haushi hakan ya dinga bata. Sai yake kawai data dinga yi, a ranta tana kiransu da 'munafukai'

Da ta shiga wajen Lamin sun gaisa dashi lafiya-lafiya, yana ta rokonta yafiya da neman gafara. Tana jin shi har ya gama, sannan ne ta sanar dashi cewa ita tayi sanadin da aka rike mishi kayanshi. Wannan kuma duk ba komi bane akan sauran abubuwan data shirya mishi, ta kakkabe zaninta ta barshi anan cikin tashin hankali, yana kiran sunanta da ihun ta mishi aikin gafara.

Ta koma gida cikin murnar wannan abu. Sai ta samu wani karin abin farincikin, an yiwa Abdullahi karin matsayi a wajen aiki, ya zama General. Ga kuma wawakeken fili da aka bashi sakamakon yabawa kwazonshi wajen kwantar da wata tarzoma da ta tashi anan tsakanin Kaduna da Abuja. Suka sha murnarsu sosai da sosai, ya yanki fili a ciki yayi musu tanfatsetsen gini, tsohon gidansu kuma ya gyarawa Innah ta koma da 'ya'yan yan uwa da take riko.

Suna cikin wannan rayuwa mai dadi da kololuwar daukaka da jindadi, Allah Ya yiwa Abdullahi rasuwa a hanyarshi ta dawowa daga Porthercourt. Sai gawarshi aka kaiwa iyaye da yan uwa da matarshi. Fadin irin gigitawar da mutuwar nan ta yiwa Ummah ma bata baki ne. Sai data susuce ta dinga sambatu.

Sumayyah ta zo wajen gaisuwar daga Jordan, saboda a gareta Abdullahi mahaifin da bata tashi a gabanshi bane. Suka sha kukansu suka koshi, kafin su fawwalawa Allah lamarinShi.

Anyi sati ana zaman makoki, kafin nan dangi duk sun watse. Sumayyah ta zauna da Yayar tata har ta gama takaba, da yake ta samu miji mai fahimta da kuma tayata son wanda take so, yasan duk duniya bata hada lamarin Yayarta da na kowa, don haka bai tsawwala ba. Shi kanshi yaje wajen gaisuwar ya musu kwana uku kafin ya juya.

A dan zaman ne Ummah take fadawa Sumayyah abinda tayi, amma maimakon taga tana murna sai taga akasin haka.

Tace, "Subhanallahi! Haba Yaya! Wannan abun ai bai dace dake ba sai sam, haba don Allah! Ni wallahi tuni na manta da duk abinda ya faru a raina, ni yanzu haka wannan zuwan ma da nayi ina so ne zan karasa har can ne. Yakamata zuwa yanzu duk mu hakura da abinda ya faru, mu manta baya. Kina kallon yadda ake komi namu wai ace babu dangin mahaifinmu a ciki? Abin fa babu dadi sam!"

Ummah ta hararetа tace, "aikuwa idan kinga kinje wajensu Sumayyah, to sai bayan raina! Na rabaki da mutanen nan har abada, kuma idan har kina daukata a matsayin Uwa kamar yadda kike fadi, to ki dauki hakan a matsayin umarni. Kuma daga yau, kada in sake jin bakinki akan al'amurana. Idan ba zaki tayani ba, to kada ki kara sa min baki!"

Amma Sumayyah bata gaji ba, har zuwa lokacin da ta koma ga maigidanta, bakinta bai gaji da yiwa Ummah nasiha da kara nusar da ita ba akan rashin kyawun abinda ta aikata ba.

Maganganun nata kuma suka cigaba da yiwa Ummah kararrawa aka, suna nukurkusarta. Wani sashe na ranta dake da sauran taushi har a lokacin yana tuhumarta da anya, anya kuwa ta kyauta? Kamar fa yadda mai Hadisi, daga bakin Ma'aiki Sallallahu Alaihi Wa Sallam yace, 'ka so wa dan uwanka musulmi abinda kake so wa kanka!' Hakan fa kamar dai yana nufin, 'ka kuma ki mishi abinda zai cutar da shi kamar yadda zaka ki wa kanka ne!'

To ga shi kuma ita ta cutar da wani duk akan son kanta. Musamman da a dan lokacin aka aika musu da rasuwar Lamin din. Mutuwar ta daketa ba kadan ba, har hakan ya sanya ta kira Hashim ta roki ya saki kayan nan daya rike.

Yace mata ai a halin da ake ciki dai yanzu wannan al'amari ya girmeshi, saboda zancen da yake mata ma an nemi kayan an rasa, ana kuma zargin manyane suka sacesu.

Jikinta ya kara yin sanyi, wannan dalili yasa tasa aka mata kintacen yawan adadin kudin, ta turawa matar Sarkin Bornu wadda taje har gida ta kaiwa Dada mahaifiyarshi kudin, ta sanar da ita sakone daga Hajiya Ummah din kawai. Don haka duk da bata je wajen rashin ba, sun ji dadin wadannan kudade. Don kuwa da aka fara biyan tarin basussukan da Lamin ya bari, basu tsira da komi ba.

Aka zo aka yi rabon gadon abinda Abdullahi ya mutu ya bari, kowa aka bashi hakkinshi. Ita kanta ba karamin kadara da kudade aka bata ba na tumunin takaba kawai, balle ayi zancen Habib da ya kasance dan shi namiji kadai.

A lokacin yana ajinshi biyu a jami'a yana karantar Geography.

*

Tun bayan rabuwar Abdullahi da Hadiza, bata kara waiwayarsu ba ko da wasa. Itama kuma Ummah bata taba nemanta ba balle ta kai Habib wajenta ko na yan'uwanta. Amma duk da haka Ummah tana sane da abinda ke faruwa da Hadiza din. Don kuwa har gida ake zuwa ana bata labarin duk halin da take ciki.

Tayi aure har sau uku amma tana fitowa, a lokacin da Mahaifin Habib ya rasu tana auren wani tsohon ma'aikacin Gwamnati ne, wanda yake da mata biyu ita ta uku.

Matashi Habib sun samu hutun mid-term semester, ya taho gida cike da doki da jindadin kasancewa da Ummahn shi.

A duniya babu abinda yake tausayawa kamarta, hidima da dawainyar da take yi dashi kadai yana da tabbacin ko Mahaifiyarshi data haifeshi ba zata yi mishi hakan ba.

Da wayonshi sarai lokacin da abubuwan gidansu ke ta faruwa, har a yau kuma, bai manta dukan mutuwa da mahaifiyarshi ta mishi akan ya kirata da Mama ba. Tun daga wannan lokacin ya yanke shawarar ja da baya da ita.

Amma bayan rabuwarsu da mahaifinshi shi ya dinga zuwa inda take, ita ce dai bata son ganinshi har a lokacin. Ya rasa wani irin laifi ya aikata a gareta har haka? Abun kuma yana matukar yi mishi ciwo nesa ba kusa ba. Ya daukarwa kanshi duk lokacin da zai je wajenta zai samu wasu yan kudade ya tafar mata da su, musamman da yaga yanayin rayuwa da suke ciki ita da yan gidan da take zaune, don kuwa iyayenta sun jima da rasuwa.

Hakan ne kadai yake dan sanyawa yaga sakin fuska a wajenta, duk da cewa dai bata daina zaginshi da cewa shi sallamamme bane a yawancin lokuta.

Zuwa na karshe da yayi wajenta, gidan aurenta na biyu da yaje, lokacin ajinshi biyar a sakandare. Ta bukaci tarin kudi a hannunshi, wai jari take so ta tada saboda kishiyarta tana mata gorin bata da sana'a. Iyayen kudin data nema sai da suka yaji kanshi yana juyawa. Yace mata, 'q ina zan samo wadannan kudade? Nima fa har yanzu bani ake yi, ba kuma tarasu nake yi ba!'

Anan tayi mishi kora ta wulakanci, tace mishi, 'ita ai dama tuni da ta sallamawa Ummah shi, don kuwa yanzu bata ma sanyashi a cikin jerin wai 'ya'yanta, tuni da ta rufe babinshi. Kada kuma ya kara zuwa inda take, kudin ma da yake kai mata ya daina bata so daga ranar. Idan kuma ya sake komawa to wallahi sai ta tsine mishi. Ai duk da dai ta sallamawa Ummah shi, amma har yanzu tana da hakkin tsine mishi kuma tsinuwar ta bishi!'

Ya koma gidansu rai a matukar bace da wannan rashin adalci nata. Ya kuma yanke shawarar daga wannan rana, ya gama.

Yana sanya kai cikin falon gidansu, ya tsinci tashin muryoyin da ko a cikin maye yake, ba zai taba kasa shaidasu ba. Ummah ce da mahaifiyarshi Hadiza suke wasu maganganu da suka tayar mishi da hankali.

43.

Hadiza ce take cewa Ummah cikin daga murya, "tunda dai ba ke kika yi min nakudarshi ba, to ki tattaro min kudaden shi na gado da aka bashi kike neman yin ruf-da-ciki a kansu ki bani, idan kuma ba haka ba kotu ce zata rabani da ke!"

Hajiya Ummah kallonta ta dinga yi cikin mamakin irin wannan karfin hali nata, ta daga baki daga baya da kyar tace mata, "kin manta ke da bakinki kika sha fadin kin sallamawa Habib ni duniya da lahira? Ko kuwa kin manta cewa tun bayan tafiyarki baki taba waiwayarshi ba wai da sunan son jin abinda yake faruwa da shi? Sai yanzu kuma rana daya ki zo sama ta ka kice wai kinzo amsar rabon gadonshi? Ashe ma ba don shi ba kika zo nan kenan?"

Tace mata, "Duk abinki dai, baki isa ki raba hanta da jini ba wallahi. Habibun ai da na ne, ni na sha nakudarshi da wahalarshi da rainonshi, ke da kika tsinceshi daga sama? Ko wannan wahalar kadai ai ta isa zama hujja a kanki. Ki daina ganin wai na koma gefe na zuba muku ido kiyi zaton zan kyaleki ne ki bi ta kan kudin gadon yaro ki zaune, ki shiga ki fito min da kudi nace!"

Ita da Ummah din sai suka hau fadi-in-fada. Duk yana jinsu, jikinshi yana rawa da kakkarwa saboda tsananin takaici da bacin rai.

Abinda ita Hadiza din bata sani ba shine, ita kanta Ummah bata ma san iyaka adadin kudaden da Habib din ya mallaka ba na gadonshi, tasan dai har da wannan gida da suke zaune, da manyan filaye da gonaki. Kudade da takardu kuma duka ta damkasu a hannun Uncle Hashim, tace ya rike mishi har zuwa lokacin da zai kammala karatunshi, idan ya tashi aurenshi sai ya bashi kudin. Hatta da wannan makarantar da yake yi, a cikin aljihun Hajiya Ummah ne ba tare data taba mishi ko sisin kwabo a kudinshi na gado ba.

Ya duba yaga wai wannan ma wadda basu hada alaka bace ko ta jini take mishi haka. Me yasa to mahaifiyarshi ba zata mishi hakan ba? Me yasa ita kullum sai dai tace ya bata? Me yasa kuma duk lokacin da zasu hadu sai dai tace ya bata kudi. Kudi dai kullum!

Bai san lokacin daya danna kai ya shiga dakin ba. Sai ganinshi suka yi tsulum kamar wanda aka jefa daga sama.

Idanu cike da hawaye yake kallon Ummah, ya ma kasa duban inda Hadiza din take saboda tsoro da gudun abinda zuciya zata iya sanyawa ya furta mata.

Ya cewa Ummah, "Ummah, ki bata duk abinda take ganin zai isheta daga yanzu har rayuwarta ta kare. Amma don Allah kada ta sake waiwayar inda nake daga yau. Ke din ke kadai kin isheni a rayuwata!"

Ya juya ya fita daga falon da sauri. Hadiza ta tashi zata bi bayanshi tana ihu da hargagin, "au!! A gabana kake nuna an gama wankewa an baka kenan! Ai ni dama nasan ba haka kawai aka barka ba, nasan dama da kyar idan ba farraku aka mana ba! Wane d'a ne zai fita sha'anin Uwar da ta haifeshi saboda wata bare? Ai wallahi daga gani dama ba kanka daya ba!"

Tayi zage-zagenta ta gama, ta koma ta zauna tana hura hanci kamar wata tsohuwar macijiya. Ummah tana zaune tana kallonta har ta gama, ta kalleta tana zare ido, "sai ki shiga ki dauko min hakkina ko?"

Ummah ta kalleta a nutse tace mata, "ki fadi abinda kike so, amma fa da sharadin ki fita rayuwar Habibu kamar yadda yace."

Ta ambaci kudaden da yawa kwarai, Ummah kuma bata yi musu ba, ta dauki waya ta kira Uncle Hashim a take aka tura mata ta lambar account din data bada.

Ta tashi cikin tsananin murna jikinta har yana rawa, ta yiwa Ummah sallama babu ko godiya. Sai data juya zata tafi Ummah ta tsayar da ita, tace, "ki

dauka wannan shine karo na farko kuma na karshe da zaki zo nan gidan da sunan neman kudi. Ke baki ji kunyar kanki ba? Tunda yaron nan ya tashi, koda wasa baki taba neman inda yake ba ko kin duba halin da yake ciki ba, sai yanzu kuma wai kice ke kin zo a baki kudi sai kace kin ba wani ajiya?"

Hadiza tace mata, "aikuwa idan kina tunanin wai zan kyaleku haka to kina mafarki ma kenan!"

Ta sa kafa ta tafi.

Saboda takaicin wannan abu daya tarar yasa bai ma yi sati biyun da yayi niyar yi ba, kwananshi biyar ya juya. Tun kuma daga ranar bai kara waiwayar lamarin Hadiza ba. Zuciyarshi na shan gaya mishi ai tunda har ta kaisu ga haka, to zancen mu'amala irin ta uwa da d'a ta kare a tsakaninsu. Idan basu yi mu'amalar kirki a yanzu ba, yaushe zasu yi ta?

A haka har ya kammala karatunshi, aka musu aure da Hidaya. Har gida kuma aka je aka sanar da su Hadiza din, amma sai danginta ne suka yi dafifin zuwa amma ita ko a leke.

Lokacin tana can a kwance ita jinya ma take yi, mijinta ya lallaba ya ranci kudin data amso a wajen Ummah, ya dankaro mata kishiya. Shekara da shekaru kudi sun ki fita daga hannunshi, karshe data tambayeshi ma sai ya sameta da diyarta Rashida wadda ta haifa a wancan gidan data fita, ya musu lilis, ya dankara mata saki. Karshe sai kishiyar ce ta ja jikinta kofar gida ta yasar. Sai yan unguwa ne suka taimaka mata suka dorata akan abin hawa ya kaisu gida.

Wannan takaici da abin kunya shi ya hanata fita. Gashi a lokacin ta fara shiga taitayinta, don kuwa duniya tuni tayi mata atishawar tsaki. Shi kuma Habibu sai yayi tunanin duk cikin rashin son da take yi mishi ne ya hanata halartar bikin nashi.

Dukiyarshi duka ta koma hannunshi bayan aurenshi, sai ya bi bayan Ummah da take da manyan shaguna na kayan kwalliyar maza da mata inda ake kai mata su daga Turkey, Japan, Indiya da sauran kashashe na duniya. Shi kuma sai ya hada har da su electronics. Amma sai ya sanya ragamar kula da wajen a hannun Ummah din, shi dai kawai sunan mai wajen ne amma bai ma san

ya yake ba, sai dai duk shekara a ware mishi ribar da aka samu a sanya mishi a akawun.

Ya dora degree dinshi na biyu akan politics saboda ya dade yana tunani da shawarar shiga harkar siyasa, koda kuma ya nemi shawarar Ummah sai ta mara mishi baya. A ganinta hakan zai kara mata wani karfi na musamman.

Bayan rasuwar Hidaya, ya kammala karatunshi. Bai shiga harkar siyasar ba kai tsaye, sai daya fara aiki da hukumar In-Land revenue ta nan Kaduna, ya kuma kara samun Ph.D akan Politics, har sai daya kai matakin Deputy Director, sannan ya fito harkar siyasar tashi gadan-gadan.

Ya samu goyon bayan Hajiya Ummah da Uncle Hashim sosai da sosai, don kuwa da taimakonsu ne sunanshi yayi shura ya zagaye fadin Kaduna da kewayenta. Ga kuma surukinshi mahaifin Shukurah wanda ya kasance shima tsohon dan siyasa ne wanda aka dama dashi a siyasar garin Kaduna.

Hadinshi da Nadiya zai iya cewa hadine na Allah. Tun bayan daya shiga harkar zabe officially, Ummah ta matsa lallau yana da bukatar karin wata matar saboda su kara samun karfi sosai da sosai.

Ya duba duka tarin hotunan da ta nuna mishi na yan matan dake cikin danginta da kuma 'ya'yan manyan mutane da sarakuna da take ganin zasu dace da tsarinshi, hotuna biyun data ware tana kara nuna mishi ne ya dan dauki hankalinshi. Yanmata ne kyawawa, zancen kyau ma ba a maganarshi don kuwa duk ta ko'ina Allah bai yi musu makusa ba. Sai dai daga ganinsu daya ta girmi daya. Take fada mishi cewa su dukansu yaya da kanwa ne, mahaifiyarsu tana da fada-aji sosai da sosai, za kuma ya iya takalawa duk inda yake son zuwa da taimakonta.

Kallon fi-sha yayi musu a lokacin su duka, a yadda yake shan takaddama da Shukurah ma kadai gani yake matsalarta ta isheshi ba sai ta kara da wata ba. Ya cewa Ummah din ta bashi lokaci zai yi tunani dai, ya kuma fadi hakan ne ba don har cikin zuciyarshi ya yarda zai yi tunanin ba.

Hadiza dai tun bayan kashin da ta ci, ta yiwa kanta karatun ta-nutsu. Ta koma gidan Hajiya Ummah da gwiwa a sage taje bata hakuri, Ummah da a lokacin yan zuga da shaidan sun gama zugeta ganin irin matsayin da Habibu yake shirin takawa. Tayi biris da ita ta kuma ki sanar da Habibu zuwanta, haka ta dinga mata zarya tana rokonta ta hadata dashi ta bashi hakuri ma, amma Ummah ta ki.

Sai can wani lokaci Allah Ya taimaketa taje fitowa daga gidan, taci karo da motarshi zata shiga. Shine ta tsaida shi, ta sanyashi a gaba da kuka da neman gafara. Ya dai furta mata shi dama bai riketa ba a ranshi, amma a ranshi ya kasa ya sake da ita balle har ya sakar mata jiki.

Haka take ta kokarin jan shi a jikinta amma abu ya gagara. A haka ta sake fitar da wani manemi dake zaune a Makarfi ta aura. Shi yayi musu hidimar komi ta biki, tun daga kan kayan gado da komi ma, ya kuma nemawa Rashida makaranta mai kyau a can tana zuwa, ya dauki nauyin karatun nata. Ya kuma ajiyewa Hadiza din mota da ake jigila da ita duk inda zata je. Abinda ke hadasu da Hadiza din kenan.

Duk zuwan da zata yi Kaduna sai taje ta gaishe da Hajiya Ummah, haka lokaci zuwa lokaci Rashida ta kan je gidan ta dan yi musu kwana biyu. Amma har lokacin daga Habibun har Hajiya Ummah din basu saki jiki da ita ba.

Rashida ce ta dameshi da waya tana kuka da ranta, tana rokon yaje ya ga Ummansu. Bata da lafiya kwarai, a kwance rake ranga-ranga amma sunanshi kadai take kira tana cewa tana son ganinshi.

Ummah da kanta tace mishi ya kamata yaje, a matsayinshi na magidanci kuma ma wanda ya fita siyasa, bai kamata a sameshi da wata baraka ba shi da iyayenshi.

Don haka ya shirya tafiya a wata safiyar ranar Lahdi, ya dauki Ammar suka tafi don kuwa daga shi har Ammar din wannan ne karo na farko da zasu je inda take.

Ya sameta din kuwa gata nan rai a hannun Allah, typhoid da malaria sun kaita kas. Takaicin halin daya samesu a gidanta ne ya bata mishi rai kwarai da gaske. Miji ya tafi ya barsu a gidan haya, a wata unguwa mai tarin

kwatami da bola, ga babu abinci. Sai ya dauki fiye da sati biyu bai je inda suke ba, kuma wai da sunan anan cikin garin yake da zama. Yana da wata matar a can yake tarewa a wajenta.

Ranshi ya baci ya jagule kwarai da gaske. Yayi waya a take ya bada umarnin a sama musu gida madaidaici a unguwa mai kyau su koma can. Don ya nuna mata ta koma gida mana abinta? Ta nuna mishi ta dai fi ganewa zama a gidan aurenta haka nan. Gwanda kawai ta girbi abinda ta shuka, don kuwa hakkinshi ne da na Ummah yake bibiyarta. Sai ta hau kuka kuma.

Ya kalleta kawai, ranshi yana cike da tausayinta, amma kuma ya kasa yi mata wata magana ko ya bata hakuri.

Ya tashi ya fita sakamakon kiran da aka mishi cewa an samu wani gidan mai kyau anan bayansu ba nisa yaje ya gani, akan hanyar zuwan ne suka tsaya da niyar sayen wani abin ya sha shi da Ammar don kuwa ko karyawa bai yi ba, suka ci wannan karo shi da Nadiya wanda ya kira hadi na Allah.

Har suka je suka ga gidan da aka samu, aka gama komi da komi, amma ba zai iya cewa ga rabin abinda aka ce ba. Hankalinshi ya linka yayi wani waje na daban, tunani yake a ina ya taba ganin wannan fuska? Menene kuma a tattare da ita dake fuzgarshi kamar wani maganadisu?

Bai ganeta ba sai da suka hadu a hold up dinnan. Kai tsaye kawai ya tuna ashe fa hotonta ya gani cikin jerin yanmatan da Ummah ta nuna mishi, duka-duka ko sati daya cikakke ba ayi ba.

A wannan rana ya kwana ya wuni cikin wani irin tunani da tu'ajjibi mai tsanani, banda zuciya da rigima, daga ganin sarkin fawa sai miya tayi zaki?

Asubahin fari ya kira Mami, ya fayyace mata abinda ke faruwa. Wannan yarinya dai ta mishi, a kwatancen da yayi mata kai tsaye tace mishi Nadiya ce! Ya kama sunan nan yana nanatawa a fili da boye sai kace wani zararre. Tace mishi ya barta da Ummah, don taga hankalinta ya fi karkata a wajen wata diyar Sarkin Gumel, amma zata san ta yadda zata bi mata.

Don haka koda Ummah tace mishi ya shirya zasu je Maiduguri, ya ga ko da wadda zai zaba cikin yanmatan danginsu, babu musu ya bi bayanta musamman da Mami tace mishi ai Nadiyar ma zata je.

Abinda daga Nadiya har Madam din basu sani ba shine, tun ma kafin su Hajiya Ummah su karasa Maiduguri, Mami sun gama magana da Uncle Hashim kan cewa Habibu ya samu mata a can. Mami ita ta kira Ummah ta fada mata cewa ita da kanta ta zabarwa Habibu Nadiya, saboda ta binciki nagartarta ta kuma aminta da ita. Kuma ko anan, sai data gargadi Ummah da cewa idan ba zata iya kawar da kai ta manta baya ba, kada aja maganar auren da nisa. Da a auro yarinya daga baya Ummah ta dinga daukar alhakinta, babu yarinyar da namiji zai aura kuma uwarshi bata sonta, taji dadin wannan aure.

✷✷

Hajiya Ummah tayi kukanta ya isheta, Mami tana zaune kusa da ita tana shafa bayanta cikin alamun lallashi.

Ta cigaba da mata magana cikin sanyin murya, tace, "ki fa auna ki gani Yaya, sanadin abinda Yaya Lamin ya miki ne kika kasa hakuri har kika yi wannan kullaci da rikon, kike aikata wadannan abubuwa da ko wasu yaran ba zasu iya aikatawa ba. To a tunaninki, idan kika yi kwatankwacin hakan su su Madam suma ba zasu kullaceki bane? Ba fa zasu taba fahimtarki ba, su ma kuma zasu iya retaliating, su ce zasu dauki tasu fansar. Ashe kenan haka zamu cigaba da tafiya babu wata maslaha ko sulhu a tsakaninmu, har 'ya'ya da jikokinmu su zo su tarar da hakan?

Ke ce babba, ke ya kamata kuma ki tsayar da wannan abun haka nan don Allah! Ki fa duba Nadiya yadda take girmamaki da kallonki a matsayin Uwa. A ganinki me zai faru idan kika kaita bango, ta daina girmamaki, ta fara mayar miki da raddi? Wallahi Girma ne zai fadi Fadi!"

Hajiya Ummah ta bude kunne tana sauraronta da kunne na basira. A yau baya take dubawa, ire-iren abubuwan da take aikatawa musamman ga Nadiya, a yau duk sai taji kunyar yarinyar ta lullubeta. Lallai ko a haka aka tsaya ita tasan cewa faduwar Girma ai sai dai wani in akwai, amma da kyar idan wannan bai zube ba. Haka kawai duniya da son daukar fansa marar amfani ta rufe mata ido, ta mayar da yarinya sai kace wata kishiyarta? Duk da hakuri da ita da take yi da kokarin da take yi a kanta?

Ta juya ga Mami tace mata, "to ya zanyi yanzu Sumayyah? Ina so in so ta nima, in bata hakkinta na diya kuma suruka. Amma wallahi da na ganta na tuna ita din jikar Lamin ce, sai inji na kasa! Mutumin nan ya cucemu a rayuwarmu!!"

Mami ta kara sanyaya murya, tace, "Yaya wannan aikin ke kadai zaki iya yin shi. Daga lokacin da kika cire tsanar Lamin a ranki, wallahi komi na rayuwarki ma sai yafi miki dadi. Ki daga ido ki dubi yarinyar nan ki tunawa kanki, bayan jikar Lamin, ita din diya ce a wajenki, kuma suruka. Sai kiga hakan ya wanke miki duk wani kullaci na ranki. Ke zaki fuskanci Ubangiji, ki rokeshi yafiyar kin sanyawa ranki salama da hakuri da afuwa da yace ayi idan an zalunci mutum, ki kuma rokeshi ta yaye miki wannan kuncin na ranki. Rayuwa dai tafiya take yi, wallahi bamu da sauran lokacin tsayawa tuhumar wani kan laifukan da suka yi mana bayan muma masu aikata laifin ne. Watakila ma idan aka waiwaya namu yafi nasu yawa a wajen Ubangiji. Ni dai ina baki shawarar, ki yi hakuri ki taushi ranki, ko kin samu salama a cikin ranki. Maiduguri kuma in Allah Ya yarda zan je, nima ina so in gano yan'uwana haka nan!"

Ta gyara gefen gado tayi kwanciyarta ta juyawa Ummah baya ta barta tana saka da warwara. Barci ya dauketa ba tare da tasan lokacin da Ummah din ta kwanta ba. Amma can cikin dare ta farka ta ganta ta fuskanci gabas a cikin sujjada, sai tayi murmushi mai dadi a cikin ranta, ta juya ta cigaba da barcinta.

44.

Cikin kwanakin gabadaya ta kasa ganewa kanta abinda ke faruwa da ita. Wani irin bacin rai na babu gaira babu dalili take fama dashi. Da abinda ya kai, da ma wanda bai kai ba sai kawai taji ranta ya hau ya baci. Shi yasa ta ke baya-baya da kowa ma a gidan don tasan ba lallai ta dinga iya kawar da kai idan an yi mata wani abun ba.

Ta koma yini a dakinta ta kure volume din karatun Qur'ani tana ji, ko ta dauka ta dinga karantawa ko Allah Yasa ta samu sassaucin ranta. Ta kuma rike hailala da tasbihi tana ta yi babu kakkautawa.

Suna zaune akan dinning su dukansu ana karin safe, ranar Alhamis ce. Bata tashi da azumi ba ranar saboda ranar girkinta ne, ga Babangidan yana gari.

Duk kayan ciye-ciye da aka cika musu kan dinning din dasu, ta kasa cin komi. Ga masa nan anyi tayi sharr gwanin kyau da miyar gyada wadda ta sha alayyahu da ganda da tantakwashi. Daga fari dai yawunta har gudawa ya dinga yi lokacin data ga masar, amma kuma tana kai ta baki da kyar ta iya hadiyewa, zuciyarta ta fara tashi.

Sai tayi tsam ta tashi, ta lalubo lemon tea a kicin ta hada shayi da ita ta zauna tana sipping a hankali.

Kan teburin ya kaure da hira ana ta raha, in ka dauke ita da take binsu da kallo kawai tana dan murmushi, sai kuwa Shukurah da take fama da tablet a hannunta, bata ma fahimtar me suke cewa.

Mami ta kalli Hajiya Ummah tana ce mata, "Ummah ni dai jibi in Allah Ya kaimu zan tafi wajen bikin Halimatu. Ina so in ga dangi sosai kafin a fara hidimar bikin nan."

Ummah tace mata, "to ni menene nawa? Allah tsare kawai zan ce muku, na gama hada gudummawata tunda ba zan samu damar zuwa ba. Idan zaki tafi sai ki wuce musu da ita."

Jin haka sai Nadiya tayi saurin cewa, "aikuwa dai nima zan biki sai mu tafi tare. Tunda dama nima kafin bikin zan tafi, kuma kinga nan da kwana hudu ne ake fara bikin."

Mami ta kalleta kafin ta maida dubanta ga Babangida daya tamke fuska, tace, "to! wannan kuma ga ki ga mijinki nan ai!"

Ta daga baki da niyar cewa ai dama sun riga sun gama yin maganar da shi, kawai sai taga mutum ya ci magani yana kallon Mami din, yace, "Mami kiyi gaba ke, ita sai gobe daurin aure zata je!"

Ta juya tana kallonshi cikin tsananin mamaki, "kamar ya? Tun ranar nan fa muka magana da kai, ka kuma ce babu matsala. Idan na tafi ana gobe daurin aure, yaushe har na huce gajiyar tafiya kuma mu juyo Kano da kwana biyu?"

Yace mata, "idan hakan bai yi miki ba kinga sai ki hakura da zuwa bikin kawai. Idan an kawota Kano din sai ki cire rana guda kije ki mata yini ki dawo!"

Kasa ce mishi komi tayi har ya hada kan wayoyinshi ya fita daga falon. Mami ta bishi da kallo tana dan murmushi kafin tace mata, "kar ki biye mishi kinji Nadiya? Fade kawai yake yi amma ai shima yasan wasa ne hakan."

Sai ta gaza ce mata komi, don kuwa tasan shi da iyakar gaskiyarshi yake fada.

Da dare ta iskeshi a dakinshi, har zuwa lokacin ranta bai gama warwarewa da wannan abun da yayi mata ba. Ta yini tana tura mishi sakon ya taimaka ya canza shawara, ya bari itama ta ramawa kura aniyarta, tunda dai shima ai ya shaida irin kokarin da Anty Lima ta musu a nasu bikin. Amma ya ki maida mata da amsa ko daya.

Ta shiga dakin ran nan a cune, dama mai neman kukane aka jefeshi da dunkulen kashin awaki. Shi kanshi kuma sai daya kula da hakan.

Ya janyota jikinshi lokacin da take zaune a gefen gadonshi, ta shaki kamshin turaren nan nashi da a lokacin take jin kamar an kara mata dadinshi a cikin ranta.

Yace, "wai maganar tafiya bikin nan dai ba zata kare bane Nadiya? Kiyi hakuri ki zauna a gidanki don Allah Nadiya, wallahi a ko'ina nake kawai idan na tuna kina gidana a zaune kina jiran dawowana, sai inji dadin hakan a cikin raina da wata kwanciyar hankali ta musamman na shigata!"

Tace, "to kuma kai da kasan mun fa gama maganar nan tun ba yau ba Baban Ammar, kuma gidan nan naga ba ni kadai bace, ga Anty Shukurah. Hakan ai ba zai zame maka wata matsala ba."

Ya fara gudanar da abinda yafi so a tattare da ita, wato bin ilahirin wuyanta da sumba, har ya gangara zuwa kunnenta ya kama masangalin da harshenshi. Yace mata, "ba zaki gane bane Nadiya! Ke din ce bani son rabuwa da ke ko da na dakika ne, ina ga kwanaki dai-daya har goma?!"

Ganin yana kokarin canza hirar tasu yasa ta ja baya daga gareshi tana kare kirjinta da hannu. Ya dakata yana kallonta cikin wani yanayi data kasa fahimta, "meye hakan Nadiya?"

Ta dan ciji lebenta na kasa, "ni dai gaskiya sai ka bari zan bi Mami sannan!"

Sai ya mike tsaye cak, wannan karon bacin ranshi ya nuna sosai akan fuskarshi, irin wanda bai taba nuna mata ba. Har sai data fara dana sanin bin wannan approach din. Amma wata zuciyar na zugata, kada ta karaya, kada ta bashi kofar da zai fara yi mata kulle da hanata zuwa sabgar dangi.

Yace mata, "ashe kenan kema ban isa dake ba Nadiya? Yanzu ban isa in gindaya miki sharadi ki bi ba? Shine zaki biyo min ta wannan hanyar? Ina fada miki wannan ne don kawai nan gaba ki kiyaye, babu abinda na tsana a duniyata irin wannan abun, holding sex against me akan wani abu can na daban da neman biyan bukata. Ita wadda take min hakan ki tambayeta kiji abinda hakan ya haddasa mata a wajena, idan ma ita take zugaki kika hau kai kika zauna saboda baki da kan gado, to ta gama dake. Tafiya biki kuma na kasheta gabaki daya. Don Allah idan ke kike da ikon kanki ki tafi ga hanya nan!"

Ya juya ya fita fuu! cikin fushi. Ta bishi da kallo, ita ba abun tayi fushi ba ko tayi dariya. Ban da abinshi, yaushe ma ta samu damar yin maganar arziki da Shukurah balle har ta zugata wai akan ta dinga guje mishi?

Ita tunda take da shi ma bata taba sanin irin wannan rayuwar suke yi da Shukurah din ba sai yanzu. Don haka sai taji ranta duk babu dadi. A ranta ma dai tasan hakan ba dai-dai bane, ba kuma haka yakamata ta bullo mishi ba. Don haka ta tashi ta gyara jikinta ta fita ta sameshi a falo a zaune yana latse-latsen channels da remote, har lokacin cikin fushi yake kwarai.

Ta karasa a hankali kusa da shi, fuskarta na nuna nadamar hakan data aikata mishi. Ta duka ta dafa gwiwarshi tare da tausasa muryarta, tace, "kayi hakuri Abban Ammar, nayi nadamar abinda na aikata maka. Don Allah ka yafe min, idan kuma zancen tafiya ne in shaa Allah na cireta daga raina tunda baka so!"

Ya dan kalleta, da gaske fuskarta ta nuna nadamar hakan, ya kuma hangi alamun da gaske take yi, zata iya hakura da tafiya wajen bikin duk da yadda take matukar son zuwa. Sai yaji ta bashi tausayi, ya kamota ya zaunar da ita cikin jikinshi yana mata magana a hankali.

"Zan fi so ko abu kike so ko nayi miki wani laifi na daban Nadiya, ki zaunar da ni ki fada min. Ko ban amince ba ko na amshi laifina a take ba, I promise idan kika yi hakuri kika dan bani lokaci kankani, zan iya canza shawara. Amma bana so, Koda wasa ki sake yi mun hakan, bana so ko kadan kinji baby?"

Yadda ya kira babyn ne cike da kulawa da so, sai taji jikinta yayi sanyi. Ta kwantar da kanta a kirjinshi tana gyada kai a hankali. Ta dauki hannunsu daya sarke da nashi, ta mannawa bayan hannunshi sumba a tausashe, "kayi hakuri!" ta furta hakan a cikin karamar murya.

Ta samu dai ya yarda ta bi bayan Mami din, da sharadin da an kai amarya to washegari ta dawo gida, bai kara mata ko kwana daya ba. Tayi sauri tace taji ta yarda ta amince.

Daren ranar dai ita da barci suka yi hannun riga, don kuwa cewa yayi sai ta fanshe mishi kwanakin da zata tafi ta barshi shi kadai yana yawo a garin Kaduna sai kace wani gwauro.

Washegari su Ammar suka tasheta daga barcin wajen karfe goma sha daya. Ta bude musu kofa shi da Farida suka shiga, su suke fada mata cewa Mami ce tace su je su tayata hira, ita ta tafi unguwa.

Lokacin kari ya wuce, kuma ba yunwa take ji ba. Tasan ko ta fita ma ba lallai ta iya cin wani abu ba. Don haka ta barsu a falo suna wasansu, ita kuma ta shiga kicin ta fara tunanin abinda zata hada da sauri ta karya.

Ta hada wapple da yayi taushi tubus, ta yi topping da whipped cream da inabi ta zauna tana ci bayan ta hada shayi ta zabga mishi lemun tsami. Don gani take idan bata ci wani abu mai lemun tsami ba tashin zuciya zata cigaba da yi.

Su Farida suna gefe ita da Ammar suna cin wanda ta zuba musu.

Sai ga knocking anyi, ta bada iznin a shiga. Sai ga Bishola, ma'aikaciyar gidan. Tana ganinta ta sha jininta, ila kuwa tana gama gaisheta, sai ce mata tayi, "Ummah ce tace a kira Ammar!"

Yaron ya kalleta da sauri yace, "to ai Ummah ce da kanta tace mu taho nan. Kuma ranar nan ma da kika ce tace inje, tace ba ita bace!"

Nadiya bata fahimci inda zancen nashi ya nufa ba, kawai sai ta kallesu tace musu, "ku je tunda ita ta aiko!"

Suka tashi simi-simi suka bi bayan Bishola.

Ta bisu da kallo a ranta tana wani tunani. Wannan wai wace irin rayuwa ce suke yi a gidan nan ne?

Taji wani irin bacin rai ya dabaibayeta, taga yau idan ta shanye wannan maganar kila zuciyarta ta buga, ta fadi ta mutu a banza babu wanda za a yiwa asara a gidan.

Kawai sai ta sabi gyale a kafada, ta wuce sashen Hajiya Ummah buguzum-buguzum kamar wata kububuwa.

Yaran suna falo suna kallo, ta haye sama da sauri ganin Ummah din bata nan kasa.

Ta ci nasarar samunta a falon kasa tana kallon labaran safiya a tashar Farin Wata.

Ta duka a gabanta tana kwasar gaisuwa, kafin ta kai ga gama amsawa Nadiya ta rushe da kuka.

Sai ta bita da kallon mamaki, murya a dan daburce ta fara tambayarta, "subhanallahi, Nadiya! Me ya faru ne? Me aka yi?"

Ta bude baki tana magana, amma yadda shessheka da kuka suka ciyota, ba a ma fahimtar abinda take cewa.

Ganin haka sai Ummah ta kamo hannunta da kanta, ta zaunar da ita akan kujera kusa da ita, tana shafa bayanta a hankali cikin lallashi da kulawa da suka ba Nadiya mamaki.

Ita har ga Allah bata ma san takamaiman kukan me take yi ba ko musabbabinshi ba. Amma bata yi tsammani samun wannan kulawar daga

gareta ba. Tayi tunanin kyararta zata yi ko tace ta tashi ta bata waje bata da lokacin wannan shirmen.

Ummah sai data ga ta nutsu, ta daina kukan, sannan tace mata a tausashe, "yanzu kiyi min bayanin abinda kike cewa yanzu. Menene akan zancen Ammar da rashin son kusancinku da menene? Na kasa fahimtar abinda kike fada sam!"

Sai ta sadda kanta kasa a kunyace, a ranta tana fadin dama tayi hakuri ta taushi zuciyarta bata zo da zancen ba. Me zata ce mata yanzu? Ta dai tari aradu da ka, ta fara magana kanta a kasa.

"Ummah, nasan cewa I'm not your favorite person a gidannan, wanda ban san dalilin hakan ba amma idan ma nayi miki wani laifine da ban sani ba, ko wani nawa ne yayi miki hakan, don Allah a madadina da nasu su duka ina rokonki da kiyi hakuri. Amma sai in ga hanani kusanci da kike yi da Ammar kamar ba mafita bace mai kyau, tunda ko babu komi naga yana son zuwa wajena, kuma nima ina son yaron. Sannan bana tunanin ina kokarin canza mishi halinshi ne ko dabi'a."

Ummah tayi shiru tana saurarenta a nutse. A ranta cewa take ranar da Sumayyah take ji mata tsoro gata nan ta zo! Tunda har an fara zuwa ana confronting dinta, ai ana gab da fara fadi-in-fada ita da suruka.

Amma abinda bata gane ba kuma take son ganewa, shine;

"... me ke faruwa da Ammar ne da kike cewa ina son shiga tsakaninku? Ban fahimceki ba?"

Nadiya ta kasa kallonta, sai ta gyara zama ta fada mata yadda duk lokacin da Ammar yaje bangarenta take aika Bisola ta ce yaje tana nemanshi?

Ummah zaune tayi sandardar a zaune cikin mamaki, don kuwa ita dai bata ma taba jin wannan zancen ba sai a ranar.

Don haka ta kalli Nadiya tace mata, "dan bani minti daya!"

Ta tashi ta dauki waya ta kira chief security ta gidan, suka yi maganarsu kasa-kasa wadda Nadiya bata jin abinda suke cewa. Amma dai ta sha jinin jikinta da cewa akwai matsala. Gabanta ya hau faduwa, a ranta cewa take dama dai bata hau dokin zuciya ta biye mata ba ta zo wa Ummah da wannan zancen.

Shukurah tana zaune gaban madubi, shafe-shafe ta gama, tayi kwalliyarta sosai cikin wata jar abaya. Wani taro ne ta hada na manyan mata yan siyasa, don su taru su karawa juna sani akan hanyoyi da dabarun samun nasarar kamfen da iya tafiyar da mulki. Don har matar Gwamna mai ci sai data gayyata.

Aka buga kofar dakinta sau biyu, ta bada izini, aka shiga.

Yar aikin ta karasa gabanta, ta duka tana mata rada a kunne. Kai kawai ta gyada mata alamun ta gamsu, ta daga gaban drawer dinta ta ciro kudi a cikin envelope ta mika mata. Ta amsa da rawar jikinta tana mata godiya, ta bude kofar dakin ta fita cikin murna. Sai tayi turus ganin Mrs. Atiku, Chief Security dinsu. Ita ce mai kula da duka securities da yan aikin gidan. Wadda bata wasa da aikinta ko kadan, bata kuma taba bada kofar da za ayi wasa da aiki tana gani. Karya da zamba da munafunci suna cikin manyan abubuwan da bata aminta dasu.

Don haka tunda Bisola taci karo da ita, tasan cewa tata ta zo karshe! Tun ma kafin ta mata magana ta fara hawaye da neman gafara, ta duka kasa takardar kudin da aka bata itama tana faduwa. Ta duka, ta duba taga kudin dake ciki shake, ta dan gyada kai tana kallonta cikin nuna alamun ba sani ba sabo, tace, "kije wajen Shu'aibu, zai baki takardar sallamarki da kudin da kika ci na wannan watan. We no longer require your service!" Ta tsallaketa ta wuce ta barta anan tana kukan nadama.

Dakin Shukurah ta wuce da take jiyo abinda ke faruwa. Duk da cewa jikinta yayi sanyi da jin abinda ke faruwa, amma wani sashe na zuciyarta yana kara karfafarta da cewa kada ta karaya. Don haka koda Mrs. Atiku ta sanar da ita cewa Hajiya Ummah tana son ganinta, da confidence dinta ta tashi ta bi bayanta. Tana fada da karawa a cikin ranta, ita din ai ta gama cin dubu sai ceto, don haka babu abinda hakan zai zame mata. A wajen Ummah da Habibu, ita din ai ta zama duwawu, ko ana so ko ba a so dolene a zauna da ita.

45.

Suka nabba'a a gaban Ummah ita da Shukurah, kai a kasa suna sauraren irin fadan da Ummah din take zubawa sosai da sosai cike da bacin rai. Saboda abin bai mata dadi ba sam.

Ta cewa Shukurah, "akan me zaki aikata haka iye? Har ki dinga amfani da sunana a cikin gidannan kina aikata abinda bai dace ba? To daga yau, kada in sake jin abu makamancin hakan ya faru anan gidan. Ammar da ne a gareku ku duka, ban ga dalilin da zai sanya daya ta dinga hana daya mu'amala dashi ba, a kiyaye. Sannan daga yau, idan na kara jin wai an hada baki da yan aiki ana yin abinda bai kamata ba, to mutum zai gamu da bacin raina kwarai!"

Shukurah ta kyabe baki cike da wani sobaranci da sokanci, tace, "Ummah kina ganin yadda dai ta janye yaron wannan jikinta duk ta kanainayeshi, shi dama Ubanshi tuni ya gama zama mijin tace a kanta. Sai a zuba mata ido kenan tana juya mutane?"

Ummah tace mata, "shi da ya zama mijin tace din ai shi ya so hakan, kema kuma da kin zage dantse tun farko da kin zama matar mijin tace din. Da

kuwa da kike ganinshi ai shi yana wajen duk mai sonshi ne da kyautata mishi and lets face this Shukurah, yaron nan ba jan shi kike yi a jiki ba, hasalima idan yazo wajen da kike baki bari ya rabeki. To zai zauna yayi ta biye miki ne?!"

Kawai Shukurah sai ta dargwaje da kuka, ta tashi tsaye tana sakin maganganu cike da rashin da'a da kirki. Ai dama ita tun ba yau ba tasan cewa Ummah din tafi son Nadiya a cikin gidan. Yanzu har ta kai a dinga mata gorin haihuwa da yi mata shune akan d'a? Kenan ita duk kokarin da take yi a gidan ba a ganinta da mutunci? To ta gama zaman gidan, zata tafi inda ake ganinta da mutunci ake girmamata.

Ummah ta kama baki cike da mamaki tana kallonta, tace, "Shukurah! Wane irin zance ne kike yi haka? Me kuma ya kawo wadannan maganganun? Ashe ban isa kiyi kuskure a gidannan in tsawatar miki ba?"

Tace, "wace tsawatarwar? Wannan ai son kai ne kawai! Idan ma fadan ne kiyi mun daga ni sai ke mana, sai ki hadamu da wasu banzaye can sanadin su dinga raina ni?!"

Ummah ta daga murya cikin bacin rai, tace, "Shukurah ni zamu zauna muna sa-in-sa dake a gidannan?"

Sai ta daga hannu sama kamar mai surrender, "kinga, gidan ma zan bar miki ni. Sai ki kama wannan akwajalar da kike neman kamawa, kiga idan zata iya yi miki rabin abinda nake miki!"

Ta juya ta fita fuuu! Tana sakin wasu maganganu marasa dadin ji.

Jikin Nadiya yayi wani irin sanyi a wajen, ta kasa motsa ko dan yatsanta ne. Da tasan abinda zai je yazo kenan, da bata dauko maganar wannan ba.

Tace, "Ummah don Allah kiyi hakuri. Wallahi da nasan haka zata faru, da na hakura na bar zancen."

Sai taga Ummah din tayi dan murmushi, tace mata a tausashe, "kada ki damu Nadiya. Ki kuma daina bani hakuri akan laifin da baki aikata min ba.

Akan gaskiyarki kike, ina so daga yau kuma idan abu irin haka ya faru ki dinga sanar dani ko Maigidanki, saboda wannan zancen bai kamata ayi shiru ba kinji?"

Sai ta gyada kai a hankali, "to Ummah!"

Tana kokarin tashi din ne taji Ummah ta mata magana, tace, "ya ki zo nan Nadiya!"

Ta gurgusa, ta matsa kusa da Ummah din inda take nuna gefen kujerar da take zaune, amma ta kasa zama akan kujerar. Sai kawai ta zauna a kasan kafafunta. Ita kuma sai ta kama hannuwanta ta rike tana kallonta da idanu masu cike da kauna irinta Iyaye.

Tace, "zauna muyi magana dake sosai Nadiya, akwai misunderstandings da dama da nake so mu warware yau!"

A lokacin ta zaunar da Nadiya ta bata labarin ko wacece Hajiya Ummah. Duk wani fadi-tashin rayuwa da suka shiga bayan abinda ya faru da su, da kuma irin burika da ta sha akan duk wani iyalin Alhaji Laminu.

Tace mata, "amma a yanzu duk na ajiye wadannan abubuwan, na nemawa zuciyata maslaha. Ina kuma baki hakuri akan abubuwan da duk na aikata miki bayan shigowarki gidannan, har a yadda muka gudanar da neman aurenki ba tare da mun baki zabi ba. Ki yafe min kinji?"

Nadiya sai ta hau share hawaye, tana jin wata irin salama da sanyi na shigarta a duka sassan jikinta.

Tace, "ni dama can ban taba rikeki ba Ummah. Kuma a yau nima, a madadina da duka zuriyar Laminu, don Allah ina neman yafiyarki Ummah. Ki yafe mishi ko Allah Yasa ya samu sassaucin kwanciyar kabari!"

Tayi murmushi wanda ya fito tun daga can karkashin zuciyarta, "na dade da yafe mishi Nadiya. Allah Ya yafe mana baki daya. Allah Yayi muku albarka ku kuma tare da duk zuriyarku bakidaya!"

Nadiya ta amsa da ameen bakin nan nata har kunne saboda tsabar farinciki da jindadi.

Ta mike kafa anan kusa da Ummah, hira suka sha sosai irin wadda basu taba yi ba. Hira irin ta iyaye da yan'uwa, ba ta suruka da suruka ba.

Ba tasan lokacin da barci ya kwasheta ba anan tsakiyar falon. Sai da Ummah ta tasheta tace ta koma daki ta kwanta. Barcin ya gama cin karfinta, ko fahimtar abinda Ummah din ke cewa bata yi. Ta dai koma kan sofa ta mike kafa sadidan ta cigaba da barcinta.

Ranar ko zarafin tashi ta dafa abincin rana bata samu ba. Dole sai a wanda aka yi anan bangaren Ummah ta daukar musu ita da Babangidan ta wuce sashenta dashi. Shi kanshi dai ranar ya ji dadin halin sukuni da farinciki data yini dashi.

*

Washegari suka dauki hanya ita da Mami da kuma Farida. Hanya suka dauka dodar a cikin motar da Babangida din ya bada a kaisu, Rav4 dinshi ja. Ya hadasu da amintaccen direbanshi, Mr. Hassan Bayareben kasar Ilorin, an cika musu bayan mota da akwatu guda da Ummah din ta bada a kaiwa amarya, da kuma tarkacen tsaraba da za a kaiwa yan uwa.

Nadiya kuma ta cika musu mota da kayan tabe-tabe, motsi kadan ta ciro lemun Teem ta bincire hancin, bata ajiyewa sai ta ga babu komi sai robar.

Farida barcinta take sha cikin kwanciyar hankali, tafiya suke yi a cikin mota kamar dai ba ma a cikin mota suke ba, babu bumps na titi, basa ko jin kwarzaben kan hanya da titi sabida sun samu kosasshiyar mota.

Mami ke kallonta tana dan murmushi ganin halin da take ciki, tace, "ba zaki daure ki ci wani abu ba Nadiya? Ga nama nan Babangida ya hadomu dashi kala-kala, ga kuma snacks da ke kika yi da kanki, amma ki ki duka ki buge da shan lemu?"

Ta dan turo baki, "ba na jin yunwar ne wallahi Mami. Ni tunanin cin nama ma yanzu tayar min da zuciya yake yi wallahi. Wannan lemun ne kadai nake jin dadinshi."

Mami ta yada kai gefe guda, tace, "ai shikenan. Idan kinji kina son wani abu dai ki fada da wuri, sai mu tsaya a duba ko a hanya ne."

Tace, "to."

Suna tafe Mami tana janta da hira cikin hikima ta manya da kwarewa irin ta likitoci therapists da suka kware a harkar bin kwakkwafin magana da zance.

Mr. Hassan ya dage yana gudanar da aikinshi cikin kwarewa da iyawa, a gefe guda kuma he's very alert ga duk abinda ke faruwa akan hanyar. Saboda bayan lasisin tuki da yake dashi, Dan sanda ne na farin kaya da aka yi musu training na musamman. Ba yaren hausa yake ji ba sosai, hakan ya ba Nadiya damar sakin jiki suna magana ita da Mami.

Abun nan daya dake damunta ta kasa gane mishi shine take yiwa Mami korafi akai. Don bayan ita bata san wa zata fuskanta da zance makamancin wannan ba.

Sai Mami din ta mata murmushi, tace mata, "kin cika tsoro ne Nadiya, shi yasa!"

Ta kalleta da mamaki, tace, "tsoron me kuma Mami?"

Mami ta gyara zama sosai tana kallonta, tace, "watakila kema baki san da hakan ba, amma a can karkashin zuciyarki tsorone yake hanaki sakewa da maigidanki. Amma kada ki damu, hakan yana yawan faruwa a cikin mata da dama. Akwai mata da yawa da zaki ga yawan yarda da suka yi da mazajensu, ita ce take hobbasawa kuma ta dadada musu rayuwar aure. Ta bangarenki zata iya yiwuwa akwai wani abu tare da Babangida da kila ke a karan kanki baki dauki hakan wata hujja ba, amma kuma unconsciously zuciyarki ta dauki hakan a matsayin wani abu na kare kanta. Kila kina tsoron idan kin sakar mishi jiki watarana zai rabu dake ne, watakila zuciyarki na

rada miki ai baya sonki dari-bisa-dari, silly excuses dai iri-iri wadanda basu da kai ma balle kafafu. Abune dake faruwa damu psychologically. Ke da kanki zaki zauna ki nutsu, ki tambayi zuciyarki me kike tsoro? Ki lalubo amsar da kanki. Idan ta magancewa ce ke kadai, sai ki maganceta. Ko ku zauna ke da shi, talk about duk wani insecurity dake addabarki. Idan kinyi hakan, zaki samu mafita in shaa Allah. Sannan kofata a bude take kullum, ko da ace bana nan, zaki iya tuntubata a kodayaushe Nadiya. I'll be glad to help!"

Nadiya tayi shiru tana saurarenta sosai da sosai. Akwai kamshin gaskiya sosai a cikin kalaman Mami. Ta mata godiya, sai kuma ta yada kai kan kujera ta hau barci.

Barci tayi sosai a cikin motar nan har tayi mamakin hakan, don ita ba ma'abociyar yin barcin mota bace. Ga shi tafiyar tasu tayi sauri sosai wannan karon.

Sun shiga Maiduguri wasu masallatan ana kiran sallar la'asar. Kai tsaye gidan da aka sauki Hajiya Ummah wancan lolacin aka wuce da su. Suka samu dafifin yan uwa ana jiransu.

Tarba suka samu sosai da karramawa. Suka yi wanka suka yi sallah, Anty Lima tana ta mata shakiyancin wai me take ci ne ta canza kala da kamanni, ko dai canza musu ita aka yi ne? Tayi banza ta kyaleta tayi ta gama abinta, don gajiyar da tayi da zazzabin dake kadata ma kadai sun isheta. Da kyar ta iya zama ta kira Habibun ta sanar dashi sun sauka lafiya, ta kira Ummah da su Mama suma suka gaisa. Ta kashe wayar ta lalubi gado ta zube har da su rufa.

Anty Lima ta shiga ta sameta cikin wannan halin. Sai ta ajiye kwanukan abinci data kai mata, ta yi kanta da sauri tana tambayarta lafiya? Jin yadda jikinta ya dauki zafi yasa ta fita da sauri ta kira Mami. Tana dubata tace ba wani abu bane, gajiyar tafiya ce kawai. Aka samo paracetamol da ibuprofen ta bata tace ta sha amma ta dan fara cin wani abu.

Ga abinci nan varieties Anty Lima ta shigar mata da su, musamman dashishi da taushen gyada da ya ji naman kaji zako-zako da man shanu da tasan tana

cin shi sosai, amma ta kasa ci. Hasalima cewa tayi warin man shanu yana so ya sanyata amai.

Ta janye kwanon daga gabanta tana danne dariyar dake ciyota, tace, "ai ce min zaki yi kawai junior Habibu ne yake tambayarki, har kike nema ki tayar min da hankali!"

Ta watsa mata idanu cikin harara, "a'ah, abinda ya fi junior mantawa kika yi! Ni gajiyar tafiya ce kawai ta sanyani hakan ba wani abu ba!"

Anty Lima tace, "haba yarinya, ai wallahi kici gaba da denying, amma ni tuni na gama harbo jirginki. Baki ga irin murmushi da kallon da Mami take ta yi miki bane ba wai sanda tana dubaki?"

Dan tsaki ta ja, "kin ji da shi dai ko menene. Idan akwai nono ko yoghurt a dama min fura ko tukudi ni dai."

Tayi saluting dinta, "an gama ranki ya dade! Ai fura da tukudi yau sai kin gaji da su!"

Ta fita da sauri sai ga ta dawo babu jimawa, hannu rike da tasa an dama fura ta sha nono mai kyau. Ta gyara zama da kyau ta sha, ta kora da maganin kafin ta koma ta kwanta.

Cikin dan kankanin lokaci zazzabin ya sauka, sai gata ta tashi an cigaba da bidiri da ita.

Da dare suka wuce gidan Anty Hauwa ita da amarya tunda a can take ita da abokanta, suka bar Mami a can.

Wata sabuwar tarar suka samu a can gidan Anty Hauwa. Ita dai suna zuwa da kyar ta iya shiryawa a tsaitsaye, ta bi lafiyar gado ta kwanta ko karfe tara bata gama rufawa ba.

Ta tashi da Asubahi ta tarar da missed calls din Babangidan bila adadin. Don haka ta kirashi suka gaisa. Fadi mata yake yana karawa, shi already gidan ya

gama mishi fadi da bata nan, anya ba dawowa zata yi ba ko kuma shi ya biyo ta ba? Ta dinga mishi dariya tana cewa 'ashe da ya zama bita zai-zai?!'

Yace, "ai baki ga bita zai-zai ba sai kin dawo na hanaki zuwa ko nan da can na shekara sannan zaki tabbatar!"

Tayi dariya sosai har ta gode Allah.

Anty Lima tana zaune tana saurarenta tana ta sakin murmushi abinta, har suka yi sallama da shi. Ta kalleta kasa-kasa cike da alamun tsokana, tace, "su yar ware ana cewa ba a so, ba za ayi ba, yau kuma ga ki kece kike i love you I miss you?! Lallai in da ranka ka sha kallo!"

Tayi dan murmushi kawai, tace, "oho miki dai. Ni ki daina tuno min lokacin kan ta waye don Allah!"

Anty Lima kuwa me zata yi ba dariya ba?

A washegarin ranar aka fara gudanar da shagulgulan bikin Anty Lima wanda ya matukar kayatar ya kuma burge.

Sai dai tunda aka fara bikin Nadiya ba zata ce ga takamaiman abinda ke faruwa ba, don kuwa cikin barci take sosai da sosai. Yanzu bata da lokacin komi sai barci, koda yaushe za ka sameta to barci take yi, abin har ya fara damunta kuma. Don kuwa tunda ake events na bikin sau daya taje wajen sisters evening, ta dawo da ciwon kai sosai da sosai har sai daya haddasa mata zazzabi. Don haka Anty Hauwa tace mata ta hakura da zuwa kawai, ta dinga zama a gida tunda ga dangi nan suna ta shiga da fita abinsu, idan taji barci kuma ta gyara kwanciya ta kwanta abinta.

Ga abinci har yanzu bata iya cin komi, sai fura da kankana kullum da lemu mai tsami. Amma biredi wannan in dai zata hadiya sai ta tanadi lemun tsami a kusa da ita. Wannan da kuma rashin ganin bakonta na wannan watan ya sanya ta fara tunanin anya?

A haka dai ta lallaba aka cinye satin nan guda tas ana ta biki kamar ba za a kare ba. Washegarin ranar da aka daura aure, suka dauki amarya aka kaita

Garin Kano. A can iyayen mijinta ke zaune, amma harkokinshi sun ma fi karfi a California. Don haka akwai yiwuwar can zata bishi da zama.

Sun kaita gidanta dake can Hotoro G.R.A. Gidanta hadadde ma shaa Allah, ya sha duk wani abu da ake bukatar samu a gida.

Suka wayi gari ita da yan'uwansu anan ana ta son barka. Wasu sun juya tun a ranar, wasu kuma sai washegari. Ita da Mami suma duk a ranar zasu juya Kaduna don kuwa gogan yana can yana jira. Don shi tun a jiya ya sanya ran zuwansu.

Da yamma suka shirya zasu tafi yadda zasu yi shigar dare. Don haka wajajen karfe goma na safe, suka fita Ita da Mami suka yiwa gidan Anty Jamilah tsinke. Ta taresu da murnarta, ita da Rabi'ah suna ta yabon irin kyawun da tayi da cika data kara. Ita dai tana ta musu murmushi kawai.

Zuwa can suka yi musu sallama, Anty Jamilah ta hadasu da turaruka da kayan shafa masu kyau. Ita da Mami din har sun dinke kamar wasu tsofin abokai. Suka yi mata sallama tana musu alkawarin in shaa Allah itama kwanan nan zata shiga Kaduna din.

Akan hanyarsu ta komawa tace su dan tsaya a shoprite, akwai spices da take son saya wadanda bata dasu a gida.

Suka shiga ita da Mami, hannunta rike da hannun Farida. Ita Mami kai tsaye sashen kayan snacks da tarkacen su biskit ta wuce. Ita kuma ta wuce wajen spices da seasonings, ta debi iya wadanda zata iya. Sai ta koma bangaren kayan sanyi zata daukarwa Farida Ice cream.

Ta kai hannu zata dauki Mint n Choco na Robofob, ita kuma budurwar ta kai hannu zata dauki fanice. Hannun nasu ya hadu waje daya, suka kalli juna a lokaci daya da niyar ba juna juna hakuri. Sai kalmar ban hakurin nata ta makale a bakinta. Cikin tsananin mamaki ta bi bayan yarinyar da take juyawa da kallo, ranta yana kiyasta mata wani abu.

Kasa jurewa tayi, ta bi bayan yarinyar da sauri tana mata magana cikin alamun rikicewa.

46.

Yarinyar ta juya tana kallonta cikin alamun mamaki. Sai Nadiya ta ja tunga a gabanta tana sauke numfashi daya bayan daya.

Tace mata, "don Allah kiyi hakuri na tsayar dake baiwar Allah, tambayarki ce nake so inyi!"

Ta gyara tsayuwarta tana kallonta, "to, Allah Yasa na sani!"

Tayi shiru tana kara kallonta, a ranta addu'a take tana karawa, Allah Ubangiji Yasa zarginta ya zama gaskiya. Idan ta daga ido ta kalli yarinyar sai taga kamar Maryam ko Anty Haulatu ko Yaya AbdulHadi take gani. Haka duka 'ya'yan Mama suke, duk ita suke daukowa a kamanni kamar an tsaga kara an karya. In ka dauke Nazifi da kuma diyarta data rasu, wadannan Abbansu suka dauko a kamanni.

Ta daga baki murya na karkarwa, tace mata, "don Allah, ba wai tambayar rainin hankali bace ba, amma ko kin san Ardo Usmanu? A can Wuro Yanka? Ko Jafe?"

Yarinyar ta kalleta cikin mamaki, tace, "Ardo dai namu? Kakana ne ai, kuma shi Jafe din da kike fadi Babana kenan!"

Kawai sai Nadiya ta rungumota jikinta, ta saki wani irin kuka cikin tsananin farincik mai dauke da tu'ajjibi da murna da mamakin wannan iko na Allah.

Yarinyar nan sai tayi tsaye ta sankame tana kallonta tana zare ido.

Haka Mami ta samesu cikin wannan hali. Da kyar ta samu ta janye Nadiya daga jikinta, suka samu suka biya kudin abubuwan da suka siya. Suka fita farfajiyar wajen, hannunta jimke cikin na wannan yarinya da tace sunanta Zainab. Idan abinda take hasashe hakane, ita din diyar Yayan Mama ne da take yawan basu labari, Yaya Jafe, wanda lokacin da aka daura auranta ma baya gari. Idan kuwa hakane, ashe tsaye take da dangin Mama da suka jima suna nema da addu'ar Allah Ya bayyanasu.

Kuka tace sosai, take ce mata, "matsayin diya nake a wajen kanwar Jafe din, Zuwai-Juwairah. Wadda suka rabu da danginta a can Wuro Yanka din tun tana yar yarinyarta, anyi neman duniya har yau bamu samu wani bayani ko kadan daga garesu ba. Yanzu har mun dawo gefe muna ta addu'a kawai da fatan Allah Yasa muna da rabon ganawa da su."

Zainab itama sai ta hau share hawaye, tace mata, "kwarai kuwa, Babanmu yana yawan bamu labarin wata kanwarshi da kullum yake cewa mu dinga mishi addu'ar Allah Ya kaddara saduwarsu. Saboda ita ne ya nemi wajen zama anan Kano shi da danginshi, suka daina yawo. Kusan kullum sai yayi mana zancenta, da yadda yake dana sani da nadamar rashin kasancewarshi a wajen a lokacin da ta bar gari!"

Nadiya ta kara fashewa da kukan dadi da murna. Da kyar Mami ta lallasheta suka shiga mota, sai ga su sun koma gidan Anty Jamilah bagatatan.

Ita kanta ba karamar murna tayi ba da jin dadin wannan labari. Nan da nan ta dauki waya ta kira Yaya AbdulHadi ta sanar dashi. Abinda yace mata shine su yi hakuri kar su sanar da Mama, gashi nan zuwa a yau ba sai gobe ba.

Don haka ta dauki makullin mota suka tafi gidan su Zainab har ita.

Kafin zuwan nasu Zainab har ta kira gidansu ta sanar dasu abinda ke faruwa. Don haka zuwa lokacin da Anty Jamilah ta tura hancin motarta cikin gidan Alhaji Ja'afar Usman dake cikin unguwar Gwammaja, a kofar gidan suka sameshi shi da Iyalinshi suna tsammaninsu.

Nan suka rankaya cikin gidan, aka zauna a falo ana maida bayanan abubuwan da suka faru.

Anan gidan suka yini har karasowar Yaya AbdulHadi shi da Nazifi can da yammaci, Allah Ya taimakesu sun samu jirgi mai tahowa daga Lagos zuwa Kano a wannan ranar. Da so suka yi a ranar su tafi Kaduna, amma Alhaji Ja'afar yace su daurewa gobe saboda tafiyar dare bata da dadi. A daddafe suka kai washegari.

Ga basu sanar da Mama halin da ake ciki ba, ga Nadiya bata yiwa Babangida bayanin abinda ke faruwa ba. Ta dai tura mishi text din cewa yayi hakuri sai gobe zasu dawo saboda wani abu na gaggawa daya taso.

Kaikayin baki ya isheta, tunda assalatu ita har ta gama shirinta. Sai data kira Mama tace mata ta shirya suna tafe da manyan baki a yau.

Suna gama kari suka nufi gidan Alhaji Ja'afar. Yaya AbdulHadi da Nazifi a hotel suka kwana, don duk da tayin da Anty Jamilah ta mishi na yaje ya kwana a can gidanta cewa yayi a'ah. Suka samesu suma sun gama shirinsu shi da Iyalanshi, matar shi daya tun ta lalle. Suna da 'ya'ya bakwai, wasu sunyi aure. Zainab da kaninta Ma'aruf sune a gaban iyayen yanzu, akwai Yayanta Fahad yana BUK, sauran kuma matane duka suna gidajen aurensu.

Motoci biyu suka dauka, wadda su Nadiya suka je da ita Nadiya din ce da Mami da Nazifi da Farida. Yayinda ta Alhaji Ja'afar kuma shine da Iyalinshi da Yaya AbdulHadi.

Kasancewar tafiyar safe suka yi, sai nan da nan gasu a cikin Kaduna kafin karfe goma ta rufa.

Mama tana zaune a tsakar gida bayan sun gama sallamar yara yan makaranta tana kokarin hada kayan wanki Maryam da Amina su yi in sun

dawo makaranta. Sai jin sallamar Nadiya tayi a saman ka, ta dago da mamaki sai tayi turus ganin Yaya AbdulHadi yana binta a baya.

Tace, "dannan! Nadiya! Sannunku. Ku ne da sassafen nan?!"

Nadiya ta tafi ta rungumota cikin murna, tace, "Mama ki shirya da kyau, yau tafe muke da bakin arziki!"

Kafin Mama ta gama tantance abinda ke faruwa, Nadiya ta fara yiwa mutanen gidan shelar cewa su kimtsa baki zasu shiga.

Sai jin sallama tayi da muryar da ko mutuwa tayi ta dawo, ba zata taba mantata ba. Girma da yawan shekarun da suka dauka ba a tare ba ba zasu sanya ta manta da wannan halittar da ke gabanta ba. Tafiya tayi ta sume gabadaya. Suka rufu kanta ana yayyafa mata ruwa har ta samu ta farfado. Kawai sai ta saki wani irin kuka daya matukar karyar da zuciyar mutanen wajen, su ma suka fara sharar hawaye. Lallai dan'uwa ba wasa ba, babu kuma wanda zai taba iya cike maka wannan gurbin nashi har abada.

Ta kama hannun Yayanta Jafe ta rike, cewa taje yi, "ashe dama kana raye? Ashe zan sake ganinka a rayuwata? Ashe dama kaima zaka iya yin fatali da ni a cikin rayuwarka, ka manta da ni? Nayi zaton ko su Dada sun sallamani saboda abinda na musu kai ba zaka cireni daga ahalinka ba!"

Ya kai hannu yana share hawayen fuskarshi, yace, "kiyi hakuri kanwata, amma ko da iyayenmu sun yayeki, ni ba zan taba yayeki ba. Dawowa kawai nayi na tarar da labarin wai an miki aure kin bar Wuro Yanka. Nayi neman duniya amma ban sameki ba. Saboda ke ne ma gabadaya na nemi rassa na zauna a Kano, na koma Wuro Yanka ko zan sake samun labarinki bayan yan shekaru, aka ce min tabbas kin je, amma rashin sanin inda muke ne yasa basu baki takamaimiyar amsa ba. Na bar musu lambar waya da inda nake zaune a Kano ko Allah zai sa watarana ki koma su fada miki, amma har yau babu wani labari. Kiyi hakuri kinji? Yau gashi Allah Ya hadamu cikin ikonSa ai."

Ranar dai gida ya cika da matsanancin farinciki irin wanda ba a kwatantawa. Aka kira Abba yaje ya ga dan'uwan Mama. Yana fita sai ga kaji manya-manya guda biyu an kai, aka gyarasu nan da nan Amarya ta dora sanwa. Yadda take murna da taya Mama farinciki kamar wata diyarta.

Su kansu su Lantana da Salame sai gasu suna rakube-rakuben zuwa gayar da Yayan Mama. Abin ya so ya bawa Nadiya dariya, lallai da gaske da ake cewa wai duniya rawar yanmata.

Mami ta wuce gida ta bar Nadiya anan don tace sai yamma zata koma.

Sun samu labarin tuni Baban su Mama da Innarta suka rasu, amma sun fada sun nanata kafin rasuwarsu, sun jima da yafe mata, itama kuma suna rokon data yafe musu. Baiwar Allah ranar tayi kuka har ta godewa Allah dai.

Da Alhaji Ja'afar ya fada mata gadonta na wajen iyayensu dake hannunshi, sai da yawan kudaden suka tsoratata. Tace mishi ita me zata yi da kudi yanzu? Ganinshi ma kadai da Iyalinshi ya wadatar. Yace a'ah, ba za ayi haka ba. Dole ta amshi hakkinta. Don haka suka yanke shawarar AbdulHadi zai amshi kudin, zai duba abinda za a dinga yi mata da kudin ta yadda duk karshen wata kawai sai dai a aika mata da ribar abinda aka samu.

Gabannin Magriba Mr. Hassan ya koma daukar Nadiya. Tayi sallama da mutanen gidan cike da kawa zuci, don bata da tabbacin ranar da zata sake fitowa. Suka dauki hanyar komawa gida.

Kai tsaye bangaren Hajiya Ummah ta wuce ta gaidata. Ta tareta cikin farincikinta har da rungumota, ta kuma tayata murna da nuna jindadinta na haduwa da Mama da tayi da danginta. Don cewa tayi ma zata samu lokaci taje gidan da kanta su gaisa, tunda tun bayan auren basu samu damar gaisawa ba dama properly.

Nadiya ta ji dadin jin hakan kwarai. Tana nan sashen taji dawowar Babangida, amma basu hadu dashi ba saboda bangarenshi ya wuce kai tsaye.

Itama da aka kira sallah sai ta koma bangaren nata. Tayi wanka, tayi sallah tare da gudanar da wasu abubuwa na musamman. Duk cikin shirin ziyartar Babangidan ne a turakarshi. Wanda ya dauki fushi ya kakaba, yau ko waya bai yarda sunyi da ita ba.

Bayan ta yi isha'i kicin ta shiga ta jefa danwake don shi kadai take son ci da man kuli, ta yanka kabeji da albasa da cucumber da tarkacen vegetables, ta zabga yaji kamar na kamun maye, ta zauna ta ci tayi nak, ta dora da lemon tea data zame mata ka'ida yanzu.

Zuwa karfe tara, ta kulle sashenta ta fita. Wani irin asirtaccen kamshi take ta kowane bangare na jikinta, duk inda ka taba da irin kamshin da yake yi.

Yana uwar dakinshi zaune akan sofa, desk ne a kusa dashi ya dora laptop dinshi yana aiki, fuskarshi saye da farin gilashi wanda ya kayatata sosai, ya kuma kara fitar mishi da kamalarshi da cikar haiba.

Ya daga kai ya kalleta lokacin data shiga dakin bakinta dauke da siririyar sallama. Ya amsa daga can kasan makoshi, don kuwa irin cika da kyawun data kara a cikin yan kwanakin ba karami bane, ko kuwa don ya kwana biyu bai ganta bane? Kokari yake ya danne duk wani kewa da jindadin ganinta da yake ji a lokacin, ko ba don komi ba don tauna tsakuwa don aya ta ji tsoro. Idan ya tashi ya sabeta kamar yadda zuciyarshi ke raya mishi ai maza sun fadi, kuma ba zai isar da sakon haushin take dokar shi da tayi ba.

Amma sai hakan yake nema ya gagara, musamman da ta bi ta gefenshi ta wuce, wani irin kamshi da bai taba ji a tattare da ita ba yana surnanawa daga jikinta yana shiga hancinshi. Ya saci kallonta har ta wuceshi, taje gefen gado ta zare hijabin jikinta. Ai sai yayi suman zauna. Wasu arnun nighties data sanya ranar suka tafi da hankalinshi kai tsaye.

Yana yawan fada mata rashin sakewa da shi da bata yi balle har ta dinga yi mishi shiga irin wannan, wanda shi kuma ba abinda yake so ga matarshi irin shiga ta kananun kaya. Abinda bai sani ba ita bayan kunya, har da tsoron irin kwarzabar da taga yana yawan yi mata idan ta sanya kananun kayan. Shi yasa wai take kokarin takaitawa musamman idan taga ranar girkinta ne.

Amma a yau, tana so ta yaye wannan hijabi dake tsakaninsu. Ta bi duka kalaman Mami daya bayan daya ta tsinci wadanda zasu mata amfani, a haka kuma sai ta hango wani abu da a da, bata bashi muhimmanci ba. Da gaske akwai tsoro a tattare da ita, tsoron ta mallakawa Babangida zuciyarta da jiki, shi kuma ya wancakalar da ita ya rabu da ita. Musamman a yadda taga Hajiya Ummah bata yi na'am da ita ba, shi kuwa baya tsallake umarninta.

Sai ta yanke shawarar bari ta dauki risk din kawai, ta so shi gabadayanshi ta kaunaceshi da duk wani flaws nashi da imperfections. Zuciyarta na fada mata da kara fada mata, he's worth it!

Ta fara takawa cikin taku na daukar hankali, har ta karasa wajenshi ta zauna a kusa dashi. Gashin kanta ta gyarashi ya sauko har kirjinta, yana ta sheki da kamshi. Ta janye laptop din daya kurawa ido kur yana kallo, amma a lokacin ko bindiga aka dora mishi a ka ba zai taba cewa ga abinda yake yo ba. Don kuwa tuni daya daina fahimtar komi.

Tace, "Habibina, shine ko sannu da hanya ba zaka ce min ba?" Cikin wata murya mai lankwashe da shagwaba da salo na jan hankali.

Ya watsa mata wani irin kallo, bakinshi a mace murus. Yau Nadiya mamaki kawai take bashi tana kara kasheshi da mamaki. Musamman data lallaba ta hade bakinsu waje daya ta bashi peck, ta janye tana kallonshi tana wani murmushi, "I miss you wallahi!"

Ai sai ya mance da wani zancen fushi da komi, ya wartota kamar wadda za a kwace mishi ita. Ya hadata da jikinshi.

Yace, "har kika fi ni Nadiya? Kwanaki dai-daya har goma sha biyu fa!"

Ta rada mishi a kunne, "then show me!"

Sai ya dagata camak gabadayanta yayi kan gado da ita.

Kewa dai kam, ya nuna mata yayi, itama kuma a yau ta dage ta nuna mishi ainihin so da kauna da take mishi. Abinda ya dadada wannan dare kenan,

aka raba dare tsakanin ma'auratan kowa yana kokarin nunawa dan'uwanshi yadda yake jinshi a cikin ranshi.

Sun gama sallar Asubahi, ta kamo hannunshi ta dora mishi wani abu a tafin hannunshi.

Ya kurawa na'urar idanu mai kama da hand thermometer idanu yana kokarin tantance menene? Zabgegen jajayen layuka biyu daya gani, da sign din '+' a samanta yasa ya daga idanu ya kalleta a wani irin gigice. Fuskarshi na bayyana tsananin shock da yake ciki. Ta kai tafin hannu ta rufe fuskarta tana dan murmushi a kunyace, sai ya bi bayan hannun nata da sumba iri-iri.

Yace, "na rantse idan kika kara bani wani surprise din a yau Nadiya, zuciyata sai ta buga!"

Ta saki kayataccen murmushi tana kallonshi cike da jindadi lokacin daya maida goshinshi akan abin sallah yana mai godewa Allah Buwayi Gagara Misali, a fili da kuma boye.

Ya kama hannunta ya mikar da ita tsaye, hannunshi na laluben cikinta da yaji shi shafal a shafe. Yace mata, "kin bani komi a yau Nadiya, bani da wani baki da zan taba iya bayyana miki farincikin da nake ciki a wannan lokacin. Allah Yayi miki albarka, yadda kike faranta min kema Allah Ya baki masu faranta miki!"

Tace, "ameen!"

Barci suka koma, sai can wajen karfe tara suka tashi. Cikinta kamar an yashe mata shi haka take ji saboda yunwa.

Ya tambayeta me take son ci?

Tace, "ita komai ma yau tana jin zata iya ci."

Amma da suka je bangaren Ummah da niyar yin karin, loma daya tayi ta hadadden cous-cous da aka yi da ya sha veggies da kwai yayi sharr, ta kasa ta biyu. Dole sai dan wake Laylah ta sake dafa mata.

47.

Yadda taga Hajiya Ummah da Mami suna tattalinta ne yasa ta sha jinin jikinta cewa sun san da zancen cikin, duk da dama ta dade tana zargin tuni Mami din ta gane, tasan kuma ita zata fadawa Ummah. Don haka fadar irin kulawa da take samu a cikin gidan a wannan lokacin ma bata baki ne. Motsi kadan idan tayi, sai duk sun zabura sun tambayeta, 'lafiya?'

Tun tana jin kunyar hakan ma har ta saki jikinta abinta.

Tun komawarsu gidan bata ga motsin Shukurah ba. Babu kuma wanda ya fada mata abinda ke faruwa, don haka itama bata tambaya ba.

Sunyi hakan da kwana biyu, da dare tana dakinta tana shirin kwanciya. Babangidan nata ya tura kofar dakin ya shiga. Cikin jallabiya yake ruwan toka, yana ta zubda kamshinshi na ka'ida.

Ya karasa shiga cikin closet dinta inda take zaune gaban madubi tana goga humra a wuyanta da gabobin hannunta.

Suka kalli juna ta cikin madubin suka yi musayar murmushi. Ya karasa ya tsaya a bayanta, yace, "mai ciki, ya ne ake kallona haka?"

Sai ta dan turo baki, "don Allah ka daina kirana da mai ciki dinnan haka. Wai sai kowa yasan matarka tana da ciki ne?"

Yayi dan murmushi, "ba zaki fahimci yadda sunan nan ke dadada min rai bane idan na fada shi yasa!"

Ta yada kai gefe daya, "to ai shikenan Habibi, na kyaleka kayi ta fadi tunda dai kana jin dadin hakan!"

Yayi murmushi yana ciro wani abu daga cikin aljihunshi. Kallonshi take yi in curiosity har ya ciro wani dan madaidaicin kwali, ya bude shi. Ya ciro wata irin siririyar sarka mai fararen stones, a tsakiyarta kwalliya ce kamar ganyayyaki na bishiya, an musu ado da wani stone din shi kuma green. Ya sanya mata a wuyanta. Tayi zaune tana kallonshi da mamaki har ya makala mata dan kunnen sarkar da abin hannu da zobe.

Ta kurawa zoben idanu tana jinta kamar wadda aka nutsa a cikin ruwa. Wasu irin emotions data rasa ko na menene suka lullubeta, sai taji hawaye suna diga akan fatar hannun nata.

Ko bata san duwatsu masu muhimmanci ba da ake kayan ado da su, ranta da jikinta sun bata wannan ba kananun abubuwa bane.

Ta karbi kwalin a hannunshi tare da zare takardar rasiti dake makale a jiki wadda take dauke da bayanin abubuwan da sarkar take da su. Sarka ce ta gwal wadda aka yi mata ado da kananun diamonds, tsakiyarta kuma wani diamond dinne shine mai kalar green din. Tsayawa fadin darajar sarkar wannan ma ba karamin bata baki bane.

Wai yau Nadiya ita ta mallakesu. Mijinta, abin alfaharinta ya mallaka mata su.

Ta kalleshi ta cikin madubin cikin karyewar murya, tace, "ban san me nayi na cancanci wannan ba, but thank you so much!"

Ta tashi ta rungumeshi. Shima ya sanya hannu ya kara riketa a jikinshi, "kin cancanci fiye da hakan Nadiya. Ai ni zan miki godiya, bayan kyauta kan kyauta da kika dinga yi mun da ba kowa ne yake da gatan samun ta ba?!"

Tayi murmushi amidst her tears, "kana dai fadin hakane kawai, kaima ka sani. Amma don me ake auren idan ba don wadannan ba!"

Sai kawai ya nutsa kanshi a wuyanta, yana ce mata, "Nya Raakna!"

(Ina son ki) da yarensu na Kanuri.

****

Anyi kwana biyu da yin haka din, Hajiya Ummah ta hadasu a falonta da dare. Tace musu akwai wani program da aka gayyacesu, 'Feed the Needy'

Wani ciyarwa ne ake yi ga marassa karfi da mabukata wanda gidauniyar "Helping Hand Foundation" take gudanarwa a garuruwa da dama. Wannan karon zasu yi ne a Kaduna, sannan salon nasu zai bambanta d sauran lokuta.

A maimakon a samu wani da zai bada taimakon kayan abinci, sai su gidauniyar su ba da kwangilar a dafa abincin a kuma raba da sunanshi, wannan karon suna so ne a samu wanda zai jagoranci gudanar da komi na wajen tun daga kan girkin har zuwa ga rabon abincin. Hajiya Ummah din tana kyautata zaton hakan zai basu exposure mai kyau, hakan kuma zai kara basu damar kara karbuwa a wajen talakawa. Amma ya suke ganin hakan? Zasu iya amsar wannan gayyata ko kuwa kawai a bari ta wucesu?

Yace mata, "to ni Ummah ga ki ga mai aikin dahuwar abincin nan, ni dai ta bangarena ai ban ga abinda zan iya cewa ba anan!"

Nadiya ta amsa a take cewa bata ga matsalar hakan ba. Zata bada duk taimakon da ake bukatar ta bayar.

Don haka suka fara shirin gudanar da wannan gagarumin shiri a cikin satin.

Kamar kuma yadda aka ce haka tsarin ya tafi. Ta nemi taimakon rakiya a wajen kawarta Aramide tunda an ce zata iya tafiya da wani, ita kuma bata bata lokaci ba ta amsa. A cewarta wa yake kin amsar gayyatar First Lady ta gobe? Sai kawai tayi dariya tace mata, "first Lady a ina?! Rufa min asiri in mutu maza su kaini ba mata ba."

Ranar tunda suka bar gida tunda safe suka yiwa wajen da za ayi aikin tsinke, suka hadu da Ara din a can tana jiransu. Sun samu yan jarida da masu aikin daukar vidiyo da hotuna ana ta yi. Hakan bai sanyaya gwiwar Nadiya ba, wadda tana haduwa da Manager din wajen itama gabadaya ta tafi ta dauko tsohuwar rigar manajanta ta sanya. Nan da nan sai ta karbe akalar aikin komi na wajen, suka hadu da sauran masu aikin dafe-dafe a wajen. Wasu ta bada umarnin abinda za ayi da yadda za ayi komi, wani kuma da kanta ma take yi. Aramide itama ta kama nata aikin suka hau yi gadan-gadan. Haka ta yini a tsaye akan duga-duginta suna gudanar da girke-girke daban-daban na gida Nigeria da kuma waje. Suka yi lemuka da snacks da dama, ga masu daukar vidiyo da mai gudanar da shirin suna aikin dauka da kuma yi mata tambayoyi iri-iri tana amsawa cikin nutsuwa da kwarewa a aikinta.

Abincin da suka yi suka dinga wrapping a take away ana lodawa a motoci ana tafiya gidajen marayu da su da kuma wani kebantaccen waje da aka tara mabukata suma ana kai musu.

Da suka gama komi, aka gabatar da ita a matsayin matar dan takarar Gwamnan Kaduna na wannan zabe da shi kanshi Habib din a matsayin wadanda suka dauki nauyin wannan aiki. Aka yi wata hira din dasu ta mintuna talatin, akan irin canji da cigaba da suke son kaiwa garin Kaduna idan Allah Ya basu damar samun wannan mulkin. Suka yi bayani na hankali, na ilimi, ba wanda ke dauke da alkawarin bogi da zantukan iska ba, akan yadda suke son kyautatawa manoma da kai cigaba a kauyuka da kuma kara kai cigaba cikin Jihar Kaduna.

Anan Nadiya tayi wata magana da ta ja hankalin su kansu masu daukar shirin, yadda take ganin yakamata ace shuwagabanni sun hada karfi da karfe wajen tallafawa mata da kananun yara musamman wadanda ake rabosu da iyayensu domin yawon almajirci. Ta kuma ce da ikon Allah, za su yi iyaka kokarinsu wajen ganin cewa sun inganta rayuwar yara kanana marassa galihu, tunda sune manyan gobe.

Yadda take maganar cikin nutsuwa da kwanciyar hankali, babu iko babu jin izza da ji da kai, ya ja hankalin mutane da dama a lokacin da aka saki vidiyon hirar tasu a daren ranar.

Kafin wayewar gari gabadaya social media ta dauka, Hajiya Nadiya matar Habibu Abdullahi Gwamnan Kaduna na gobe! Yadda kasan an jima da saninta.

Sai gashi an fara citing kalamanta da tayi a interview din.

Da misalin karfe goma na safiyar washegarin ranar duk sun nabba'a a falon Hajiya Ummah suna kallon shirin, Ummah ta dauki remote ta rage sautin karar talabijin din lokacin da aka karkare shirin. Murmushine sosai akan fuskarta, ta kalli Nadiya din dake aikin gyangyadi daga zaune don kuwa har lokacin gajiyar da tayi bata gama sakinta ba. Duk da tausa ta musamman da Habibin nata ya raba dare yana mata.

Ta kalli Babangida da yake satar kallonta, fuskarshi ta gaza boye jindadin yadda shirin ya karbu sosai da sosai a wajen mutane.

Tace mishi, "Alhamdulillah, ina ga mun kai matakin karshe a bangarenmu, wannan karon dai Nadiya ita ta kai mu ga wannan matakin nasarar. She did well, fiye da tunanina gaskiya. Babangida ka riki yarinyar nan da mutunci, ita tana yin duk iyaka kokarinta saboda taimaka maka ne kai kadai ba don wani abu ba, saboda ta dauki nasararka a matsayin tata, ba don tayi suna ko shura bane."

Ya lumshe idanu a tausashe yana dan jinjina kai.

Ummah a ranta take cewa, 'yanzu na kara gane bambancin dake tsakaninku da Shukurah. Ko da ace ta fiki shekaru da yanayin wayewa, sai dai a zahirance Nadiya ta fi Shukurah din exposure da iya bi da mutane sosai da sosai. Abinda tun farko yakamata in duba kenan kafin in ja Shukurah cikin harkokina. Amma son zuciya ya hanani."

Duk da haka tana godiya da Allah bai sa idanunta sun rufe gabadaya har ta kasa ganin hakan da wuri ba. Ga shi yanzu daga ziyartar show daya da Nadiya tayi a kwana daya, sun ga canji da tunda Shukurah take tata fitar basu ga kwatankwacin shi ba.

Saboda ita Shukurah tana da wani hali na nuna isa da izza da ji da kai, tana kuma amfani da kudi ta ce zata sayi mutane ba wai tayi amfani da halinta

ba. Mutane da dama kuma a harkar siyasa ba kudi suke so ba, loyalty suke bukata. Suna so su samu assurance din cewa koda ka hau mulki, ba zaka juya musu baya ba idan ka samu abinda kake so. Hali na nagarta da girmamawa da kamala suna matukar jan hankalin mutane. Nadiya kuma tayi amfani da wadannan a jiyan, abinda Shukurah bata taba gwadawa masu bibiyarta da take mata baya ba.

Abin kamar wasa, cikin dan kankanin lokaci sai ga sunanta ya karade ciki da wajen Kaduna, fiye da na Shukurah. Wasu ma sai suka fara shiga social media da kansu suna yabawa halin Nadiya da irin yadda suke girmamata da maigidanta, abinda a da basu samu hakan ba.

Kasancewar gidauniyar Helping Hand Foundation babbar kungiya ce wadda tayi shura a cikin Nigeria da kewayenta wajen taimakawa marayu da marassa karfi, wadda kuma tayi fice kwarai da gaske ba ga talakawa kadai ba, har ma da manyan kasar. Haskasu Nadiya da aka yi daga bangarensu ba karamin cigaba ya kai musu ba, bugu da kari rawar ganin da Nadiya ta taka wajen gudanar da ayyukanta sun matukar taimakawa wajen kama zukatan duk wani wanda ya kalli wannan shiri.

Mutane da dama kuma sai bayan wannan shirin sannan suka san cewa Habibu din matanshi biyu. Nan da nan kuma sai mutane suka fara raba kafa. Nadiya ta fara samun kira daga manyan mutane da manyan women leaders da aides, wadanda yawancinsu ma na bangaren Shukurah dinne suke zamewa suna komawa wajenta.

Ita kuma sai take kaffa-kaffa da kowa, musamman masu kai mata gulmar Shukurah da yadda take wulakantasu da musu iko da kudi. Ita kuma da taji ka fara wannan maganganun sai tayi gaggawar katseka, tace maka kawai kuyi maganar data kaika, idan kuma wannan ce kadai to kayi hakuri kawai ka tafi.

Sauran abubuwan da Shukurah tayi fushi ta tafi bata karasa ba sai suka koma hannunta. Su da kansu women leaders din suka tara mata taron karawa juna sani da manya-manyan mata yan siyasa da suka jima ana

fafatawa dasu a wannan harkar, aka yi zaman anan cikin gidan. A nan ne tasu taje daya da matar Gwamnan Kano Haj. Badariyya Kamal, wanda suke sa ran zai yi tazarce a wannan karon. Suka yi musayar lambar waya da ita akan cewa za su cigaba da zumunci, kuma idan Nadiya din tana da wani bukata ko tambaya na daban, zata iya tuntubarta.

Da za su yi sallama da ita bayan taron ya watse, ta rakata har gaban motarta inda securities dinta ke jiranta, take fada mata cewa, Shukurah ta jima tana tura mata takardar son ta bata damar ganinta amma tana ki, tace mata, "kina da wasu qualities na musamman da ake son matar shugaba su kasance dashi. You are sincere, sannan duk wani magana da zaki yi kina da interest na talakawa da son kyautatawa kasarki, don haka keep it up Nadiya, muna tare dake in shaa Allah!" Tayi mata godiya sosai da sosai.

A cikin satin Mami tayi musu sallama ta juya Jordan. Ta musu alkawarin idan zabe ya zo nan da watanni hudu, za ta dawo da izinin Allah domin tayi zabe kamar yadda kasa take bawa duk wani danta dake rayuwa a wata kasa ta daban wannan dama.

Ta tafi din ba da jimawa ba aka yi bikin bude Madam Zarahs Arena. Wanda ta dauki bakuncin manya-manyan kasa da dama da kusoshi na Gwamnati. Aka yi bikin taro aka gama lafiya, Madam ta fara gudanar da aikinta. Sai ta fara dakatar da sauran ayyukanta da take yi a sauran wajaje, saboda tana so wajen ya amsu ya kuma ginu a garin Kaduna cikin dan kankanin lokaci. Nan gaba kadan idan ta samu yadda take so, zata bude musu manyan rassa a garin Maiduguri da Abuja.

Ta bangaren Habibu ma cikin ikon Allah sun fara rounding up kamfen dinsu, duk inda zasu shiga sun shiga, suna kuma ganin nasara da cigaba. Saura kuma ya rage suyi ta addu'a da jiran zuwan lokacin zabe.

Zaman daya samu ya sanya ya kara daukar duk kulawarshi da nutsuwarshi ya maida akan Nadiya da abinda ke cikinta. Laulayin nata ya lafa kwana biyu, tana kuma iya cin abinci yanzu sosai. Don haka jikinta yana ta kara murmurewa gwanin sha'awa.

48.

Shukurah ta hau dokin zuciya kwarai da gaske bayan fadan da Ummah tayi mata. Ta dauki makullin mota ta tafi gidansu kai tsaye ba tare da wani tunani ba.

Dama can gidansu gidane na sangartattun yara wadanda gata ya yiwa yawa. Mahaifiyarsu macece da bata son ganin laifin yaranta ko kankani, shi yasa tun tashinsu basu ganin kan kowa da gashi. Babu kuma wanda ya isa dasu balle ya ce zai sanya musu kara yace kada su tsallaka.

Mahaifinsu ba mazauni bane, shi yasa ba wani rawa yake takawa a cikin rayuwar tasu ba duk da cewa dai yana kokarin tsawatar musu shi ba kamar mahaifiyarsu ba.

Tana fadawa Mommynsu abinda ya faru, itama ta hau zubda nata fadan da zagi, wai Hajiya Ummah ta ci mata mutunci tunda har ta zagar mata diya.

Ta kuma ce mata ta wuce daki tayi zamanta, Hajiya Ummah din zata je ta sameta har inda take. A takamarsu su dukan, irin rawar da Shukurah take takawa ga kamfen dinsu, ga mahaifinsu shima dake bada nashi taimakon ta bangaren kamfen din Habibun, ai gani suke yi sun fi karfin wulakanci a wajen Hajiya Ummah.

Don haka koda Ummah ta kirata kan batun Shukurah, sai ta rufe idanu ta dinga zazzaga mata masifa, tace mata Shukurah ba zata koma ba har sai Habibun yaje da kanshi, itama kuma Ummah din sai ta ba Shukurah hakuri na muzantata da tayi a gaban Nadiya.

Ummah tayi murmushi sosai kamar tana gabanta, tace mata, "Hajiya Talatu, kiran da kika ga nayi ba wai don ina tsoron barin Shukurah gidannan bane kamar yadda kuke tunani, saboda naga alamun tana ganin kamar idan babu ita din ba zamu iya rayuwa bane ko kuma ba zamu samu nasarar zabe bane? Bayan kuma ba haka bane, ita kanta ta san da hakan, yaudarar kanta kawai take yi. Na kirane a matsayina na babba, wadda na dauki Shukurah tamkar diyata. Kwarai na yi mata fada saboda ta aikata ba daidai ba, don haka babu zancen bada hakuri a cikin wannan magana. Maigidanta kuma da kuke son gani, in fada miki gaskiya ma da na ce mishi ta taho gida cewa yayi umma-ta-gaida-assha. Don haka ki mata fada ki kuma kara da mata nasiha, ta dawo dakinta tunda nan ne marufar asirin kowace mace. Ta kama mijinta da abokiyar zamanta ta rike, su cigaba da zaman rufawa juna asiri. Ita rayuwa ai yar hakuri ce, zaman aure ma ya gaji haka kuma. Duk lokacin data shirya dawowa ina maraba da ita Hajiya. A gaida maigidan!"

Ummah ta kashe waya ta bar Hajiya Talatu da waya a hannu cike da mamaki.

Ta cewa Shukurah tunda hakane, ta kara mike kafa kawai ta cigaba da zama anan. Tana da tabbacin Hajiya Ummah da kanta zata kwaso kafa tazo bikonta. Ta kuma bi kalaman mahaifiyarta ta zauna a kansu daram, ta kara mike kafa tana jiran Habibun ko Ummah.

Sai dai me? Har ta kwashe sati biyu babu alamun wani zai je yayi bikonta. Zaman gidan ya fara takurata. Don kuwa dama dai can duk rayuwar bogi ce ake yi a gidan. Mahaifinsu yana da kudi babu laifi sai dai bashi da sakarwa iyalinshi kudi. Shi idan ya aurar da yarinya ma to ficika bata kara hadaki da shi sai in ta kama dole. Yayunta kowa na gidan aurenta, ba wata tsayayyar sana'a ba suke yi ko aiki duk kame-kame ne kamar dai ita. To gwanda ita din ta fisu fantamawa da budi na gidan aure. Don kuwa babu laifi Habibu ya tsaye mata sosai da sosai, yana kokarin sauke hakkinta dake kanshi, haka ko kudin kashewa zai bata yana kokarin bata masu dan kauri.

Rashin godiyar Allah ne ya sanya har take bi ta hanyar mayar da auratayyarsu tana karbar wani abu a hannunshi tunda dai babu ta inda ya rageta. To itama wannan din tun fara zancen aurensu da Nadiya ya fita harkarta, tunda ya samu wadda tasan hakkinshi da iya sauke nauyin dake kanta ta wannan bangaren meye na shi na biya?

Yawace-yawacen kamfen data fara ne ta fara zarar wasu yan kudade daga nan, tasan kuma Hajiya Ummah tasan da hakan amma bata taba mata maganar ba koda wasa.

Sauran kudaden da suka rage mata a cikin akwunt dinta ta cirosu, da Mamansu ta gani ta lallaba ta karbe rabi a hannunta. Ta kuma koma suka sake cinye na wajen Shukurah din da ita.

Da suka kare sai ta koma gefe kuma ta zuba mata idanu.

Cikin sati na uku da zamanta a gidan idanunta suka fara raina fata. Musamman ganin yadda mutane suka karkata hankalinsu ga Nadiya gabadaya, ake neman a manta da ita.

Sai gata ta fara kiran wayar mutanenta data tattara, tuni su kuwa da suka nufi wani Sarkin da suka fahimci dai bata da wata fawa yanzu. Wadanda suka samu wajen zama a wajen Nadiya da Hajiya Ummah suka zauna, wadanda basu samu ba kuwa sai suka canza sheka.

Cikinta ya duri ruwa sosai, tsoro ya dabaibayeta. Babban abin takaicin shine duk cikin Yayunta aka rasa wadda zata iya tallafa mata da wani abu, bayan kuma a da kullum cikin bani-bani suke daga su har Mommyn tasu.

Ga Daddynsu tunda taje gidan ma sau biyu suka hadu, yana ta yawace-yawacen daya saba shima don bai cika zaman gida ba.

Yana ganinta a gidan da safe ya tambayeta me taje yi gidan? Mommynsu ita ta dinga mishi bayanin abubuwan da suka faru, bayan ta hada karya da gaskiya. Ya gama saurarenta tsaf, ya kalli Shukurah yace, "gida dai ba zan hanaki zama a ciki ba, amma ki sani, you are on your own!"

Ya dauki kan wayoyinshi ya fita abinshi.

Gani na biyu data mishi magana ta mishi akan ya taimaka ya bata kudi tana son sayan kayan bukatu, kamar dama can jiranta yake yi. Ya rufe ido ya

mata cin mutunci sosai. Ya rantse ya kuma maya, kwandalarshi ba zata shiga hannunta ba. Shi yace tayi yaji? To shi wallahi ko mijinta mutuwa yayi abin Allah Ya kiyaye, ta dawo gida, sai dai ita da uwar da ta daure mata wani gu su dinga ciyar da ita amma ba da shi ba. Ya kara da cewa ta gode ma da take samun ci da sha mana.

Ya fita yana baza babbar riga Mommy ta bi bayanshi da sauri tana kara mishi tunin kudin da yayi alkawarin bata jiya. Suma da kyar ya lalubo ya mika mata su yana mata mitar ta fa dameshi da bani-bani.

Ta koma falon tana kallon kudaden a wulakance. Shukurah na rakube a gefe tana kallonta, tace, "Mommy bani dubu goma a ciki mana?!"

Ta zaro ido har tana hadawa da dafe kirji, "wace irin dubu goma Shukurah? Dududu dubu ashirin ce fa ya bani a cikin dubu hamsin. Ni wannan da zan miki lissafin abubuwan da zanyi da ita ma da wallahi duk inda kudi suke sai kin nemo min kin cika min su."

Ta wuce dakinta tana cigaba da mitarta.

Sai Shukurah ta rufe fuska da tafin hannu tana jin kamar ta kwala ihu.

Duk yadda taso daurewa ta cije, kasawa tayi. Sai gata bayan kwana biyu tana neman Habibu a waya, ta yi ta kira tana shiga tayi kara amma bai taba dagawa ba. Daga baya ma idan ta kira sai taji a kashe.

Ta sake rufe ido wannan karon ta kira Ummah. Wadda ta daga a kiran farko, suka gaisa da ita kamar babu wani abu dake faruwa. Har tana tambayarta ya Mommynsu da Daddy? Take ma bata labarin ai Daddyn nasu a gidanta ma yayi karin safe dazu, suna tare har wajen Azzuhur saboda wasu filayenta da yake son saya.

Sai kawai ta barkewa Ummah da kuka. An ce fadan da yafi karfinka ka maidashi wasa. Sai a lokacin Shukurah ta fahimci ashe bata da wayo ko kadan. Shi wanda take takamar dole ne su Ummah su nemeta saboda shi, gashi can yana cigaba da zuwa inda suke ba tare da sun ma sani ba. Da

alama kuma ko zancenta ma kila bai taba yiwa Ummahn ba. Wata zuciyar tace mata to zancen me zai mata? Shi a wajenshi ai ko yanzu kasuwa ta tashi to dankoli ya gama cin riba. Ko kun rabu da Habibu yanzu ai ba shi da asara, saboda yasan da taimakon daya yiwa su Ummah, in dai sun samu mulki ko kina nan ko ba kya nan ai dolene su rama mishi.

Anan ta fahimci cewa ashe ita duk tutiyar banza da wofi take yi. Don kuwa ba ita ta ke yiwa Ummah alfarma ba, su suke mata. Dama dai masu magana ai sun ce wuya makarantar kare.

Jin kukan da take yi tana karawa yasa Ummah ta fara tambayarta lafiya? Amma ta kasa magana, sai hakuri da take bata kawai.

Ummah tayi murmushi a hankali, tace mata, "har kin karaya ne tun yanzu Shukurah? Ai nayi tunanin ma watakila sai mun shekare a hakan kafin ki fahimci duniya da yadda take?"

Ita dai bata iya cewa komi ba sai shiru da tayi tana jan hanci da shessheka.

Ummah tace mata, "ban yi fushi dake ba Shukurah, haka ma mijinki baya fushi dake. Kuma kamar yadda na fada miki ne tun wancan karon, kofarmu a bude take idan kin shirya dawowa." Ta kashe wayar.

Amma duk da haka din sai ta yakice maganar komawa. Ta cigaba da lallabawa a haka, tana fatan Allah Yasa Ummah taji tausayinta taje tace su tafi. Amma abin ai da kunya, ta kamo kafa ta taho kuma ta koma babu wanda yaje biko?

Ta cinye wata fiye da daya tas a haka. Gabadaya watan nan har wani canzawa tayi, fuska ta fara mata kurzunu-kurzunu da dabbare-dabbare.

Ta ture kwanon abinci data gama ci tana hararar kwanon kamar shine mai laifi, "yanzu saboda Allah gida kamar wannan ace wai ba za a yi abinci da nama ba ko kifi? In babu su ko vegetables a dinga zubawa mana. Ni dai gaskiya ban saba da cima irin wannan ba!"

Ta fadawa Mommy hakan tana turo baki cike da shagwaba. Hajiya Talatu ta kalleta baki a bude, "to, gori ne nan kike min ko me? Ai kin dai fi ni sanin cewa mahaifinku bai cin nama balle kifi, don haka ba zai kawo ba. In kina so ki sa kudinki ki saya mana? Da kike mana gorin kuma baki saba da wannan cimar ba, ina ba ni ce nace ki baro gidanki ki zo ki nan ki kwarzabeni ba ko?"

Ta kalli mahaifiyar mamaki kwance akan fuskarta. Amma tsabar mamakin ma ya hanata cewa komi. Kawai sai ta tashi tsam daga kan dinning din, tace, "wallahi babu wani Daddy baya cin nama, kawai mako ne yasa yace bai ci don kada ya kawo shi nan!"

Ta haura da gudu dakinta na da inda ta sauka ganin Mommy din tana shirin wartota. Gyale kawai ta dauka da makullin mota ta fita. Mommy din tana kicin, sai jin tashin motarta tayi.

Kai tsaye gidan matar babban Yayansu Anty Hadiza ta yiwa tsinke. Ma'aikaciyar asibiti ce ita. Duk cikin yayunta daga ita sai Yaya Buhari ne kadai suka nuna jin haushinsu na rashin karbar ban hakurin da Ummah ta yiwa Mommy. Suka kuma fadawa Shukurah din itama bata kyauta ba, ba kuma haka ake yi ba.

Amma da yake a lokacin kanta rawa yake yi, sai ce musu tayi ba sonta suke yi ba shi yasa.

Amma ko a yanzu da halin data shiga, Yaya Buhari ne kadai mai taimaka mata da wani abu.

Anty Hadiza ta kama baki ganin yadda Shukurah din ta koma, duk ta wani birkice. Tana ganinta kuma sai ta saki kuka, ta dinga rera shi Anty Hadiza na bata hakuri har tayi shiru.

Tace, "Anty Hadiza na tuba, don Allah ki maidani gidan Habib wallahi na dauki darasina!"

Sai tayi dan murmushi, ai dama tasan ranar yau na zuwa. Amma maimakon ta zauna tuna mata baya da ce mata ai dama na fada miki, sai ta samu ta

kara lallashinta. Ta zubo mata abinci shinkafa da miya ta ji kaji, ga wani romon na kayan ciki da ta dafa shi da sinadarai na gyara jikin ya mace. Sai zama tayi a gefe baki dage tana kallon yadda Shukurah take kai lomar abincin nan hannu baka hannu kwarya.

Ta gama cin abincin tayi gyatsa tana kallonta, "wallahi rabon da in ci nama tunda na bar gidan Habibu!"

Anty Hadiza dai wannan lokacin ta kasa daurewa, sai ta saki dariyar data jima tana dannewa. Shukurah ta jingina da kujera tana kallonta har ta gama, tace, "don Allah ba tashin-tashina zamu yi ba, ni dai yanzu ki taimaka ki fada min abinda zan yi in gyara wannan laifi da na tafka!"

Anty Hadiza ta zaunar da ita a ranar tayi mata nasiha da fada sosai irin wanda bata taba yi ba, don Shukurah bata taba bata damar hakan ba. Amma da taga yau ta zauna kuma tana sauraronta sai data juye mata duk wani abu dake ranta. Ta bata shawarar tayi hakuri ta zauna da abokiyar zamanta lafiya, uwar miji kuma ta riketa da mutunci don kuwa babu namijin da zai kyale matarshi ta raina mishi uwa matukar dai yasan inda ke mishi ciwo.

Maganganu dai masu dama da tsayi wadanda rabinsu tana yinsu ne a lokacin da take taimaka mata tana kimtsawa. Har zancen yadda take hana miji hakkinshi na aure da kuma neman ya mata wani abu kafin ya kusanceta sai data mata, ta kuma nuna mata hakan babu kyau.

Ta shiryata cikin wata shadda ruwan gwaiduwar kwai mai kyau, suka dauki hanya a motarta sai gidan Habibu.

Hajiya Ummah sai jin sallamarsu tayi kamar daga sama.

Anty Hadiza ita ta kai Shukurah har gaban Hajiya Ummah ta kuma bata hakuri kan duk abubuwan da Shukurah din tayi. Tace ita dama bata riketa ba, amma irin wadannan halaye data tsira ba zasu karbu bane a wannan gida. Ta amsa cewa tayi laifi kuma zata daina da yardar Allah, kafin Anty Hadiza ta rakata dakinta.

Da dare Ummah ta sake hadasu waje daya ta musu fada da nasiha sosai game da zamantakewa. Bayan sun tafi ta sake jimawa da Habibun tana kara gayar dashi muhimmancin tsayar da adalci a tsakanin iyali. Don yadda taga yayi biris da Shukurah din baya ma nuna alamun yaji dadin dawowarta gidan sam. Tasan ba karamin jan aiki bane a gabanshi.

Ranar Nadiya tayi kwanan rungumar filo. Duk da cewa ita da kanta ta dinga so ya dawo da Shukurah din da kuma kwatanta yadda ba zata bari wani abu ya dameta ba idan ta dawo din, amma ina, ta gaza. Wannan lokaci da suka kasance a tare da babu abinda yake rabasu, sunyi wani irin sabone mai wuyar fassarawa. Don haka ita dai ranar barci sai barawo yayi awon gaba da ita.

49.

Sun hadu da Shukurah din washegari a bangaren Hajiya Ummah. Ta sameta ita kadai a kan dinning, sai ta ja kujera a daya gefen ta zauna, tace mata, "Ina kwana?"

Ba don tayi tunanin za ta amsa ba. Ga mamakinta kuma sai taga ta amsa mata din.

Bata nuna mamakin hakan ba, sai kawai ta janyo kwano ta fara zuba farfesun naman kan sa da ya sha taruhu da daddawa yana ta tashin kamshi mai dadi. Ta fara cin abinta a nutse. Wayarta ce a hannunta tana chatting da Aramide wadda a lokacin tana Lokoja.

Haka Ummah ta fito ta samesu. Ta zauna a kan kujerar data saba zama, Nadiya ta zame tana gaisheta. Itama Shukurah sai ga ta ta zube har kasa din

tana gaidata. Hakan ya matukar ba Nadiya mamaki kam har ta kasa boyewa, don kuwa tun zuwanta gidan wannan ne karo na farko data dukawa Ummah lokacin da take gaisheta. Kullum a tsaye take ko daga zaune bata ko dan rankwafawa.

A kwanakin da suka biyo baya haka zaman nasu ya cigaba da gudana. Shukurah bata tsokanarta da magana kamar da, sai dai kuma bata shiga sha'aninta, itama kuma bata shiga nata. Iyakarsu dai idan sun hadu a falon Ummah su gaisa, daga wannan shikenan.

Amma mu'amalarta da Ummah da ta Habibu din tana matukar bakin kokari wajen ganin cewa ta gyarata, tana kuma kokarin jan Ammar jikinta. Sai dai ta fahimci ba karamin jan aiki bane a gabanta. Don kuwa daga Ammar din har Babanshi suna da wani hali na wuyar sabo, musamman idan suka saba da halin mutum, suna da wahalar canza yanda suke kallonshi a cikin ransu.

Amma da yake da gaske din shirin take so, ba don komi ba sai don fahimtar da tayi Habibun ba ta tatan yake yi ba, ta Nadiya da abinda ke cikinta yake yi. Sai ta samu kanta da damuwa da fatan inama ace ita ce take samun wannan kulawar? Sai ta cigaba da zage dantse kamar yadda Anty Hadiza tace mata. Ta kuma dage da addu'ar Allah Ya tsari zuciyarta da kishi marar misali, da bakin ciki da hassada ga kowa. Wannan duk shawarwarin Anty Hadiza dinne, kuma cikin ikon Allah ita kanta tana jin dadin yadda yanzu duk bata jin wannan haushin Nadiya da take ji a da.

Sai yanzu take da na sanin rashin haihuwa da wuri, watakila da ko don saboda danta ko diyarta Habibu ya dinga ganinta da mutunci. Tana sane ta dinga afa contraceptives don kada ta haihu da wuri kada jikinta ya sakwarkware. Shawarar mahaifiyarta da sauran yan'uwanta. Gashi yanzu haihuwar take nema ido rufe amma shiru kake ji kamar an shuka dusa.

***

Wata uku da dawowar Shukurah din aka kira Nadiya gida, Abbansu bai da lafiya sosai suna asibiti a yanzu haka. Lokacin cikinta har ya shiga wata na shida. Ta tafi hankali a tashe.

Asibitin da aka kwantar da shi suka wuce kai tsaye ita da direba.

Ta samu wajen dankare da matanshi da yayan duk sunyi wani wujiga-wujiga. Lallai maigida duk rashin kirkinshi dai maigida ne babu zancen musu.

Ta shiga wajenshi ta sameshi a kwance ana mishi karin ruwa. Bayan sun gaisa da matan ta tambayesu ya mai jiki? Aka kaita wajen likitan daya duba shi tana tambayarshi me ke damun mahaifinsu?

Ya ciro wasu charts na gwaje-gwaje da aka yi mishi yana nuna mata tare da yi mata karin bayani.

Abban ciwon mara yake damunshi da kuma matsalar rashin yin fitsari. Idan ya tashi yin fitsarin musamman cikin dare ko da safe, baya iya yin da yawa sai dai yayi dan kadan. Kuma yana samun matsalar iya rike fitsari, musamman idan ya kwanta da dare sai dai yaji ya tashi cikin fitsari, ko kuma bayan ya yi fitsarin sai ya dawo yana diga kadan-kadan. Ga shi duk ya kumbura, kafafunshi da fuskarshi sunyi suntum.

Sun yi mishi gwaje-gwaje da dama, a awon PSA da suka mishi, ya tabbatar musu yana dauke da cutar Benign Prostatic Hyperplasia (BPH). Common cuta ce wadda aka fi samunta a dattijai maza wadanda suka haura shekaru arba'in a duniya, kuma ta fi yin kamari ga irin masu yawan aure-aure dinnan ko yawan neman mata. Bayan matsalar fitsari ma suna tunanin kodarshi ta dan tabu amma ba da yawa ba, akwai kuma yiwuwar yana fama da matsalar low sperm count. Don haka zuwa gobe zasu kara yin wasu gwaje-gwaje don su tabbatar da zarginsu.

Zasu dorashi akan magunguna, zuwa nan da sati biyu idan basu gamsu da aikin magungunan ba to sai sun kai ga yi mishi aiki gaskiya.

Tayi shiru tana sauraren bayanin da yake yi mata har gama, ta mishi godiya tare da tashi tsaye. Sai data tsaya ta fara biyan duk wani abu da aka biyosu ta sayi magungunan da duk abinda za a bukata kafin ta koma dakin da aka kwantar da shi.

Ta zauna anan tare da matan tana kara yi musu maimaicin bayanin da likita yayi mata har zuwa lokacin daya farfado. Suka dukufa a kanshi suna tambayarshi ya jiki?

Sai zuwa yamma sannan Babangida yaje da kanshi ya dauketa bayan ya shiga har dakin da aka kwantar da Abban ya gaidashi ya mishi ya jiki. Shima sai daya sake ganawa da likitan da case din Abban yake hannunshi. Likita daya fahimci ko surukin wanene yake kulawa nan da nan ya kara shiga cikin hankalinshi, kulawa sama da kasa ya sake daukowa ya dora akan Abba.

Suka rabu dashi akan cewa daga yanzu komi na kulawar Abba din yana hannun Habibun, don haka duk wani abu daya taso ya fara sanar dashi. Sannan koda aikin ne ya taso, to shi zai dauki dawainiyar aikin.

Yana komawa dakin ta tashi ta fara gyara lullubin jikinta don tasan karshen zancen. Mama ce da Lantana a wajen lokacin da yaje, ya duka yana yi musu sallama tare da sanya hannu a babbar rigarshi ya ciro sabin kudi wrapper na dari biyar ya mikawa Nadiya data karasa wajenshi, yace a ba Mama an siyawa Baba magani.

Ta mikawa Mama kudin wadda ta sanya hannu biyu ta amsa tana musu godiya tare da fatan Allah maidasu gida lafiya.

Suna bada baya Lantana ta kaiwa kudin nan damka tana lalasu a hannu baki har kunne, cewa take, "kai! Auren 'ya mace mai dadi idan aka dace! Don Allah kiga irin wannan abin alheri da Malam yake gani iri-iri daga aurar da mace daya kadai!"

Mama ta kalleta cike da takaicinta amma bata ce mata komi ba. Ta raba kudin nan gida biyu ta soke a zaninta, ta mikawa Mama daya rabin tana ce mata, "gwanda ki boye wadannan kafin sauran su zo su ga ni su sanya miki wawa. Allah na tuba kuma me za a siyawa Malam yanzu? Duk wani abu da za a bukata sun kawo sun ajiye mana fa!"

Tsabar haushi Mama kasa ce mata komi tayi, ta cigaba da jan carbinta tana lazumi abinta, ta bar Lantana na cigaba da santinta da zubawa Nadiya da mijinta Habibu godiya.

****

Cikin satin suna ta kaiwa da kawowa wajen duba jikin Abban wanda aka sallamo daga asibiti bayan kwana uku. Yara ana ta shiga da fita kullum kaje gidan kusan a cike yake da yaya da jikoki yan dubiya.

Bayan kwanaki sha hudu suka sake komawa, likita yace dole sai sunyi mishi tiyata saboda abun ya riga ya taba mafitsararshi ga kuma koda da take kokarin tabuwa.

Aka sanya ranar aiki, aka yi cikin ikon Allah aka yi lafiya aka gama.

Sai dai likita yace akwai yiwuwar ba lallai ya sake haihuwa ba. Kai auratayya din ma gaskiya zai iya daukar lokaci mai dan tsayi kafin ya iya.

Suna komawa gida bayan an sallamesu ya tara matan duka, ya yi musu bayanin abinda likita yace. Ya fada musu su dukansu ya basu zabin duk wadda taga zata rabu dashi ko kuma zata cutu saboda haka ta fada mishi, gwara kawai ya sallameta akan ya dinga shiga hakkinta. Suka yi shiru su duka suna kallonshi, Mama dai tashi tayi ta fita ma daga dakin abinta ta cigaba da ayyukanta da take yi. Yaya AbdulHadi ya sake siya mata firjin babba ta hada da dayan da take da shi, don haka abubuwan sanyi da take yi ana saida mata yanzu ta kara yawansu. Don kuwa yanzu har daga gidajen biki da suna aikawa ake ana yi a kai musu.

Suma sauran duk sai suka tashi suka fita alamun dai babu mai niyar rabuwar. Duk da haka sai ya kara tsayar da amarya, yace mata ita ce karama a cikinsu, wadda ko haihuwar fari bata yi ba. Ba zai iya cigaba da zama da ita ba bayan shi babu tabbacin zai iya ma tsinana mata wani abun nan gaba. Don haka tayi hakuri amma ya sauwake mata igiyarshi dake kanta biyu. Ta kuma yi hakuri ta yafe mishi idan ya taba yi mata wani laifi.

Daga Mama har Nadiya babu wanda yaji dadin wannan hukunci daya yanke, sai dai su dukansu sun san cewa hukuncin daya yanke shine dai-dai. Sai kawai suka yi mata fatan Allah Yasa hakan ya zame mata alkhairi kawai. Zumunci kam ai sun riga sun daura shi da yardar Allah, za kuma su ci gaba da yi koda bata gidan.

Ta je ta kwashe kayanta tayi sallama da mutanen gidan.

Su kuma matan suka rukufa a kan maigida ana ta aikin jinya. Wannan zaman jinyar da yayi duk shi ya kara tsayar da duk wani samu nashi, ragamar kulawa da gida ta koma hannun Mama da Nadiya. Don ma su Anty Jamilah da sauran Yayunsu suna nasu iyaka bakin kokarin.

Tuni su Salame aka dawo cikin hayyaci don sun gane dai babu fa wani Sarki sai Allah. Ranar nan Nadiya taje gidan duba Abban sai ta tsinto Salame a kofar dakin Mama tana tayata zuba kunun tsamiya da zobo a cikin jarkoki suna jerawa a firjin ita da su Maryam. Lantana din kuma tana bakin kofar kicin tana aikin taya Mama din dahuwar abinci.

Ta kama baki cikin mamakin wannan abu, a ranta tace, 'lallai dai wato in da ranka zaka sha kallo har ka gaji! Dama wannan rana zata zo?!'

✷✷✷✷

Watanni uku ne bayan hakan, suka nabba'a a falon Ummah su dukansu family din a ranar wata Juma'ah da dare a cikin watan Afrilu, inda ake fadin sakamakon zaben da aka gama gabatarwa a ranar Alhamis, jiya kenan. Kasancewar an daga zaben da kusan watanni biyu sakamakon wani canji da Gwamnati tayi na tsare-tsaren zaben, amma da tuni an yi an gama ma.

Tana zaune da rindimemen cikinta Tubarkallah, wani lokacin har rinjayarta yake yi idan zata tashi. Hannunta damke cikin na Babangida, bakinta dauke da Bismillah. Ji take yi kamar ta fada cikin Talabijin din ta dubo rahotannin da kanta.

A gefe daya Ummah ce da Shukurah da Mami da itama taje cikin satin da kuma babban danta Ma'aruf, wannan shekarar ya hada degree dinshi akan Social Work, a University of Washington Zarqa (Zarqa shine babban gari na biyu a cikin Kasar Jordan). Farida da Yayanta Fu'ad suna tare da mahaifinsu da bai samu damar zuwa ba saboda karatun yaran da kuma wajen aikinshi da ba a jima da yi mishi karin matsayi ba.

Ga sauran amintattun mutanensu duk suna warwatse a zaune a falon suna zaman jiran jin sakamakon in a bated breath.

Duk da cewa daga yadda ake fadin irin nasarorin da suka samu a wurare da dama, suna da tabbacin suna da jagorancin tafiyar, amma duk da haka basu sakankance ba.

Har zuwa lokacin da mai gabatarwar yace, "sai kuma gari na karshe wato nan cikin Katsina City, an samu kuri'a dubu arba'in ga jam'iyyar BOP, kuri'u dubu hamsin da biyu ga jam'iyyar CPA, da kuma kuri'u dubu tamanin da dari hudu da takwas ga jam'iyyar New Hope Party..."

Ya dakata da maganar na dan lokaci, Nadiya ta ja numfashi sama, "....Da wannan muke cewa Jam'iyyar New Hope Party ita ce ta lashe zaben wannan karon a jahar Katsina da rinjaye ga sauran jam'iyu da kuri'u har dubu goma sha biyu. Don haka muke cewa congratulations to our new Governor, Alhaji Habib Abdullahi Makam tare da shi da mataimakinshi Malam. Abubakar Khamis. Allah Ya baku ikon sauke wannan nauyi da ya rataya a kanku, Allah Ya tayaku riko!"

Falon gabaday sai ya dauki Kabbara da shewar murna da farinciki, aka shiga yiwa juna barka.

Ta rungumoshi cike da tsananin farinciki da murna, tace, "Congratulations Habibi!"

Murmushi yake sosai lokacin daya rungumeta shima, yace mata, "I know we will make it dama, Alhamdulillah!"

Ya duka ya tafi yayi sujjada anan wajen, ita da su Ummah duk sai suka rufa mishi baya. Suka kai goshinsu kasa suna yiwa Allah godiya da wannan nasara da suka samu.

Falo ya rincabe da murna da farinciki, wannan ya rungume wannan, wancan ya rungumi wancan, sai ga su ita da Shukurah sun rungume juna cikin rashin sani. Suka yi kokarin janyewa, Nadiya tayi karfin halin rike hannunta tana kallonta fuska cike da farinciki. Tace, "ina tayamu murna Anty Shukurah, Allah Ya bamu ikon taya mijinmu sauke nauyi da hakkin daya hau kanshi."

Sai tayi dan murmushi, tace mata, "ameen ameen Nadiya!"

Zuwa lokacin kam duk wani abu dake ranta ta saukeshi. Sai dai ta kasa sakin jiki da Nadiya ko kadan, sai ita din take kokarin shiga jikinta tunda dai ta kula ta sauko. Ko babu komi, tana son kwanciyar hankalin mijinsu. Bata son abinda zai raba mishi hankali ko kadan, shi yasa take kauna da kwadayin su hade kansu da ita. Bata kuma son abinda zai taba tarbiyar yaransu, tana so ne su tashi su dukansu cikin farinciki da kaunar juna, wanda hakan ba zai taba samuwa ba matukar suka tashi suka ga iyayensu kansu a rarrabe.

Ita din ai victim ce na irin tsarin wannan gidaje, ga gidansu nan kowa wanda suka fita ciki daya ta sani da kuma uwashi. Musamman kannensu dake tasowa a yanzu, zaka yi mamaki idan kaga karamin yaro na nunawa dan wani dakin yan ubanci tsantsa. Babu kuma yadda za ayi dasu tunda tushen matsalar daga iyayensu yake.

Mutane suka fara yi musu sallama suna tafiya tare da kara tayasu murna.

Zuwa karfe goma sha daya duk an watse sai su ne kadai a falon suna cigaba da maida yadda aka yi.

Ya dubi yadda ta kwanta tayi lamo a kusa dashi, ya kalleta cike da kulawa, "baby lafiya?"

Ta girgiza kai a hankali tana dan yin hamma, "babu komi, barci kawai nake ji."

Sai ya tashi tare da kama hannunta, yace, "to muje mu kwanta. Ai kin ma yi kokari yau. Ke da kike kwantawa tun karfe tara."

Babu musu ta mike, suka yiwa su Ummah sai da safe. Shukurah itama ta bi bayansu tana cewa itama kwanciyar zata je tayi.

Suna zuwa sashenshi wanka tayi, ta yi shirin kwanciya ta kwanta. Babu jimawa shima yaje ya bi bayanta ya kwanta.

Cikinta yayi wani irin girma mai ban mamaki, gashi har ta shiga cikin watan haihuwarta, duk scanning din da ake yi mata tace kada su duba mata gender ko wani abu. Tunda dai abinda ke cikin yana lafiya, idan ya fito sun gani da idonsu. Don haka yanzu bata iya aikata mishi komi. Duk da cewa yana mata matukar kara da kawaici, haka zasu kwanta da shi su tashi baya taba neman komai a wajenta duk kuwa da cewa tana ganin yadda haka din yake damunshi. Ta kuma yi suggesting ko ya dinga kai kwanan nata wajen Shukurah a lokacin da yaga ba zai iya jurewa ba? Yayi kici-kici da fuska a lokacin yace mata kada ta sake mishi wannan zancen baya so. Don haka bata kara tada mishi zancen ba.

Yadda taji yana shigewa jikinta da shafarta yasa taji ta fara shan jininta.

Yace, "celebrating nake yi Nadiya kada ki hanani, ai nayi kokari ko? Yakamata ace har award din Sarkin hakuri da dagawa matarshi kafa kika bani."

Ta dai san bata da bakin hanashi, don haka ta kyaleshi ya dinga juyata son ranshi. Har zuwa lokacin daya samu abinda yake so din, ya ja ta cikin jikinshi ya rungume tsamtsan kamar ya tsaga kirjinshi ya maidata ciki.

50.

An sanya ranar handing over wato ranar da za a rantsar dasu kwanaki arba'in masu zuwa. Ana sanya ran azumi nan da kwanaki uku, don haka a kiyasce dai bayan sallar azumi da sati daya kenan.

Duk cikin satin basu samu zama ba, suna ta karbar baki iri-iri yan taya murna da kuma shirye-shiryen karbar mulki da Habibu yake yi, don haka ba yawan zaman gidan ba ma yake yi.

Mami tana nan anan zata yi azumi, tace sai an shiga gidan Gwamnati da ita sanna zata juya ta tafi, saboda hutu ta dauka a wajen aikinta mai tsayi. Sessions da take yi da patients dinta kuma yawanci suna yi through Google Meet, don haka bata da matsala.

Suna ta shirye-shiryensu da tsara yadda suke ganin zasu tafiyar da mulkinsu, ita Nadiya ba ta wannan take yi ba. Don kuwa cikin kwanakin duk a tsaitsaye take, ita kanta tasan bata jin dadi amma kuma ta ma rasa me ke damunta. Shi yasa ma bata fadawa kowa ba kawai ta daure tana cigaba da al'amuranta.

Sun kai azumi na takwas, ta tashi cikin dare zata yi fitsari. Ita kadai ce a sashen nata saboda Habibu yana wajen Shukurah.

Tayi fitsarin ta koma ta kwanta, sai kuma barci ya gagareta. Zuwa can kuma sai wani fitsarin ya taho. Tun safiyar ranar dama ta tashi tana zubar da wani ruwa mai kala kadan-kadan. Ganin bata jin ciwon komi kuma EDD dinta sai nan da sati daya ma zai cika, sai bata kawo komi a ranta ba.

Wasa-wasa sai gashi ta fara zaryar zuwa bandaki. Tun tana yin fitsarin har abu yazo ya gagara, sai dai kawai ta tsuguna ta tashi. Tafi-tafiya ma sai tafiyar ta fara gagararta. Nan dai tasan abin ba na wasa bane. Sai ta lalubo waya ta kira Babangida, amma wayar tashi a kashe. Ta manta idan zai kwanta barci wayarshi a flight mode yake sanyata, ta sake kiran ta Mami itama din dai a kashe. Ta cije lebe, a ranta tace bari kawai ta lallaba ta tafi sashen nasu da kanta. Cikin ikon Allah kuma duk ba wani ciwo ne take ji na

azo a gani ba, wani barci ma yake janta, don haka sai kawai ta koma ta kwanta.

Can taji kamar an mintsineta, ta fara jin ciwo a mararta da kwankwasonta sama-sama, nan ta sake tashi ta nufi bandaki. Kafin ta karasa sai jin wani abu ya fashe tayi, sai ga ruwa yana bin kafafunta.

Bata san lokacin data durkushe a inda take ba saboda wani gigitaccen ciwo daya riketa a take. Ta dafe baya tana murkususu har dai ta samu ciwon ya lafa.

Ta sake lalubo wayarta a sukwane tana bin jerin contacts dinta har idanunta dake wani dishi-dishi suka dira akan sunan Shukurah, ta danna mata kira cikin fatan Allah Yasa ta daga.

Sai data kusa katsewa sannan ta daga muryarta cike da gagin barci, tace mata, "don Allah don Annabi Anty Shukurah ki kira min Mami ta zo, bayana zai cire!"

Tayi jifa da wayar tana sakin wani kakkarfan salati bayan da taji wani ciwon ya sake turnuketa.

Shukurah ta zabura ta tashi sakamakon jin wannan ihun da tayi, a ranta tace babu lafiya.

Ita kadai ce a sashen nata, don kuwa tun dawowarta har yau basu daidaita da shi ba, fushi yake yi sosai tun karfinshi. Itama kuma data gaji da ban hakurin sai ta koma ta zuba mishi idanu kawai, Allah Ya gani ai tayi iyaka bakin kokarinta, hakan kuma ba shi zai sa ta zubar da ajinta ba don tana so ya sauka daga dokin zuciya daya hau ba.

Ta dauki zane ta dora akan doguwar rigar barcinta ta fita da sauri taje ta bugawa su Ummah kofa.

Sai ga Mami da Ummah da Shukurah din bangarenta a sukwane. Da kyar ta iya tashi a duke taje ta bude musu kofar. Lokaci daya tayi wani wujiga-wujiga

da ita. Mami tayi saurin tarota tana kamata, ta dubi Shukurah da jikinta ya dauki rawa ganin halin da Nadiya take ciki.

Tace mata, "kiyi sauri ki je ki bugawa Babangida kofa, ya dauko mota ya zo mu tafi asibiti."

Ta juya babu musu ta fita da sauri.

Nadiya ta kama hannun Mami ta rike kamar zata karyata, "ki taimaka min Mami, kuguna zai karye!"

Mami tace mata, "daure Nadiya, in shaa Allahu babu abinda zai sameki kinji?"

Tayi kokarin daga kai, amma abin ma sai ya gagara.

Tace mata, "wani abu zai fito..." ta tafi ta sake dukewa a wajen.

Mami ta zabura ta jata daki a sukwane, tana gyara mata kwanciya ta duba sai ga kan da. Ai nan da nan sai ta hau aiki.

Kafin dawowar Shukurah da Babangida daya rigata zuwa saboda saurin daya dauka har da hadawa da gudu-gudu, yar yarinyar ta fado tana ta tsala kukanta.

Anty ta dagata sama tana hailala, uwar sai ta koma kasan tiles ta yada kai tana salati tana karawa a matukar galabaice.

Ummah tana falo tana kaiwa-da-kawowa bakinta dauke da salati itama da sallallami, sai jin kukan da tayi. Shima da yaji kukan sai ya nemi danna kai cikin dakin a sukwane, tayi gaggawar dakatar dashi. Tace yayi hakuri ya bari a gama kintsasu tukun. Haka ya ja tunga shima ya tsaya anan, amma gabadaya ilahirin jikinshi bari yake yi. Kukan yarinyar jin shi yake har cikin kwanyarshi, so yake yi kawai ya sanyasu a cikin idanunshi.

Mami ta yankewa diyar cibi, ta nadeta a cikin shawl mai taushi bayan ta gogeta tas da man zaitun. Shiru-shiru uwa bata biyo baya ba.

Nadiyar na kwance ita dai gata nan, don kuwa maimakon ciwo yayi kasa ma sai wani sabo daya taso. Kafin ma Mami tace mata bari ta tadata tsaye ta jijjiga ko tayi kasa, sai ga sabuwar nakuda ta taso.

Mami tayi salati ta kara da hailala, sai ta sanya murya tana kiran Ummah. Dama ita kanta kara ce ta hanata shiga, sai kawai suka danna kai ciki ita da Babangida, Shukurah dai ta kasa shiga. In banda rawa babu abinda jikinta yake yi. Dama haka haihuwar take, take nemanta ruwa a jallo? Gaskiya da sake.

Suka shiga suka samu wani sunkucecen dan har ya ma fi yarinyar girma. Cikin ikon Allah kuma sai ga mabiya din ta fado.

Ummah ta karbi yarinyar ta rike, Babangidan ya rabe ta bayanta yana lekenta, kyakkyawar diya da ita Ma shaa Allah, babu abinda ta bari na uwarta, tana ta tsotson baki alamun tana neman tsotsa. Ummah na tsokanar 'daga gani wannan acici ce!' amma hankalinshi yana ga Nadiya da Mami da take kokarin gyara dayan yaron.

Ta gyareshi tsaf ta mika mishi shi, ya amsheshi cikin rawar hannu. Sai daya lalubi kujera ya zauna.

Mami ta taimakawa Nadiya ta tashi suka wuce bayi. Ta zaunar da ita akan stool yayinda take kokarin hada mata ruwan wanka saboda jiri.

Sai lokacin Shukurah ta shiga dakin. Sai ta lalubo kayan goge-goge ta shiga gyaran dakin.

Ita ta gyare wajen tsaf ta goge ko'ina, Mami kuma na can tana gasa Nadiya da tawul mai zafi. Don tace mata wanka zata mata mai suna wanka.

Kafin kiran Asubahi Maijegon da yan biyunta sun fito tsaf da su an gyaresu.

Ranar Ummah da kanta ta shiga kicin ta tukawa Nadiya tuwon dawa da miyar kuka, tana da kominta a ajiye dama, miyar ma dumamata kawai tayi

tunda tana da ita a cikin firjin a ajiye. Ta zuba yajin daddawa wanda Nadiyar bata rabo dashi a cikin yan kwanakin da man shanu. Ta kuma hada mata kunun gyada mai kauri sosai.

Tana zaune a gefen gado Ummah ta shiga kwanon. Ji take kamar ta kwato shi saboda yunwar data ke ji.

Ta daure dai har ta kai mata kafin ta amsa. Ta gyara zama tana ci hannu baka hannu kwarya.

Shukurah da Mami na zaune suna kallonta cikin dan murmushi.

Ummah ta wuce sashenta don yin sallah, shima Habib din ya tafi masallaci.

Ta gama cin abincin tsaf, ta wanke hannunta, ta gyara kwanciya yaran na gefenta. Ta lumshe idanu sai barci mai dadi ya kwasheta.

Shukurah itama ta lallaba ta koma nata bangaren don ta huta kafin wayewar gari. Mami kuwa nan ta gyara zama akan sofa tayi kwanciyarta tana lazumi.

Zuwa wayewar gari su Mama sai jin labarin haihuwar kawai suka yi.

Duk da cewa Mami ita ta karbi haihuwar, amma ba bangarenta bane. Don haka sai da likita taje har gida ta dubata ita da jarirai, ta tabbatar musu da cewa lafiyarta lau babu wata matsala.

Mama taje gidan ita da su Maryam da Salame, suna falo tare da sauran yan'uwan su Mami da iyalan Uncle Hashim da suka je.

Ta fito daga wanka da misalin karfe sha daya na safe. Mami ta sake yiwa yaran wanka, yan barka sun gama ganinsu suna kwance cikin baby net dinsu suna barci.

Ta zura doguwar riga marar nauyi. Jin jikinta take yi shafal, kamar in aka hureta zata iya faduwa. Kai ita gabadayanta ma jinta take yi kamar wadda aka canza.

Ta fito ta sameshi zaune a gefen gadon ya kurawa yaran idanu yana kallo, Ammar a gefenshi yana tambayarshi, "Daddy wadannan duk kannena ne?" Yana dariya ya amsa mishi da, "ehh! Duk naka ne."

Ta karasa gefen gadon ta zauna itama tana kallonsu cike da murmushi, ya bita da kallo har ta zauna.

Kallonta yake yi da wani kallo da bai taba yi mata shi ba, da so da kauna da wata tsantsar girmamawa da mutuntawa irin wanda bai taba jinsu a ranshi ba akan kowa bayan Ummanshi.

Ya riga ya gama nuna mata irin godiyarshi tun da Asubahi din kafin ya tafi sallah, lokacin data fito wanka su kuma su Ummah sun fita don yin sahur, Mami na bayi tana wanke yaran, ya tattagota cikin jikinshi ya rungume yana rada mata irin farinciki da jindadin dake ranshi a lokacin, da dimbin godiya da alkawarurruka iri-iri na nuna mata so da kauna irin wadanda ba za su kwatantu ba ita da yayanta har su gama rayuwarsu a doron duniya. Amma ji yake kamar duk wadannan basu isa ba. Kamar bai ma nuna mata komi a cikin irin farincikin dake ranshi ba.

Ta maida hankalinta ga Ammar dake watsa mata nata kalar tambayoyin, ta biye mishi tana amsawa a nutse, wani tayi dariya. Yana saurarensu yana murmushi a tausashe shi kuma. A haka Shukurah ta shiga dakin ta samesu. Taji wani abu ya dan taba mata zuciya, ga su nan dai idan ka gansu ka ga the perfect family. Masu son junansu da kulawa da juna sosai, ita kuma tayi saken da bata kasance a cikinsu ba. Ta ji jikinta yayi sanyi kwarai, tana son ta gyara kuskurenta amma ta rasa ta yaya? Shi kuma Habibu ya ki bata damar yin hakan.

Ta kalli Nadiya a sanyaye tace mata, "Ummah ce tace a tambayeki idan da abinda kike son ci ki fada sai a dafa miki."

Tayi dan murmushi tana girgiza kai, "a'ah, ba ni da zabi gaskiya. Duk abinda aka dafa zan ci. Nagode."

Ta gyada kai, ta juya ta fita.

Shi kuma ya gyara zamanshi yana kallonta a nutse. Yace, "kinga har zuwa yanzu bamu yi maganar abinda kike ganin ya dace a sanyawa yaran nan ba."

Ta girgiza kai kanta a kasa, "ai ni duk abinda ka sanya musu ba ni da zabi. Allah Ya raya su."

Ya jinjina kai, "to ameen ameen Maman biyu!"

Ta jefa mishi hararar wasa, ya yi murmushi.

Yayi Bismillah ya dauki babbar yayi mata duk abinda Uba ya kamata yayi, kafin ya dauki namijin shima ya maimaita mishi.

Ya dora mata su duka akan cinyoyinta, "to ga Abdur-Rahman da Ummulkhairi!"

Ta kankamesu a jikinta tana dan murmushi, a ranta take addu'ar Allah Ya bata ikon kulawa da tarbiyantar dasu bisa tsari da tarbiya na addinin musulunci.

Ummah da taji anyi mata takwara kamar ta dauki Nadiya ta goya a bayanta saboda murna.

Wannan haihuwa taje musu da sauyi mai matukar dadi a rayuwarsu. Don kuwa a ranar da Hajiya Hadiza taje ganin yaran lokacin kwana hudu da yin haihuwar kenan, sai ga shi Ummah ce da kanta tayi mata jagora zuwa bangaren Nadiya. Ta dauki yaran ta mika mata su, ana ta raha da tsokanar juna da hira su biyun kamar wasu tsofin aminai. Haka da zata tafi ma sai da Ummah din ta rakata har waje, tana kuma kara maimaita mata lallai fa ta zo wajen rantsarwa. Ita kuma tana dariya take ce mata, "ai ko bata zo ba, ita Ummah din ta wadatar!"

Ummah itama tayi dariya sosai, tace, "ke dai Hajiya ki zo, saboda zuwan naki shi zai sa komi ya zamana a kammale kuma a tsare."

Sai suka yi sallama da ita akan haka din. Zuwan da tayi cikin dar da taraddadin me zata tarar? Sai ta koma gida cikin farinciki da sukunin zuciya kwarai da gaske.

Madam da ta tashi zuwa ganin jikoki kuwa abin ba a magana. Aka dinga sauke kayan jinjirai na sa wa da na wasa yadda kasan za a bude shago, don wasu kayanma sai sun girma sannan za su fara sanyasu. Yini guda tayi anan, kafin ta tafi da cewar ba zata dawo taron suna ba saboda washegari Abuja zata je.

Haka suka cigaba da yin jegonsu mai dadi suna karbar yan barka. Ranar suna aka yi hidima kwarai da gaske. Abinci dai a ranar an ciyar da masu azumi bila adadin, a masallatai da gidajen marayu. Kyautuka da sadaka iri-iri haka Habibu da Hajiya Ummah suka dinga yi.

Aka yi hidimar suna aka gama lafiya, aka tafi aka bar maijego da Abulkhairi da Khairiyya, -yadda suke kiran yaran- suna karbar jego mai suna jego a wajen Mami da Ummah. Ga Mama itama da take a gefe, hadin tukudi mai kyau ta bada Amarya ta yo mata, da tsumi jarka-jarka haka aka kai mata da sauran abubuwa.

Mami kuwa gyara take mata na ainihin Bare-bari din kamar wata sabuwar amarya. Don haka kafin zagayowar ranar arba'in dinsu, ita da yaran sun yi wani irin kubul-kubul dasu yadda kasan rainon yis. Duk inda ta baza a gidannan kamshi kawai yake tashi, jikin nan ya kara budewa ma shaa Allah komi ya zauna daram.

Shukurah dai ta lallaba a wannan dan zaman sun daidaita da Ubangidan, wai masu iya magana suka ce a rashin uwa akan yi uwar daki. Kuma in dama ta ki sai a koma hagu. Amma fa duk da haka, idan yaga gilmawar Nadiya a gidan nan sai ya dinga binta da kallo yana hadiyar yawu kamar wani tsohon maye. Don kuwa Nadiya din ce tayi wani irin canzawa ta ban mamaki.

51.

Gab da sallah sai ga Safiya ta je, hutun karshen semester suka samu. Don lokacin da aka yi haihuwar suna tsaka da jarabawa. Nadiya ta ji dadin zuwanta sosai da sosai, musamman da tun bayan auren nata babu wata maganar kirki data kara hadasu da ita. Ita dai bata taba neman Nadiya ba, ita kuma idan ta nemeta din bata samu. Sai ta hakura da neman nata.

A dan zaman da tayi da Nadiya sai take bata hakuri akan abinda ya faru kafin aurenta, ta fada mata cewa kunyar abinda tayi ne a lokacin ya hanata kiran Nadiya kwata-kwata, saboda bata san me zata ce mata ba. Ita kuwa Nadiya tace mata ita dama can bata taba riketa a cikin ranta ba, kuma in dai akan wannan zancen ne, to don Allah ta ma daina bata hakuri.

A wannan lokaci suka zauna suka yi hira irin ta yan'uwantaka a karo na farko a rayuwarsu. Nadiya ta fahimci ashe kallon da take yiwa Safiya a da ba haka bane, kwarai akwai sangarta da rashin sanin girman na gaba a tattare da ita wanda hakan ya biyo bayan rashin tsawatarwa ne daga Madam. Amma kuma tana da saukin kai da wayon zama da mutane. Don haka a dan wannan zaman da suka yi, Nadiya tayi kokarin nuna mata sakacin tarbiyantar da ita da Madam tayi, da kuma kokarin gyara mata a duk inda taga ta kuskure.

Da yake tace tana nan har a rantsar da Habib kafin ta wuce Maiduguri, sai kawai aka gyara mata daki anan wajen Nadiya ta zauna.

Zaman nata ya yiwa Nadiya dadi sosai, don kuwa duk da cewa ga Ummah da Mami suna tsaye a kanta babu gajiyawa, amma akwai wani abun da dole sai shakikinka zai yi maka shi ko kuma ya sani.

*****

Aka yi sallah lami-lafiya lau, sati ya zagayo aka yi bikin rantsar da su. Ranar da za ayi rantsuwar suka yi ankon wani dandatsetsen swiss lace ita da Shukurah din, daga Nadiya din har Babangida basu san da shi ba, don kawai ita Shukurah tace ya bata kudin kayan fitar ranar rantsuwa, ya dauka ya bata babu musu. Itama Nadiya sai ya dauki adadin abinda ya ba Shukurah ya bata, yace ta sayi abinda zata dinka din. Da ce mishi tayi ma ya bari, tunda ita dai kayan lefenta ma bata gama sanya ko rabi ba, ga na fitar suna ma bata sanya wasu ba. Tace mishi a ciki ma ba zata rasa na sanyawa ba, sai yace to ta rike kudin shi dai ya fita hakkinta.

To kuma sai ga kayan a dinkensu inji Shukurah, ta musu anko. Duk da cewa zaman nasu har zuwa lokacin kadaran-kadahan ne, in ka gansu ba zaka ce sunyi irin wannan kusancin na a zo a gani ba, amma kuma suna zaune lafiya. Sannan babu jan magana da jan fada, akwai kuma girmama juna cikin zaman nasu yanzu. Musamman bayan haihuwar Nadiya din, Shukurah tana kokarin leka Nadiya din a duk safiya bayan da Ummah ta hanata fitowa, a cewarta tayi zamanta a bangarenta ta huta. Abinci ma sai dai a dafa a kai mata ko kuma ita ta dafa. To Shukurah din kan shiga wajenta su gaisa, watarana ma har ta dauki yaran ta musu wasa ko ta tafi bangarenta ko na Hajiya Ummah da su. Aka ce wai mai da wawa, kusan da wannan zan iya cewa ta shawo kan Babangida din. Gashi a yanzu shi kanshi Ammar din ya sake da ita.

Haka suka yi shigar wannan leshi ruwan sararin samaniya da adon kananun fulawoyi masu kalar giwaiduwar kwai da kuma brown. Gyale da takalma kadai suka bambanta su, Nadiya ta sanya gyale brown, da takalmi da jaka ta LV suma brown ne. Shukurah kuma sai ta sanya ruwan Gwaiduwar kwan.

Suka tsaya a bayan maigidansu lokacin da ake rantsar dashi, su Khairiyya suna hannun su Mami da ke zaune a can kasan step suna kallo, aka yi handing over da komi, yan jarida da masu video suna aikin dauka.

Daga nan kai tsaye gidan Gwamnati aka wuce da su, inda suka hada yar kwarya-kwaryar liyafa ga abokansu na kusa da kuma yan'uwa da abokan arziki. Aka ci aka sha mai kyau, aka basu souvenirs din jakunkuna madaidaita masu dauke da hoton Habibu da mataimakinshi, da lemuka da snacks a ciki da memo da biro, kyauta daga Madam.

Duk suna zaune akan kujeru da aka zagaye wajen da su, tattausan kidan wakar 'Mad Over You' ta Runtown take tashi a wajen. Mami ta tashi ta wuce filin rawar a hankali ta fara takawa ita kadai, sai mutane suka fara dan murmushi da yar dariya ana kallonta. Zuwa can kuma sai Madam ta bi bayanta, ta fara manna mata sabin yan dari biyu a goshi suna dariya. A hankali wajen sai ya cike da yan rawa, aka fara liki da casu kamar ba gobe.

Shukurah itama dai ta mike daga baya ita da abokanta biyu, take tambayar Nadiya din ba zata shiga bane? Tace mata inaa, su je dai suyi tayi. Don haka ta tashi ta barta ita da Aramide da Anty Lima da itama taje wajen taron.

Suna ta hirarsu ta abokan da suka jima basu hadu ba, yan rawar suka fara dawowa suna zaunawa su ma. Sai ga shi an bar Safiya ita kadai a filin rawa.

Anty Lima tace, "kai, Allah Ya shirya mana Sofia, wai dama yarinyar nan har yanzu bata daina wannan shirmen ba?!"

Nadiya ta kalleta kasa-kasa, "kaji fa dan wuta yi da konanne, ke baki yin rawar ne a wajen biki? Naga dai daga ke har ita din za ni ce ta tarda muje mu?"

Ta kyalkyale da dariya kuwa, tace, "ke ki kyaleta tayi kinji? Lokacine. Mu ba gashi mun girma mun daina ba?"

Tace, "babu wani girma wallahi, shiriya dai!"

Suna wannan tattaunawar sai ga Fu'ad ya shiga filin rawar ya fara yi mata mannin yan dari biyar shi kuma. Nan fa kallo ya koma sama, don kuwa shima rawar ya biyeta suka fara anan. Nadiya sai baki kawai ta sake tana kallonsu kamar wasu mahaukata. Musamman da taga wai iyaye da yan uwa na musu shewa da tafi. Ta girgiza kai cike da takaicin wannan al'amari, a ranta take cewa ko yaushe Madam da Safiya din zasu gane Annabi ya faku?

Sai ga Safiya din tazo ta zauna dabas akan kujera tana goge zufa, ta dauki gorar ruwa mai sanyi ta kafa a baki ta shanye. Ana canza waka wai Fu'ad ya hau daga mata hannu taje, zata mike Nadiya ta zabga mata harara, tace, "na rantse da Allah kina komawa wajen rawar wannan sai na tadeki kin fadi akan wannan dan iskan 6 inches din takalmin naki!"

Ta kuwa koma ta zauna amma tana kyalkyala mata dariya, "wallahi ke dai Adda har yanzu baki gama wayewa ba sai an kwana biyu kila!"

Ta tabe baki, tace, "aikuwa in dai wannan dabi'ar kike kira wayewa to wallahi kina da sauran samun sanayya akan wayewar mutane. Ke yanzu ina wayewa ga diya mace, musulma, ta tashi ta dinga tika rawa a gaban iyayenta da yan'uwa da mazan da ba muharramanta ba, ana kallonta. Ina kika baro addininmu da al'adarmu Safiya? Ni dai kullum ina fada miki wallahi ki dinga kiyayar kanki, don kin iya rawa ba a hanaki ba, kiyi kayanki ke daya mana..."

Anty Lima ta katseta ta hanyar cewa, "... ko ta jira idan tayi aure ta dinga yiwa mijinta ba! Kinsan fa mazajenmu like that chic-thing. Twerking da...."

Nadiya ta katseta, "...to kara turata don Allah ni ina kokarin yi mata nasiha da fada."

Anty Lima ta daga hannu sama tana yar dariyar tsokana, ta tashi ta bar wajen ta koma wajen Mami bayan ta karbi Khairiyya dake hannun Hajiya Hadiza.

Nadiya ta maida kallonta ga Safiya, "ni dai ina kara miki fada da jan kunne Safiya, ki rage wadannan abubuwan. Don kina zaune a kasar waje kina ganin babu mafadi a gabanki, hakan bai baki damar dagewa ki dinga cin karenki babu babbaka ba. Kiji tsoron Allah wallahi. Wannan raye-rayen naki ni bana ganin fa'idarsu wallahi. Maza da dama kuma basu cika ganin mace mai wannan raye-rayen da mutunci ba sam!"

Tayi kasa da kanta jiki a sanyaye, "in shaa Allah Adda zan daina. Ai na Tiktok da Insta din ma duk na daina fa, na goge duk accounts dina wallahi."

Tayi dan murmushi "hakan yayi. Allah Yasa to Safiya. Allah kawo miji nagari mu sha biki!"

Ta tabe baki, "tab! Ai ni da aure ba yanzu ba tukun. Sai na gama karatuna na zama cikakkiyar likita, an bude min asibitina sannan."

Nadiya tayi dan murmushi kawai.

Bata san lokacin da Fu'ad ya fito daga filin rawar ba, sai juyawa tayi ta ganshi ya ja kujera a kusa da Safiya din ya zauna yana janta da hira. Ta bisu da kallo tana dan murmushin ganin yadda ya dauki gabadaya hankalinshi ya maida gareta. Duk wani motsi da zata yi to akan idanunshi suke, baya ko kifta ido haka yake kallonta tana mishi magana cikin jan aji da kwainane.

Ta kara murmusawa, a ranta take cewa, to bari mu ga yadda zata kaya dai!

Zuwa bayan isha'i an gama taro, sunyi sallama da mutane, aka tafi aka barsu su kadai da tarin ma'aikatan dake shake a gidan.

Ummah ta samo mata wata yar dattijuwa, Baba Adama, daga cikin danginsu dake nan zaune a Kaduna, wadda zata dinga tayata kulawa da yaranta har zuwa lokacin da zasu gagije.

Kowacce daga cikinsu tana da dakinta babba, falo mai dauke da bedrooms biyu kuma dukansu manya ne kuma well furnished. Duk da cewa dakunan daya yana kallon daya ne, sai daya ba Shukurah zabi ta fara zaba.

Shi na shi yana gefe da su kadan, kusa da dakunan yara.

Kasancewar bangaren baki a can waje yake kuma akwai doguwar tafiya kafin a karasa, sai kawai ta nunawa Baba Adama daya dakin dake bangarenta tace ta zauna. Ammar yana wajen Ummah. Suna hutun makaranta ne a lokacin, kuma tace tana so su je Maiduguri da shi a cikin satin. Don haka sai

idan ta dawo sannan za a mayar dashi wajensu. Duk da cewa dai Ummah na nuna take-taken ita zata rikeshi a hannunta.

Suna shiga daki wanka kawai suka yi, ta kwantar da su cikin crib dinsu bayan ta shiryasu. Itama ta fara nata shirin na kwanciya.

Washegari da safe wajen karfe goma ya bukaci ganinsu a falonshi. Ta riga tayi wankanta ta shirya, yaran ma ta shiryasu tsaf. Sai ta goya Abulkhairi, Khairiyya kuma ta rungumeta ta wuce falon nashi cikin shigar doguwar riga ta atamfar Holland mai ruwan ganye. Ta cake daurin dankwalin nan sassalkan gashinta ya fito wanda ta kame da band a keyarta. Daga ita har yaran kamshi kawai suke zubawa mai taushi.

Ta sameshi shi kadai a falon da takardu a gabanshi yana dubawa, ta duka ta gaidashi ya amsa mata a nutse yana binta da wani irin kallo kasa-kasa. Musamman data kwantar da Khairiyya a gefenshi ta kuma duka tana shirin sauke Abulkhairi. Sai ya saki ajiyar zuciya, ya ture takardun gefe yana shirin damkota, tayi sauri ta zille tayi gefe tana sakar mishi wata irin dariya a tausashe. Ya lumshe idanu yana jingina kanshi da kujera, "ni kike tsokana ko Baby? Zaki yi bayani ne duk ranar dana kamaki a hannuna!"

Tayi murmushi ta ajiye mishi Abul akan cinyarshi, kamshin turarenta na kara kai mishi karo.

Sallamar Shukurah ce ta sanya ta matsa daga gefenshi, ta koma kujerar kusa da shi ta zauna.

Ta kalleta tana dan murmushi, "Anty Shukurah Ina kwana?"

Ta zauna a kusa da ita, "lafiya lau Maman biyu, ya gajiya?"

Ta amsa mata da, "gajiya ta bi lafiya ai."

Ta matsa ta dauki Khairiyya kafin ta kalli Habibun itama tana gaidashi, "Honey barka da safiya!"

Ya amsa mata a hankali.

Hadasu yayi ya sake musu nasiha da wa'azi na sabuwar rayuwa da suka shiga, da kuma nuna musu girman irin nauyin da ya hau kansu, ya kuma hada da rokon yana fata zasu bashi hadin kai su tayashi ya sauke wannan nauyi. Duk suka amsa da 'in shaa Allahu'

Daga nan ya dawo kan yadda zamantakewarsu zata kasance. Zasu cigaba da yin kwanaki bi-biyu kamar da, ga masu aiki nan da masu girki a gidan, su samu lokaci su zauna da su saboda su sanar da su irin cimar da suke so a dinga yi. Bai hana yan aiki yin abinci ba, amma yana rokon alfarmar duk wadda yake a wajenta ta dinga yi mishi girkin dare da hannunta, zasu iya? Duk suka ce babu matsala in shaa Allah.

Ya gyada kai, "ok! Nadiya yaushe kike yin arba'in?"

Ta kalleshi bakinta na son yace ya taimaka ya bari tayi kwanaki sittin, amma tasan ba zai karbi maganar da hannu biyu ba musamman da yake ga Shukurah nan, sai ta langwabe kai gefe guda, tace, "nan da kwanaki uku masu zuwa."

Yace, "It's settled then, nan da kwanaki ukun idan kunyi canjin girki sai dokar ta fara. Akwai mai tambaya ko karin bayani?"

Suka yi shiru suna kallonshi.

Ganin haka sai ya gangara kan ainihin zancen daya sanya ya tattarasu, wato wa zata rike mukamin First Lady a cikinsu? Shi yana tunanin idan zasu iya, su yi running din ofishin su biyu. Tunda dai babu wata doka ta Constitution da tace dole sai mutum daya ko kuma ga wani na daban da zai iya rike kujerar. Amma me suke gani?

Nadiya ta gyara zama tace, "ni dai ina ganin kawai gwanda mutum daya yayi wannan din, saboda gudun samun matsala da abinda ya danganci haka. Bugu da kari kuma gaskiya ni bana ma ra'ayin hakan gaskiya. For the time

being ina so in samu lokacin kula da yarana da kuma tunanin abinda zan yi da rayuwata."

So take yi in da hali, ta samu ta cigaba da Masters dinta ko da ta online ne. Bata gama yanke shawarar abinda zata yi ba har yanzu saboda so take yi sai ta fara mishi maganar taji yanda ya karbi zancen sannan.

Shukurah kuma cewa tayi, "ni dinma zan so ace mun rike din tare gaskiya. Amma duk abinda kuka yanke, bani da matsala ni."

Yayi shiru yana tunani kafin ya nisa, yace, "to shikenan. Shukurah zata kula da abinda ya shafi ofishin First Lady, amma title din First Lady ku dukanku zaku amsa regardless of ga wadda take rike da ofis da sauransu. Kema Nadiya akwai kungiyoyi da dama da suke yi min zancen suna so su gayyaceki tun bayan wannan shirin da kuka gabatar kwanaki. Don haka zamu zauna mu fitar da wani program kawai, ta yadda koda sau daya ne a wata za a gabatar da wani shiri na daban domin wayarwa da mata kai akan abubuwa mabanbanta, in yaso ke sai ki dinga jagorantar shirin. Ina tunanin hakan ma ai wani aikin ne na daban ko?"

Ta gyada kai cikin yin na'am da hakan. Da haka dai suka kare zaman bayan ya hadasu da Aides dinsu, suka gabatar musu da ma'aikatan gidan da duk abubuwan da suke yi.

Har tour dinsu aka yi a cikin gidan, haka kuma an hadasu da wasu matan guda biyu wadanda zasu dinga taimaka musu game da harkokin gidan Gwamnati da siyasa for the time being, kafin kansu ya gama wayewa.

*

Kwanaki uku kenan, ta gama shirinta cikin kayan barci marassa nauyi, saman rigar net ne yayinda kasanta kuma silk ne, sai dan wandonta na 3-quarter shima silk.

Tayi addu'a ta tofe jikinta da na yaran, ta gyara gado ta kwanta abinta.

Barci ya sureta mai dadi sosai, sai jinta tayi cikin jikin mutum. Ta juya a hankali tana fuskantarshi ta cikin hasken bedside lamp guda daya data bari a kunne mai taushin haske saboda yaran.

Ta kai hannunta ta kamo nashi dake yawo a jikinta, ta dan turo baki cikin yanayin alamun ban tausayi, "kai Abban Ammar, abin ma ai da tausayi!"

Bai dakata da abinda yake yi ba, sai ma kara zafafa sumbata iri-iri da yake manna mata a duk inda bakinshi ya kai a jikinta.

Yace, "ni ai dama na dade da sanin ba ki tausaya min Nadiya ko kadan. Shikenan daga kinyi 'ya'ya sai ki manta da ni, kika shareni kwata-kwata, kika wancakalar da lamurana. Yanzu kuma kina fada min wai da tausayi? Tausayin me zan ji, bayan ma nine abin tausayin?"

Ta dan janye jikinta daga nashi tana kallonshi, "ni dai don Allah kayi hakuri ka bari mu kara kwana biyu tukun. Ka ga fa su Abul basu gama yin kwari ba."

Ya kama baki yana kallonta cikin mamaki, "lallai ma, kin kuwa ma san abinda bakinki yake furtawa? Ina ganinki ko sati uku baki cika da haihuwa ba kika fara sallah. Nayi hakurin, na kara hakurin akan wanda nayi, yanzu kuma kike wai bani wani labari na daban?!"

Ya rarumota ya hade da jikinshi, "na rantse da Allah na gama hakurin, yau dai, da yardar Allah sai mun samo wasu yan biyun!"

Da yake itama maganar tata bata gama kaiwa zuci ba, don kuwa itama tayi kewar mijinta. Jan baki ne kawai da tsokana, sai ta biye mishi. Suka raya wannan dare cikin tsananin kauna da soyayya mai sanyaya rai. Yayi sa'a har ya gama cin angon nashi yaran basu motsa ba.

52.

His Excellency (Dr.) Alhaji Habib Abdullahi Makama. Magidanci dan kimanin shekaru arba'in da takwas. Yana daya daga cikin Gwamnoni wadanda suke da karancin shekaru akan karagar mulki a wannan lokacin.

Ya fara aikinshi da gasken-gaske ba da wasa ba, Yayi sa'a kuma ya dauki amintattun mutane a matsayin wadanda zasu tayashi rikon mulkin, don haka komi yana tafiya cikin dadin rai. Dan abinda ba a rasa ba bai wuce sukar makiya da yan adawarsu da suke binsu suna bata musu suna da kokarin nunawa Talakawa da mutane babu aikin da suke yi. To da yake dai idanu ko da ba mudu ba amma sun san kima, talakawan suna ji kuma suna gani a aikace irin aikin da Gwamnatin tashi take musu babu dare babu rana, sai sukar tasu take faduwa a banza.

Cikin watanni takwas kacal da yayi da karbar aiki, an ga canji irin wanda aka jima ba a gani ba a cikin garin Kaduna da Kauyuka.

Ya tsayawa makarantu na Gwamnati da asibitoci da kuma ma'aikatanshi, babu jinkirin yin albashi, asibitocin Gwamnati an cikasu da magunguna na kyauta. Kuma duk wanda aka kama da kokarin satar kayan Gwamnati babu bata lokaci ake cireshi daga kan mukaminshi. Wannan ya matukar sayo mishi mutunci da kima a wajen mutane kwarai da gaske.

Haka suma matan nashi suna matukar kokarinsu wajen ganin sun sauke nasu hakkin dake kansu.

Duk da cewa Nadiya bata fita ko'ina, tana gida tana kula da yaranta. Hakan bai hanata tashi tsaye wajen ganin cewa tayi nata kokarin ba. Ta dukufa wajen ganin cewa ta inganta rayuwar kauyuka.

Ita da Shukurah su kan zauna su zabi kananun kauyuka, a duba matsalar da tafi addabarsu, abin amfanin gona ne? Ko kuwa matsalar ruwa ce? Ko kuma matsalar rashin kyawun hanya ne? Sai ayi compiling din binciken, a turashi

ofishin Mai Girma Gwamna daga ofishin First Lady. Inda shi kuma zai dora alhakin bincike da kwangilar yin aikin a hannun Kwamishinoninshi domin a gabatar da aikin. Haka kuma baya yin kasa a gwiwa, ya kan tashi wani kai tsaye domin yaje yaga aikin da aka yi. Idan kuma damar hakan ta samu sai ya taka yaje da kanshi.

An gina rijiyoyi bila adadin a kauyuka da dama ta dalilin haka. An gina masallatai da makarantu na Arabi da boko a Kauyukan da suke da karancin wadannan, haka kuma an samarwa manoma da dama taki da iri na noma sosai. Ciki da wajen Kaduna idan ka zagaya zaka ji kalamai na yabo da sanya albarka ta wannan Gwamnati daga mutane tana tashi kawai.

Yaranta suna ta girma da wayo tubarkallah. Idan ka gansu baka taba cewa wai watanninsu tara yanzu. Rarrafe suke yi zuwa ko'ina, don Abul da yake ya fi Khairiyya kazar-kazar da rashin gwabin jiki har ya fara tsayuwa yana kokarin takawa.

Baba Adama ta tafi gida tun bayan da suka cika watanni hudu. Ita da Maigidan nata suka yi mata sha-tara ta arziki lokacin da zata tafi.

Ummah kuwa da gaske dai ta kwace musu Ammar. Ta hanasu rikonshi kiri-kiri, tace tunda ga yan biyu nan a gabansu, kuma da wasu masu zuwa nan gaba ma da Allah kadai Yasan iyakarsu sai su bar mata shi a wajenta tunda ita babu kowa a gabanta, ta samu mai tayata debe kewa.

A halin yanzu Ammar din yana wajen su Nadiya din, Ummah din ta tafi Umarah tun watan daya wuce.

Gida ake gina mata mai suna gida a can Shagari Low cost. Tace dama can ai estate din Makama mallakin Habib ce, don haka ita zata koma nata mallakin itama.

Yace mata, "Ummah ko dai munyi miki wani laifi ne? Barin estate dinnan kai tsaye sai kace ana korarki? Naga dai zamanmu lafiya lau ko? Idan kuma ginin cikin estate dinne bai miki ba to ki fadi irin wanda kike so sai a rushe

wancan a gina miki shi din. Amma don Allah kiyi hakuri kada kiyi nisa da mu. Gidan wallahi fadi zai min sosai idan baki nan!"

Tayi dan murmushi mai kayatarwa, a babban falonshi suke da yake shakatawa tare da Iyalinshi a cikin gidan Gwamnatin.

Ranar wata Asabar ce taje gidan da hantsi domin tayi musu sallama saboda washegari jirginta zai daga kasar Jordan. Taje ta gano Mami wadda ta samu minor accident a hanyarta ta zuwa aiki ta samu gocewar kashi a hannu, daga can ne kuma zata wuce Saudiya yin Umarah. Bata fadi ranar dawowa ba saboda tace sai sun ganta kawai.

Tace mishi, "laifin me kuma Babangida? Kada ma ka sanyawa ranta wannan abin, don kuwa ba haka bane. Kawai dai naga lokaci yayi daya kamata in barku hakanan, in koma cikin 'yan uwa nima. Ka Girma yanzu, ka zama abinda mu da kai muka jima muna fata. Bayan hakkin iyalanka dake kanka, ga na Jihar Kaduna gabadayanta, ba zan kara maka wani nauyin ba. Ka cigaba da jagorantar da rayuwarka data iyalanka da Jaharka yadda kake yi, in shaa Allah Allah zai dafa maka!"

Yadda kasan wani karamin yaro haka ya koma a lokacin, yana tuno yadda tun tashinshi bai taba rabuwa da Ummah ba sai ta sanadin lalura. Son samu daga shi har ita su zamana a waje guda kamar yadda ya tashi a gabanta, ace koda mutuwa ce tazo ta dauki dayansu a gaban dayan.

Yadda duk damuwa da rashin jindadi suka bayyana akan fuskarshi sai abin ya bata dariya, ta sake murmusawa tace, "in banda abinka Babangidana, dukanmu muna cikin garin Kaduna ai ba wahalar ganin juna zamu samu ba. Yanzu ma ai ba waje daya muke zaune ba, gashi kuma dukanmu muna zaune lafiya lau? Me ya canza?"

Yace, "wannan ai daban yake Ummah, nasan dai komi daren dadewa zamu dawo mu sameki a inda kike. Tashin naki ne bana jin zan iya dauka ko kadan Ummah, don Allah ki sake shawara!"

Tayi murmushi kawai, daga karshe dai yasan cewa ta gama yanke shawararta, babu zancen canzawa.

Haka Iyalan nashi suka shigo suka sameshi zaune jugum-jugum a gaban Ummah din, jikinshi duk yayi sanyi. Jin labarin tashin Ummah daga Estate din su ma kansu bai yi musu dadi ba. Haka suka dukufa a gabanta suna rokon tayi hakuri, ta daure su karasa zamansu kamar yadda suka faro. Amma ta riga ta gama yanke shawararta, don zancen da take yi musu ma tuni filin data saya an fara foundation din gini. Tana sa ran lokacin da zata dawo daga Saudiyyah an kammala ginin sai dai ta tare kawai.

Ganin ta dage dole suka yi hakuri, suka yi fatan Allah Yasa hakan ya zame musu alkhairi gabaki dayansu.

Ta karasa yinin ranar anan gidan cikin jikokinta suna ta wasansu da kaiwa da kawowa a gabanta, ranta fal da farinciki da jindadi. Sai da yammaci sannan direba yaje ya dauketa domin taje tayi sallama da sauran yan uwa da dangi.

Kwana biyu ayyukanshi kanshi sai da suka dan yi sanyi saboda har lokacin ya ki hakurarwa kanshi da zancen barinsu da Ummah zata yi. Sai da Nadiya ta dage da bashi baki da nuna mishi yayi hakuri ya marawa hukuncin Ummah baya, ya kuma cigaba da addu'ar Allah Yasa hakan shine mafi alkhairi a garesu, sannan ya iya samu ya hakura din.

Ko sati biyu Ummah din bata yi da tafiya ba, Shukurah ta dawo gida daga ofis dinta da yammacin ranar Talata. Maigidan nasu yayi tafiya zuwa garin Kano domin amsa gayyata ta musamman da Maigirma Sarkin Kano, Alhaji Ibrahim Auwal yayi mishi domin bashi lambar yabo da girmamawa akan kwazo daya nuna na dawowa da ma'aikatan Makarantar Gwamnati fiye da dubu biyu da aka cinye musu albashi na tsayin wata bakwai, tare kuma da gurfanar da wadanda suke da wannan alhaki a gaban Alkali. Wannan jajircewa da yayi da nuna gwaninta da kwazo yasa Mai Girma Sarkin Kano din ya gayyaceshi fadarshi domin jinjina mishi da bashi lambar yabo da girmamawa.

Tana zaune a babban falonsu inda suke karbar baki. Tare take da wakiliya ta musamman da Matar Shugaban Kasa, wato Hajiya Badariyya Kamal ta aika mata. Sun samu damar hayewa kan karagar mulki su ma.

So take yi Nadiya ta amsa tayin gayyatarta, tana so ta nadata shugabar gidauniyar tallafawa mata da yara ta Nigeria baki daya.

Akwai manyan mutane da dama da suke harin kujerar, wadanda suke da matakin ilimi wanda ya fi na Nadiya din nesa ba kusa ba. Sai dai basu da zarra da tsayawa tsayin daka akan abu kamar na Nadiya din.

Hajiya Badariyya tana sane da cewa duk wani taimako da zai fita daga ofishin First Lady din, Nadiya ce a bayanshi. Don kuwa ita ce take ba Shukurah shawarar ga abinda yakamata ayi, ita take binciko da zakulo mutanen da suke taimakawa. A takaice dai Shukurah ce ke da alkalamin zartar da hukunci, amma Nadiya ita ce bango kuma mai shan wahalar aikin.

Tace me zai hana ta fito domin a taka rawar da ita? Kuma tayi aikin a inda ya dace, mutane zasu sani kuma su gode mata?

Abinda tace mata a lokacin shine a isar mata da sakon godiyar wannan karramawa da aka mata, kuma a sanar da Her Excellency, tayi hakuri ta bata lokaci tayi shawara da Maigidanta wanda yayi tafiya a halin yanzu. Da zarar ya dawo sun tattauna, zasu sanar da su shawarar da suka yanke. Suna cikin yin sallama ne Shukurah din ta dawo.

Ta tsaya suka gaisa da bakuwar, Nadiya kuma ta rakata zuwa bakin kofa inda security dake tsaye ya bude mata kofar, suka sake yin sallama.

Ta koma falon ta sameta tana ciro takardu daga jakarta, ta zauna a gefenta tana daukar Abul da daya daga cikin ma'aikatan gidan dake kula da yaran ta kai mata.

Shukurah ta mika mata wata takarda, tace, "wannan dazu aka turota ofishinmu. Sai dai ina tunanin kina bukatar ki gani ko menene ta kunsa."

Ta karbi takardar tana dubawa cikin daurewar kai. Mamaki yasa ta hangame baki tana kara duban takardar.

Request ne Madam ta aika da kanta ba sako ba, wani wawakeken waje ne da yake fuskantar Arena dinta take so ta saya. Taje ofishin sayar da filaye an ce mata waje na Gwamnati ne, ita kuma filin take so sosai domin ta hadeshi da nata ta kara fadada wajen. Duk da cewa ta fada musu ko ita wacece da kuma matsayinta a wajen Mai Girma Gwamna, amma sun kekashe kasa sun ce basu san wannan zance ba. Idan ba sanya hannun Gwamna suka gani ba ba fa zasu bata damar sayen fili ba.

Shine ta tura wannan request wajen Shukurah. Dama tun farkon cin zaben sai data yiwa Nadiya maganar wannan fili tace tana so ya zamana aikinta na farko da zata yi idan ta shiga ofis, to ta mallaka mata wannan filin. Bayan da suka yanke shawarar Shukurah ce zata shiga ofis ba karamin fada da bacin rai Madam ta haddasawa Nadiya ba.

Kiranta tayi musamman ta zazzageta fiye da kima, akan me zata ce ba zata karbi matsayin First Lady ba? Kuma akan wane dalili zata ki shiga ofis?

"...kenan kina nufin duk wahalar da na sha zata tashi ta tafi ne a banza ko? Duk irin kudaden dana kashe don ki kai matsayin da nake son ki kai a banza kike so su tafi kenan? To wallahi kinji na rantse miki, kinyi kadan Nadiya! Kada ma ki kuskura ki bari wata rana tazo in nemi wani abu daga Gwamnatin Kaduna in samu wani tsaiko, na rantse da Allah sai kin ga irin bacin rai wanda baki taba ganin irinshi ba a duniyar nan. Sakaryar yarinya kawai, banda tsabar bakin ciki da son kai ma irin naki, ana kokarin a rufa miki asiri amma ke baki sani ba ko? Tunda kin ga yanzu ke kin zama matar Gwamna wato ni zaki ajiyeni a gefe kenan, ga yar iska ko?!..."

Ire-iren fadan nata kenan data dinga yi, ya zamana tun Nadiya din tana kokarin bata hakuri don su rabu lafiya, har ta tsaya kawai tana sauraron fadan nata har ta gama ta kashe wayar tana jan tsaki kala-kala. Ta dafe kai tana girgiza kanta hawaye na mata ambaliya a fuska. Zagin da Madam din ta mata don taba rai ya taba ranta, amma gorin data dinga mata ne yafi dagula mata lissafi.

Ya zata ce wai don ta shiga cikin daula shine take so tayi mata tawaye? Bayan dama can ba ita ta daga baki tace tana so ba? Hasalima tun farko ba kushewa ta dinga yi ba saboda gudun faruwar irin hakan? Tana kuma sane ta ki karbar shiga ofis din, ta koma ta bayan fage tana taimakawa masu bukata.

Saboda har da tsoron irin abin da Madam zata iya daukowa ne ta dora mata. To gashi tun ba aje ko'ina ba ma kuwa ta dauko musu gingimemen aikin da yafi dala girma, babu kuma gammon dorawa.

Ita yanzu me ya kamata tayi? Damka wannan fili a hannun Madam daidai yake da daukarwa kansu wani jan aiki ba karami ba, dama tuni har abokan gaba sun fara cece-ku-kuce akan shi. Tun a tsohuwar Gwamnati ake rigimar abinda yakamata ayi dashi saboda manyan mutane da dama suna kai mishi hari, wasu na so su yi hotel wasu na so su gina wani wajen shakatawar, Gwamnatin ta sanya hannu da cewa zata gina asibitin yara masu lalurar shan Inna da kuma mata masu lalurar yoyon fitsari ne. Wannan abu bai yiwa mutane da dama dadi ba.

To kuma har Gwamnatin ta sauka basu kai ga fara yin aikin ba, duk da cewa an fitar da budget din komi da komi. Kuma cikin yarjejeniyar da suka yi da tsohon Gwamna din kafin ya marawa Habibu baya a matsayin magaji, har da alkawarin zai dora daga inda Gwamnan ya tsaya ne. Kuma yanzu kawai sai su zo su damkawa Madam shi saboda tana takamar ta taya shi kamfen? Ita bata yin abu don Allah ne? Kuma duk alfarmar da itama aka yi mata a baya bata isheta ba sai ta dora da neman wani abu dai?

Ta duba dai ta ko'ina taga babu ta yadda ma za ayi su aikata wannan danyen aiki. Don haka ta daga kai ta kalli Shukurah, tace mata ta manta da maganar kawai. Koda ma an sake turawa da maganar tace Maigirma Gwamna ya hana.

Itama Shukurah din sanin rashin yiwuwar hakan yasa bata ja maganar da tsayi ba, ta tashi ta wuce dakinta a ranta tana cewa 'sun fi kusa!'

Yanzu kam ta daina tsanar Nadiya, duk da cewa dai har lokacin basu gama sakin jiki da juna ba can-can, amma taimakon da Nadiya take mata wajen zakulo ayyukan alkhairi suna yiwa mutane da sunan ita Shukurah din da ofishinta ne suke hakan, ya matukar sayo mata mutunci da daraja a idonta sosai. Tunda itama yanzu mutane sun santa sosai, ana ta yaba mata da sanya alkhairi. Don haka take kara lallaba Nadiya din tana binta a hankali.

53.

Nadiya ta tattare takardu ta kaisu can cikin kaya ta musu boyo na musamman.

Har Maigidan ya dawo daga tafiyarshi bata sanar dashi halin da ake ciki ba.

Ta sanya dai amintacciyar security dinta, Hannatu Bishir, ta fara duba mata possible wajaje a kusa da inda Madam din take wanda za a iya saya a madadin waccan din.

Madam da bata san abinda yake faruwa ba kuwa tana can tana ta kara hawa da kumbura cikin bacin rai.

Ta sake kiran Nadiya a karo na biyu ta mata tatas, tace mata wallahi idan bata yi wasa ba akan wannan maganar sai ta yafewa duniya ita tunda ita ta zaba akan ta. Banda tsabar butulci da cin mutunci irin nata, har ita zata yiwa haka? Ta hana a bata fili? Ita Madam?!

Nadiya tayi mata bayani iyaka bakin kokarinta, amma Madam din ta ki ta saurareta balle ta fahimta. Da ta fada mata cewa ta sanya a duba mata wani filin, sai ta katseta ta hanyar cewa, "idan ba wanda nake so zaku bani ba, ku rike abinku bana so! Nadiya ni ai na fi karfin in nemi alfarma a wajenki wallahi, sai dai in baki umarni. Tunda kuma kin rainani, kije zaki gani. In dai nice, zaki zo har inda nake ki sameni!"

Ta katse wayar da wannan kalamai nata masu razana kwalwa.

Ita kanta Nadiya sai data dimauce da jin hakan, tayi ta kiran Madam din hankali a tashe amma ta ki dagawa.

Ta rasa yadda zata yi da ranta, kuka ta zauna tana yi wiwi, Madam tana nema ta mata baki akan abinda bai taka-kara-ya-karya ba.

Tana so ta yiwa Habib magana amma tana jin kunyar da irin idanun da zai kalli Madam, saboda shi mutum ne strict akan duk wani abu daya taba mulkinshi, baya cutar da talakawa kamar yadda baya saba alkawari. Tana da tabbacin akan Madam ba zai canza ra'ayi ba. Yadda kuma yake ganinta da mutunci da girmamawa, bai kamata ta zubar mata dasu ba wajenshi. Don haka tayi ta jinjina abin a cikin ranta ita kadai kwana da kwanaki.

Kusan kwana biyar da yin zancen kenan, ta tashi da safe wata bakuwar lamba tana danna mata kira a wayarta. Tana da wata wayar ta musamman don amsa kiran daya danganci wani lamari na siyasarsu, amma wannan ta wareta ne musamman saboda yan uwa, kuma su kadai suke kira.

Tayi kamar ba zata daga ba, sai kuma ta daga tana cewa watakila emergency ne. Tayi sallama tare da daga kiran, sai ta jiyo muryar Madam kasa-kasa tana amsawa kamar wata barauniya, ta gyara zama tana gaidata cikin taraddadin yau kuma da me taje mata?

"Mommy, ina kwana, kun tashi lafiya?"

Madam tayi wata irin doguwar atishawa yadda kasan wani dan tsako ne zai fita daga hancin nata, ta ja hanci alamun mura take yi, tace mata, "Nadiya, ki taimakeni ki rufa min asiri, ki zo ki ceceni don Allah!"

Nadiya ta tashi tsaye a sukwane, hannu dafe da kirji tana tambayarta, "Subhanallahi, Mommy lafiya?"

Don kuwa daga yadda taji muryar Madam din ta tabbata akwai matsala. Matar da duka-duka kwanaki biyar kenan data gama ihu da bugun kirjin babu wanda ya isa ta nemi taimako a wajenshi, ita ce take kuka da neman taimakon kuma? Ai da babbar magana ba ma karama ba!

Madam sai ta fashe da kuka, tace, "kin ganni nan kwanana biyar a cell yau Nadiya, azaba kawai ake gana min ban ma san me na aikata ba wallahi. Don Allah ku zo ku ceceni. Sun hanani kiran kowa balle a san halin da nake ciki, kuma sun ki fada min laifin nawa. Yanzu ma wata constable ce na samu ta bani aron wayarta da kyar da magiya..."

Nadiya ta fara rarumar gyale cikin dimaucewa, Madam a cell kuma? Wannan tashin hankali da me yayi kama?!

Tace mata, "kina ina ne? Kin san inda aka kaiki?"

Tace, "muna Lagos. Ina gama waya dake ranar nan dama ina kan hanyar airport ne zan je Lagos, ina dira suka kamani a filin jirgin, amma ban san ina suka kaini ba. Sun amshe kayana da komi nawa a can, kuma sun hana ni magana da kowa!"

Kafin Nadiya ta sake yi mata wata tambayar, taji wani yana magana cikin hargowa. Kafin kuma taji kit! An kashe wayar.

Fadar irin tashin hankalin data shiga ma ba karami bane ba a wannan rana.

Duk wanda ya kamata ta kira, ta kira, amma babu labarin Madam babu alamarta.

Sai da aka kwana biyu, shima da taimakon wani mai bincike na musamman da Babangida ya ba aikin, sannan suka samo labarin inda take.

Washegari Nadiya din da Anty Hauwa da taje Kaduna din jiya, suka dauki hanyar Lagos. Tare da Lauya da securities biyu da Gwamna ya hadasu da su.

Tafiya suka yi cikin badda kama, saboda sun san idan yan adawa suka samu labarin halin da suke ciki ko kuma yan jarida, ba karamin matsala za iya samu ba.

A Area C Command Police Station aka riketa, wanda yake a Herbert Macaulay Way, dake a Sabo, Yaba anan Lagos din.

Suna zuwa suka samu ganin DPO da taimakon Lauyan da suka je dashi.

Bayan sun zauna a gabanshi, suka sanar da shi abinda ya kaisu da kuma tambayar me yasa aka kamata ba tare da takardar data bada umarnin a kamata din ba da kuma laifukan da ake tuhumarta dasu? (wato warrant?)

Ya gyara zama yace musu su kansu dokar daga sama taje musu, directly daga ofishin Brigadier General Abdussalam Oluwalu (CON) ta je. Suna zarginta ne da safarar miyagun kwayoyi. Duk da ba a kamata da kayan ba kai tsaye, amma an kama mutane da dama wadanda suke distributing kwayoyin anan cikin Lagos da Kaduna, wadanda duk suka bada tabbacin kayan daga hannunta suka fita. Sannan an samu waje na musamman a cikin Arena dinta ta Kaduna, inda suka samu stock-stock na kwayoyi, wadanda zasu yi kimanin miliyoyin kudi.

Nadiya ta dafe kanta daya fara wata irin sarawa tana jin kamar zai balle. Tashin hankali wanda ba a sa maka rana! Neman kudin Madam din kuma yanzu har ya fara kaucewa ka'ida?

Suka bukaci son ganin Madam din amma yace ina, a dokar da aka basu na su ci gaba da riketa ne kawai har zuwa lokacin da za a shiga kotu da ita. Daga nan kuma sai dai zancen yanke hukunci. Suka kada, suka raya, yace ai kaf cikin ofishin nan babu wanda ya isa yayi jayayya da ofishin Brigadier Janar.

Hankalinsu duk ya tashi ya dugunzuma, lallai fa gaba da gabanta, wai aljani ya taka wuta.

Anty Hauwa ta fita tana kiraye-kirayen waya don a samu wanda zai iya yi musu wannan taimakon. Itama sai ta lalubo Habib ta sanar da shi.

Ba su samu ganin Madam ba sai can da yamma tare da taimakon Habibun wanda ya san wani dake tare da Brigadier din, aka yi musu izinin ganawa da ita.

Yadda suka ganta abin tausayi kamar su zubar mata da hawaye. An kulleta a wani dan akurkin daki mai dan banzan duhu da sauro, ga doyi. Bugunta kawai ake yi kamar jaka, babu dare babu rana.

Tayi wani irin baki na ban mamaki, fuska duk sai tarin kuraje. Kayan jikinta sunyi raga-raga, daga ganinta fatar jikinta bata ga ruwa ba tun lokacin da aka kai ta wajen.

Tana ganinsu ta rushe da kuka, su kansu matsar hawayen suke yi cike da tausayinta daya cika musu rai.

Wadda ta rakata wajen nasu ta cire mata ankwar da aka sanya mata, ta dangwarar da ita a wajen, ta juya ta tafi tana kara nanata musu mintuna sha biyar kadai aka bata.

Suna zama akan kujera Anty Hauwa ta matsa tana tambayarta, "Zahra'u, me ya hadoki da Brigadier ne haka har zai sanya a daureki? Me ya kaiki?"

Ta kai hannu ta share hawayen fuskarta. Tace, "wallahi bani da gami da shi ko kadan, amma akwai matarshi da muke huldar kasuwanci da ita. Tana son shiga cikin kasuwancina ne ni kuma na hanata, nace itama taje tayi nata. Shine ta bi min ta karkashin kasa, ta sanya aka kamani akan laifin da ban san na aikata ba!"

Nadiya ta gyara zama da kyau tana kallonta, don taga alamun kamar ma bata san me suke zarginta da shi ba, tace, "to ina zancen miyagun kwayoyi kuma da ake yi? Akan hakane fa aka kamaki."

Ta dafe baki, "kwayoyi kuma? Ni?!"

Tace, "baki san zancen ba? Saboda sun ce an kama wasu zasu yi safarar kwayoyin nade cikin lemukan energy drinks daga Kaduna zuwa nan Lagos din don har sun samu sun shigo da shi ma. Kuma da aka tambayesu suka ce daga Arena dinki suka daukosu, sannan anyi bincike a wajen an samu kwayoyi da dama wadanda za su iya cin miliyoyin kudi!"

Madam ta dora hannu aka ta saki wani irin ihun kuka kamar wadda zata hau bori. Sai kuma ta hau zage-zage kamar wadda ta fita daga hayyacinta. "Ni za su yiwa haka? Ni za a ciwa mutunci a min zamba cikin aminci? To wallahi-

Tallahi ba zan yarda ba, duk wanda yake shirin wulakantani wallahi sai na ga bayanshi!"

Anty Hauwa da Nadiya suka kalleta cikin alamun tambaya, Anty tace, "su wa kenan? Me kike fada ne? Don kuwa dolene sai kin fada mana abinda yake faruwa mun fahimta, sannan ne za mu iya taimakonki Zahra'u."

Ta share hanci tana jan majina, kafin ta fara zuba musu bayanin yadda Mijinta Alhaji Shehu Balogun, ya yaudareta ta hanyar hada hannu da ita wajen bude Arena dinta lokacin da take neman masu sanya hannun jari, shi kuma yayi amfani da hakan wajen yin yarjejeniya da ita kan cewa zai dinga sana'ar sabon lemun energy drinks daya fara yi a wajen, amma kuma sai da yayi mata alkawarin cewa ba zai dinga gudanar da cinikayyar kwayoyi da yake yi ba a can, ya kuma ce ya yarda. Ashe yaudararta yake yi, zuwa lokacin data fahimci cewa yana sayar da kwayoyine kawai da sunan energy drinks, kuma a cikin arena din nata yake yin hakan ba a ko'ina ba, harkar tasu ta riga tayi nisa.

Da tayi confronting dinshi sai yace mata ai ba wai jimawa zai yi ba, kawai zai dinga sayarwa dinne na dan lokaci kafin ya samu zaunannen waje. Amma har aka dauki lokaci mai tsayi ba ya da niyar fasawa, hasalima sai kara yawan kayan suke yi. Ita kuma da taji tsoron kada ta kai maganar wajen yan sanda, yan sandanmu na Najeriya da basa tsoron Allah, tunda da yawansu ma manyan yan sandan duk abokan cinikayyarshi ne, sai ta tuntubi aminiyarta wato Hajiya Zainab Oluwatolu, matar Brigadier General Oluwatolu, kuma distant cousin din Alhaji Shehu din ce wadda dama can ta sanadinta ne suka hadu da shi. Sannan kuma yana dan jin maganarta.

Akan ta taimaka mata, ta bata shawarar yadda za ayi su rabu da shi Shehu Balogun din salin-alin ba tare da hukuma ta shiga zancen ba. Saboda in hukuma ta shiga sunanta zai baci, kuma zasu iya cin ta tarar kudade da yawa.

Ita kuma budar bakinta sai ce mata tayi, me zai hana ta mata hanyar da itama zata shiga cikin wannan sana'a?

Tace mata, "ke baki da wayo ne? Baki san babu abinda ke kawo kudade manya-manya a wannan zamani wanda ya kai wannan harkar ba? To ni idan ba zaki shiga ayi da ke ba, ki hadani da su ni ina so in shiga. Na miki alkawarin babu abinda zai samu wajen sana'arki, not even the President will dare to touch you. Saboda Ubangidanshi na yanzu wanda ya tsaya mishi, Kawu na ne!"

Madam da jin haka sai jikinta ya fara rawa, ita tana neman mafitar da zata fissheta ashe shuka ce tayi a idon makwarwa! Ta fara lallashinta tana kokarin ta samu su rabu lafiya, amma matar nan fir ta ki.

Ransu ya hadu ya baci a lokacin, sai ga shi sun fara sa-in-sa da musayar kalamai ta cikin wayar har da gore-gore. Hajiya Zainab tayi rantsuwa ta maya kan cewa idan har ba zata mata hanyar nan ba, ita kuma tayi alkawarin sai ta fallasata.

Ta fusata ta kwaso wani mahaukacin zagi ta laulaya mata, tace, tayi duk abinda zata yi. Tunda dai bata ga laifin da ta aikata ba ai babu dan iskan daya isa yace zai kamata. Wannan waya haka suka rabu dai baran-baram.

Washagarine ta sake kiran Hajiya Zainab da niyar su yi sulhu, don kuwa ita ce kadai take ganin tsayayya ta fanninta da idan ta samu matsala da ita to tana ruwa.

Sai tace mata taje Lagos ta sameta kawai su tattauna a nutse saboda maganar ta fi karfin ayi ta waya. Bata san da abinda ta shuka mata ba ta amince mata a take, ta shirya ta tafi. A shirinta idan sun gama shiryawa da ita, ta sa Balogun ya rabu da harkarta, to zata yi kamun kafa da ita, ko da cin hancine ta bada don a bata wannan fili data sanyawa ido. Ita kuma Nadiya zata ci kaniyarta ne. Idan ma ta bata haushi to wallahi zata iya yin abinda tayi aka tuge Habibun a kan mulki ko kuma ta hanashi yin ta-zarce. Da wannan niyar ta hau jirgin Lagos ta tafi.

Ashe ita Hajiya Zainab ta gama shaka da abinda Madam din ta mata. Dama abotace suke yi ta cudeni in cudeka, babu Allah babu kauna ta fisabilillahi a cikinta. Kuma dama dai ita Zainab din ta jima tana bakin ciki da hassadar halin fantamawa da Madam din ke ciki. Saboda Madam ta kasance mai

matukar tutiya da tinkaho, duk wani hali da take ciki na nasara to kawayenta sai sun ji, ta dinga fadi musu kenan tana nanatawa, ga shi kuma matakan nasara tana ta hawansu, kasuwancinta yana buduwa a kullum, bata kuma kunya ko shayin goranta musu hakan da musu burga. Wannan yasa da damansu kawai suna zaune da ita ne saboda abinda tare da ita zai musu, amma ba don suna sonta ba ko suna jindadin zama da ita din ba.

Hajiya Zainab tace dai ita ta gaji da wannan rashin mutuncin, kwanton bauna ta mata, tana jiran samun weakness dinta ko daya ne wanda zata yi amfani da shi ta janyota kasa daga matakalar data haye, to da yake Madam din tana da kaffa-kaffa, kuma tana kokarin gudanar da kasuwancinta bisa bin doka da ka'ida na kasa, sai bata samu komi a kanta ba sai yanzu.

Kai tsaye ta kira yan hukumar kula da safarar miyagun kwayoyi a Nigeria wato NDLEA ta fada musu Madam din tana safara. Su kuwa dama zaman jira suke yi, kuma a sace sun jima suna bibiyar Alhaji Shehu Balogun din da wannan zargin amma da yake mutum ne mai dan banzan wayo da kuma cewa yana da hadin baki da manyan kasa a cikin maganar, sai hakansu bata cimma ruwa ba. Don haka suna jin cewa matarshi ce, sai kawai suka bankado tsofin files dinsu, suka yi ram da Madam a airport ba tare da ta kai ga haduwa da ita Hajiya Zainab din ba. Suka kuma gudanar da bincike a Kaduna inda suka samu wadannan kwayoyi a wani daki can da aka boye a kasan store din da suke ajiye energy drinks dinsu a Arena din Madam. Da kuma suka bibiyi lamarin, sai aka kama mota shake da wadannan lemuka, a karkashin kwalayen kuma hodojin iblis ne. Suka kuma bada shaidar daga can suka daukosu. To a rubuce a jikin takarda dai Arena mallakin Madam din ce da duk abubuwan dake cikinta, don haka ita suka sani, kuma ita suka kama.

To ga wannan manyan shaidu dake hannunsu, ga kuma matar Brigadier data bada ajiyar Madam din. Kowa kuwa yasan Brigadier din shi yake rike da Lagos a wannan lokacin, har ya ma fi Gwamnati fada-a-ji. Don haka babu zancen sakin Madam.

54.

Su duka saurarenta suke yi cike da tsananin mamakin jin wannan abu.

Nadiya ta kalli Madam din jikinta a sanyaye, tana jin wani abu mai kama da bacin rai na shiga jikinta. Tace, "yanzu Mommy kina son cewa mijinki dealer ne na kwayoyi, kin kuma san da haka din amma kike zaune da shi? Har ma kike kokarin kin sanar da hukuma hakan duk da cewa ana gudanar da cinikayyarta a kan idonki?!"

Madam tace, "to ni ina ruwana Nadiya? Yayi harkarshi inyi tawa, as long as bai ja ni cikin matsalar data sameshi ba game da hakan ni ai bani da wata matsala da shi. Shekara da shekaru kuma a haka din muke, babu abinda ya taba faruwa sai yanzu."

Kawai gani suka yi Anty Hauwa ta mike tsam, zata fita tana share hawaye. Nadiya ta rikota tana rokon tayi hakuri ta koma ta zauna, don ita kanta bata tunanin zata iya zama ta cigaba da sauraron abinda ke fita daga bakin Madam. Da kyar ta koma din ta zauna, amma ranta ya gama baci, hakan kuma bai boyu ba akan kyakkyawar fuskarta.

Ta kalli Madam tace, "ke yanzu ko kunyar kanki baki ji ba, ki kallemu wai kina fada mana kin san mijinki ba mai halastacciyar sana'a bane amma kike zaune da shi a haka? Zahra'u ina zaki kai son duniya ne wai da mukami da son arziki? Muna kallonki a matsayin wadda tayi fice da zarra a cikinmu muna jin dadi da godewa Allah, ashe ba ta hanyar halali kike samun kudin ba?"

Ta bata fuska itama tana kallon Anty Hauwa din, "a'ah, ni fa ki daina hadani da wannan harkar tunda dai ba yin ta nake yi ba. Ni wai ina ruwana da abinda yake yi ne kam? Ni dai nasan kasuwancina na halaline, kuma ban yarda ya gauraya min kasuwanci da nashi ba, to ni ina laifina anan?"

Anty Hauwa tace, "aikuwa ke ma kina da naki kason laifin, har ma fiye da nashi din. Don me yasa ba zaki kai kararshi ba? Don me yasa kike boye laifinshi? Bugu da kari kuma da kike cewa wai kudinki na halal ne kema, how sure are you ba da kudin haram din kika fara kasuwancin ba tunda tun asali da kudinshi kika fara?"

Tace, "ai lokacin bai fara wannan sana'ar ba, sai bayan ma dana maida mishi kudin dana ranta na fara kasuwancin nawa sannan!"

Anty Hauwa ta kalleta kamar ta bugeta don takaici, tace, "to me kenan kika yi? Hakan dai ai ba shi zai wankeki daga cewa kina sane da shi ba kika kyaleshi ko?"

Ganin maganar tasu ta ki mutuwa, kuma ga lokacin da aka basu yana gudu, sai Nadiya ta dakatar dasu.

Ta kallesu duka tace, "Mommy, wadannan duk uzirirrika ne kawai kike badawa amma ba zasu taba wankeki daga zargin da kike ciki ba. Saboda a tsari da doka ta kasa ma, idan kasan mutum yana aikata wani laifi, to koda kaima din baka aikatawa matukar dai ka sani din, kuma wai har kokarin kare mutum kake daga sanin hukuma, to kuwa daurin kudin goro ake muku, don haka kema kina da naki laifin. Ban kuma taba zaton cewa zaki iya aikata irin hakan ba sam. Kina sane da diya a tsakaninku, yanzu idan kika janyo Safiya cikin zancenku fa? Ki ce mata me idan ta ji wannan abin kunyar?"

Madam tayi kasa da kanta tana muzurai. Ta share hawayen fuskarta tana kallonsu dai-dai lokacin da constable din data kai Madam ta koma daukarta, tace, "yanzu mafita zamu tsaya mu nema. Me ya kamata mu yi? Kuma ta yaya zamu shawo kan wannan matsalar?"

To amma har aka dauke Madam din a gabansu tana kara rokonsu da kuma yin magiyar su taimaka su dauketa daga wannan azababben waje, basu gama sanin takamaiman abinda yakamata su yi ba.

Wasa-wasa sai karamar magana ta zama babba, sai ga shi sun share kwanaki uku a nan suna ta buga-buga da neman yadda zasu yi. Sun samu ganin har Commissioner of Police, amma abinda ya fada musu shine case din gabadaya ba a hannun yan sanda yake ba yanzu, a hannun NDLEA yake don haka babu abinda zasu iya yi a kai.

Sai gashi connections din Madam da take tutiya dasu sun kasa tsinana mata komi. Duk wanda yaji a irin halin da take, sai ya hau mata yan kame-kame da zamiya, daga karshe dai babu wanda za su sake ji daga gareshi.

Abin sai data kai har shi da kanshi Habibu yayi tattaki yaje Lagos din, sannan ne suka samu da kyar aka bada belinta. Case din su an mayar dashi can Abuja, zamansu a kotun zai kasance sati mai zuwa. Haka suka tattara suka dawo Kaduna jikkunansu a sanyaye.

Duk wannan abin da ake yi, an nemi Alhaji Shehu Balogun da amintaccen na hannun damanshi a Nigeria an rasa. Tuni suka daga kasar waje.

Amma da Madam ta tsananta bincike, sai aka tabbatar mata da cewa yana Nigeria, a Porthercourt gidan wani amininshi da yake tsohon soja ne da yayi ritaya, yana bashi tsaro.

A wuya take da shi kwarai, kai da kowa ma na duniyar nan. Taga tana zamanta kalau yaje ya janyo mata wahala, ya kuma koma gefe ya boye abinshi saboda tsabar rashin kirki. Tace ashe har yanzu bai gama saninta ba!

Allah kadai Yasan yadda aka yi, a zaman kotu na farko da aka yi sai ganin Alhaji Shehu Balogun suka yi ya bayyana a kotu. Ana zaune kafin shigowar Alkali, wasu samudawan kattai guda biyu suka shiga dashi kotun rike da hannunshi, daga gani dai ba shi da niyar zuwa, suka ajiyeshi a can benci na karshe suka kuma zauna a gefenshi don tsaronshi kada yayi yunkurin guduwa.

Madam tana sahun gaba a zaune ta maka wani dankareren bakin gilashi, ta juya tana kallonshi tare da zame gilas din fuskar tata yadda zai kalli tsakiyar idanunta da kyau, sai ya kawar da kai gefe daya a muzance.

Nadiya da Anty Hauwa da Uncle Yasir duk suna zaune a gefenta har zuwa lokacin da Alkali ya shiga, bayan sun zauna aka kira shari'ar ta su. Madam ta tashi taje gaban alkali ta durkufa. Bayan an gama bayanin abinda ake zarginta dashi, aka tambayeta shin da gaske hakane? Tace 'a'ah'. Ta yiwa alkali bayanin duk wani abu data sani akan harkokin Alhaji Shehu din, ta kuma gabatar da takardun harkokinshi na kwayoyi da yake boyewa a cikin safe dinshi, yayi zaton bata san pin dinshi ba. Lauyan data dauka ya kara gabatar da wasu shaidun wadanda ma'aikatanta ne da kuma wadanda aka zakulo cikin wadanda suke taya Alhaji Shehu din safarar miyagun kwayoyin.

Ta ko'ina an yi mishi kawanya, saboda sun gabatar da duk wasu shaidu da takardu a gaban Alkali wadanda ya yarda da amincinsu ya kuma karbesu a take.

Ya daga kai daga kan takardun da magatakarda ya mika mishi, "kotu tana bukatar ganin Alhaji Shehu Balogun idan yana kusa. Idan kuma baya kusa ta bada awa biyu kacal a zo mata da shi gabanta a duk inda yake!"

Wadannan kattin maza da yan sanda haka suka tisa keyar Alhaji Shehu Balogun zuwa gaban Alkali manta sabo. Sanin cewa an riga an daureshi da jiniyoyin jikinshi yasa bai yi wasa da hankalin hukuma ba, ya amsa laifinshi a take. Ya kuma fadi sunayen abokan kasuwancinshi da kotu ta bada dokar tana bukatar a gurfanar dasu a gabanta su dinma nan da kwana uku.

Bayan shaidun da aka gabatar a gaban Alkali da wadanda hukumar NDLEA itama ta hada, Alkali ya fadi sakamakonshi. An yankewa wadanda aka kama da kwayoyin suna rabawa shekaru goma sha biyar a gidan yari da aiki mai tsanani. Alhaji Shehu Balogun da yake shine mai distributing da kuma sayenta da sayarwa da safararta, an yanke mishi shekaru ashirin da biyar a gidan yari da tara mai tsanani. Madam kuwa duk da cewa kotu ta wanketa daga laifin da ake zarginta da shi, to amma kotu din bata manta da cewa Madam din tana sane da ayyukan maigidanta ba kuma maimakon ta sadashi da hukuma sai ma take kokarin boye laifin nashi, tana da zabin zuwa gidan yari na tsayin watanni goma sha biyar ko kuma a ci ta tarar kudade masu dimbin yawa. A take tace da Alkali taji ta amince zata biya tara. A haka wannan taro ya watse.

Suka tsaya a kofar wajen suna taya juna murna da son barka. Jindadinsu su duka shine yadda aka gudanar da komi ba tare da wani dan jarida ya samu labarin abinda ke faruwa ba. Akwai rumors dake tashi sama-sama, amma kuma babu mai labarin abinda ke faruwa takamaima face shakikansu. Hakan ba shi ya hana jikin Madam yin sanyi ba sosai da sosai. Wai dama haka mutane suke da duniyar baki daya? Yanzu-yanzu mutum yana kaunarka amma kuma jimawa kadan bashi da makiyi kamar ka? Babu ma ya Mijinta Alhaji Shehu Balogun, ta ga ita har ga Allah bata nufinshi da cuta, tunda da tana da niyar hakan da tuni tayi. Tana sane kwarai da bibiyar matan da yake yi kamar wani dan bunsuru, bata taba nuna mishi hakan ba duk wai don a zauna lafiya ne, su taru su duka su rufawa juna asiri. Ashe shi a ranshi ba haka bane?

Suna nan tsaye aka fito da su za a wuce dasu zuwa gidan gyaran hali, hannu daure da ankwa.

Ta roki dan sandan daya rikoshi daya bata yan mintuna tayi magana da shi. Babu musu ya dan ja gefe daya yana fada mata ya basu minti biyu.

Ta kalleshi sama da kasa, wani murmushi na takaici akan fatar bakinta, "ba haka kaso lamarin ya kasance ba ko Shehu? Sai kuma da yake Allah Ya fika, kuma Shi ba azzalumin bawa bane sai gashi reshe ya juye da mujiya!"

Ya saki wata yar dariya, "kada kiyi tunanin wai kin ci nasara Zahra, kada fa ki manta da cewa kada mage ba yanka bane. Don kuwa abinda kike so ba zai taba faruwa ba, nan da dan lokaci zaki ganni na fito na cigaba da harkokina. Ba dai Nigeria ba ce?"

Ta tabe baki, "wannan kuma matsakarka ce Malam. Za ka bani takardata ta saki ko kuwa sai mun sake durkufa a gaban Alkali a karo na biyu?"

Ya jefa mata wani irin kallo kamar wata wadda ciwon hauka ya kama, "saki kuma? Ai ni da ke babu wannan abun wallahi. Kuma ko shekara dari zan yi a gidan yarin wannan, to ba zan taba sakinki ba. Sai dai mu mutu daga ni har ke a haka!"

Ta saki wani dan murmushi mai ciwo, "zamu gani ne ai!"

Ta wuce ta barshi a nan.

Masauki suka koma su dukansu suka huta daga wannan kujiba-kujiba da suka sha. Washegari duk suka tafi suka bar Madam anan. Don kuwa tace ba zata bar Abuja ba sai ta tabbatar da cewa babu auren Alhaji Shehu a kanta.

Nadiya ta koma Kaduna. Bayan sun zauna da Habibu ta mishi bayanin abinda Maidakin Shugaban Kasa take bidarta dashi, ya bata goyon bayanshi dari-bisa-dari. Don kuwa cewa yayi, 'bai ga wanda yayi deserving hakan ba kamarta'

Don haka da karfin gwiwarta ta mayarwa First Lady da amsar cewa ta amsa tayin gayyatarta.

Bayan wannan abu na farko da tayi shine kokarin samo gurbin karatun 'Communication and Public Relations' a Jami'ar Washington DC, ta online. Domin ta samu ta kara karfafa sanayyarta akan al'amuran da suka shafi mutane don gudanar da aikinta cikin dadin rai.

Itama Shukurah ta samu Malama ta musamman data kware akan Politics tana zuwa har gida tana yi mata tambihi akan siyasa da abinda ya danganceta. Don haka ta kowane bangare dai, His Excellency Alhaji Habib Abdullahi Makama, da iyalanshi suna kokarin rike amanar da Allah da Talakawa suka dora a hannunsu.

Madam dai tunda ta samu da kyar da jibin goshi aka raba aurenta da Alhaji Shehu a kotu, ta tsallaka itama ta bar Nigeria. Don kuwa sai a lokacin ne yan jarida suka samu labarin abinda ke faruwa. Nan suka yi mata caaa, kamar zasu cinyeta danya. Wayarta ma sai kasheta tayi gaba daya saboda yawan kira data dinga samu.

Ummah tace mata taje ta sameta a Saudiyyah suyi Umarah, in taga zata iya zama to ta zauna a can har kura ta lafa sai su koma tare. Don haka ta yiwa garin Makkah tsinke.

Tunda ta sauka a masaukin Ummah wanda ya kasance gidane irin na baki (Guest Inn) a madadin hotel, babu abinda suke yi sai ziyartar ka'abah da masallacin Harami. Su yi sallah, su yi dawafi, su bada sadaka, su koma masaukinsu. Wasu ranakun su tafi Madina, wasu ranakun kuma su shiga kasuwanni ko kuwa su je kananun garuruwa wajen abokan cinkayyar Ummah wanda Madam din ta fahimci tana da jama'a da dama a nan.

Ummah kullum cikin yiwa Madam fada take da nasiha a hankali cikin hilata don kada ta ji kamar fada take yi mata. Ta kan ce mata, 'kin dauki rayuwa da girma kwarai da gaske Zahra'u, shi yasa kike da yawan buri. Son abin duniya ya na neman ya miki yawa, hakan kuma shi ya sanya idanunki suke rufewa ki kasa bambance tsakanin fari da baki, d'a da bako, yan'uwa da makiya. A ta haka ne watarana ke da kanki sai kin nemi kanki kin rasa. Ki sassautawa kanki, ki dan dagawa duniya da neman kudi kafa, ki kama Allah da iyayenki da 'yan'uwanki, ki kuma zama mai kyautatawa duk wani wanda zaki zauna dashi koda kuwa baki sanshi ba. Saboda ita duniyar nan da kike gani ba madawwama bace, kuma bata da tabbas. Yanzu a duniya kin taba zaton mijinki da aminiyarki zasu taba aikata miki kwatankwacin abinda suka aikata miki? Amma sai gashi sun aikata din, kinga wannan kadai shi zai nuna miki ainihin ko wanene mutum? Wani kwayar halitta wanda bashi da tabbas koda na dakika daya ne. Yanzun nan yana sonka, amma anjima kadan kuma baya sonka. Don haka ki kama Allah kawai, ki nemi lahirarki tun kafin lokaci ya kure miki."

Ta karbi maganganun Ummah da gaske, ta kuma daura aniyar gyara halinta da dawo da rayuwarta bisa kan tsari da ka'ida.

Abu na farko da tayi bayan data dawo gida Najeriya bayan ta shafe watanni biyu a Makkah, ta baro Ummah a can wadda itama tace cikin watan da zai kama zata dawo, shine ta sayar da Arena dinta tare kuma da neman lasisin mayar da ita can Maiduguri.

Haka ta sayar da kadarorinta da dama dake nan Jos da Kaduna, domin Maiduguri take da niyar komawa da zama gabadaya. Don kuwa Ummah tace mata galantoyi da yawo barkatai ba nata bane ba yanzu, musamman da yake babu aure a kanta. Ita 'ya mace a duk inda take da halin da ta tsinci kanta, miji shine mutuncinta. Idan kuwa babu shi to yan'uwanta ne da iyaye.

Komawarta Maiduguri din kuma ba ita kadai ya yiwa dadi ba, har yan uwa da dangi sun fita jindadin hakan. Don kuwa wajen shakatawar data gina wanda yafi na can Kaduna girma da tsaruwa ma, ta dauki yaran dangi da dama ta basu aiki a can, har ma da wadanda matakin karatunsu bai kai ba.

Haka gidauniyoyinta da suka yi sanyi saboda ganin ta samu abinda take so a hannun mutane, suka cigaba da aiki babu kakkautawa anan Maiduguri din da kewaye.

55.

Watanni shida ne bayan wannan, abubuwa duk sun lafa suna kuma tafiya cikin tsarinsu da yardar Ubangiji.

A cikin wannan satin ta yaye yan biyunta. Ummah ta aika Hindatu, -wata matashiyar yarinya jikar kawunta Tasi'u da ta roki alfarmar a bata ita riko bayan data dawo kasar da zama.- Taje ta amshi yaran aka kaiwa Ummah din don ta yayesu.

A cikin satin kuma aka gayyacesu wajen mashahurin taron da matan Gwamnoni na Nigeria suka saba hadawa a duk shekara, don karawa junansu sani da ba juna shawara akan abubuwa da suka cabe musu a game da mulkin nasu. Daga karshe kuma suna bada awards na abubuwa da dama a taron. An gayyaci Nadiya da Shukurah duka, sai Nadiya din ce ta samu zuwa, saboda Shukurah bata jin dadi sosai. Laulayi take fama dashi ba mai sauki ba, ko ruwa ta hadiya sai ta dawo dashi. Don haka bata samu damar zuwa ba.

Ita kadai ta tafi sai security dinta daya, tayi masauki a Gibson hotel inda duk aka yi musu masauki ita da sauran masu zuwa.

Washegarin ranar da taje aka yi taron, an kuma bata award din wadda ta fi kwarewa akan aikinta da kuma tallafawa marasa karfi. Yayinda Shukurah aka bata award din wadda tafi kowa iya shiga mai kyau da tsara kwalliya.

Anyi taron cikin dadin rai da raha, aka kammala. Wasu tun a ranar suka juya gida, ita kam sai ta kara kwana biyu anan saboda tana so ta ga Her Excellency kafin ta juya gida. Tayi magana da PA dinta tace sai nan da kwana biyu sannan zata iya ganinta.

Suka fito daga dakin taron suna yin sallama da junansu, hankalinta yana kan wayarta suna magana da abokiyar aikinta lokacin da aka bude mata bayan bakar range Rover dinta ta shiga.

Sam bata kula da mutum a gefenta ba sai da kamshin turarenshi ya fara shiga hancinta sannan. Ta juya da sauri sosai, sai idanunta cikin nashi

Mamaki yasa ta kasa iya cewa komi sai bakinta data hangame. Tace "yaushe ka zo nan?!"

Cikin tsananin mamakin ganinshi a wajen. Don kuwa ko mintuna talatin da suka wuce sunyi waya da shi, ya tayata murnar award din da aka bata, amma kuma koda wasa bai fada mata cewa yana Abuja ba. Abinda bata sani ba shine tun a safiyar ranar yaje can, za su yi wani zama da yan majalissu a ranar da yamma.

Direba ya ja mota suka fara tafiya, yayinda ya juya ya kalleta yana kasheta da murmushinshi, "ai anan ma nayi lunch dina."

Ta dan turo baki, "shine kuma ko ka fada min?"

Kasa daurewa yayi ya jata cikin jikinshi yana sumbatar gefen kumatunta, ta fara kokarin janyewa saboda kaucewa idanun direba da security dake gaban motar wadanda suke kamar ba ma a cikin motar suke ba, amma shi kuma ya ki bata damar hakan.

Yace, "to menene amfanin sanar dake din ni da nake so inyi surprising dinki?"

Sai bata ce mishi komi ba, ta janye jikinta daga nashi da kyar ta koma ta zauna tana kallon hanyar inda suke nufa.

Direba ya shigar da motar farfajiyar hotel din Fraser Suites dake nan Garki, security ya bude mishi murfin bangarenshi ya fita. Ana kokarin bude mata daya bangaren, ya dakatar da shi tare da bude mata da kanshi. Ta fita daga cikin motar hannunta sarke cikin nashi, bin shi take yi cike da alamun tambaya. Musamman da taga kai tsaye ya wuce da su ciki, sun shige elevator tayi sama da su.

Tace mishi, "ina da masaukin da aka kama min fa."

Yace, "na sani, na kuma sanya an dauko miki kayanki daga can saboda zamu zauna anan din na dan lokaci mai tsayi ne."

Suka fita daga cikin yar motar, suka taka har zuwa kofar dakin da yayi masauki ya bude musu kofar suka shiga suite din.

Babban dakine sosai, komi kyal-kyal gwanin kyau yana ta tashin tattausan kamshi mai dadi.

Kai tsaye bandaki ya shige ya dauro alwala, ya fito ya sameta a tsaye a wajen daya barta tana kallonshi da mamaki. Yace, "zan fita masallaci, daga can kuma wajen meeting zamu shiga ina tunanin sai bayan Magriba sannan zan dawo. Idan kina bukatar wani abu zaki iya kiran room service sai su kawo miki."

Bai bari ta ce wani abu ba, ya duka yana bata peck a baki kafin ya fita da sauri.

Sai ta bishi da kallo, kafin kuma ta dan girgiza kai tana sakin murmushi. Ta fada toilet itama don dauro alwala.

A daren ranar ya iskota zaune akan kujera dake tsakiyar falon, ta gama shirin barci amma laptop ce a gabanta tana aikin dannawa furiously, hankalinta kacokam akan abinda take yi.

Ya tsaya a gaban mirror yana taje sumar kanshi, yana satar kallonta ta cikin madubin. Yayen da tayi har ta fara mayar da jikinta, duk da cewa dai dama can ba wani rama tayi ba, amma duk da haka sai data dan fada da kuma duhu da fatarta tayi. Shayarwar yara biyu ai ba wasa ba. Amma yanzu gashi nan har wani sheki take yi na musamman, jikin nan ko'ina bul-bul. Musamman kugunta daya kara budewa yayi daram. A yadda take zaune dinnan ta dan duka, cikin riga da wando na barci marassa nauyi, surarta ta fita yadda yakamata.

Ya dan lumshe idanu yana girgiza kai kafin ya ci gaba da shirin shi. Har ya gama sanya farar singileti da wando sweat pant ruwan madara, ya bi jikinshi da turaruka ya fesa, Nadiya bata san me yake yi ba.

Ya wuce kai tsaye ya dauke laptop din gabanta, yayi saving aikin da take yi tare da kasheta. Haka ya dauki wayarta ya kashe, duk tana zaune tana kallonshi.

Ganin kallon alamun tambaya da take jefa mishi yasa yace mata, "daga yau har zuwa ranar da zamu bar dakin nan, ban yarda da daukar waya ko laptop ba. Kai ko maganar aiki ban yarda ba wadda bata shafi rayuwarmu ba (personally)."

Tayi dan murmushi tare da langabar da kanta gefe, "to Alanguburo (ranka ya dade) ya kake so inyi da tarin ayyukan dake gabana ne kuma?"

Yace, "ban sani ba Nadiya, ni dai kawai abinda na sani shine yanzu lokacina ne, ban kuma yarda wani abu ya gifta min a tsakani ba. Finally na sameki ke kadai din ki, babu laulayin ciki, babu rainon ciki, babu na yara, sannan babu zancen aiki da na mutane da marassa lafiya da sauransu, don haka sai na fanshe duk wadancan kwanakin da yan biyuna da aiki ya dinga hanani cin amarcina da kyau!"

Tayi dariya sosai, "ashe kace nan da wata daya ma ba zamu bar nan ba? Don kuwa ni dai nasan lokutan da yawa!"

Yace, "babu matsala ai, we can rectify that, my love."

Ya sungumeta ya nufi gado da ita yana manna mata wata gigitacciyar sumba, wadda ke fita tun daga karkashin ranshi, tana kuma fada mata irin tsananin kewarta da yayi. Ga su dai a gida daya, su kwana su tashi a waje daya a wasu ranakun, but this, wannan na daban ne. Su kadai ne, babu aiki, babu kiran waya ta ujila, babu yara da sau tari suke katsesu a al'amuransu ko kuma su raba dare dasu a zaune. Yanzun su kadai ne, ya kuma samu Nadiya din yadda yake son samunta, pliant, loveable, da kaunar nan tata mai kashe jiki da sanyaya zuciya wadda a wajenta kadai yake samu.

Cin amarci wane lokacin da tana amarya? Wannan ai honeymoon ne mai lasisi suka sha wanda babu kamarshi a tarihin rayuwarsu.

Satinsu guda anan, fita idan ba ta kama dole ba to babu inda suke zuwa. Itama tun bayan zamansu da Her Excellency bata kara fita waje ba, sai dai sau tari idan ta gaji da zaman dakin su fita nan kasa wajen shakatawa su zagaya su huta, ko kuma su je wajen cin abinci su ci maimakon a kai musu har daki.

Anan ta samo wani cikin. Allah Ya taimaketa dai wannan bashi da tsarabe-tsarabe irin na yan biyu, don haka har cikin nata ma ya girma ya fito ba kowa yasan da shi ba.

*****

EPILOGUE

SHEKARU GOMA A GABA!

Rayuwa ta mika musu bakidayansu, ta kuma yi musu albarka fiye da tunaninsu. Hajiya Nadiya Auwal, mata ga Alhaji Habib Abdullahi Makama, toshon Gwamnan Jahar Kaduna.

Ya rike wannan mukami har sau biyu, don kuwa tazarce yayi wanda Talakawa da al'ummar Jahar Kaduna suka mara mishi baya har ma fiye da lokacin farko daya fita takara. Haka kuma anyi ittifakin cewa kaf a tarihin Jahar Kaduna ba a taba ganin jajirtaccen Gwamna ba kamar shi.

Mutane da dama sun so ya sake neman kujerar Shugaban Kasa, amma yace a'ah, wanda yayi ma a baya Allah Ya sanya albarka. Yanzu kam yana son karkata hankalinshi ga iyalinshi ne kawai.

Nadiya a halin yanzu marikiyar Masters ce, tana aiki da wata Private University anan Kaduna din inda take koyar da Home Management. 'Ya'yanta shida, Yan biyu yanzu shekarunsu sha daya, Juwairah yar kimanin shekaru takwas da yan watanni, bayan ita akwai wasu yan biyun duka maza, Hassan da Hussaini, shekarunsu biyar. Sai Fatima (Maamah) itace autarta shekarunta uku.

Shukurah kuma Yayanta uku, Muhsin, Mus'ab da kuma Ruqayyatu. Ita Shukurah din yanzu tana aikine da hukumar kare hakkin dan Adam ta kasa.

Kawunansu a hade yake sosai, haka ma yayansu sun taso cikin kauna da girmama juna da kuma iyayensu, don kuwa a lokuta da dama ma baka iya bambance dan wannan dakin da na wancan.

Shekaru uku da suka wuce su Mami suka dawo Najeriya da zama gabadaya ita da iyalanta. A kuma cikin shekarar ne aka yi auren Safiya da Fu'ad, dama can Nadiya ta jima tana zargin akwai wani abu a tsakanin yaran, don haka bata yi mamakin jin zancen ba. Suka sha biki sosai da sosai kamar babu gobe, Safiya ta tare a gidanta dake nan Kaduna. Ba a gina mata asibitinta na kashin kanta ba bayan ta kammala karatunta, amma kuma tana aiki da wani babban asibitin kudi anan Kaduna din, sannan kuma tana zuwa asibitin Gwamnati lokaci zuwa lokaci. Diyarta daya a halin yanzu.

Alhaji Habib yanzu babban dan kasuwa ne, wanda yake safarar jewellies, kayan ado na maza da mata har ma da furnitures daga sassa na duniya

daban-daban. Shagunanshi suna da manyan rassa a jahohi daban-daban a cikin Najeriya, nan Kaduna, da Maiduguri, Abuja, Kano har ma da Lagos.

Ita kanta Nadiya tana da babban wajen cin abinci mallakinta, wanda yayi shura ya kuma yi fice a cikin Kaduna kwarai da gaske. Don kuwa wajene wanda yake tafiya da zamani sosai da sosai, haka ba a abincin nan kasarmu Najeriya kadai suka tsaya ba, suna lekawa har kasashen ketare suna yin irin girke-girkensu.

Haka kuma, ita din yanzu tana rike da gidauniya har guda biyu ta tallafawa mata da marayu tata ta kashin kanta.

Aikin Hajji ya kwashi iyalan nashi suka je gabaki dayansu banda yan kananun, su a wajen Ummah aka barosu.

Ranar da suka dawo, a gidan Hajiya Ummah suka yi masauki gabaki dayansu. Aka yi musu tarba mai kyau, abinci iri-iri, babu irin wanda ba a dafa ba.

Suka hau kan babban dinning table wanda ya daukesu gabadayansu tsaf, har da sauran kujeru ma. Kowa ya zuba abinda yake son ci, babu abinda ke tashi a wajen sai tashin sautin muryoyinsu kawai suna ta hira cike da nishadi da kauna irin ta yan'uwantaka.

Nadiya ta harari Khairiyya wadda ta dauke sauran soyayyen kifi guda daya daya rage akan farantin Mus'ab, ta kuma kaishi baki ta taune tana gaggaba mishi dariya.

Tace, "wai don Allah me yasa kin cika tsokana ne Khairiyya? Ba na hanaki cin kayan kannenki ba?"

Ta turo baki tana cewa cike da shagwaba, "To Mommy na ga ya zauna yin tsentseni ne, yanzu wannan sai kiga har mu tashi daga nan bai gama cin abincin ba. Ni kuma ina so in ci ne."

Tace, "to amma ai ba haka ake yi ba ko? Sai ki tambayeshi kiji idan ba ci zai yi ba kafin ki dauka. So kike yi ya miki bore ke kuma kice zaki nuna seniority ki ci zalinshi ko?"

Ammar ya katseta, yace, "Mommy da ma kin daina shiga tsakanin wadannan yaran wallahi. Yanzun nan zasu baki kunya a bainar jama'a. Kin gama tare mishi fada yanzu, yanzu kuma zaki gansu sun hade kawuna suna shan hannu da dariya abinsu."

Shukurah tace, "ai ni dama tuni na gama fita daga cikin harkokin yarannan da kike ganina. Ni ai tun ranar nan da suka gama yace min zani a kasuwa ita da shi, nace to anyi babu kari. Shi yasa bana taba ce musu komi idan suna abinsu."

Wajen suka dauki dariya sosai da sosai.

Ummah kallonsu take yi, a cikin ranta wani irin farincikine irin wanda bata taba jinshi a rayuwarta sai in tana cikin wannan zuriya.

Ba ita ta haifi Habib ba, don haka 'ya'yanshi ba jikokinta bane na jini. To amma kuma so da kauna da shakuwa dake tsakaninta da su, sun ma fi na wadanda suka hada jini din. Komi yaran suka dauko, kaji sun ce granny, granny. Duk da cewa itama Yakumbo din suna sonta akwai kuma shakuwa a tsakaninsu sosai, to amma fa bata kamo kafar shakuwarsu da Ummah ba ko kadan.

Sai zuwa dare sannan ya hada kan matanshi suka wuce gida. Su kadai suka tafi, don Ummah tace a bar mata yaran su zauna tare da ita har su koma hutu. Saboda tana so ne ma a cikin satin su je su kaiwa Yakumbo ziyara a Makarfi koda ta yini daya ne ko kwana.

*

Bayan an kwana biyu, sun gama hutawa da kuma karbar baki yan sannu da zuwa, ta fita a yammacin ranar Alhamis zuwa gidansu.

Ruwa aka gama yi babu jimawa, garin yayi luf gwanin sha'awa. Ta fita a cikin silver Jaguar F-Pace sport car dinta, sabuwar mota ce wadda bata jima da siya ba.

Allah Ya buwaye mata, sai gashi ta wayi gari rayuwarta tayi kyawun data fi karfin abubuwa da dama a cikin rayuwa. A halin yanzu ita da kanta bata san iya adadin kadara da kudade data mallaka ba, wanda kuma duka cikin buwaya ta Ubangiji nata ne, mallakinta, ba tare da wani ya taimaka mata da asin kwabo ba.

Ita take tuka kanta a hankali, cikin jin dadi da ni'imar da ruwan sama din ta saukar mata. Gidansu ta yiwa tsinke, bikin Amina da Fatima ke tunkarosu a cikin wannan watan. Ita Maryam an jima da yin aurenta, ta samu miji a cikin yan'uwan Mama, a yanzu haka tana can Kano da zama ita da yayanta.

Ta yi horn a bakin gate din gidan, yaran gidan suka dinga rige-rigen bude mata kofa. Ta danna hancin motarta farfajiyar gidan ta shiga, ta kashe motar tare da fita a hankali tana gyara gyalen data rataya a kanta.

Ta tsaya a jikin motarta tana karewa gidan kallo, shine dai gidan da suka tashi, aka kuma rainesu a ciki. Wanda a shekarun baya kadan suka sayi sauran gidaje dake makwabtaka dasu, aka sake rushe tsohon aka yi sabon gini na zamani. Lantana tuni ta jima da barin gidan itama. Saboda bayan wasu yan lokuta, tace ita ba zata iya wannan rayuwar ba, ta nemi saki shi kuma ya sallameta.

Aka warewa matan dakunansu, shima Abban haka aka ware mishi nashi bangaren daban, ta yadda zai dinga cin karenshi babu babbaka ba tare da wani ya jiyo shi ba balle yasan wainar da yake toyawa. Irin rayuwar da taso ace ta rayu a cikinta kenan, irin wannan tsarin tayi burin ace shine a gidan a lokacin da take nan.

Saboda idan ta zauna ta duba baya da kyau, sai taga cewa raini mai yawa daya shiga tsakaninta da matan mahaifinta ba komi bane ya assasa hakan ba face mu'amalarsu da take ji da duk wani sirri daya kamata ace nasu ne su kadai, wadanda bai kamata wani kunne yaji ba face su. Shi yasa ta rainasu, bata sonsu, bata girmamasu, shi kanshi Abban nasu sai da rainin ya so shiga tsakaninsu ai.

Bata son kannenta na baya su dandana irin wannan rayuwar data dandana a baya, shi yasa ta bada shawarar ayi haka din. Musamman da bayan yan

shekaru da yawan shan magunguna da yake sha, ya samu lafiyarshi garas duk da cewa dai har lokacin babu tabbacin zai sake iya haihuwa.

Bayan wannan kuma haka suka samu shago babba aka zuba mishi yadika da shaddodi na maza inda ya fara gudanar da sana'arshi, duk sunyi hakan ne saboda zaman hakanan din bashi da dadi musamman ga mutum mai iyali irinshi.

Ta nisa a nutse, kafin ta taka a hankali akan takalminta mai matsakaicin tsayi na Chanel da mahadin jakarta data sanya kan wayoyinta da sauran abubuwan da zata bukata a ciki.

Ta shiga bangaren Salame da a halin yanzu da ita da Mama suke amsa sunan Hajiyoyi. Ita da su Yaya AbdulHadi da su Anty Jamilah suka biya musu aikin Hajji a wata shekara, suka je su duka suka sauke farali.

Ta zauna akan daya daga cikin kujerun falon, suka gaisa da ita cikin girmama juna. Haka diyan Salame din da kuma na Lantana data bari a gidan bayan tafiyarta, suka dabaibaye Nadiya din suna gaidata, ta dinga amsawa da fara'arta tana tanbayarsu game da karatunsu. Su dukansu sun girma Tubarkallah, hankali ya ratsasu, haka kuma kowannensu karatunshi yayi nisa na Arabi da boko wadanda su yayun nasu suka tsaye musu.

Ta zauna a cikinsu tana sauraren matsalolinsu da korafinsu daya bayan daya, Salame na daga gefe tana musu dariya idan sun ce wani abun. Bayan dogon lokaci dai ta mata sallama ta wuce wajen Mama.

Ta sameta zaune a kan kafet, Aminatu tana yi mata tsifar kai. Su duka suka daga kai suna amsa sallamar da tayi. Sai kuma fara'a ta fadada akan fuskar Mama.

Tace, "Lale marhabun da Hajiyoyi. Har kun fara fitowa ne?"

Ta lalubi kujera ta zauna tana kallonta, "ai Anty Jamilah da Anty Haulatu ne suka tasoni wallahi ba shiri. Zancen abubuwan biki dana hidima suke so muyi

da ke wai don su fara shiri da wuri. Kin sansu ba dai son bidiri ba da casu in dai akan bikine"

Mama tace, "ki fada musu to su ma daina wahalar da kansu, don kuwa babu wani shagalin biki da za ayi. Haka Abbanku ya fada ko a dazu da safe da zai fita."

Amina ta zumburo baki, sai tayi dan murmushi tana kallonta. "ke kyale Abba kinji? Ba da gaske yake ba fa. Bikin autarmu guda wai ace babu shagali? Ai wannan sam ba sai yiwu ba."

Sai lokacin suka gaisa da Mama din. Ta kuma fara jero mata ire-iren abubuwan da suke sa ran yi da bikin, aka kira Salame taje don ayi maganar da ita. Tace, "ni ina ruwana da shiga harkar yara? Duk abinda kuka tattauna da yan'uwan naki mu namu ai Allah sanya alkhairi ne. Amma don Allah dai kada ku sanya shashanci da kide-kide a ciki."

Ta tashi ta fita bayan ta fadi haka. Don haka ita da Mama suka tsara abinda za su tsara.

Sai can gab da Magriba ta tashi zata tafi. Ta cewa Mama, "a gaida Abba idan ya dawo. na so ace yana nan da mun gaisa."

Mama tace mata, "zai ji in shaa Allah. Ranar nan ai yace Maigidan naki har shago yaje ya gaisheshi, ya kai mishi jallabiya da sallaya tsarabarshi ta Makkah."

Tayi dan murmushi a tausashe, don kuwa Koda wasa bai fada mata hakan ba. Yanzun ma kuma saurin komawar da take yi kenan, saboda ranar girkinta ne. Ga Ogan sam bai jurar ya koma gida ya tarar ba ta nan. Lokuta da dama ya sha mata korafin hakan da nuna yadda baya jin dadi, don haka take kokarin kiyayewa. Ta musu sallama da cewa idan sun gama maganarsu da yayun nata, zata kira Mama ta sanar da ita yadda ake ciki.

Ta shiga motarta, su Sa'idu suka bude mata gate zata fita. Tana kokarin tayar da ita taji alamun shigar sako cikin wayarta, sai ta dakata tare da ciro wayar daga jakarta. Kamar yadda tayi zato, Habibin nata ne.

'Ban taba sanin cewa ni din mai tsananin sa'a bane, sai da kika shigo cikin rayuwata. A lokacin da ni kaina ban taba sanin cewa ina tsananin bukatarki a kusa da ni ko gefena ba. Ki ka haskaka min rayuwata fiye da hasken tauraro da duk wani abu mai sheki a duniyar nan. Ki ka dusashe hasken duk wata 'ya mace da take a cikin rayuwata idan ba ke daya dinnan ba tal! I love you baby. Rayuwata da ta iyalina bata taba daidaituwa idan ba kya kusa da mu. Shi yasa a duk lokacin da zan shigo gidana, nake samunshi duhu dindim matukar ba kya nan ... Where are you my sunshine? You are the peace and happiness I have been longing for in my life... Come back to me my baby....!"

Da wasu irin kalamai masu nauyi da suka sanya ta kafa kai a jikin sitiyarin motarta tana sakin wani irin murmushi mai cike da tsananin shauki da soyayyar Maigidan nata.

Koda wasa, kuma a kowane yanayi yake ciki a tare da ita, bai taba bude baki ya ce mata ko wani ba, she's his favorite a cikin matan nashi ba. Amma ita ta sani. Koda bakinshi bai furta ba kuma, gangar jikinshi da zuciyarshi suna fada mata. Ita ce haskenshi kamar yadda shima ya ke hasken rayuwarta da duniyarta baki daya.

Haka itama bata taba yin amfani da wannan 'weakness' din nashi ba domin ta kuntatawa abokiyar zamanta. Sai ma kokarin boye shi da take yi, domin su samu mijinsu ya tashi a gaban UbangijinShi a cikin sahun masu kyautatawa ga iyalansu. Tunda kuma baya taba kokarin nuna musu bambancinsu a fili, a kullum addu'arta bai wuce ya kasance miji mai saisaita adalci a wajen Iyalanshi ba har abada.

Ta maida wayar jaka bayan ta tura mishi amsa a layi guda daya kacal... 'ina nan zuwa gareka, Maigidana Abin alfaharina!'

Ta yi ribas, ta fita daga gidan nasu ta tunkari nata, wanda take fatan ta mutu a cikinshi, ta kuma tashi a matsayin matar Maigidan har a gobe kiyama. Zuciya cike da doki da shaukin sanyashi a cikin idanunta.

Karshe.

➽➽✿☆➽➽

To the girls who dream of meeting a prince but end up falling for the misunderstood villain!

Alhamdulillah! Ma shaa Allah La Quwwata illa Billah!

Wannan labari kirkirarre ne, ba ayi duba da rayuwar wani/wata wajen rubutashi ba. Idan hali ko yanayi ko tsari yazo daya da naka/ki, to arashi ne kawai.

Ina matukar godiya kwarai da gaske ga duk mambobin group din HADAKAR FIKRA 2024, wadanda adadinsu ba zai fadu ba. Your love, comments, da karfafawar gwiwarku ne ya kawomu wannan karshe mai kyau. Da fatan labarin Nadiya ya fadakar tare kuma da nishadantar da ku. Allah Ya bamu ikon amfanar darasin dake tattare da wannan littafi, kurakuran ciki kuma Allah Ya yafe mana bakidaya ameen. Nagode, nagode, Allah Ya bar kauna. Ma'assalam. Sai mun sake haduwa da ku in shaa Allah.